Compiled by Umar Dalha Funtua.

✳CIRANIN AMANA✳

1-5

By
AsmaBaffa

BISMILLAHI

INA MIKA GODIYATA GA DUBBAN MASOYANA ,DA FATAN ZA KUJI DADIN WANNAN NOVEL KAMAR YANDA KUKA JI A MA'AIKACIYAR GOMNATI READERS,ALLAH SA A FARA LAFIYA MU GAMA LAFIYA.

Sanye take cikin wata jemammiyar rigar atamfa ko kugu bata kai ba,ga wani wandon yadi ja ajijinta dogo,ta nannade kafa daya iya gwiwarta,wata dagargajajjiyar p cap ce a kanta,tafiya take tana bouncing har wani dinginsa kafa daya takeyi,irin tafiyar nigogi maza takeyi tana shan kamshi tare da dauke kai sama tana hura hanci,tafiya takeyi tare da sa hannayenta a aljihunta tana bouncing tare da yin doro tana kwobarewa hadi da budawa.

Bata kula kowa kawai kwana take sha,wata dandazon majalisa ta maza tazo,tana zuwa aka fara ihu da tafi sai Amana,kallonsu tayi tare da kara kwobarewa tace sai Baba,sa'a dai sa'a dai tayi Gaba bata kara yin magana ba tafiya kawai takeyi,wani yaro taci karo dashi,sai da ya buya a lungu yace Maza Mazaje Cike da bala'i ta dago kanta aifa sai ta hango yaron,da gudu yaron ya zura,ta bishi itama sai da ta kure masa gudu har cikin gidansu yaron ta kamoshi a gaban Uwarsa ta hau jibgarsa kamar Allah ya aikota,mutane sun taru amma ba Wanda ya riketa saboda kowa yasan halinta,in tayi fushi ba a iya tsaidata,suna ji suna gani ta farfasawa yaron nan jiki sannan ta gyara p cap dinta sosai ta da kyar take gani tsabar janyo hular da tayi, gaba tayi tare da bouncing,ta kusa zuwa kofar fita daga gidan tayi tsalle tayi ball da wani baho da ta gani a hanyar kofar fita daga gidan sai da bahon yayi raga raga,sai da ta fita ta bar gidan

sannan mutane suka sami bakin tsine mata tare da Allah wadai da zuriyar Gidan baki gaba dayansu,kowa da abinda yake fada akan wannan matashiya da sauran yan uwata tare da iyayensu.

Har kofar wani gidan kasa tazo kato da alama shine gidansu,Babanta ta gani a waje tare da mutane a kofar gidan Sallama tayi musu tare da cewa Allah barmana Baba,sai me gida wlh,tayi cikin gida,da wani gurjejen namiji ta hadu da gani katon dan Wiwi ne,lips dinsa sun nuna da tafin hannunsa,cije baki yayi tare da karkace shi gefe,ke dan Uwarki daga Ina haka?hannayenta biyu a Aljihunta tana hura hanci tare da ja baya,ta kara yin doro tace kafa ja girmanka Hamza,dan zan iya takeshi kasan da wa kake magana dan tsab zan Zagi Amarya uwarka,kasan Halina ko?

Jinjina kai Hamza yayi tare da cewa zan tattakaki in bakiyi hankali ba,bani da mutunci,to ni din an fada ma mutuncin gareni cewar Wacce aka Kira da Amana.tsaki taja tare da banke Hamza tayi cikin gida,tana shiga Ashar ce take tashi a gidan ana ta dambe tsakanin yan mata gidan,

Iyayensu ma sai dirko ashar sukewa junansu,ruwan Ashariya kala kala ce ke tashi a gidan,nan take ran Amana ya baci ko kallonsu batayi ba ta wuce cikin dagargajejen dakinsu,Wanda yake daf da ruftowa.

Sallamar megidan sukaji da alama shine babansu,shima Ashariya ya Shiga dannawa yaran tare da iyayen su hade da kallon wata yar yarinya bata wuce 7yrs tana gatsine da harara yace tafi can shegiya da kai kamar kuda,kallon sauran matan nasa yayi da yaransa maza da mata yace wacce bata fasa ba taci ubanta shegu tsinannu,tambadaddu,bakin da aka sauka a gidan ne suka fito daga masaukin da aka basu suna bada hakuri,

Matan ne sukayo kan bakin da masifa kamar zasu cinyesu da zagi na tashin hankali.

Me gidan ne yayi tsalle ya dire yace kar tsinanniyar data kara zagar min bakina,bakin Alkhairi,dole kuma na dinga saukar baki a gidana,wlh babu yar wata katuwa da ta isa ta taka min birki.

Wata ce a cikin matan nasa tace tambadadden dan iska dama dole kace haka munafuki,Allah ya isa duk ka tarwatsa mana yara,ka lalatasu,dayar ma tace an dai ji kunya kwarton Banza,wata tsohuwa ce tukuf itama ta fito tana ba kwarto bane yaro na,kar ku kara zagar min da shegu jarababbu,haihuwar Asara.

Watace ta zaburo itama a cikin matan ta nuna me gidan,tace ga tsohon haihuwar asara kwarto maci amana.Amana ce ta fito daga dakin tana budawa tare yiwa mutan gidan kallon banza,tace kuna yawa fa,kuna da matsala,dan Allah ku rufe mana baki wlh ko yanzu ayi abin kunya a nan wajen nan ko Baku gane bane eh?

Me gidan yace yawa Yar Amanata kiyi maganinsu,sai Baba kaima fa Baba kana da Matsala fa,ka dinga kiyayewa duk kabi ka jona mana masifa da irin abinda kakeyi a gari.

Baba ne ya kalleta zaki ci Ubanki kema shegiya me suffar maza,jibi yanda kikeyi, wa zaki

samu ya aureki haka? Shi yasa baki da mashinshini,kinyi kwantai anyiwa kannenki aure ke kina shirme a gari,

Cike da takaici ta kalli kanta tare da sa hannu daya a Aljihu tare da cewa Baba ni ba gudun maganarka nakeyi ba,bana tsoronku ku kanku kun sani,kawai biyayya nake ma amma dole a fadama gaskiya ka gane Tsoho kana yawa wlh,wannan abin da kakeyi ba me kyau bane,shi yasa muka lalace,dole na fada ma gaskiya,ka gyara badan mu ba ko dan Allah kaji tsoronsa.

Rufe min baki shashasha ubanki nakeyi? Hmmm Allah baka Hakuri Baba nasan yanzu zaka iya tsine min.

Ta inda kikafi yan uwanki hankali kenan akwai biyayya ga iyaye,ga sallah akan lokaci,cewar Baba Dariya amana tayi kadan tare da fadin Allah barmana Baba,ammafa Baba Allah shirya mana kai.ki kiyayeni Amana cewar Baba,sorry Baba Amana ta fadi,

Baba yau ba dan tsire ne?cewar Amana, Babane ya watsa mata harara tare da cewa ubanwa zai sai miki tsire maganin me kike min a gidan nan,ke ba saurayi ba  bare nasa rai zan samu kudi,tafi kiban waje shashasha.bouncing ta kama yi tare da kwobarewa tana kunkuni,wofi banza da baki kamar gidan tsutsa cewar Baffa.Anayin kiran sallar Magriba Amanace ta Riga kowa yin Alwala da Sallah a gidan.

Ummanta tana zaune tana tace gasarar kokon siyarwa na safe,bata da niyyar tashi tayi Sallah,Amana ta kalleta a hankali sannan tace Ummammu Anyi fa Sallah ni halina dake kenan wlh anata ta Sallah ke baki da Niyyar tashi,

Wacce aka kira da Umma ce ta daure fuska ke jarababbiya saurarammin,niba uwarki bace zaki dinga gaya min magana inda kika ga dama?,ko ni sa'ar ubankice,har ni zakiyiwa wa'azi kamar kanwar uwarki,sai da safe ki taso sakalo sakalo na sammiki koko,kin dauki aikin banza a kanki,kin rasa me sonki tallanma kinki yi kince ke boko zakiyi ayi mugani ai duniya ce,

Haba Umma daga cewa kiyi sallah shine kike min baki?kin San ma'anar duniya ce,ku gidan nan Baku da aiki sai zage zage,duk kun gama kwashe mana Albarka,taya zamu samu miji,kuma boko tun daga primary waye yake daukan nauyina?itacen kara nake yowa a kauyen nan haka gashi har ina ss2,ai abin ku jinjina minne amm kullum kunfi so kuga na shiga duniya dan na samo muku kudi haba Umma,ya kike haka ai gwara idan bake kika haifeni ba ki fada min nasan matsayana tun wuri.

Ke tashi ki bani waje jakar banza.wani bakin cikine ya cika zuciyar Amana,Sam basuyi dacen iyaye ba,yo ni da za a dinga min fada wani ciyar dani akeyi?sutura ake min ko sabulun wanki bare na wanka ba ayi mana a gidan nan,kuma sai a bimu da zagi nifa bazan dauka ba cewar Amana tare da ficewa daga gidan.

kowa a gidansu babu na gari a cikinsu,gaskiya Allah kawo min sanadiyar tafiya Cirani na yi wajen kudu,na huta kawai da bala'in gidan nan,Allah sa Baba ya turani cirani nima irin su Hamza na tafi na huta da masifar gidan nan.

Wannan wanne gidane kenan,da alama babu me tarbiyya a gidan kaf. bari muji tarihinsa.

GIDAN BAKI kenan gidane Wanda me Gidan yake saukar mutane Baki idan sunzo gari suna

Neman masauki sai ya saukesu amma iya mata banda maza,baya saukar maza a gidansa,shine dalilin da ake kiran da gidan Gidan Baki.
Gidane Wanda yake cike Da mata da maza.da yan gidan da kuma baki iya mata amma.

Baba me gidan shine Sulemanu Harka dan Asalin kauyen Albasune LGA ne dake Kano state,Amma aikin gini yasa ya koma garin Wudil da zama,Babar Sulemanu Harka wato Ille ta haifi yara kanne da Yayyen Sulemanu harka amma duk su nutsatsune suna zaune a can kauyen Albasu lafiya da iyalensu yayinda Sulemanu ya dauke Uwarsu wato Ille,saboda tana sana'ar soya kosai sai wayo yake mata tana ciyar masa gida da kudin da take nema,.

Ille ita kanta tasan Sulemanu Harka ba mutumin kirki bane amma ba yanda ta iya dashi,haka take Sana'a tana ciyar masa da iyalensa,
Sulemanu Harka matansa 4 Haule itace ta farko ana ce mata Goggo,yaranta 10 Maza 4 mata 6 Safiyya itace Babar Amana suna kiranta Umma, yaranta Uku maza 2 mace 1 Amana.
Laure Hajiya kenan ta uku yaranta 5 Maza 3mata ,
Sai Raliya Amarya tana da yara 8 maza manya 4 sai mata ma 4.gaba daya yaransa 25 kusan mata 4 kacal akayiwa aure, matan suna gidajen mazajensu a kauyen Albasu wasu a garin Albasun,
Saura mata da yawa suna a gidan ciki harda Amana,maza kuwa ba wanda yayi aure cikinsu kawai iya shege sukeyi a garin, Sulemanu Harka sana'ar gini yakeyi sosai tun yana da kuriciya har ya girma yayi yara magina.baya taimakawa iyalansa da kwandala sai matan banza,Sai kuma yaci me kyau a waje yasha me kyau,ga sutura me kyau,sai ka Rantse Sulemanu ba a gidan kasa yake kwana ba,
Yaransa duk ba munana suna da kyansu,Amana tafi kowa kyau a gidan sai dai wasu su fita haske shima da kadan don itama fara ce Amana.

Talakane na karshen karshe,saboda ko ya samu baya tsinana komai ga iyalinsa,sai dai yaci tsire da kudin,domin kullum yana gaban tukubar me nama,gidansa kuwa ko masara ya kasa siya musu ko wacce Sana'a takeyi tana ci da kanta da yaranta,Sulemanu Harka gawurtaccen dan Neman matane,kaf kauyen da wasu garuruwan sun sanshi,shi yasa idan yaji baki mata to shi zai basu masauki yana zagawa wajensu.

Bashi da Amana,ko yarinya ka kawota gidansa riko sai ya ci amana ya lalata ta karfi,haka baki wasu su gudu wasu su tsaya su sha harka,yaransa ma sunsha kama Baba da mata,matansa har fakonsa sukeyi idan dare yayi,sabo da ko yar uwar matansa ne sukazo sai ya zaga wajensu ya kwashi Harka,
Bashi da abokin da ya wuce limamin garin domin halinsu daya,
Sulemanu Harka ko yarsa kaje nema idan baka da kudi to bazai baka yarsa ba,kuma idan kana zuwa zance wurin yarsa to sai ya dinga rokonka kudi,haka gaba daya sai Allah ya bashi yara gaba daya tantirai,Amana ce ta gari a hakan lol kaf gidan babu me nutsuwar Amana a hakan.
Mazan gaba daya wasu barayine,wasu yan wiwi,wasu yan Neman mata, domin suma suna lallabawa wajen baki masu sauka,na gidan aure ma ko wacce da rashin mutuncin da take

shukawa a gidan mijinta,kullum a kawo kara da Sulhun yaran Sulemanu Harka ake,babu na ciki babu ga na wajen,kowa da halinsa,

Su Kansu yaran sun San basuyi dacen iyaye ba,su kuma iyayensu mata matsalarsu rowa, zagi da tsinuwa kala kala,sun gama raina mijinsu saboda ya zubar da mutuncinsa.a cikin labari zaku ci gaba da jin Halin kowa a Gidan Baki.

Amana kyakyawar yarinyace ta kwatance fara ce Amma ba kar ba,doguwace ga shape,duk inda kake neman diri to kazo wajen Amana, shekarunta 18 going to 19, gashine da ita ya wuce kafada kadan baki wuluk,gata da idanu dara dara masu tsananin kyau,gashin gira dumbul dashi,dan bakin nan cut,lips light pink,hancinta dan dai dai bai cika tsini ba kuma ba gajere ba,ga dimple idan tana magana bare tazo yin dariya,hakora yar yar dasu kar kar,saboda kullum cikin yin aswaki take ko yaushe,skin dinta me laushin gaske, gata da tsafta ba laifi.

Amana yarinyace me son al'adun maza,haka take tun tana karama rayuwarta da maza takeyi,shi yasa kaf garin wudil bata da kawa mace ko daya, sai Maza,bata da mutunci ko kadan idan ka shiga safgarta,ko uban waye komai girmansa,macece me karfi da zafin nama,ga juriya da taurin rai,idan fada ya hadaku tofa sai dai a mutu bata ji ba ta gani,idan ta fara dukan mutum sai ta gaji da kanta,kowa daya Santa tsoronta akeji ko a gidansu Amana sarauniyace dan ko waye bai is a ba,iyayenta kawai take dagawa kafa,

Ba wani abu na nafeela takeyi ba amma duk farilla tana cikawa,Sallah bata wuceta duk inda take,gata da son ilmi,gidansu ba a sasu a islamiyya bare boko amma har gona take zuwa tayo ciyawa ko kara ts siyar ta sayi littafan schl,haka ta gama primary yanzu tana ss2 a wata government schl ta garin,duk da ba wani turanci ta iya ba amma tana iya karantawa,haka islamiyya ma,tana da haddar izu 30 ga wasu littatafan tayi,duk gidan ita kadaice take zuwa schl,har yaran gidan sabo da tsoron Amana da sukeji take korasu makarantar Allo dolensu suke zuwa,

Kuma idan baka kawo mata haddar karatun ba sai ta farfasawa yaro jiki,ba ruwanta don kaninta har kashi ta tsaga masa garin duka bai iya karatu ba,har yayyenta tsoronta sukeyi sun san karfin Amana,ba mutunci ba daga kafa,shi yasa a gidan ita kadai ce take sa doka kuma dole abi dokar,

duk masifar Amana bata yi a schl tunda wani malami ya kusa korarta daga schl din gaba daya sai ta daina komai da take musu,sai kadan kadan takeyi, domin tunda ta fara schl take jibgar dalibai,tare da karya kafafun yaran mutane,domin har malami cin kwalarsa takeyi ta fesa masa mari,

Gata da kokari da tsafta,shi yasa aka bata head girl,tunda aka bata mukami idan yaro yayi late sukaganta a gate juyawa sukeyi gida sabo da sun San dole sai ta fasa ma jiki,ta gagari malaman bare abi wa yaro hakkinsa,

Amana yar rigima ce sosai,tunda aka haifeta Ummanta ta zabi wannan suna Amana aka radawa yarta,wajen aiki kuwa ta iya girki kala kala domin Amana har wajen wata Bilkisa me tuwo tuwo take zuwa tana tayata girki ta bata kudi,dasu take biyan bukatunta da dama,

Amana Ummanta bata da halin kirki,ga son kudi,bata iya taimakawa yaranta da ko kwandala,kowa yaro da babba dake gidan Sulemanu Harka Neman na kansa yakeyi,kowa ta kansa yakeyi babu me taimakon wani da ko kwandala,gwara Amana tana bawa babanta wani abun idan ya rasa,har su Hamza takan sai musu kokon safe watarana,sabo da Amana ta fisu zafin nema,ba ruwanta kullum cikin Neman hanyar samu take,kuma in taje neman aiki wajenka tofa dole ne ka bata aiki tayi ma,kuma sai ka biyata dai dai da guminta, sauran yan matan da basuyi aure ba maza suke damfara da yaudara su sami kudin sabulu da sauran kayan sawa,shi yasa suka fi Amana sutura da yawa,sabo da Amana bata da saurayi sai abokai,bata da kayan sawa,atamfarta kodaddu kala 2ne sai tsimmokaran da take sawa,suma wasu wandon duk na su Hamza ne da kannenta,take dauka idan zasu jefar sai ta karba ta wanke taci gaba da sawa tana hadawa da rigar atamfa,Ummanta tana Sana'a tana samun kudi amma sisi bata iya bawa Amana,hatta kokon Safe sai dai Amana ta siya, idan ba kudi ta tafi wajen abokanta maza ta samu,amma tana bawa kannen Amana Maza,basa shiri da Amana da Ummanta sabo da Umman Amana tafiso Amana ta dinga damfarar maza tana samo musu kudi,amma Amana taki yarda kuma bata da me sonta.

Shi yasa Amana tace abokai maza sunfi mata muhimmanci,ga kyauta,gashi basu fiye gulma da hassada irin ta mata ba,Namiji ko ya kuke mutunci zaka moreshi,sabanin mata da yawa sai su dinga yi ma hassada ma,idan sunga ka fisu sai gulma da bakin ciki.

Yawan Hulda da Maza yasa Amana takeyin acting din maza, sauran yan uwanta duk Suna Neman mata,matan ma sabo da son kudi Neman maza sukeyi,Amana ce kadai cikinsu Bata ma da saurayi bare ma ya taba jikinta,kuma mazan da take Hulda dasu tsoron jarabar Amana sukeyi ko yatsanta basa rikewa.

Ci gaban labari

Amana ce ta tashi da asuba tayi Sallah sannan ta fito wajen Ummanta dake gaban murhu zata dama kokon siyarwa,naira ashirin Amana ta mika mata ba wata gaisuwa ba komai,duk dama gidansu haka suke ba a gaishe da kowa,ungo wannan kudin Umma a bani koko damun farko nake bukata kuma yaji gaya a dauraye masa kai da gasara sosai,karba Umman tayi ba kunya tace kawo robarki,tana kwobarewa da takama ta mika mata,koko na a dauraye masa kaifa da gasara in baiji wlh gobe wajen su Zainaba zanje na siya,

To karki isheni kamar wacce ta bani million,cewar Umma,wucewa Amana tayi wajen kakarsu Ille tace karbi tsohuwa bani kosan 10 bana bukatar raini shi yasa kikaga ni komai siya nake da kudina,ba a min kallon banza saboda ni da kudina nake gadarata,iya kudinka iya shagalinka,ille dai shuru tayi tare da zubawa Amana kosanta tace ga gyaran biyu nan nayi miki,Amanace tace kwashe abinki zuciyata bata mutu ba bare ki fadawa danki kin ci dani,na girmi tallafinki,babu Wanda yake ci dani a gidan nan, Ille ce ta kwashe kosanta guda biyu jeki matsiyaciyar yarinya,shegiya wulakantacciya.

Ae naji gwara ni ummata bata haifi me bin mata ba,kin haifo Baba kin jawo mana bamuyi dacen iyaye ba,duk mun lalace,wa yasan me kikayi lokacin kuruciyarki,shi yasa Baba ya

gadoki,kisa ya kori waccen yan fulanin daya kawo gidan nan,wlh idan na kara kama Baba dasu suna iskanci a dakinsa sai na dagargaza musu kai,

Ille ce ta fashe da kuka kowanne yaro yazo yaci mata mutunci akan ta haifi Sulemanu Harka.

AsmaBaffa

Comments dinku shine jin dadina fans tnx a lot.

✳CIRANIN AMANA✳

5-10

By
AsmaBaffa

Haka Sulemanu Harka ya shigo ya riski mahaifiyarsa tana kuka,lafiya Iya?gata nan Amanace tsinaniya taci min mutunci,cike da takaici Baba ya kwantarwa da Iya hankali ya mike ya nufi wajen Amana a fusace,Amana tana shan kokonta da kosai,ya fado dakin,Gani yayi fuskar Amana ba rahma nan take ya tsorata yace haba Yar Amanata a dinga salalawa Iya mana,a hankali fuska a daure tace an gama Baba,amma ka fada mata bana so a dinga taimakamin a gidan nan,tunda an San baza a iya tsinana mana komai ba to a daina yi min rangwami da sauki ko arahar abinci bana bukata,da kudina nake Harkata,shi yasa nima nake bearing da Amana Suleiman Harka a schl,

To Amanata a dinga hakuri kinji,sai Baba kar kaji komai,Baba jiya ma fa na kamaka wlh da wata yangwadaddiyar tsohuwa,saura kadan na fasa muku kai,kawai dan Kaine Baba,dan Allah Baba idan iskancin nan zakuyi ka dinga tafiya inda baza mu ganka ba,Amana zamu bata fa dama leke kike min a zaure na?to ka daina mana?cewar Amana,

Kaci sa'a wlh na tuna kai Babane da tuni na Tara ma mutane,wai Baba baka jin kunya ka tsufa haka,kasan bala'in da kake dorawa kanka kuwa,?uwaki Amana kiyi min Addua nima ina so na daina na kasa,ban San dalili ba,wlh na gaji da bata lokacina ina ma Addua Baba bazan iya ba,yanzu kai dadi kakeji da muka zama haka,kalli yaranka fa yanda kowa yake babu na gari,

Ni kadai ce bana iban Harka nan irin taka,kana yawa fa Baba idan na gaji nima na kusa, zan kwace kawai nima nabi sahu,Haba Amana me kike fada haka cewar Baba eh wlh Allah kawai nima fuskewa zanyi na amsa sunan Amana Harka.

Wlh Baba duk randa na kamaka tsanarka nakeyi,bana son ganin ka,jeka kawai Baba za kasa na kasa shan koko na Wanda ba wani ne ya sai min ba da kudina nake harkata.

Baba jikinsa yayi sanyi Amma bazai iya daina halinsa ba,ya rasa dalili,

Amana duk tafi bashi matsala a gidan sabo da tana masa nasiha amma bazai iya dauka ba,gwara kawai ya turata Neman kudi kudu ya huta da halinta,kuma da alama zata nemo kudi sabo da Amana tafi kowa a gidan zafin nema,ga juriya da kwazo.ga karfi ga bala'i dole za a buga da ita,

Amana ita kadai tafi duk yayansa Amfani a gidan,gata me tsananin kyau da diri.

Zama Baba ya gyara kusa da Amana,tare da riko hannunta,kwace hannunta Amana tayi tare da cewa Baba ni ka daina rikeni kar nima ka mai dani irin watsatsun matan da kake Harka dasu,haba Amanata nifa Babanki ne duk abinda zanyi bazanyi da yarana ba,to naji Baba mene ne,yawwa Amanata so nake kema na turaki Lagos Neman kudi,kije Cirani kiyi Sana'a ki dinga samomana kudi,watakil ma Allah ya baki miji me kudin gaske a can ko? Dariya Amana tayi cike da jin dadi zata bar jarabar gidansu,tace Allah barmin Baba,wlh sai Baba,shi yasa watarana kake birgeni idan kayi tsiya ta wani wajen sai kayi dadi ta nan,Allah dai ya biya.

Dadi Baba yaji yanda zai dinga tsula tsiyarsa Amana bata gidan bare ta dameshi da wa'azi.

Kallonta yayi yace yawwa ta wajena,kudi zan baki masu yawa Wanda zasu isheki amfani a can Lagos kafin ki fara Sana'a.

Sa'a dai sa'adai Baba cewar Amana tana murmushi.

Nan da sati biyu zaki tafi Amana,akwai abokina zan masa waya shi zai kaiki wajen kwana,amma Baba ba irinka bane ko ?ai shi Amana daban yake yawwa yanzu naji batu Allah kaimu sati biyun cewar Amana, Baba yace kinga duk manyan maza na suna jahohin kudi cirani,amma basa tsinana min komai sai lalacewa da suka kara yi,

Duk cikinsu babu Wanda yaje lagos suna cross river wasu suna Abuja,wasu Enugu,jibi Hamaza na turashi nassarawa lafiya amma jibi da yazo gida doya kawai ya kawo min,sai 3qurtr da ya zo dasu,dariya Amana tayi tace Baba rannan saura kadan na masge Hamza bashi da mutunci har ni zai zaga,shi din banza,Baba ne yayi dan turancinsa daya koya a garin Tafa kusa da Abuja,yace control control Amanata,

Cike da farin ciki Baba ya fito,

Amana shirin Makaranta tayi ta fito tare da yin ball da wani pow da ta gani a kofar dakinsu,tayi gaba zuwa schl.

Sabon Malami ta tarar a jinsu har an shiga,cike da gadara tana budawa ta shiga class din,Malamin ta gani a kan wata kujera da ba Wanda yake hawanta a ajin sai ita,

Wajen malamin ta karasa tare da cewa daga wannan kujerar,mamaki ne ya kama sabon

malamin,yace ke dan uwarki ni zaki fadawa haka,sa'an ki ne ni? Kujerar daga gidan ubanka kazo da ita,ko ta ubanka ce cewar Amana,bude baki malam yayi,yan class kowa yayi luf,

Ke wlh sai na koreki daga schl din nan bari na fadawa p.c hannu Amana ta tura a aljihu tace uwar principal zaka fadawa,p.c yaci uwarsa ka fada masa ni Amana na fada uban p.c yaci Uban sa,

Kujerar ta janye malamin na kai ta zame kujerar da karfi ya fadi kasa ta matsa gefe ta zauna tare da harde kafa daya kan daya.malamin mikewa yayi tare da karkade rigarsa ya fice fuuu wajen p.c,

Wajen principal yaje ya fada masa komai,principal dai ya gaji da halin Amana,nan take aka karkada kararrawa aka tara Assembly duka makarantar,

Guri yayi tsit PC yace ina Amana Suleiman Harka?da sauri tace yes gani nan,nasan a kaina akayi taro, ko bakace ba zan fito gani,

Ta fito ta tsaya gaban dandazon mutane hannayenta biyu cikin Aljihu tana kallon kowa dai dai,PC yace kinwa sabon malami rashin tarbiya da cin mutunci gaban aji?yes nayi masa kuma ko gobe ya kara zan sakeyi masa komai naga dama,

PC ne ya daka mata tsawa ke yar matsiyata,yar gidan Sule tantiri me Neman mata bafa tsoronki akeyi ba,wlh yau sai kowa ya zaneki a malaman schl din nan cewar pc,

karya kake Saminu PC,gaka nan bakin kwarto dan iska,wlh akan ka zagi iyayena ko ku dakeni gwara na bar makarantar,babu Wanda ya isa ya taba iyayena ya kwana Ify,makarantar ku din banza shegu gaba dayanku,PC ne ya cakumo Amana da niyar dukanta nan Amana ta riko makwallaton wuyan PC kamar zata zareshi daga wuyan,ba shiri PC ya saketa,amma Amana zagi takeyi iri iri sai da ta gaji ta kada kai ta kalli PC tare da cewar Wanda ya kirkiro boko ma yaci uwatas,uban uban uwar Bokon an daina bokon dan uwarsa.ta kada kai ta bar schl din,tazo bakin gate zata fita ta tsaya ta zubawa me gadi rankwashi kwas,sannan tayi gaba,

bagazan bagazan ta shiga gidansu,ba Wanda ta kula ta cire uniform dinta ta tattarosu waje ta hada da jakar schl din da littafan a tsakar gida ta zuba musu kananzir ta cinna musu wuta,bal bal suna ci har suka kone kurmus,sannan ta kwashe tokar ta watsar a waje tana bin iska tace bye bye Boko ni da zan tafi Cirani Lagos garin turancin da Bokon gaba daya,

Wani Nishadi taji ya mamayeta da ta tuna zata tafi lagos,

Wanka tayi ta sa wani wandon jean kato Tsoho tukuf gwiwar duk ta yage,tasa rigar Atamfa katuwa ta kai cinyarta,p cap ta sa wata kalar tsohuwa tukuf da ita,ta fita,wani Namijine ya ce sai Amana ya garin ne,kallonsa tayi easy T.j easy dai,ya kk?Ify Amana ,kwana 2,wlh tj wai schl ne zasuyi min iya shege tuni na kwancewa PC number 8 dinsa,dariya tj yayi yace bakya farke shege ko ki kiramu muzo da yaranmu a yi maganinsa haba Amana ya kike masu sauki ne,kyalesu nayi kawai sabo da Lagos zan je Baba,

Iyye kice kin kusa fasowa gari gaskiya Dad dinku yana birgeni,murmushi me kyau Amana tayi ina zuwa tj ku zama cikin shiri zan muku hanya kuma kuzo, sai Amana cewar tj ya zaro 200 ya bawa Amana ga wannan kya danyi eh yane,godiya nake tj,haba share kawai aike tamuce,jiyafa

Majalisa ta cika ana ta jiranki baki zo,ai ina nan zuwa yau,sai mun ganki.

Rabuwa sukayi da tj,wasu yan matane sukazo wucewa sunci kwalliya yan makarantar k.u.t wudil ne,sai yanga sukeyi suna yiwa Amana kallon banza,bata kula su ba.har wani turanci sukeyi su a dole yan University suna degree,tafiya Amana tayi tana kwobarewa tare da takama tana wani budawa,

Shekewa sukayi da dariya suka tafa,wata a ciki tace oh budurwa har budurwa kyau iya kyau amma jibi ta kashe kanta,

Amana dai bata kulasu ba,sai wata tace inye kaga maza fa,wannan da gani shaye shaye takeyi,ko ciwon hauka ya kamata,

A fusace Amana taci birki tare da juyowa,ganin yanda amana ta canja lokaci daya yasa yan matan nan suka tsorata,zasu yi gudu gashi sun sa takalmi me tsini da damammen skert,

Daya Amana ta cakumo ta hau dukanta sai da ta karya mata hannu daya,sauran su biyun sun fara gudu Amana ta damkosu saida ta sumar dasu sannan tayi gaba abinta ko juyowa batayi ba,

Ran Amana ya baci ta fasa zuwa inda tayi niyya ta koma gida,Ummanta ta gani tana yin Alalar siyarwa ta Rana,can gefe Amarya tana Awarar siyarwa,Goggo shinkafa da miya,Hajiya shinkafa da wake duk na siyarwa.

Ko wacce ranar girkinta ita zata ci da Sulemanu Harka da sana'ar da takeyi.kowacce tana ci da kanta da yaranta,Amana kuwa ummanta bata bata sai dai ta siya,sabo da bata da saurayi.

Wajen Amarya Amana ta nufa tare da mika mata kudi Bani ta Naira Dari nama biyu zakisa min kuma Manya,harara Amarya ta watsa mata,ubanki ne ya bani kudin?ko bashi ya baki ba wlh in bakisa 2meat ba sai na tankadar da tukunyar miyar baki dayanta,ba shiri Amarya ta zuba mata shinkafa da Nama biyu manya harda gyaran guda,karba tayi tare da cewa cire gyaranki,na fada muku ku daina yi min mutunci a kan na siyi abunku,bana son a dinga taimaka min,

Gyaran da Amarya ta sa mata ta cire tace jeki yar Iskar banza.

2weeks ta cika Amana ta gama shirin tafiya Lagos,fitowa tayi sanye da wani 3qtr jean Wanda wandon kaninta ne Yusuf ta yanke da Almakashi ya dawo gajere,wata falkekiyar t-shirt din Hamza ta sa ja ta gama kodewa da jemewa,siririn gyale ta daura a kanta,da wata kwarababbiyar Jakarta karama tasa yan tsummokin kayanta ciki,

Umman Amana sai murna takeyi zasuyi kudi,yarta ta tafi Lagos,yan gidan suma dadi sukeji masifaffiya zata tafi su Shana,Babane ya kalli Amana sai da dariya ta kusa kwace masa irin wankan lagos da tayi,Babane yace Amanata ki canja kaya jibarki kamar inyamura haka zaki je lagos?Yo Baba so kake nayi yawa,Lagos ce fa gwara na saje dasu.

Har tasha Baba ya kaita ya biya mata kudin mota sannan ya bata dubu Hamsin saboda kafin

ta fara aiki,sosai Amana ta Adana kudinta,gashi irin katuwar mota ta hau lexs,
Amana anyi kicin kicin cikin Arna,motarsu ta tashi sai washe baki takeyi tana yin guntun turancinta,sun kwashe tafiya me nisa cikin duhun dare,har sun wuce rabi sun kusa zuwa,kitttt driver ya gangare kasa yana ihu yan fashi,ai kuwa sai karar bindiga ce ke tashi,Amana ko a jikinta,nan yan fashi suka fito da kowa waje,motoci suka gani birjik an taresu,ga wasu motoci daban na Alfarma sun kai wajen 10 a Jere,daga gani na wani me kudin ne,Amana motocin me kudin kawai take kallo ta manta a gaban yan fashi take,

Wani daga cikinsu ne ya bugawa Amana tsawa amma ko tsoro baiga taji ba,su Kansu yan fashi dariyar shigar Amana sukeyi,wani azababben gaye me tsananin kyau da kowa yake tunanin Bature,kyau kamar Aljani,da ganin yanda yake tafiya Naira ta ratsashi,sai kallonsa akeyi kowa,yan fashi ne suka nuna shi da bindiga tare da nuna masa wata tsohuwa sukace kayi sex da wannan maza ko yanzu mu aikaka lahira,
Wani takaici da bakin ciki ya mamayeshi,sai hawaye a idon wannan hadadden saurayi suke zuba sharrrrr,tsohuwa da kamar kakarsa ce,gata Arniyace,kuma shi da bai taba zina ba ko da budurwa sai wannan tsohuwar,cikin matsanancin tashin hankali ya riska,tare da dana sanin zuwa Kano a mota,bai bi flight ba,

Amana ita kanta sai taji saurayin ya bata tausayi,taya zata iya cetoshi,sai kallo take kare masa,gashi kamar Aljani sabo da kyau,a ranta tace wannan da gani bature ne Allah sarki ko Hausa ma naga Alama baya ji.

A ranta tace dole na taimaki me kyan nan,Amana ce ta buda tare da kwobarewa da 3qutr tanta,tace easy sir easy dai,wa yace daku ba ku ba,ai wlh ba mazaje sai ku,duk wajen nan Matane,Allah dai ya biya ogoginmu,sai Mazaje,irinku kuna birgeni Allah wlh ba a shiga dawa dan karya, haka Amana taci gaba da yi musu kirari sosai,murmushi  ogan yayi na jin dadin yanda Amana take kodasu,

wani yace Yan mata ina kudi,dubu hamsim din da Baba ya bata ta mika musu ai Mazaje ko Baku tambaya ba dole na  Baku,ai nakune dama,ko wiwi kwa danyi eh yane,murmushi Oga yayi tare da cewa sai yan mata me kikeso yanzu ayi miki sabo da ke ta wajen mu ce.Amana taga ma kallai yan fashin nan masu saukin kai ne,kuma basu fiye zalinci ba.nan ta fara magana
Allah taimaki Oga waccan me kyan nake so a bani shi ya kaini har lagos a motocinsa,Allah bar mana oga kar ya taba tsohuwar can,kawai ni a barni dashi,yarinya mun baki shi,kema kina son ki dan dandanashi ko,ai Oganmu tunda na ganshi nake kwadayinsa a dan bani shi nayi masa Eh yane ka gane,

Oganne ya dakawa handsome tsawa kai mike tsaye, Allah ya taimakeka ka godewa wannan yarinyar,ka kuma tabbatar ka kaita inda take so.shi kam wannan me kyau ya cika da mamakin wannan yarinya marar tarbiyya me 3qtr.abin ya bashi matukar mamaki,lallai tafiya mabudin Ilmi ce.

Sauran mutane kowa kallon Amana yake har Wanda basa jin Hausa ma.

AsmaBaffa
✳CIRANIN AMANA✳

10-15

by
AsmaBaffa

Wannan saurayi tunda Amana ta fara magana yake kallonta yanda take acting kamar a film,gashi a kankanin time ta canja musu ra'ayi,wani farin ciki ne ya mamayeshi,yarinyar nan ta taimakeshi a rayuwa babu abinda zai mata sai addua,

Kudinta ogan yan fashin ya mika mata karbi yan mata kuje,haba Oga ai nakune idan na karba nayi fariya,nifa sabo daku na taho dasu,an gaisheki yan mata kuje abinku,daya ne a ciki ya bugawa handsome tsawa maza kuje a kaita inda take so,Amana ce tace wa me kyau hey guy basu rabonsu su samu suma,nan take kuwa ya rubuta musu check na 5 hundred thousand,sukace tayi kadan ya kara musu 1million,sukace tayi kadan,Amana ce tayi magana ai sai Oga ayi masa afwa haka,angama yar Oga kuje kawai cewar wani daga cikin yan fashin,

Wannan jerin motocin suka nufa da handsome da Amana wata dalleliya da tafi ko wacce kyau a tsakiya ita wani guard ya budewa Amana ta shiga,saurayin bai so kazama ta shigar masa mota ba amma ganin Yan fashin zasu iya canja ra'ayi yasa yayi shuru ya shiga shima,su biyu a bayan motar,shi da Amana,kana yawa master wlh kayi sauri ka bawa guards dinka dama suja motocin muyi gaba,zasu iya canja mind yan fashi basu da tabbas,ya kana abu kamar baka son lafiyarka Baba cewar Amana,harara ya watsa mata,easy man ya kake yawane eh,sabo da kai fa na taimakawa wlh ganin za a hadaka da tsohuwa,nasan duk da Allah bazai kama ka da laifi ba amma tsohuwa tukuf haka,gata Christian,

Harara ya kuma watsawa Amana,ka Adana Hararar ka malam kar nayi fushi wlh zan iya ma dukan tsiya na jefarka a hanya,banda mutunci,dankwalin kanta ta cire ta zaro pcap dinta tsohuwa ta saka,

Kamar Handsome yayi dariya ya maze,aswakinta ta dakko a jaka sabo ta fara dirzar bakinta,yayinda motocin suka dau hanyar lagos gaba daya guda 10 a Jere suke tafiya,sai satar kallon Amana yakeyi yanda take dirzar hakoranta da aswaki,sanda ta zaro harshenta ta fara yi har can ciki har kakarin Amai takeyi,ita kadai nan ma yaso yin dariya,

Amana dai akwai tsafta sai dai kayan jikinta sun ji jiki da yawa,sai da ta kusa kwashe 1hr tana aswaki,sannan ta gama,tace Baaba dan miko min ruwa kuma ka sauke glass,ko kulata baiyi

ba,turancinta tayi am talking to u Mr Man,guard dinsa dake gaban motane ya mika mata ruwan roba, tare da sauke mata Glass,ta kuskure bakinta tare da shan ruwan ta jefar da robar cike da takama,

Mudubi ta dakko karami ta dinga duba hakoran nata sai da ta gama tace perfect,itafa turancin lagos ta fara tun yanzu,kasa kasa me kyau yake kallonta,sanyin ac ne ya fara gigitata, Jakarta ta duba ta dakko wani dan towel light blue sabone Baba ya siya mata shi,har turare ta fesa masa na tafiya lagos,

Ware towel din tayi tare da rufe jikinta da kafafunta da sanyi ya ratsasu,kamshi kawai me kyau yaji,ya dan bigeshi ba laifi kuma turaren da dadin kamshi,minti 2 ta fara bacci baji ba gani,a nutse takeyin baccinta,

Magazine yake dubawa sanye da wani glass fari kal siriri a fuskarsa ko kallon Amana bai kara yi ba,yana duba jaridarsa yana kora ruwan juice,tafiya sukeyi tare da sheka gudu,Driver me kyau ne ya kauce hanya tare da kasa control din motar,nan suka kafa tangal tangal a titi,kafin kace me ya daki motar gabansa ta baya ma ta dakeshi,Allah yasa duk motocin tawagar me kyau ne,nan take Amana ta farka firgigit,amma ko a jikinta bare ta razana,me kyau ya gama firgita amma yaga Amana tsaki taja tare da cewa kai malam parker mortar nan ka bani tukin,ba shiri driver ya gangare kasa suma sauran motocin haka sukayi,saida suka duba lafiyar motocin me kyau sannan driver cike da girmamawa yace Sir a bata key din,

Me kyau kuwa dan ya kure Amana yace a bata ta tukashi,yasan bata iya mota ba,inda take talaka haka ina suka ga motar da zata koyi mota,da gani ma bata da iyaye karuwan tasha ce,

Karbar key tayi tare da fita da karfi ta zauna a mazaunin Driver tacewa driver koma wata motar kar hanjinka yayo waje bana saurarawa a hanya nikam,ai kuwa a cikin motocin ya shiga daya,guard daya dake gaba ya gama tsurewa karfa yarinya bata iya mota ba ta kashesu a hanya.

Key Amana tayiwa motar tare da bata wuta sosai,har wani jiny jiny tayi sannan ta take motar tare da hawa titi,ta fara tafiya a nutse da mitar a cikin nutsuwa na gaba tayiwa Alama su tsaya a baya itace a gaba coz gudu zata sharara,

Ai kuwa ta fara tuki gashi gudu take tsulawa me uban yawa sosai tare da over taking da takewa motoci,amma kai baka is a kace gudu takeyi,irin tuki ne na kwararru,manyan drivers ba kowa ya iya irin tukin Amana ba sai babban kwaro,kamar ka hau jirgi ba wani gargada a titi haka take tuki suuuuuuuuu kawai kake ji,haka takeyin tukin,kafin kace me tayiwa sauran motocin tazara sosai basa hango motarsa duk da suma gudun sukeyi kamar zasu tashi sama,

Amana wucewa takeyi yuuuut yuuut,vol ta karo na kida ta cika motar har stiyari take duka idan kida yayi dadi,kadan Kadan take kallon me kyau ta mudubi,

Ga shegiyar pcap dinta kamar zata rufe mata ido,kara kallon mudubi tayi ai kuwa carab suka hada ido da me kyau,Wanda yake cike da mamakin wannan Aljanar yarinya kamar namiji har ma tafi mazan,

A cikin motocin tayiwa daya Alama da ta shiga gabansu ta nuna mata hanya,saboda sun kusa shiga garin Lagos,me kyau ya gama cika da mamakin Amana,suna shiga lagos Amana ta ciro

wata yar wayarta Nokia 1110 da Baba ya siya mata second sabo da kira,number abokin Baba ta kira bugu daya ya dauka ta sanar masa ta iso,

Yace to ki shiga taxi kice ta kaiki mytwelve,parker motar tayi tacewa me kyau na kawoka iya nan zan wuce ni ka gane?

Wani driver ne ya karbi tukin,shi kuma me kyau Wanda tunda suka hadu sai yanzu ya kara kare mata kallon ba tare da yayi magana ba ya Mika bundles na 1k guda biyu

Ganin bata da kudi yasa tace sabo da bani da kudi zan karba amma ka kiyaye ko dan gaba bana son taimako,bana son a dinga taimakamin ni ka gane ko,harda zare masa ido,kai man ko kurmane?idan baka jin Hausa ka fada min na iya English dina,har ta gama surutunta bai yi magana ba,kawai da hannu yayiwa driver alama dasu tafi,kudinta ta boye a jaka zata tafi ta hango ana fada a gefen titi,da Sauri ta karasa wajen su,Wanda suke fadan kawai Amana ta fesawa ko wanne cikinsu mari daya tace Wanda yaji zafi ya rama dan Ubansa,

Ai kuwa yarabawa bata sani ba duk basa jin Hausa nan take suka rufeta da duka,sai da sukayiwa Amana jina jina,da kyar wasu suka taimaka mata suka janyeta gefe,amma saboda da taurin rai irin na Amana ko hawaye batayi ba,Jakarta ta duba ta tare da zaro yar kudigar wayarta ta kira wayar abokin Baba tare da fada masa inda take yazo ya dauketa wai an mata duka.

Masifa ya farayi tare da cewar bazai zo ba idan bazaki hau taxi ba ki shekara a wajen,nan lagos ce fa ditt ya kashe wayarsa,ba shiri ta mike da kyar ta fada taxi tare da fada masa unguwar da mutumin yace mata.

Har mytwelve ya kai Amana basu san Layin ba sai da ta kara kiran wayar sa sannan ya ce Aisha 12 street,sai da suka isa can sannan ta biya driver kudinsa ta dauki jakarta da kyar.

A bakin wani shago taga tsohon mutumin abokin Babanta,

Har gidan da yake ya kaita amma da alama gidan karuwai ne saboda ko ina dakuna ne gashi duk mata arna da musulmai,

A tsakar gidan yace ke yan mata lagos ba a aikin banza kawo kudin dakinki,murmushi Amana tayi tare da yin wani yar jijjiga tana doro,ta zura hannaye a Aljihu tace Tsoho kenan da Alama baka sanni ba,amma ni da ka ganni bana Neman sauki da rangwame a wajen mutum,sannan bana son a dinga taimakamin,da kudina nake harkata,ka Bini a hankali ka gane ko,tsohon bariki na fika iya shege,mamaki ne ya kama dattijon nan dan ko a karuwai bai taba saukar irin Amana ba,

Kaga tsohon banza yi min kudin dakina naji,dubu Dari a shekara kudin dakinki,dattijon banza harda dariyar mugunta irin ya San Amana bata da kudi,nan take yaga ta karkace ta Ciro bundle daya na 1k sababbi kar kar ta mika masa,tace oya karba iya kudina iya shagalina,

Na biya na shekara guda kar kuma ka dawo ka takura min zan iya ballaka a gidan nan.

Key din dakinta ya bata ta shiga harda toilet,ko ciwon raunin da yarabawa suka ji mata bata ji,wanka tayi a toilet din room dinta,ta sa wata rigar atamfa da wani falkeken jean blue,ta fito har wajen tsohon nan,tace Man tashi maza ka rakani kasuwa,yanda yaga Amana a dire gata komai

da jikinta takeyi ba wani lako lako,tsorata yayi ya sata a gaba har kasuwa,ta siyo tabarma,da risho da kayan girki,Tsoho yace ke da zaki siyo katifa yan mata,

Tsoho kenan ka gane Neman kudi nazo ba jin dadi ba,shi kuwa Tsoho sai kallon Amana yake yana lashe baki,a ransa yace dole na dandana wannan yar chamai mai din.

Har tukunya Amana ta siyo guda biyu,komai biyu ko daya take siya har ta gama suka koma gida,yau baza ta fara girki ba,a kasuwar ta samu wata me saida doya da miya,nan ta siya taci a wajen,ta siyawa tsohon ma,harda shan lemon kwalba,

Wani me shayi da kwai ta gani tace ayi min hadin kauri,ta manta yanda zata fada da turanci sai tace thick thick tare da gwadawa da hannu 2 cups harda Tsoho,saida suka koshi sannan ta ga wani bahaushe me gashin kaza taje ta siyo biyu manya ta dauki tata ta bawa tsoho tasa,sannan suka Shiga Taxi har gida,

Tsoho dai sai mamaki yakeyi,tare da jin dadi ya samu budurwa me kudi,zai like mata ta zama kawarsa.

Dakinta ta shirya tsab sannan ta fara zaga gidan sannan ta dan leka waje ta kai 1hr a waje amma kafin kace duk ta fara sabawa da mazan layin nasu,ganin kudin da me kyau ya bata suna da yawa har wasu ta siya abinci suka ci,wasu lemo ta siya musu,duk majalisar data je ko shago sai ta raba musu lemuka sunsha hira,kullum haka takeyi har ta kwashe 2wks a lagos,duk ta saba da mutane amma iya maza,dan bata saurarar mata ita,

Yanzu da kaje Layin kace Amana kowa ya Santa,gata dama da karambani,ko mai ta gani sai ta koya kuma ta iyashi,har yau bata samu aikin yi ba,yayin da kudin me kyau daya bata suka kusa karewa,abin na damunta gashi tsohon nan yaki nemo mata aikin,

Amana tana ganin rayuwa kala kala a lagos gasu da Neman mata kamar yan akuya,ita kanta duk abin ya isheta,ko wanne yace zai kawo mata hari,baren ma tsohon daya bata masauki ya dameta da zuwar mata cikin dare wai sai ta yarda sunyi xxx ita kuma baya tsarinta tana tsoron Allah,

Amana zuwanta lagos ta kara wayewa da gogewa fatarta ta kara haske sosai ta kara yin smooth,ta zubar da kayan da tazo dasu daga kano ta siyi wasu wajen 10 amma fa duk ba skert ko doguwar Riga,gaba daya wando dogone pencil da 3qtr maka maka kamar yar America,kamar ta hada dangi da lilwayne wizzy yanda take Burma wanduna manya ga T-shirt dinta har gwiwa suke kawo mata wai shigar kamala takeyi sabo da masu kawo hari hh, p cap kuwa ta siyi kala Uku masu dan kyau,

Har inner wear ta dan siyi abunta,always pad ma da yawa ta siya ta ajiye,Amana har ta fara koyon yarubanci,ga broken English, ga grammar ma tana karuwa sosai yayinda kudinta suke barazanar karewa.ta fara Shiga wani hali

15-20

By
AsmaBaffa

Amana tana haki tare da addua ta koma gida,Dan Uzuri me gidansu ta gani a tsakar gida suna ta fada da karuwan gidan,sai bin Amana yakeyi da kallo yana lashe baki,yanda yaga zaman lagos yasa Amana ta kara fari sosai tayi yar kiba ga uban hips da breast masu matukar birgewa,yau ya kashi takobin dolene ta bashi zumarta ya sha,ya gaji da hakuri,kuma Dan uzuri gani yakeyi Amana yar iska ce itama karuwa ce duba ga yanda take Hulda da maza da abubuwan da takeyi tare da yanayin shigarta,kai kana kallon Amana zaka San cikakkiyar wayayya ce,

Sai dai zargi da zato ya jawo ya fassara Amana bai bai,domin Amana babu namijin daya taba koda rike mata hannu da niyyar iskanci,ko saurayi bata da shi,har so take taga Wanda zaice yana sonta zai iya aurenta a suffarta,gashi tasan babu me sonta,ta cire a ranta baza ta taba aure ba saboda babu me sonta a haka,itama har so take ta ganta ta dawo kamar mata masu aji da birgewa amma ta kasa.

Da dare misalin 2am tana bacci akan yar tabarmarta,ji tayi kamar ana shafata a hankali dama ita bata da nauyin bacci,firgigit ta farka,mutum ta gani kwance a jikinta touch light ta haska sai ga Dan Uzuri makale a jikinta,Tsoho dashi ko kunya baya ji dan ya girmi babanta ma

Mikewa tayi tare da cewa tsohon banza fitar min a daki wlh iya kwadayinka baza ka sameni ba dakiki,zama Dan uzuri yayi yana mata magiya kan ta amince masa,ka tashi ka fita kafin na kar Karyaka,haba tawan Amana ta,nifa abokin Babanki ne ko dan wannan kya taimakamin,nasan ma kin San komai da ganin Alama kema yar gari ce cikin harkar zumar nan,a fusace Amana ta suri Tsoho Dan uzuri ta bugashi da kasa tare da daga kafafunsa ta lankwasa su saura Kadan su balle kana ta daukeshi ta jefashi waje ai kuwa Dan Uzuri ya saki kara da kuka,

ji kake garam ta kulle kofar ta tare da cewa dan iska ragowar wiwi,ko karfi babu dan kwaya duk ya tsiyace kwanjalallen banza,wannan in banda cuta me zai shafawa mutum,shi da Baba duk together Allah shiryesu,

Ta kwanta tana tunanin halin babansu duk shi ya ja musu,sai ga hawaye idon Amana sharrrr sabo da tuna yan uwanta da gidansu da tayi da mamanta,tare da halayen family nasu,gasu kowa ya tarwatse a gidan babu wani na gari.

Bata marmarin ta koma gida Sam ko kadan,mikewa tayi ta daura Alwala ta fara nafeela ganin bacci ya gagareta,ga tunanin yanzu bata da wani aikin sunyi fada dame shayi,dole gobe ta fita Neman wani.

Washe gari kuwa haka ta dan sha tea dinta tare da siyo kosai tayi Karin safe,ta yi wanka hade da shiryawa cikin wata farar T-shirt fara kal kal siririya dai dai jikinta amma me tsayin gaske ta kai gwiwarta gaban rigar da hoton mace me gashi pink,wandon jean tasa black da fari fari a cinya yayin da wani aka yanka gwiwoyinsa crazy jean dai shi ba 3qtr kuma ba dogo ba gashi birmeme irin nasu wizzy,jikinsa duk aljihuna,wata farar p cap tasa gashinta ya wuce kafada ta tufkeshi ta cusa a cikin hular amma dole ya fito,takalmi tasa black flat me igiya baki,tayi kyau,bata fiye sa dankunne ba,powder kawai da lipstick ta shafa ta fesa body spray dinta me dadin kamshi sai shining takeyi ta fito,amma matsalar bouncing takeyi tare da kobarewa tasa hannu biyu a aljihu,

Tana fitowa tayi ido hudu da Dan Uzuri ya zura mata ido tare da marairaicewa yana mata shagwaba pls babyna aji tausayina mana,wani kallon banza ta watsa masa,sauran karuwan dake gidan su suka kalleta tare da tabe baki,

Ta fara tafiya suka kyalkyale mata da dariya,dawowa tayi a fusace dama haushinsu take ji,wani ruwa ta gani cikin bucket a wajen pampo dauka tayi cak tare da juye musu shi a jiki,ta fara ball da botikin robar saida ta ragargazashi sannan tace ugly prostitute with ur big mouth tayi waje,arnan karuwan nan sun tsorata da bahaushiya Amana mukus sukayi.

Duk inda Amana ta ratsa a lagos gaisuwa ake kaiwa wajenta,saboda girman kai irin na Amana bata taba nuna talaucinta,bata wulakanta kanta,da ta roki wani kudi gwara ta kwana da yunwa, bata harkar karanta shi yasa kayanta masu yar tsada take siya,

Da ace a kauyensu ne to da sai tayi shigarta ko wacce iri tunda kowa yasan asalinta kuma ga talauci bata samun kudi sai yan dabaru,amma yanzu alhmdllh tana samu dole ta kankaro girmanta da mutuncinta, ba raini bata son a rainata shi yasa kullum ake ganinta kamar me kudice.

Direct wani lafiyayyen wajen suya ta nufa wajen masu kudi ne da manyan yara su ke zuwa wajen.manyan guys both christains da musulmai suna zaune a kujerun dake wajen wasu na cin abinci wasu suna jiran take away,

Da ganin wajen Kasan bana talaka bane,a me kudi ma sai ka isa zaka shiga wajen,shiga ciki Amana tayi tana bouncing tare da sa hannu daya a aljihu daya kuma tana danna karmar wayarta touch screen amma yar karama da ita.

Chewgum take taunawa a hankali bakin yake motsawa sai ka kula sosai zaka gane tana cin chewgum, duk da masu kudin gaske ne a ciki kuma manyan yara babu ruwan wani da wani,ba Wanda zai kalleka ma kowa harkar gabansa yakeyi,amma Amana tana shiga wajen duk Wanda yayi tozali da ita bazai so yayi missing kallonta ba,sabo da ko iya tafiyar ta yanda take gadara kamar yar wani shugaban kasa,tana budawa,ga tafiyarta kanta a mazanma sai manyan shegu su keyin irin tafiyar da Amana keyi,ga p-cap dinta yanda ta wani kusa rufe mata ido,Riga har

gwiwa ga creazy wizzy jean habawa ai kowa kallonta yakeyi,gata yar fara me kyau sai shining takeyi ga shape,sai ta birge wasu yayin da wasu ta basu dariya,
Kowa dake wajen maza da mata dariyar Amana yakeyi,ita kuwa ko a jikinta,

Manager wajen ta kira a waya sai gashi ya fito wani katon Igbo Arne,yasan Amana ta taba taimaka masa sanda wani yazo zai yankeshi da wuka,ita ce ta taimaka masa,dan haka ya fito da fara'a dauke da murmushi a fuskarsa,yana zuwa ya mika hannu tas suka tafa,da karfi yace Hausa girl How far noooo?tsaki taja tare da riko hantsar wandonta tace a dey woooo bro Steven ,how u na?am fine,wani yorubane ya shigo Frnd din manager shima yasan Amana nan ma suka tafa yana up my girl,u r shining beb,murmushi tayi me kyau wanda ya sumar da mutanen wajen,that's my man cewar Amana,taci gaba man I need a job here,life no easy my man,u know everything Sir,u know how things work,murmushi manager yayi never mind my Frnd u don't have problem with that.nan manager ya bawa Amana aikin me kawowa mutane Abinci,

Za a dinga biyanta 10k duk wata,tayi murna da godiya sosai,a ranar Amana ta fara aiki sabida dama ma'aikata basa sa Uniform,dan danan mutane suka saba da ita amma iya maza dan ita bata kula mata sai maza
Tsakaninta da mata hi hi kawai.yau duk Wanda yazo wajen suya meat dinan da nishadin Amana yake tafiya,dole ta baka dariya,tunda Amana ta fara aiki anan basu sami Matsala da kowa ba,aikinta takeyi,sosai suke jin dadin aiki da Amana a wajen,sun kara samun customers a wajen sosai dalilin Amana
Amana tayi 3wks a wajen wannan suya Meat kamar kullum duty yamma takeyi 5-10pm sanye take cikin Riga fara kal yau ma iya Gwiwa me rubutu da manyan baki Golden a jiki,rigar me hannun singlet din mazace amma ta mata,sai ta Dora wata yar top iya kirjinta ta tsaya amma me budadden gabace top din Golden color,
Wandonta blue jean,da dan karamin takalminta kamar canvas amma dan siriri me kyau Golden shima,p-cap Golden,ga wata doguwar sarka har Rabin cikinta da wata karama da yar wata a makale a wuyanta,a takaice sarka Uku ce a wuyanta duk wasu yan sirara kamar zaren Sarkar Gold haka suke sunyi bala'in mata kyau,powder da pink lipstick kamar kullum su ta sa,
Manager ne ya zo wajen Amana jiki na bari,kiyi Sauri za a hada take away a kaiwa master mota,wanne master kuma Amana ta tambaya?baza ki gane ba shine Wanda yafi kowa a kudi a masu zuwa wajen nan,ke kaf lagos kafin ki samu Wanda ya fisu kudi sai kin tona,zaki dinga jinsu a news.jiya ya dawo daga America,cikin harshen turanci suke maganar.

Baya shigowa yana mota,watace a cikin ma'aikata ta shigo a guje tana manager kaga ga Sir can kaga cars dinsa sun kai 12 wasu kala da babu irinsu,tabe baki Amana tayi tana kallonsu yanda suka haukace akan sunga me kudi, kafin kace me masu hada suya meat sun hada me uban yawan gaske diff colors,Amana ce ta karba tana budawa tare da takama da isa tana bouncing,ta isa wajen jerin motocin nan,ita kanta ta firgita da ganin hadaddun cars din,
Wacce tafi ko wacce kyau ta nufa kafin ta karasa guards sun tarbeta a hanya tare da karba

Can gaban motocin Amana ta ga ana fada mata da maza,wajen ta karasa tana zaginsu da

turanci,kafin kace me Amana ta siye fadan,ta zagesu sannan ta juyo zata koma cikin wajen aikinsu yayinda motocin Master suka taso suna garawa a titi a hankali,

Juyawa tayi ta kalli motar ai kuwa sukayi ido hudu da me kyau Wanda ta taba taimakawa da yan fashi suka taresu,Amana bata taba jin tana tsoron wani ba sai wannan me kyau din,mugun kwarjini yake mata,

Ya ganeta tsab amma sai ya dauke kai kamar bai taba ganinta ba,itama Amana hakan tayi don bata son raini.

Amana zaman lagos yasa ta fara zuwa wata hadaddiyar football stadium,manager ne yake daukanta a motarsa ta rakashi haka wuraren hutawa na manya Steven yake kaita,manager steven ma akwai kudi ba laifi ga son jin dadi da hutawa,

Shi yasa tunda Amana ta zama best Frnd dinsa take jin dadi, yana kashe mata kudi ya siya mata irin kayan da take sawa masu tsada,abinci taci me kyau har saloon yake kaita.

In kaga Amana yanzu zakace wata mawakiyar raps ce tazo daga turai,gashi motocin manager tana driving dinsa yanda take so,Amana ta iya mota both auto an manual tun a garinsu ta koya wajen maza Frnd dinta yan tasha direbobin Mota,

Shi yasa ta iya tuki sosai,haka tukin machine ta iya,keke,ta iya sweeming sosai shi yasa ma take zuwa beach na lagos,karambani ne da Amana shi yasa tun a kauyensu ta iya abubuwa da yawan gaske na rayuwa.

Yau ma manager yace taje gida ta shirya zasuje gym,kamar kullum yauma cikin shigarta take Riga light blue me dogon hannu har gwiwa,da wandon jean dark brown pencil ,takalminta Brown tasha sarka guda daya siririya kamar azurfa ta kai har cikinta,

Yau gyale dark brown ta dan Nada a kanta Wanda yasha acuci maza,sai kamshi takeyi,

Wurin aikinsu ta dawo wajen Manager su,yau kamar tafi kullum kyau sai kallonta akeyi,shi kanshi manager sai da ya kasa dauke idonsa a kanta,yana wow u look so cute,murmushi take yayin da dimple dinta ya lotsa abin birgewa tare da cewa tnx,haka abokan aikinta ma suke ta yabawa,manager ne ya karaso suka fito da niyyar fita,wasu kalar Jerin motocin ne suka tsaya guda biyar ne yau,jikin manager ne ya kama rawa da sauri ya isa wajen motocin nan ya kyale Amana tsaye.

Glass din aka sauke kasa suuuuuuu da hannu kawai akayiwa manager magana nan ya gane me master yake nufi, da sauri ya koma wajen Amana tare da riko hannunta, master ne yace a baki suya meat dinsa ki kai masa,hmm kuma sai ni kadai zan kai?haka yace to,nifa bai taba yi min ko da daga hannu ba guards dinsa ne suke min bayani sai yau da kansa ya min magana amma Da hannu ya kwatanta min kuma na gane.

Ita dai Amana shuru tayi nan aka hada mata suyar masters ta fito har motar da taga an zuge glass kasa ta karasa,ta window ta mika wa me kyau suya meat dinsa shikam kare mata kallo yayi a ransa yana dariyar wannan yarinya kamar namiji,wani tunani ne ya fado masa a ransa amma sai ya barshi,kallonsa tayi tana jira taga ko zai mata magana amma shuru sai ma gira daya dage daya irin Ify? A rude ta tsorata tare da matsawa daga jikin motar,manager ne ya cillo mata key din motarsa yace let's go,cafe key dayi tare da shigewa motar manager shima ya

shiga gaba,nan fa Amana ta fara tuki cikin kwarewa da bajinta,

Motocin me kyau tayiwa over take ta wucesu fiiiiii, bayan sati daya yau suna wajen da manyan masu kudi suke zuwa domin wasanni,wasu ball,wasu table tennis,handball,bolly ball,wasu keke suke tukawa etc kowa da abinda yakeyi a wajen,wajene kamar a england,wajen manyan masu kudi tsabar son jin dadi irin na manager ya dauki Amana suka je wajen suma,

Amana dama ta iya table tennis da football ba laifi,dan haka wani dan yaro ta gani me matukar kyau fari kar dashi,yana gefe yana buga ball dinsa shi kadai,manager yana can zasu fara handball da wasu,

Amana zama tayi shuru ita daya,wajen yaron nan ta nufa tace let's play nan suka fara buga ball dinsu sosai,sai nishadi sukeyi kamar wani danta,sai yi sukeyi abin birgewa shi kanshi yaron yaga Amana ta iya ball,suna ta dariya,me kyau ne a tsaye a bayansu ya jingina da wata bishiya ya harde hannaye a kirji yana ta kallonsu, sai murmushi yakeyi.

Amana ce take ta cinye dan yaron nan da bai wuce 3yrs ba,haushi yaron yaji tare da kwace ball dinsa ya kwadawa Amana a jiki,ya dauki juice din dake kusa dashi ya watsa mata,tare da rufeta da duka,

Amana a ranta ta tabbatar wannan yaron bashi da kunya bashi da tarbiya,sai zagin Amana yakeyi,nan fa ran Amana ya mugun baci da wannan sangantarcen yaron marar tarbiya,tun yana dan haka amma yake irin wannan abu na cin mutunci,cinci (kinci) uwarki tayaka(talaka) kawai wannan yaron yace da Amana,

Amanafa ta gama kulewa ba imani ba tausayi ta sa kafa tayi short da yaron nan,nan yaron ya fadi can Tim bakinsa ya fashe sai jini,har wajensa taje ta mikar dashi ta fesa masa maruka har biyu,fuskarsa ta kumbura,dagashi tayi sama da hannu daya yana kuka yana am shory(sorry) Anty,bajan kayaba,zare masa ido tayi baka da kunya kana zagin manya,ko Baka da tarbiya?idan ka kara zagin wani na kamaka sai na ballaka na yankaka,

Jikin yaro na tsuma da karkarwar tsoro,ga baki na jini fuska ta kumbura,yace bajan kayaba promise u Anty.

Saukeshi tayi kasa ta zaro wani farin handkerchief ta goge masa bakinsa da fuskarsa,sannan ta bashi ruwan roba yasha,harda wanke masa fuska,tare da goge masa kayan ball din daya sa,bayanta ta juya tare da cewa sorry my boy Kaine u r too stubborn boy,gashi ka jawo zan ma illa,shoyi(sorry) Anty,ya haye bayanta tare da sakalo hannayensa ta wuyanta yana wasa da sarkarta,keke taje biya kudi tare da cewa yaron little rikeni kam zamu tuka keke,

Dariya yaron ya kamayi yana murna ya riketa kam kam,ta hau keken dashi a bayanta. Ta dinga tuki liiiii liiii iska na kadasu,yaron sai dariya yakeyi,

Bayan ta gama ta kara karbar hayar machine Lifan nan ma yana bayanta ta dinga tukasu.

Bayan sun gama yana gadon bayanta suna zaga wajen yayi bacci a bayanta.

AsmaBaffa
✳CIRANIN AMANA✳

20-25

By
AsmaBaffa

Wajen jakarta ta koma ta dauko wani dogon towel karami a ciki ta Goya yaron dashi a bayanta ta daureshi tam tam,ta koma cikin bishiyoyin dake wajen tana ta dan yawo dashi tana jijjigashi,tana jin son yaron a ranta tana inama danta ne wannan yaron, wajen table tennis ta koma duk table din a kwai mutanen da sukeyi wani table ne guda daya taga mutum daya ne a wajen securities sun zagayeshi suna bashi tsaro,yana ta buga tennis dinsa a nutse,wajen ta karasa tare da cewa Hello guys,juyowa mutumin yayi sai taga Ashe me kyau ne a wajen,

Guards din yayiwa umarni su dan matsa gefe ba tare da yayi magana ba,a ranta tana ko dai kurma ne mutumin nan,Allah sarki na tausaya masa,ga kudi ga kyau sai Allah bai bashi kunnen ji ba,Allahu Akbar,ita kadai take zancen zucinta ta,

Maganar kurame tayiwa me kyau da hannu wai tazo su buga game,a ransa yayi dariya wato ta zata shi kurma ne gashi har maganar kurame take yi masa,

Sai satar kallon yaron da ta Goya a bayanta da towel yakeyi Wanda yake bacci hankali kwance,da hannu ya tambayeta wannan dan natane?ai kuwa tace ae tare da murmushi tana kara jijjigashi,shareta yayi still tana tsaye a wajen sai buga game dinsa yake

cike da nishadi ko wannensu,gashi ta gama kasheshi da dariya kamar wata namiji yanda takeyin abu,a ransa yana gata me kyau she need to change her character wa zai aureta a haka,

Yaron dake bayanta Wanda take cewa little boy shine ya farka daga bacci,

Ido 4 sukayi da me kyau da yaron nan yaron ya buga kara tare da cewa Daddyna kayyi(kalli) nayi new Anty tace na daina zagin mutane,ta hau dani keke,da yifan(Lifan) har ma zaneni tayi Dana jageka(zageta), murmushi me kyau yayi Wanda ya jawo hankalin Amana kansa ta kura masa ido tare da jinjina kyau irin na wannan mutumi.

Yaron dake bayanta ta kwance ta saukeshi,da gudu ya tafi wurin me kyau,me kyau kuwa sai kallon yaron yakeyi yanda Amana ta fasa masa Baki tare da kumbura masa fuska,

Da sauri Amana tace my boy ina zuwa Jakarta ta dauko ta zaro wasu chocolate masu dadi guda 4 da sweet ta mikawa yaron,sai murna yaron yakeyi yana new Anty zakijo jidanmu?murmushi tayi tace yes,yace mu dinga kwana taye kina kaini cukul(SCHl) OK my Boy

zanzo insha'allah,bye Amana ta dagawa yaron hannu tayi tafiyarta gabanta sai faduwa yake sakamakon me kyau da take gani kusa da ita,sai da ta bar wajen ta samu saukin zuciyarta ta daina bugawa.

Wurin Manager ta koma shima ya gama game dinsa suka wuce take away ya siya itama Amana ya siya mata ya sauketa a gida kana ya wuce. Shi kuwa me kyau securities ya wa Umarnin su zo akai yaronsa hospital a dubashi, ana ta jin labarin me kyau,

waye me kyau?

Me kyau dai Amana ce ta sa masa suna amma asalin sunansa ALIM USMAN MUSA,Babansa USMAN MUSA DA MAHAIFIYARSA FATIMA asalinsu yan Ethiopia ne,shi yasa idan ka gansu kamar wasu larabawa don a Ethiopia ma su daban ne kalar nasu kyau ya wuce na kasar Ethiopia,

Gaba daya dangin Fatima da iyayenta du suna kasar Ethiopia,

yayin da family Usman na jini suke a Nigeria,sabo da su dama su Usman Baban Alim da kannensa su Biyu a kano aka haifesu,anan suka taso suka girma har Sukayi karatun degree suka gama,dukiyar su ta gado ce tun asali su masu kudi,sun gaji dukiya,basa aikin Gomnati sai zallar business,Usman duk yafi yan uwansa kudi nesa ba kusa ba,sabo da yafi yan uwansa neman kudi,

Babar Usman wato kakar Alim,da kannen Usman Haj Sameera da Alhj Ishaq da iyalansu suke zaune a birnin kano cikin shahararriyar g.r.a shi kuwa yayansu Usman  Musa sabo da harkokin tafiye tafiye da business ya koma Lagos da zama tare da matarsa da yaransa, Haj sameera tana auren wani engnr da yaranta maza uku mata biyu, sai Alhj Ishaq yaransa bakwai maza 5 manyan samari sai mata  biyu,ko wannensu mata daya daya garesu,babu me biyu,kuma alhmdllh suna zaune lfy suna zumunci cikin so da kaunar juna,kasancewar matar Ishaq yar kano ce  basa shiri da fatima matar Usman,

Sameera ma kanwar Usman basa shiri da matar Usman saboda da bata kaunar dangin mijinta kaf,Fatima bata son kowa ya rabesu har Babar Usman wato Haj khadija,suna kiranta Hajja, Usman zuwansa ethiopia wajen sauran danginsu a nan Allah ya hadashi da Fatima kyakyawar mace ya aureta har Allah ya azurtasu da yara.

NURA shine na farko 38yrs yake yana da mata zainab da yara biyu mace da namiji,yana zaune a Finland can yake aiki tare da iyalansa, sai ALIM me kyau yaro da kudi yafi kowa kyau a gidansu,ga dukiya da Allah ya azurtashi dasu,yayi degree da masters nasa a harkar kasuwanci a Germany, 31yrs yake, ASIYA 25yrs take wata uku kenan da gama degree dinta a London, sai Ameer Wanda yake Finland wajen Nura yana karatunsa yana level 2,21yrs yake kuma shine auta.

Ranar da yan fashi suka tare Alim kano yaje wajen danginsu ya dawo yan fashi suka taresu har Amana ta taimakeshi,

USMAN MUSA Baban Alim dattijon arziki ne,me hakuri da kyauta tare da son talaka,duk inda

ake Neman mutumin kirki to azo wajen Usman Musa,
HAJ FATIMA kuwa Sam bata da mutunci ko kadan,bata son talaka,bata kauna wani ya rabi yaranta musamman Alim da yake me kudin gaske,
Bata kauna taga yaranta maza suna son wata mace don kar ma ta kwace mata yara,kishi takeyi sosai da matan yayanta maza,Nura ita ta zabo masa mata yar gidan wani kusa a Nigeria, bata kauna taga Nura na nunawa matarsa soyayya wai zata kwace mata yaro,sai ta dinga kishi,da farko da ta sa Nura ya auri Zainab sai murna takeyi ganin Nura bai son Zainab,kasancewar zainab ta gari ce sai ta sace zuciyar Nura,ganin Nura na nunawa zainab so tace lallai sai ya saketa,Nura kuwa yaki yarda haka Abbansu ya nemawa Nura aiki a Finland ya turashi can da iyalinsa,sai bakin ciki Mum Fatima takeyi,

Amma tace duk ranar da Nura ya dawo Nigeria dole ya saki matarsa Zainab,shi yasa Nura yaki dawowa Nigeria,yana son zuwa amma halin Mahaifiyarsu bazai barsu ba,Abbansu ma ya ce kar ya dawo,shi kanshi halin Fatima matarsa na damunsa,yanda take wulakanta danginsa da Wanda ya rabesu gashi yana kaunar matarsa,addua kawai yake mata Allah shiryeta.

Alim yaro da kudi,babban dan kasuwa ne na gaske,sosai yake neman na kansa,bai dogara da kayan wani ba,da kudinsa yake harka,me kwazone da basira tare da zafin nema,ya mallaki dukiya da kadarori masu matukar yawa tun yana 17yrs yake Neman nasa yana karatu yana business.dan Jari Abbansu ya bashi me yawan gaske ya fara juyawa,kafin kace me Allah ya albarkaci abin.

Kyakyawan gaske ne na karshe,fari ne sosai sai kace dangin turawa,idanunsa ma dara dara masu kyau wasu Golden kamar irin kalar na mage shi ba na mage ba,irin dai na turawa,gashinsa kuwa baki ne sosai me santsi da kyalli,girarsa kuwa wow har hadewa takeyi,hancinsa siriri ba sosai ba,normal hanci me matukar kyau,bakinsa karami da shi red, habarsa yar doguwa,dauke da siririn saje da dan gemu kadan,sumar kansa ya tarata da dan yawa gyaran gashin sa ma abin kallo ne,

jikinsa me yar kiba ba ramamme ba kuma ba me kiba ba,gashi karkarfa da damatsa,kirjinsa me fadi sumul dashi,gashi dan dogo dashi ba da yawa ba,yatsunsa kansu abin kallo ne da birgewa,namiji ne na gaske ko ina Alim ya shiga sai ya haske wajen,Amana idan ta tsaya kusa dashi duk da cewar itama yar farace amma sai ta tashi a chocolate me hasken gaske lol,

Alim mutumin kirki ne na gari ga hakuri da kawaici,me kyauta,ba ruwansa da duniya,baya magana sai da dalili,idan zakuyi 1wk tare da Alim indai ba muhimmin abu bane to baza kaji maganarsa ba,ko a cikin danginsa iya gaisuwa ke hadasu sai su kwana 2 basu ji yace ko hi ba,yafi yin magana da hannu,ido,etc amma bakinsa baya magana sosai,shi yasa Wanda basu sanshi ba sai suce kurma ne,haka frnds dinsa sai su yini tare amma daga gaisuwa baya kara cewa komai,

Best Frnd dinsa Mubaraq shima wani hadaddan handsome chocolate ne yaso ya canja halin rashin magana na Alim amma ya kasa.Mubaraq dan gidan wani minister ne a Nigeria,kuma shi

lawyer ne,sosai Alim yake kaunar Mubaraq, shima Mubaraq haka.
Halin Mum fatima kuwa abin yafi yawa a kan Alim domin kuwa sai da ta tursasa Alim Auren mata har guda biyar tana sawa ya sakesu dole,

Matarsa ta farko da mum dinsa ta aura masa Salma ce baya sonta yana kyautata mata,ganin haka Mum ta ce dole ya saketa ko ta tsine masa,haka ya saketa yanzu haka Salma ta auri wani mijin tana zamanta Ify, Ramlat Mum ta kara aurawa Alim itama baya sonta,amma tana hutawa,nan ma Mum ta koreta, Sakeena ma hakan take,sai Maryam itama tasa aka saketa, ta biyar itace Nusaiba itace wacce Alim ya dan fara Sonta har yayi saduwar aure da ita ta samu ciki,itace Alim ya hada dabara sai suka dinga nunawa Sam Alim azaba yake nuna mata,shi yasa Mum ta kyaleta tare da Alim,har cikinta ya isa Haihuwa ta haifi zankadeden yaronta me sunan Abba Usman suna ce masa Aabid,satinta biyu da haihuwa Allah yayi mata rasuwa,
Alim yayi bakin ciki duk da cewar ba wani sonta yakeyi ba Nusaiba yarinyar kirkice, shekarar Nusaiba daya da rasuwa Mum ta koma Ethiopia kasarta ta samowa Alim wata yar Uwarta Sageera,amma Sam Abban Alim yace wlh bazai aura ba,ya gaji da Halinta,tana sa dansa auri saki ganin Alim me hakuri ne,Abba yace idan ta sa Alim ya auri wata matukar bashi ya nemo da Kansa ba to taje ya saketa,shike nan Alim ya samu lafiya,
Sai dai Mum ta kulle a ranta baza ta bari wata ta kwace mata danta ba,haka kawai wata tazo ta cinye mata dukiyar yaro ba,

Yayinda take burin Asiya yarinyar kirki yarta ta auri miji na gari me sonta kajifa son kai.Aabid dan Alim a wajen Mum yake zama shi yasa Sam Aabid bashi da tarbiyya,saboda yanda take kaunar jikanta bata yi masa fada,
Ko kukansa taji ta dinga zage zage za a kashe mata jikanta,ko makaranta idan yace baya so to baza ta bari yaje ba,

Aabid ya gama lalacewa tun yana karami ya iya zagi da cin mutunci iri iri,shima baya son talaka wajen kakarsa Mum duk ya koya,Alim abin da ya dameshi wajen Mum yaje yace ta bashi Alim su zauna tare sabo da ya samu abokin zama a gidansa so bored yake.

Sabo da son da Mum kewa Alim ta yarda da kyar ta bashi Dansa Aabid,watan Aabid Uku kenan tare da Alim suna rayuwa tare,yau da suka hadu da Amana yaune birthday na Aabid ya cika 4yrs da haihuwa,yaune kuma Amana tayi maganin rashin kunyar Aabid,

Har ga Allah Alim yaji haushin Amana irin dukan da tayiwa dansa amma sabo da hakuri da kawaici irin nasa bai nuna ko ransa ya baci ba,kuma dama rashin kunyar Aabid ta dameshi ya rasa ya zaiyi dashi,amma gashi ya hadu da Amana ta koya masa hankali.

Ci gaban labari

Asibiti suka nufa da Aabid nan doctor ya dinga masifa taya za ayiwa yaro irin wannan dukan,amma Alim shuru yayi bai ce komai ba,bayan sun dawo da dare gidansu ya tafi wajen

Mum tare da Aabid,Mum tana ganin Aabid baki da fuska a kumbure ta gigice tana Ify me ya sami jikana?Alim ne yayi Sauri yace Mum wata yayiwa rashin kunya ta zaneshi,
Aifa Mum tuni ta fara zagi tana wacce shegiyace yar matsiyata ka nuna min ita wlh sai na batar da ita, a hankali Alim yace calm down Mum shi fa ya zageta,dan uwarta ita wacece da baza a zageta ba,ai da nasan gidansu har iyayenta sai sunyi nadamar haihuwarta,Aabid ne yace Mum ki kyayeta ina conta ta au dani keke,ta ciya min sweet,
Rufe min baki sai na kwato ma yancinka,kai dama Alim na lura ba son yaron nan kake ba,idan baka so ka dawo min da jikana aikin banza na gaji da shirmenka,
Kai a dole me hakuri ko kana gani za a kashe bawan Allah,nan fa Mum ta fara lilita Aabid tana Lallabashi tare da cewa bazai koma wajenka ba sai yayi 1wk a wajena ya huta,ba yanda Alim ya iya haka ya mata sallama ya koma gidansa.

AsmaBaffa
Tnx alot readers.
✳CIRANIN AMANA✳

25-30

AsmaBaffa

Mum din Alim ce ta dauki Aabid sai lallabashi takeyi ta rasa inda zata sa kanta,haka ga bacin ran yau birthday na Aabid amma ko dan party ba a shirya masa ba,part din Abba ta nufa da Aabid dauke a kafadarta,ko sallama kasa yi tayi ta shiga zuruf tare da cewa kalli yanzu dan Allah Abban Alim abinda yaron nan yakeyi ya dace,jiba yanda yana gani wata Jaka ta Zane min jika,Abin haushi ma Alim ya kasa hadawa yaron nan ko dan birthday party,
Kallonta Abba yayi da mamaki tare da cewa party addini ne ko dole ne,wannan dabi'ar yahudawa ce da mutanenmu suka daukarwa Kansu da shirme,da ka hada birthday party gwara ka yini kana karatun Qurani,ko tasbihi,ko azumi kana yiwa kanka addua sosai a wannan rana yafi ka kunna kida.

Tabe baki Mum tayi tana yo dama ai haka zakace,ni dai kawai Allah ya hadani da miji ba wayayye ba,kana da kudi,ka zaga duniya,kana shiga mutane amma ka kasa wayewa,na tabbatar duk yarana halinka na gidadanci suka dauko, fuuu tayi waje dauke da Aabid ranar kusan kwana tayi a zaune tana jinyar Aabid dinta.
Alim ne kwance bisa lallausan royal bed dinsa Wanda ya kai karshe wajen haduwa,tunani

yakeyi yanda zai samo me kula da Aabid wacce zata bashi tarbiyar da ta dace uwa ta ba danta,kafin Allah ya kawo masa wacce yake so ya aura,

Arniyar Wayarsa ya jawo tare da kiran Mubaraq best Frnd dinsa,yana dagawa a hankali Alim ya fara magana sai ka saurara sosai zaka ji me yake cewa,bakinsa da kyar yake motsawa Frnd maganar da ka bani shawara kan na nemo me kula da Aabid kafin na samu nayi aure,so ya kake ganin za samu?

Mubaraq ne yayi Dariya yace bari zanwa Mama na maganar a samo wata ka barmin komai a hannuna,alright Frnd cewar Alim.

Bayan sati daya tsakani Mubaraq ya kawo wata dattijuwa gidan Alim,Alim shi bai da damuwa nan ya karbeta yana zaune a luntsumemiyar kujera kafa daya kan daya yana latsa waya,ko a bai cewa Rakiya dattijuwa ba,tunda tazo ko da ta gaisheshi ma hannu kawai ya daga mata kamar wani sarki,a.c ce kawai ke ratsa Rakiya har karkarwa takeyi,

Wani remote ya dauka tare da dannawa minti daya sai ga wani me aiki ya shigo da sauri,Umarni ya masa kan ya tafi da Rakiya yayi Abinda ya dace,suna fita ya tura Driver ya dauko masa Aabid wajen Mum,

Sai da Mum ta zage driver tas sannan ta yarda Aabid ya bishi,

Rakiya aka kaiwa Aabid Nan fa yaro ya canja fuska yana yatsina tare da toshe hanci kamar yaga kashi,

Da dare ko da Rakiya tazo shiryashi sai da ya zageta sosai sannan ya tafi part din Daddy sa,Alim duk abinda zakayi zai wahala ya ma magana bare ya hanaka,dan haka tun Rakiya na hakuri da Halin Aabid har ta fara dukansa, kuma Alim bai taba ce mata ta daina ba,

Yana kallonsu watarana Alim na zaginta ita kuma rakiya tana zaneshi amma Alim bai ce musu komai,har Rakiya ta kwashe 2mnths tana kula da Aabid,yauma kamar ko yaushe Suna palon Alim suna kallon film sabo da Alim shi ba ruwansa da kar a shiga inda yake matukar baza ka takurashi ba

,Alim yana ta aiki a system Rakiya tana canja Chanel taga wata tasha suna haska BF ta bar tashar Abinta Suna ta kallon,Alim ne yaji nishi kamar ana Sex da sauri ya kalli TV yaga abinda yake faruwa,Aabid yana ni ki kaimin cartoon Chanel amma ko kallonsa Rakiya taki yi,da Sauri Alim ya dauki remote ya kashe TV gaba daya,ba tare da yace komai ba ya ebo kudi ya mikawa Rakiya yace take this na gaji da Halayenki maza na Sallameki,zama tayi zata fara bashi hakuri,securities ya kira sukayi waje da Rakiya.

Sosai Alim ya shiga matsanancin bacin rai,Mubaraq ya shaidawa matsalar,3days aka kawo wata budurwa ita kuma,nan ta fara kula da Aabid,Aabid kuwa ya tsani wannan budurwa sabo da tsawar da take daka masa,

1mnth ltr budurwar nan ta kamu da son Alim kullum sai ta dinga zuwa tana zama a kusa dashi,yau ma yana nutse kan wata chair 2 seater yar budurwa ta fito tana karairaya tana zuwa kusa da Alim ta zauna kafadarta na gugan tasa,mikewa yayi har ya daga hannu zai mareta ko

me ya tuna sai ya fasa,itama kudinta ya bata ya koreta,

Basu gaji ba suka kara kawo wata tsohuwa Yakumbo,nan ma Ya kumbo ta dinga yiwa Alim sibare tana satar masa kudi,ba shiri ya sallameta itama,haka Mubaraq ya dinga kawowa Alim masu kula da Aabid amma basuyi dace ba,sai ma kara lalata Aabid da sukayi,ko wacce halin tsiyarta daban.

Gashi Aabid kullum zancen new Antynsa yakeyi shi ita yake so a kaishi wajenta ta hau dashi keke,Aabid da Alim basa wata hira a tsakaninsu bare wasa,saboda Alim bai son Surutu.shi yasa in ka shiga wajensu sai kagansu shuru kowa harkar gabansa yakeyi kamar basu San juna ba,ko da Aabid yazo yana so suyi wasa da Alim sai kaga Alim yayi murmushi ya bashi hakuri cewar yaje yayi shi kadai,

Watarana yayi kuka haka har ya saba,babu wata shakuwa tsakanin Uban Alim da dan Aabid.

Shi yasa Aabid ya cewa Alim Daddy ka kawo min new Anty ta nafi sonta,shareshi Alim yayi a ransa yana tab wannan yarinyar marar tarbiya me yin abun maza,Amma tunda Aabid ya dameshi zai kai Aabid wajenta Saturday ya yini a wajenta yaga me zai faru.

Haka Alim ya kulla shawararsa.

Gidan baki kuwa can wudil kauyen su Amana Baba yaji Amana shuru tunda ta tafi Amana sau Uku ta kirasu a waya suka gaisa da yan gidan gaba daya,shi kuwa Baba sau daya ya taba kiranta yajita Lfy shike nan bai kara ba,itama Umman Amana ko ta kan Amana bata bi bare tasan halin da take ciki,su kuwa sauran kanne da yayye dadi ma sukeji jaraba ta bar musu gidan zasu Shana,yayinda manyan mazan suke kudu suma cirani suka tafi suna can suna sheke ayarsu.

Wani abokin Baban Amana dake jigawa state ne ya aiko da yarsa yar 16yrs domin Baban Amana ya taimaka ya kaita makarantar Boarding dake garin kacako kasancewar kusa suke da garin,haka sulemanu harka ya karbi Amanar yarinyar nan hannu bibbiyu zai kaita schl ranar Monday,yarinya dai Mariya tana nan dakin Uwar gidan Sulemanu harka kafin a kaita schl,Sulemanu sai kallonta yake yi duk inda ta gifta,akan haka ma ya rage fita wajen aikin yayinda ya gama danawa Mariya tarko.matansa suna hankalce dashi sunga take takensa,sabo da haka suka kara kafawa suka tsare kan a samu a tseratar da yarinya daga tarkon mijinsu fasiki.

Yau Saturday 10am motocin Alim suka parker a bakin wajen suya nasu Amana,manager guard yayi wa magana,few seconds sai ga manager,yau Alim magana yayi da kansa,pls I need to see that Girl dake aiki anan she look like a Boy,nan manager yace oh Amana Hausa Girl.yeah cewar Alim

Cikin harshen turanci Manager yace tana gida sai yamma take zuwa aiki,Alim yace bani Address nata idan ka sani,da sauri manager ya bawa Alim Address na Amana,

Juya motocinsu sukayi har gidan Dan Uzuri,Alim yasha mamakin ragargajewar gidan,yanzu wannan yarinyar anan take zama Amma kayan da take sawa bai dace ace anan take zama ba,

Gashi gaba daya yaga unguwar tantiran yan iska yan bariki take zama,layin su Amana kuwa a

unguwar ma na daban ne sai ka shahara a iya shege sannan zaka iya zama ciki.
Sosai Alim yake mamaki tare da cewa no wonder yarinyar take karshe wajen rashin kunya.dole ma Amana baza ta taba zama ta gari ba cewar Alim,Dan Uzuri ne ya karaso jikin motocin Alim a gigice,
Guard ne ya masa magana tare da kwatanta masa yarinyar da suke nema.
Da Sauri yace Amana yanzu baza a sameta a gida ba tana majalisarsu.
Suna haka sai Ga Amana sun fito daga wani corner tare da wasu maza su Uku,sai hira sukeyi.
Alim yana kallonta ta mudubin motarsa a ransa yace lallai wannan ta shahara.

Kafin kiftawar Ido Dan Uzuri ya isa wajen Amana tare da Nuna mata jerin motocin Alim wasu kalar da bata taba gani ba,Dan Uzuri yace wlh ba ruwana Amana Idan masu kudi kika tabo,baza ki jawo min bala'i ba,dama nasan rashin mutunci sai yasa kin hadu da ajalinki,gasu can sai kije wajensu ke suke nema,haka gari banza masu kudi haka baza suzo nemanki ba,
Kallon guards din Amana tayi ta gane Me kyau ne mamaki tayi yanda yasan gidan da take sai ta tuna dasu manager nan tace tabbas manager ne ya basu Address dinta,a fili tace to me nayi musu kuma hmm bari naje naji,

Da Saudi Dan Uzuri yace ke kika sani wlh kar ki nuna kin sanni,idan sun hallakaki na buga waya can kauyenku,aikin banza me jaye jayen tsiya,to nafi karfinki li'ilafi kuraysh baza ki jawo min ba,lakadaja akum a kanki.
Dan Uzuri wani lungu yasha tare da boyewa ciki yana lekowa yaga me zai faru yasan Amana dai kam sai dai ya bugawa Sulemanu Harka waya ya sheda musu ai Amana ta tsufa a prison.
Bude mata kofar motar Alim akayi ba tsoro ta shiga,Amana basu saba da gaishe da mutum ba ko iyayensu basa gaidawa dan haka Sallama kawai tayi ta zauna a cikin motar wani sanyi da kamshi yana Ratsata,ta lumshe ido wani niima,bugawar zuciya hade da kwarjinin me kyau sun taru sun mamaye mata zuciya.

Ta rasa dalilin da yasa me kyau yake mata kwarjini,kuma sai ta dinga jin masifar tsoronsa,da kyar ta iya daga kai ta kalleshi jin shuru baice komai ba,Subhannallah wani azababben kyau taga ya kara,Wanda ya wuce kwatancen me tunani,gashi sanye cikin wata rantsatsiyar shadda ta garari milk color,dinkin irin pencil dai dai jikinsa ga kan nan bai sa hula ba sai gashi baki sidik luf dashi me yawa yash gyaran fuska,ga wani dan Saje da dan gemu das.
A hankali kamar bazai magana ba cike da gadara da izza yana latsa waya ba tare da ya kalleta ba,ya Umarci Guard ya dauko Aabid a dayar motar,nan da nan matakan tsaro suka dauko Aabid ai ido hudu Amana tayi da Aabid da karfi ya kwalla kara ta murna da jin dadin ganin New Antynsa,nan ya karaso da dan gudunsa ya dane jikin Amana sai murna yakeyi,tare da cewa new Anty zan biki,alright My sweet Boy, I missed u cewar Amana,mic (miss)you too Aabid ma yace,ta gefen ido Alim ke kallonsu yana jin Dadi a ransa,Aabid dinsa zaiyi farinciki yau.a hankali Alim yace kuje da Dare after Isha zanzo na daukeshi,Ok Baàbaà sai kuma tace au Sorry pls.

Daukan Aabid tayi tare da sabashi a kafada nan Aabid ya ce Bye Daddy shima Alim ya daga masa hannu suka ja motocinsu suka tafi, sun bar Amana cike da Mamaki mutum bai Santa ba amma ya kawo Mata dansa.Dan Uzuri ne ya fito daga inda ya boye shima yana mamaki a ina Amana ta samo masu kudi haka har yaronsu suke bata raino.

AsmaBaffa
✳CIRANIN AMANA✳

30-35

By
AsmaBaffa

Ina mika Godiyata ga dubban masoyana makaranta wannan novel.

Dan Uzuri a fili ya firta ko ni Dana taso cikin lagos banyi aboki ko da me Mota ba,amma wannan me suffar mazan gashi tayi masu motoci ma,ko da yake mace ce suna kwashe zumar ta dole haka ta faru.

Wajen Amana ya kara ta watsa masa masa wani matsiyacin kallon da ya sa Dan Uzuri ya bar wajen ba shiri tare da cewa yarinya duniyace bariki ce kici kema watarana ta cinyeki.ni dai ina fada miki kar ji jawo mana abin kunya a gida ato.

Share shi Amana tayi ta dauki Aabid suka shiga zaga gari,sai wasa sukeyi,sai kallon Aabid mutane keyi sunga bature dan Madara,gida suka dawo tayi musu girki suka ci suka sha sai bacci,bayan sun tashi daga bacci,daukansa tayi suka shiga wani boutique na yara,ta siyawa Aabid wata farar Riga Armless da jean black 3qutr na yara a kantin ta gwada masa dai dai shi,sweets dasu biscuits ta siya masa  da yawa sannan ta kaishi wajen aski dan kansa ba gyara,nan Amana tasa akayi masa wani arnen aski na yan gayu,na samari masu ji da Kansu,yaron sai yayi masifar kyau,bayan sun gama gida suka dawo ta cire masa kayan jikinsa ta wankesu fes ta shanya,abinci suka kara ci sannan tayi wanka shima yaron tayi masa,

Vaseline ta shafa masa hannu da kafa,gashin nan ta shafawa man gashin da take amfani dashi ta kara gyara masa gyaran gashin da akayi masa,

Turare ta fesa a kayan yaron da ta siyo masa sannan ta sa masa,sosai ta shiryashi yayi kyau,itama shiryawa tayi cikin wandon jean pencil dogo Red,rigarta T-shirt siririya amma doguwa har gwiwa tasa fara,ta fesa turaruka sosai,sannan ta dauko siririn gyale Red yafa sai tayi kyau sosai,

Sai kamshi sukeyi,karatun qurani ta fara Koya masa suna yi dama Amana tana son Bawa yaro tarbiyar karatu,nan da nan yaro ya iya suratul Iklassi,sai wasansu sukeyi har magrib tayi sukayi Sallah da Azkar,

Kayansa data wanke sun bushe kwasosu tayi ta linke tare da zubawa cikin leda wata me kyau irin ta gift,bayan Sunyi Sallar Isha ta kara fesa turare ta fesawa Aabid shima sai dariya yakeyi yana tsokanarta,

Karatun da Amana ta koya masa Aabid yake ta faman nanatawa yana jin dadi,suna Haka Dan Uzuri ya fado dakin jiki na bari tare da cewa kiyi sauri ki kaiwa masu kudi dansu yana waje yace kuje.

Tsaki Amana ta ja tare da gallawa Dan Uzuri Harara ta dauki Aabid yana New Anty ci goyani pls,goyashi tayi a bayanta tare da daukan ledoji biyu a hannunta suka yi waje.

Tana dubawa ta ga motocin sa sai taga wata Azazababbiyar mota guda daya sabuwa gal me shegen kyau a kalla ta ba million 30 baya,horn ya danna musu nan ta gane yau a mota daya yazo,karasawa sukayi wajen motar,Aabid sai faman washe baki yake yana rera karatunsa,

Mazaunin baya ta bude tare da saka ledojin a baya,sannan ta bude gaba ta zaunar da Aabid dake ta faman yin karatunsa,kan Aabid ta shafa tare da manna masa kiss a kumatu good night my Boy,murmushi kawai yaron yayi tare da fafin Anty Jan kwana da ke,kijo muje jidanmu,zanzo da kaina Boy never mind ok,kai kawai ya daga mata amma Baiji dadi ba yaso ta bisu sunyi bacci tare,

Alim Wanda ke a mazaunin Driver tsayawa yayi tsam yana ta kallon Aabid dinsa da Anty Amana,gashi har karatu yaji a bakin Aabid,gashi ta kaishi aski,ta sa masa sabon kaya abin sai ya birgeshi shar shar dasu,dubanta ta kai wajen Alim taga sanye da 3qtr da wata black T-shirt yayi kyau,ga wani kida na tashi a motar me ratsa zuciya,

Amana hannunta biyu cikin aljihu tacewa Aabid bye shima yace bye ta wuce abinta tana bouncing ba tare da ta yiwa Alim magana ba shima bai mata ba.

Motarsa ya ja ya bar unguwar a nutse,yayinda Amana ta juya ta shiga gidansu cike da Mamakin halin Alim baya magana ko kadan kuma shi ba kurma ba,ko dan yana da kudi ne oho.

Alim kuwa mamakin yanda yaga Aabid yake neat dashi gashi ta gyarashi harda sabon kaya ga abinda yafi birgeshi shine karatun da yaji a bakin Aabid yanzu dama wannan yarinyar tasan addini yana ganinta me kamameceniya da maza Jahila Ashe tasan addini
Tunani ya Shiga sosai akanta.

Dole ya dauketa ta kula da yaronsa kuma shima dole ya gyara mata zama ta daina abubuwan maza,nan tunaninsa Alim ya tsaya cak.

Kwance Amana take kan tabarmarta tana tunanin gidansu da halayen yan Uwansu nan kewa

ta cika mata zuciya  tana so taje gida taga yan Uwanta,da iyayenta amma sabo da halayensu Sam bata marmarin ta koma,nan take hawaye ya fara kwaranya a idanunta tana tausayawa Kanta,gasu da iyaye amma ba gata,ba a damu dasu da rayuwarsu ba su dai kawai an haifesu ne gasu nan a zube a duniya.

Gidan Baki kuwa Baba har yau yaki kai Maryam makaranta tunda aka bashi Amanarta yaki yarda ya kaita,so yake ya cimma Burinsa,kamar kullum yau cikin dare ya lallaba dakin Goggo Uwar gida inda Budurwar take,suna cikin bacci ya lallaba ya fara shafa kafar maryam yana murzawa a hankali,yarinya tana ta baccinta,nan ya kara kaimi ya koma kirjinta ya shiga shafa boobs dinta a hankali yana lumshe ido,sosai yake washe baki yana latsawa tare da murzawa,kamar a mafarki Maryam ta mike zumbur tare kwala ihu,Goggo ce ta mike cike da mamakin Ganin Baba yana ta aikin shafa boobs din yarinya,

Goggo ce tayi tsalle tare da make masa hannu tana zaginsa tsohon banza wlh kayi asara yar cikinka yar Abokinka Yar Amana kake Neman lalatawa rayuwa,wlh nayi Nadaman Aureka,matsiyaci mazinaci,fasikin banza kuka ta saki da karfi nan take matan gidan suka fito dama sun San haka zata faru ba wata wata suka fara zagin Sulemanu Harka shima yana zaginsu,Maryam sai kuka takeyi,su kuwa ashar ce kawai ke tashi a gidan,

Da kyar Goggo ta lallashi maryam, washe gari da sassafe Goggo tasa Maryan ta shirya da kanta ta dauketa ta kai ta makarantar kwana tayi mata komai daya dace.

Ko da Sulemanu Harka yaji labari an kai Maryan schl Ashariya da tsinuwa ba wacce baiwa Goggo ba da sauran matan gaba daya.

Maman Alim ce zaune a kujera sai Huci takeyi tare da tabbatarwa kanta Alim bai isa ya auri wata ba koda zata mutu sai zabinta,gashi ta rasa inda zata shawo kan Abban Alim,tunani ta shiga kan taje wajen kawarta Hajiya Talatuwa suyi shawara yanda zasu bullowa abin,tana zaune wata yar Aikinta cikin ma'aikatan tazo tare da ajiye mata juice tazo tsiyayawa jikinta Na rawa sabo da tsoro ta zubar da kadan a kasa,kafin ta dago da kanta Mum ta kwada mata wani mahaukacin Mari kafin tayi wani yunkuri Mum tasa kafa ta daketa nan wannan dattijuwa ta Daki jikin kujera tare da zubewa kasa wanwar,

Mum kuwa mikewa tayi ta hau sama dalaf dalaf tare da Jan tsaki sunfi goma tare da cewa shashashai talakawan banza matsiyata.

Alim da jerin motocinsa ne sukayi parking a gidansu,bayan an bude masa kofa ya fito cike da tafiyar nan tasa ta izza da kasaita sanye yake cikin wata farin yadi kal dinkin fitted ya amsheshi yasha kyau hannunsa dauke da wayoyinsa guda biyu yana latsawa,cike da yanga kamar bazaiyi magana ba yayi sallama a palon Abbansa,nan ya samu Abba yana shan fruits,har kasa ya gaishe da Abbansa,Asiya kanwar Alim ce ta shigo cikin shiga ta alfarma,wata shadda ce maroon a jikinta tasha aiki,laaa Ya Alim sannu da zuwa kallonta Alim yayi ke kuma yaushe kika dawo daga kano?jiya Na dawo,bro ina Aabid? Yana schl mana,ya Alim Ya Nura yace ya kiraka wayarka a kashe,zan kirashi later, ok ,Ya Alim? Tsawa ya buga mata ke kin dameni ban son surutu,shidai Abba yana jinsu har Mum ta Shigo,

Harara ta zabgawa Alim wato da ban shigo ba Abbanka kawai zaka gaisar ka wuce ko?am sorry Mum tsaki taja, nan Abba yace sarkin kishi aikinki kenan kishi.

Shuru tayi daga bisani tace dama haka zakace mana tunda sun nuna sunfi sonka, kallon Alim tayi tare da cewa Ina jikana? Murmushi yayi tare da cewa yana nan Ify yana schl.
Hirar Nura dake Finland suka farayi Mum kuwa daure fuska tayi bata kaunar ayi mata zancen Nura saboda ya gudu da matarsa yana Nuna mata so,sun kwace mata yaro suna cin kudinsa a banza ya daina sonta.

Alim shikam halayen Mum dinsu mamaki ke bashi,Asiya ma Sam bata kaunar halayen Mum dinsu,
Yau Sunday yaune Alim ya shirya domin kai Aabid wajen Amana saboda ya dameshi kan yaje wurin Antynsa.
Amana kuwa yau bala'i ya sameta sunyi fada da wani Igbo yayan manager sosai sukayi fada akan ya shafa mata wuyanta,
Zaginsa ta farayi Wanda ya fusata ya cafki boobs dinta a taron mutane,nan take Amana ta dauki kujera ta kwada masa a kai,sai jini tako ina,

Ba tare da Manager yayi tunani ba ya fesawa Amana mari har Uku tare da korarta daga wajen aiki. Ita Amana ba korar ce ta sata zub da hawaye ba illa irin yadda bro din manager ya shafa mata breast agaban mutane Wanda ba a taba kwatanta mata hakan ba,

Tun Saturday da yamma tana gida tayi kuka ta gaji har yau Sunday idan ta tuna Babansu Sulemanu Harka shi ya ja musu sai kaga Hawaye Na sintiri akan fuskarta idonta ya kumbura yayi jajir bata da wani kuzari,gashi wani marar Imani yana binta bashin dubu sittin 60 gashi kudin hayarta ya kare Dan Uzuri ba mutunci,abincinta saura kadan ya kare dama da aikin ta laru zata biya wasu don Dashi take son shiga dama sai ta samu ta rage wasu to gashi aikin da ta dogara ma dashi an koreta.

Addua takeyi sosai da nafeela kan Allah ya kawo mata mafita a wannan Al'amari,11am tana zaune a dakinta tayi tagumi hawaye Na zuba Dan Uzuri ya rufto dakin ko lura da Kukan da takeyi baiyi ba yace ke yar chakwaskwas  kizo inji masu lokaci me kudin nan yana waje ya bar dakin da sauri kamar zai kifa.

Fuska Amana ta wanke idon nan a kumbure jajir dashi ta fito, Wanda ke binta bashi taci karo dashi,yana busa sigari yace ke yayane?kwana 2?ina kudin ne? Fuska a daure Amana tace kasan bazan ci ma kudi ba dama lalura tasa Na karba, ke yarinya naga kina wani masifa ne,mu zakiwa Jan ido dan me cin uwarki yanzu Na makeki kuma wlh gobe ba mutunci dole kibiyani,dalla ware banza, Amana yau dan tana cikin Bakin ciki ne da tuni an kwashi yan kallon,Alim dake mota sauran jerin motocin suna bayansa yana kallon Abinda ke faruwa, kuma da Alama fada sukeyi.

Tunda ta taho yake kare mata kallo yau salab salab take tafiya fuskarta ba annuri, ido ya kumbura Jajir haka ta karaso jikin motar kanta a kasa tana wasa da zoben azurfarta me matukar kyau.

AsmaBaffa
✳CIRANIN AMANA✳

35-40

By
AsmaBaffa

Ina ganin sakonninku ta ko ina readers ina godiya sosai.

Tun kafin a bude motar Aabid ya fara ihu da murna yana kiran New Anty,idonta cike da kwalla ta daga masa hannu,ganin zata iya fara kuka yasa ta yi saurin bude motar tare da daukan Aabid ta juya cikin sauri ta bar wajen,Alim kuwa yasan tabbas da gani tana cikin damuwa ba haka ya saba ganinta ba.

Motocinsu suka juya suka wuce direct office ya nufa,ita kuwa Amana yini sukayi da Aabid yana debe mata kewa,bakin cikinta ya yaye sai dai in ta tuna sai kaga tayi shuru kwalla Na Neman zubo mata,karfinta ya gaza,mace me raunice tunda ta taso cikin wahala take tunda ita ke ciyar da kanta,Sana'a kala kala da rayuwa duk tayi,gashi yanzu ba uwa ba uba ba wani Wanda zai taimaka mata ko tana kusa dasu baza su amfana mata komai ba,sai bacin rai da bakin cikin halayyar su,a rayuwa ta ya mace ace babu Wanda ya dau nauyinta,ita kewa kanta komai ,dole yanzu ta gaza kuma dole ta shiga wani yanayi.

Wajen magrib sukayi wanka ta shirya Aabid ta mayar masa da kayansa da yazo dasu tare da fesa musu turare,wani cornflakes ta hada musu ita da Aabid suka sha suka koshi,sunayin Sallar Isha wani ya shigo tare da sanar da ita ana kiranta a waje,

Aabid ta goya suka fita dan tasan bazai wuce Daddynsa ba,tana fita ta hango wata bakar mota me shegen kyau da tsada guda daya,da alama shi ya kawo kansa,wajen ta karasa yana zaune a mazaunin driver cikin shiga ta alfarma,kamshi da kyalli yakeyi,ba bata lokaci ta bude gaban motar ta zaunar da Aabid Wanda ke kuka shi wajenta zai kwana,da kyar ta

lallabashi,haka kawai taji bakin cikin dake damunta ya dawo sabo dal,nan take ta fada tunanin rayuwarta bata da wani plan,bata ma San inda ta nufa ba,ita ba karatu ba,ita ba aure ba to waye ma zai aureta a haka,ga shi bata ma gaban iyayenta su Burunsu ta nemo musu kudi,ba ruwansu da halin da zata shiga,

Nan take zuciyarta ta kara karyewa ita waye ma zai so ta a haka yanda take kamar namiji,wani hawaye masu dumi da zafi ne suka shiga ambaliya a fuskarta,sheshekar kuka ta farayi ba shiri ta rungume Aabid kam kamar zata Fasa masa kashi taci gaba da kukanta a hankali,duk inda taso danne hawayenta da zuciyarta abin yaci tura,

Shuru kakejin motar babu Wanda yace ko ehem,kukanta kawai ne ke fita kadan.

Alim kuwa wani tausayinta ne ya lullubeshi da alama akwai Matsala babba tare da ita,bai ce mata komai ba illa bundle Na 1k dubu Dari kenan ya mika mata,Aabid kuwa shima kukan ya fara,yana Anty wane ya dakeki?

Ki fadawa Daddy ya fadawa sojoji,murmushin yake Amana ta farayi ga hawaye Na zubar mata har ta samu saukin zuciyarta,ba tare da ta kalli Alim ba cikin rawar muryar me kuka tace Na gode Allah kara budi ta juya tare da barin wajen tana share Hawaye.Alim yayi tunanin bai kamata yanda take kula da dansa ba ya kyaleta haka iya kudi kawai ya bata bai ji matsalarta ba,

Horn ya danna mata Wanda ba shiri ta juyo a firgice tare da dawowa wajen motar budewa Alim yayi tare da kiranta ta side din kofar sa,ya kai 5mnt tana tsaye gabansa ba tare da yayi magana ba,da kyar ya furta what's wrong with u?meke damunki?da kyar ta kalleshi kadan sannan tace ba komai Na tuna iyayena ne,suna ina parent din naki?ko sun rasu Alim ya tambaya.

Hawaye ne ya zubo mata sannan tace suna kano state, CIRANI aka turo ni lagos Neman kudi,

Da Sauri Alim ya zaro ido waje Ci...ra...ni? Kai ta daga masa tare da cewa yes,mamaki da alajabi ne suka cika Alim,yace aikin da kikeyi fa yau naje bakya zuwa?ae an koreni munyi fada da wani yana son taba min jiki that's y.

Tausayinta Alim yaji tare da cewa wannan Unguwar da kike a lagos bata mutanen kirki musulmai bace,gidan da kike zama Na karuwai nai,hmmmm aini na jawowa kaina tunda da yarda Babanmu ya kawoni cirani, Amana tace tayi shuru.

Damace tazowa Alim dan haka yace ko zaki Bini gidana Na baki aikin kular min da Aabid?matarkafa?cewar Amana,ta Dade da rasuwa,eyya Allah ji kanta, ameen cewar Alim,jeki gobe zan turo driver ya daukeki kiyi shiri.OK tnx Allah kaimu.

Nan ta wuce shima ya bar unguwar cike da mamaki.

Amana tana komawa dakinta tsalle, rawa,sannan tayi nafeela ta godewa Allah cike da murna ta fice kudin da Alim ya bata ta je a Daren ta biya bashin da ake binta,

Bayan ta dawo gida Dan Uzuri tayiwa bayani sannan ta bashi kyautar dubu goma sai murna

yakeyi.

Washe gari da wuri Amana tayi shirin komai iya kayan sawa Dana kwalliya ta dauka kawai ta zuba a wata trolley da Manager ya siya mata kafin suyi fada,kayan girki etc kuwa duk ta bawa Dan Uzuri su.

Har kayan sawa ta bayar da wasu iya sababbi ta eba,har boutique taje ta kara siyo inner wears da wasu kayan ta shirya komai irin zata koma gidan yan gayu masu kudi.

Yau Abincin da Amana taci ma me tsada ne,tun 3pm take jiran azo a dauketa amma shuru har tayi la'asar shuru,sai wurin 5:30pm sannan wani driver da motarsa daya me kyan gaske yazo Duk Wanda Amana ta sani dake unguwar sai da tayi musu sallama,da ance unguwa zaki canja da zama? Sai ta yatsine fuska tana yanga sannan tace wlh kuwa Na gaji da zama a nan unguwar tayi min kauye da yawa,Na samu babban aiki a company, haka Amana ta dinga sambada karya kala kala ita dole big girl kar a rainata.

Dan Uzuri har bakin mota ya raka Amana yana hawayen karya,yana to 'yata ga number ta a dinga tunawa da mu,ki tsare mutuncinki kamar yanda Na sanki da kamila,nutsatsiya,a yafemana Amana yar albarka ya karafashewa da kukan maula, driver kuwa Jan motar yayi ya dauki hanyar Gidan Alim,Amana kamar anyi mata bushara da gidan Aljanna saboda murna.
A lagos dinma wata tsantsararriyar GRA suka shiga wacce kaf lagos ba kamarta a kyau sai ka cika me Naira za ka Gina gida cikinta, yawanci turawa ne da sauran jar fata suke zama a cikinta,saboda komai nata tsarin turai ne,gidan da ya fi kowanne kyau,girma da tsaruwa suka nufa,wani gate katon gaske suka nufa wani remote driver ya matsa sai ga gate yayi sama ya dage kansa,abin fa ya bawa Amana mamaki da alajabi tunda take rayuwa bata taba sanin wannan unguwar ba,da badan ita bata da tsoro ba to da tuni ta fara kuka za a yankata,

Cikin harabar gidan kuwa ma'aikata da masu tsaro birjik,wasu sun hau tsani suna goge glasses Na windows,wasu Na bayin flowers wasu kuwa motoci suke gogewa dukkansu sanye da Uniform dark blue wando da riga fara,motoci ne birjik gasu nan sai ka rasa wacce zaka zaba,
Wani new design Na sweeming pool kamar kogi haka yake yabi ta wani lungu ya mike sosai ruwan garai garai blue shar dashi,

Driver ne yace fito hajia,Jakarta ya ja har ciki suka shiga,kalle kalle kawai Amana keyi,kofar ma wasu numbers akayi dialing,sanyi da kamshi ya bigeta,ga wasu kujeru a palon ko a film bata taba ganinsu ba,
Wata TV a jikin bango kusan Rabin bango,sai wasu manyan flowers suna walwal da haske tiririn kamshi Na fita daga jikinsu,sai wani center table Na glass,wanda shima matsa wani abu akeyi a jiki yana juyawa a hankaki,
Center carpet kuwa dake palon idan ka taka sai ka zata nutsewa zaiyi dakai cikin kasa,tana nan zaune tana baza ido wata dattijuwa ta kawo mata abinci saida ta cika gabanta da kayan ci da sha,

Amana da maza ta saba bata Hulda da mata  hannu ta dagawa dattijuwar nan tace ai sai Iya Allah dai ya saka,kallo dattijuwa tabi Amana dashi tunda ga shigar Amana matar a ranta tace wai wa kuma Alhaji ya kwaso mana me kama da maza haka,
A mazan ma yan jagaliya,wani matsiyacin kallon matar tayiwa Amana tare da tabe baki taja tsaki tayi gaba,Amana wacce zuciyarta ke tafasa game da matar nan taso daukan mataki sai kawai ta shareta tare da Dora hannunta a kahon zuciyarta ta danne tana lallashin kanta tare da cewar sorry Amana calm Down be patients a fili takeyin maganar,Amana duk kayan dake jikinta ganinsu takeyi masu tsada Na yan gayu amma tana shigowa gidan Alim sai ta raina kanta gaba daya.

Top din data Dora saman rigarta ta cire ta Dora saman kujera ta gyara zamanta a kasa kan tiles ita Amana bata son zama ko kwanciya a kan laushi kujera ko bed
Shi yasa ta baje a kasa tare da jawo tiren abinci ta fara ci ba tsayawa hannu biyu ta jefar da cokular a kasa tasa hannu dayan hannun tana yagar kaza daya kuma ta dauki Apple ta balla,ta dauki kankakana,ta gutsiri waina ta dangwali miya,ta yagi kaza ta kora lemo ko ruwa ta ebo fried rice ta watsa a bakinta.

A fili cikin santi tace banza ta fadi Allah sakawa me gidan nan da Aljanna,wuyanta ta Sosa tace me bamu Allah ka bashi,Wanda bazai bamu ba Allah Bamu tare
Sai da taci tayi bamkam kadan ta rage,Karambanin Amana inda taga matar ta shiga nan ta mike ta fara lallabawa zata ga mene a ciki,handle din kofar ta murda a hankali sai ta ganta a wani daki ya gaji da haduwa,wata kofar ta bude ta cikin dakin sai ta ganta a wata doguwar Palo ya gaji da haduwa yasha kayan alatu,kara mikewa tayi sai taga wata kofar
Budewa tayi sai kawai ta ganta a wani makeken kitchen,hade da store,kofar baya kuma ta kitchen zaka fito compound,

Komawa tayi ta kara shiga kitchen nan fa ta kwashi kallo,fridge ta bude tare da dauko wata fura bowl guda dan karami tayi sanyi,a tsaye ta shanye furar tas ta ajiye bowl din ta dawo palon da take,
Wani cycle steps ta gani daga palon yayi sama,ga wata kofa opposite din wacce tabi dazu,nan ma kara budewa tayi bed room ne da toilet ciki,ta kara bude wata kofar sai ta kara ganinta a compound amma tana hango wasu part guda biyu a gidan da har can taje taga Ashe daya part din Na yan aiki mazane daya kuma part din Na baki ne da mata yan aiki,

Baki ta tabe tare da cewar ni dai bazan zauna a bangaren can ba wannan part Din da Alama shine Na Alim dan haka a nan zan zauna yafi haduwa kajifa Amana,har magrib tayi tana palon,cycle steps din nan ta fara takawa har ta haura sama,
Wow......nan Amana taga aljannar duniya kiri kiri,wakeken Palo ne yasha kujeru Na garari,ga dinning can gefe,wata tafkekiyar plasma TV,da wasu manyan speakers,flowers manya, sai tafkeken hoton Alim a manne,
Jikin bangon kansa abin kallon me,komai Na saman fari kal ne,Na kasan kuma peach color,yan aiki kuwa light brown ne nasu,
Amana fa ta gama rudewa da kallon haduwar gidan,wani kofa ta gani a cikin Palon guda

biyu,daya ta nufa ta bude a hankali,wani tangamemen bed ne da sip zureriya,sai madubi,har bedsheet komai fari kal neat,

Ko ina gidan kamshin dadi da sanyin ac, daya room din ta bude subhannallah ta firta a fili komai fari shima yafi ko ina kyau da tsaruwa, komai Na dabanne,
Alim ta hango zaune kan sallaya yana Sallah, Aabid Na jikin gado a zaune yana game.

Asmabaffa
✳CIRANIN AMANA✳

40-45

By
AsmaBaffa

Murmushi Amana ta saki kana ta kutsa kai cikin dakin da sallama, a gigice Aabid ya waigo tare da kwala ihu ya rugo a guje wajen Amana tare da daka tsalle ya daneta yana oyoyo new Antyna I miss u,
Dariya Amana ta saki tare da kankame Aabid suna ta murna tana shafa masa kai,my sweet boy I really miss u,yau tare zamu kwana,za muyi wasanmu cewar Amana,shi kuwa Aabid Jan Amana yayi har Bed din Alim yana nuna mata game dinsa,
Amana kuwa ta manta da wani Alim dake zaune kan sallaya yana Azkhar,kan gadon ta haura tare da Aabid suka fara wasa ba ji ba gani sai dariya sukeyi,kafin kace me sunyi waja waja da bed din Alim,pillows duk a kasa rabin bedsheet dinma yana kasa,

Alim kuwa ba shiri ya daina azkhar tsananin mamakin me suffar maza ya rufeshi,idan banda rashin tarbiya taya zata shigo musu gida har bed room ta hau kan bed ko gaisuwa babu ba komai,in hakane ai tafi Aabid ma rashin tarbiya,ina bazai iya zama da wannan ba,

Rashin tarbiyarta yayi yawa da kuruciya da hauka,ran Alim yayi matukar baci kan abinda Amana tayi yanzu,wata razananniyar tsawa ya daka musu,wanda suka gigice gaba dayansu,musamman Aabid nan take ya fashe da kuka saboda ya tsorata sosai,
Cikin tsananin fushi Alim yace ke baki da hankali?baki da tarbiya?dabbar inace ke?dakikiya jahila wacce bata san me takeyi ba,jakace ke?wa ya baki damar shigowa har part dina,kuma bedroom har bed dina,zaki shafa min cuta a bedsheet,dakikiya dan Na daukeki aiki ba dama Na baki da zaki zo ki min halin mahaukata ba,
Da karfi yace get out now,Amana wacce mamaki da bakin ciki suka taru suka cunkushewa a zuciya,idonta ya kada yayi jajir tabbas yau da badan Alim bane Wanda Allah ya sa mata tsoronsa,kunyarsa da kwarjinin da yake mata to da wani ne yau sai dai a dauki gawarta ko

tasa,amma Alim ne tsoronsa takeji amma duk da haka Amana sakkowa tayi daga bed din tana kumbura tare da cijewa,tace hey Baabaa control mana ya kake yawa,hannuna tasa biyu a aljihu tana tafiyar gadara,wannan ai yawa ne master eh idan dan Na hau Bed dinkane ai sai kace na sauka,ya zaka dinga zagina,

Bed din ta nuna masa idan akan wannan bed din ne easy master ni laushi bai dameni ba ko a kujera bana zama bare bed a dalilin danka Na hau,amma ka sani bed dasu kujeru basa birgeni,kaci sa a Kaine ka zageni haka,cije lips tayi jajir dashi gwanin sha'awa tace a kiyaye master tayi gaba abinta ta dawo palon kasa Wanda aka ajiyeta tun farko.

Alim kuwa mamaki ya gama kamashi yayi mutuwar tsaye,Aabid kuwa kuka ya sa an yiwa new Anty fada,kukan ne ya dami Alim,ba shiri ya figi hannun Aabid ya sauko dashi palon kasa wajen Amana,Amana ta bararraje tayi mala mala a kan tiles tana tunanin duniya,kawai tuna irin zagin da Alim ya mata takeyi,
Idonta ya tara kwalla du duniya babu Wanda ya taba zaginta haka sai me kyau,sabo da bakin ciki kawai kuka Amana ta fara babu damar ramawa.

Yana zuwa da Aabid ya ganta haka kallo daya yayi mata ya dauke kai Aabid ya jefa a kan cikinta,a firgice ta mike ba tare da tace komai ba tsaki taji ya ja tare da ficewa daga gidan gaba daya tare da escort dinsa.

Sai lokacin Amana ta sauke ajiyar zuciya tare da saurin kallon Aabid tace kai yaro Daddynka masifaffe ne wlh,idan Na gaji guduwa zanyi,Aabid kuwa dariya yayi kamar me hankali yace Anty me kirkine Daddyna,zai daina fushin fa.

Suna zaune suna kallon cartoon wannan matar ta dazu ta dawo tana watsawa Amana kallon Banza tace taso ki dauko jakarki Na kaiki dakinki,Amana bata ce komai ba ta dauki Jakarta hannunta rike Dana Aabid har part din yan aiki mata aka kaita,mata birjik kowacce da uniform dark blue skert da Riga me cola da dogon hannu fara kal,sai gyale dan siriri fari.
Ko wacce bin Amana take da kallo,sun ganta kyakyawar budurwa ajin farko,ga shigar niggogi tayi abin dariya,ko ina matan dariya sukeyi suna gulmarta,
Bata kulasu ba amma sun ga dan gidan Oga Alim a hannunta,wannan ya nuna me renon dansa ya dauko,

Tunda suka ga haka sai suka tsani Amana suna jin haushinta tare da yi mata hassada tazo ta fisu fada wajen me me gidan gashi ita CE me renon dansa,sunga irin matan daya dauko a baya sun sami kudi da fada a part dinsa ma suke zama amma kwana kadan ake korarsu da wannan suka kwantar da hankalinsu cewar Amana ma korarta za ayi kwanan nan zasu ji abin tsiyarta,

Ko wacce da abinda take fadi kan Amana,har aka kaita wani daki lafiyayye,dan gado karami sai sip karama da madubi da toilet dinta ba sharing, kamar dakin dai yan mata,komai yaji,kayanta ta ajiye sannan tayi wanka sukayi sallah tare da Aabid, sannan tayi masa wanka tare da shafa masa mai sai kamshi sukeyi towel daure a kugunsa,suna ta hirarsu tana koya

masa karatu har 9:30 Na dare sannan Alim ya dawo,ya duba ko ina baiga Aabid da Amana ba,da sauri ya kira wannan dattijuwar shugabar ma'aikata mata na gidan wato Saude,

Tana zuwa Alim yace Aabid da wannan yarinyar fa?soshe soshe Saude ta kama sannan tace Na kaita part din yan aiki suna tare da shi a can,harara Alim ya watsawa Saude yace ni nace ki kaita wani waje har yarona za akai wajen yan aiki?how dear u ko kin taba ganin me kula da Aabid a part din masu aiki maza ki kawo min su nan,

Da sauri Saude tace ayi hakuri Ahaji hakan baza ta faru ba insha'allah,jiki Na bari cike da jin haushin Amana ta fada dakin bako sallama,to uwar iya kizo inji Alhaji yana part dinsa ki dauki kayanki da Aabid can zaki zauna,munafuka saura ayi dan hali muna nan muna zuba ido kwanan nan za a koreki,kar kice zaki mike kafa matsiyaciya.

Amana ta dau Aniyar cin uban su saude sai nan da yan kwanaki,
Aabid ta nade cikin towel sosai fuskarsa kadai ake gani,goyashi tayi ta kinkimi akwatinta ta tafi part din Alim zuciyarta cike da tsoro,
Ta rasa dalilin da yasa take jin tsoron Alim,a palon kasa ta sameshi yana kallon News,sallama dauke a bakinta ta shiga,taga bakinsa ya motsa amma Sam bata ji muryarsa ba.
Aabid ta sauke cikin towel yayi fresh dashi,ba tare da Alim yayi magana ba ya mika mata uniform dinta,karba tayi tana budawa taga skert, a ranta tace yaufa akeyinta,a fili kuwa cike da tsoro tace master....master ban iya sa skert ba pls ka bani uniform me wando,
Ko kallon inda take baiyi ba kuma baice komai ba,shuru Amana tayi  can tace to Master a bani kayan Aabid zan sa masa,sannan ka nuna min dakina zan je Na kwanta.
Sai da ya dauki 15mnt sannan ya mike yace biyoni ki karbi kayansa,a hankali ta bishi har bedroom dinsa ya nuna mata Sip wani part shake da kayan Aabid,akwati ta cika guda da kayan sawar Aabid har uniform din schl dinsa sanannan Alim ya gwada mata address din dakinta,godiya sannan ta sauka kasa dakin da ta fara shiga da farko me kofa biyu,daya kofar wacce zata kaita kitchen,bedroom din ya gaji da haduwa kamar Na Amarya,
Aabid ta shirya cikin kayan bacci itama tasa nata ta sukayi Addua suka kwanta tare,Aabid ya makalkaleta ya rungumeta sai kamshi sukeyi bacci me dadi ya kwashesu.

Washe gari da asubar fari Amana ta tashi Aabid sukayi sallah abinda Aabid bai taba yi ba sallar Asuba amma yau Amana ta sa yayi har azkhar ta fara koya masa,ita Amana fa yanzu bata da burin da ya wuce taga yaro me tarbiya,tana sha'awan hakan saboda gidansu kaf babu me tarbiya,shi yasa ma ta ke son koyawa yaro tarbiya duk da cewa ita bata da ita,ta sani amma tana so ta koyawa wani,shi yasa take koyawa Alim tofa kaji su Amana.
Wanka da brush tayiwa Alim sannan ta shiryashi cikin uniform din schl dinsa,ta yi wanka itama tare da tsaftace lungu da sako Na jikinta sannan ta fara shiri,uniform din Ma'aikata da Alim ya bata Riga da skert su ta ebo,tana kunkuni tasa pant da wani tight iya gwiwa,sannan tasa skert din,Amana kwai diri da sura,kamar an gwada ta skert din das a jikinta,sannan tasa rigar,gyalenta ba fari Alim ya bata ba kalar skert ne dark blue,Amana gaba daya ji take a takure take ta dabaibaye,ita da wando ta saba,
Gyalen maimakon ta yafa sai ta daura kawai a kanta ta gyaran room din tas,sannan ta fesa

turarenta ta fesawa Aabid ma,7am ta riko hannun Aabid suka haura saman Alim,

Aabid da gudu ya shige bedroom Alim yana cikin bacci yaji Aabid Na tashinsa Daddy ina kwana Anty ce tace Na dinga Ce maka ina kwana,

Alim a hankali ya mike tare da shafa kan Alim yana morning son har kayi shirin schl,ae Daddy Anty tana jirana zanci abinci ta kaini schl,maza to jeka kace tazo ina nemanta,

Da gudu Aabid ya koma wajen Amana yace Anty Daddy yace kizo,gabanta ne yayi mugun faduwa kamar kwai ya fashe mata a ciki haka ta shiga dakin tana tafiya bata saba da sa skert ba,kawai garin tafiyar niggoginta skert ya hardeta ji kake rim ta fadi a kasan tiles Na dakin Alim,Alim dake kwance nade cikin bargo yana kallonta,ko sannu bai mata ba,haka ta mike tana Sosa kanta,tunda Alim yake bai taba sanin uniform din ma'aikatansa Na da kyau ba sai a jikin Amana,a ransa sai ayyana irin kyanta da kyan diri irin Na Amana amma take cutar kanta kullum abubuwan maza takeyi.

Ko gaisuwa Amana bata yi ba kawai sallama takeyi ita bata saba da gaida mutane ba,shima Alim bai damu ba yace kije kitchen ki hadawa Aabid abinci, kece kullum zaki Na dafa masa abinci,ki kaishi schl ki daukoshi ke da driver,

To kawai Amana ta furta tare da fadawa tunanin family dinta,jibi gata da son karatu, amma su iyayensu Sam ba ruwansu da ilimin yaransu,gashi suna son karatu ba dama,a fili kuwa cewa tayi master dan Allah ka sani a makarantar Aabid kaga ni a ss2 Na tsaya sai mu dinga zuwa muna dawowa tare,

Bazan saki ba cewar Alim,kafin ya rufe baki Amana tace master lada zaka samu Ina fada ma taimakon irinmu zai iya jefaka a aljanna,Fice min da gani cewar Alim, baki ta zumbura tare da ficewa tana kunkuni.Alim a ransa yace lallai yarinyar nan bata da kunya karshe,zan gyarata very soon.

Kitchen Amana ta shiga Wanda ke part din Alim,Dattijuwa Saude ta iske a ciki tana shiryawa Alim girki,ko sallama Amana batayi ba ta fara shiryawa Aabid da kanta abinci, minti kadan ta soya chips, da egg,sai tea me kauri,ta damawa Aabid oats da madara.

Saude sai kallon Amana takeyi tana dama haka take da kyau,lallai karfa yarinyar nan ta karbe gidan nan watarana, a fili Saude ta ce insha'allahu hakan ma baza ta faru ba,

Amana tana aikinta sai ji tayi Saude ta bangajeta, a zuciye Amana ta shaki wuyan Saude tare da makata jikin bango sannan ta dinga zagin Saude tare da kara makure Saude ta kwala mata ludayin miya a goshi kafin kace me goshin Saude ya kumbura ya fashe yayi wani sumtum,Amana kuwa ta gama aikinta ta jera komai a tire ta dauka ta haura saman Alim,

Ganin haka yasa Saude tace wlh baza ta kyale Amana ta mata illa ta tafi a banza ba,Saude Ce ta suri mubirgin miya tabi Amana a guje har Saman Alim,tunaninsu Alim bacci yakeyi,turus suka ja birki ganin Alim zaune cikin shiri da Alama fita zaiyi,Saude uwar makirci nan take ta fashe da kuka tace Alhaji kalli yanda wannan yarinyar tayi min duka a kitchen,ta fasa min kai

akan kawai nayi mata nasihar gishirin zaman duniya,yar daba ta fara dukana harda cewa itace ajalina ta kara fashewa da kuka,Alim sarai yasan karyar Saude, Saude kuwa ganin Alim bashi da niyyar magana yasa ta kara bude baki zatayi magana,ji kake fafff Amana ta make mata baki tare da cewa ki kyale mana master dallah haka karki sa masa headache,

Bakin ciki yasa Saude shako wuyan Amana,Amana kuwa me karfin maaza Hannu tasa ta mirdewa Saude hannu, wayyooooo cewar Saude tana ta kara,Amana tace ina daga miki kafa Iya ke babbace kija girmanki kafin Na fara taka ki,wannan abin ba komai nayi miki ba wlh ki kiyayeni ko a garinmu Na kano bani da mutunci ki tambayi tarihina kiji,

Saude da kyar ta kwaci kanta ta arce da gudun tsiya,Alim Na kallonsu a ransa yace naga Alama yarinyar da ta ja da yan fashi ta fansheni ai ta kai karshe a duniyanci.
A fili kuwa tsaki yaja sannan a hankali yace idan Aabid yayi late a schl sai kin karbi punishment,da sauri ta zauna ta bawa Aabid yaci ya koshi itama taci sannan ta daukeshi ta wanke masa baki neat ita kuma ta dauko aswaki zurere Na itace ta sa abakinta sukayiwa Alim sallama driver ya daukesu a rantsatsiyar mota ta kai Aabid schl sannan suka dawo tare da driver,tana ta dirzar bakinta da itacen aswaki,Amana idan tayi brush da asuba to duk cin abinci ko sallah sai tayi aswaki haka tsarinta yake,har palon ta shigo tana aswakinta,
Alim taci karo dashi zai fita ba Wanda ya kula wani ta wuce dakinta ta kuskure bakinta ta kwanta sai bacci.

AsmaBaffa

[6/27, 9:25 PM] +234 808 968 1079: ✳CIRANIN AMANA✳

45-50

By
AsmaBaffa

Amana duk baccin nan da takeyi a kasa ta kwanta,jiya da ta hau bed jikinta damunta yayi saura kadan ta makara a sallar asuba,shi yasa ta sauka kasa,sabo da Aabid ta kwanta a kan bed,

12:30 pm Amana ta farka,sallah kawai tayi ta fada kitchen ta shirya lafiyayyen abinci sannan tayi wanka ta shirya cikin uniform dinta,sai kamshi take zubawa saboda uniform kala biyar Alim ke bawa ma'aikatansa kuma duk shekara sai an sake musu new,a hankali Amana take tafiya saboda skert dinta bata iya tafiya da shi ba mantawa tayi ta taka kayam kayam da sauri,shi yasa a kullum sai ta fadi wajen sau biyu ko uku,

Wucewa tayi wajen driver zuwa dauko Aabid saboda 1:30pm ake tashinsu,Amana yan gayu har takama takeyi tana kamewa a bayan mota,

Tana zuwa schl din har an tashi Aabid da gudu ya shigo motar yana rungume Amana,schl bag dinsa ta karba suka karaso gida,

A palon sama suka iske Alim zaune cikin 3qtr brown da Riga coffee color,sai kamshi yakeyi part din dama yan aiki sun gyarashi neat ko ina kyalli yakeyi, Suna shigowa suka rafkawa Alim sallama tare da cewa Daddy mun dawo cewar Amana kaji shishigi wajen Amana,

Daya room din opposite Na Alim ta kai Aabid ta cire masa uniform tare da jefa kayan a washing machine,ta hau yiwa Aabid wanka,a towel ta nadoshi ta fito dashi Palo yana bayanta ta zaunar dashi a kujera,komawa tayi ta shanya kayan da ta cire masa,sannan ta fito da sauri tana ta fiyarta zata dakkowa Aabid kaya ji kake timmm skert ya harde ta fadi,wannan karan sai da taji ciwo a kafarta,Alim ko a bai ce ba Aabid ne kadai yayi mata sannu,

Abinci ta dauko musu suka ci abinsu a Palo,Alim sai satar kallonsu yakeyi yanda suke wasa da cokula,

Bayan ta shirya Aabid cikin uniform din islamiyya nan kuwa ba nisa a kusa da gidan Alim Islamiyyar take,a kafa ta kai Aabid ta dawo ta gyara wajen da suka bata kana ta wuce room dinta.

Mum Alim zaune a bakin makeken bed dinta da Alama nazari takeyi a ranta tana ta tunanin yanda zata bullowa Abban Alim domin so takeyi tayiwa Alim aure tana jin tsoron karfa Alim ya hadu da wacce yake so,

Bari zanje gidan Alim da kaina next Wk zamuyi magana dashi dole ya karbi zabina haka ta gama sake sakenta sannan ta fita kitchen wajen masu girki tana zunduma musu ashar basu gama girki a kan lokaci ba,

Gidan baki kuwa yana nan inda yake sai abinda ya karu domin lalacewar tayi yawa,yayyen Amana mata guda biyu an sako su daga gidan miji suna nan an hadu ana sheka tsiya,Baba kuwa wato sulemanu Harka ya shagala wajen wata bakuwar bazawara da ta zo wajen matarsa wato umma Babar Amana kenan sun bude harka a boye suke fasikancinsu a gidan liman abokinsa,wani dakinsa da yake harkar bokanci anan suke kwashewa tare da wannan bazawara me suna Salamatu, har yau matan gidan basu gano ba,har Babar Amana bata sani ba sabo da Salamatu ta kware wajen rike sirri,bata wasa da sirri.

5pm Aabid ya dawo daga islamiyya, 8pm Amana ta dauko abincin Aabid ta zo sama part din Alim,Aabid yana can yana wasansa Alim yana cike wasu takaddu Amana tayi sallama ta shigo dauke da tire,ta kalli Alim Wanda ya ke cikin jallabiya fitted fara tas sai sheki yakeyi,yayi kyau matuka kamar aljani cewar Amana,sai kuma tace barka master asha aiki Lfy master,

Ko kallonta Alim baiyi ba yana jinta,TV Amana ta kalla taga ana nuna wasan Barcelona da Chelsea, da sauri ta ajiye abincin gefe,wata uwar sufa tayi a kasan center carpet kamar zata fada cikin TV din,ta tsura ido tana kallo,

Can Messi ya fara yanke yan wasan Chelsea Ya wuce zai kaita raga Amana da karfi ta fara uhum....uhummm...yawwa....yanke shege....sai Messi.....a....goal.......sai tafi ta fara raf raf tana murna kamar an mata bushara da gidan Aljanna,Alim dake aiki cak ya tsaya yana kallon abinda Amana takeyi,

Can kuma Iniester ya dakko ball Amana tace ehem..good idea mikawa Suares mana ai kuwa Iniester kamar yaji ya mikawa Suares,

Amana ta fara ihu cikin siririyar muryarta tana tafi Suares ya buga sai ta daki pose ta dawo ai Amana tace Oh.....God..tayi kararrawa...shege yayi kararrawa, dakiki Suares ya zakayimana haka dabba shashasha dolo,common ka buga ta ka wani makata sama,

Ana ta ball tayi zafi Chelsea suka farke 1-1 Amana tayi lakwas tana zage zage,Alim kuwa tsayawa yayi yana kallon abinda Amana takeyi kamar tv, ana ball fa can wani lokaci Suares yaci daya,minti kadan messi ya karawa Chelsea,sai ga Amana ta mike tsaye tana ta tafi da tsallen murna,kuma gashi an tashi 3-1 Barcelona sun cinye Chelsea.

Juyowa tayi taga Alim ya kafe ta da ido a tunaninta shima ball din yake kallo shi kuwa Alim tunaninsa anya Amana kalau take kuwa.

Abinci ta jawo tare da cewa Aabid my Boy zo maza muci abincinmu sai wasa kakeyi kana gani munci ball ko murna baza ka taya ni ba,shi dai Aabid dariyarsa yayi ya zauna,

Abincin ta bude wata hadaddiyarr jallop din taliya da doya tasha kifi,ga wani lemon dabino da kwakwa da ta hada me sanyi da dadi,ga wani flask dan karami ta hada coffee lafiyayye,wani plate kuma kankana ce da yawa ta yanka da pork ciki,gefe guda kuma wani farfesun kazane sai kamshin dadi,

Kallon Aabid tayi tace boy da wanne zamu fara?Alim tun a ido yasan girkin zaiyi dadi da ace zasu bashi to da ba shakka zai ci,amma yaga Amana kwatakwata bata iya tayi ba a rayuwarta,idan zata ci mene a gaban mutum baza tace gashi ba,kuji Alim din nan da kwadayi,to Amana a gidansu basawa juna tayi haka suka taso,

Yau kamar Amana tasan Alim me yake sakawa a ransa,taga yanda yake kallonsu,kawai sai tace uhm mutum da yake siyo kayan abinci a cinye a dinga hanashi,ban taba yi masa tayi ba,yau dai bari Na gwada ko zaici,

A plate ta zuba girki ruwa ruwa malam yana tiriri da kamshi ta je har gabansa ta ajiye masa gashi ko zaka iya ci,dawowa tayi ta zauna,a ransa yace to iya taliyar zata bani jibi fa abubuwa,bai gama tunani ba yaganta taje kasa ta dawo dauke da wani glass jug da karamin glass cup,lemon kwakwa ne ciki ta ajiye masa,ta ebo farfesu nan ma ta ajiye,kankana ma ta zuba masa tasa ta ajiye masa,sannan suka cin nasu da Aabid,kafin kace me Amana da Aabid sun cinye girkin su tas komai coffee kawai basu sha ba,

Alim yana gani yagansu sun fara exercise suna motsa jiki sai tsalle sukeyi,suna faman sheka dariya kamar tababbu,can Aabid ya kwanta yayi flat Amana ta danne masa kafafu yana tasowa a hankali yana komawa,sosai sukeyin gym dinsu,shi Alim mamaki yakeyi har yaushe Aabid dinsa ya koyi irin abubuwan nan?lallai in hakane yarinyar nan ta cika shedaniya,su kuwa kala kala suke gym dinsu idan ta kwanta tayi Sai ayiwa Aabid ma,wurin 30mnt sunayi sannan suka gama,bayan sun huta suka fara shan coffee dinsu,

Alim kuwa sai abincin Amana yakeci yana lumshe ido bai taba cin abinci me dadin Na Amana ba a duniya,saida ya cinye komai ya shanye komai,

Aikinsa yaci gaba da yi sai da ya kwashe 1hr lokacin Amana harta kwashe komai ta gyara wajen,coffee ta hado masa shima a cup ta ajiye masa sannan ta fara koyawa Aabid assignment suna gamawa suka tafi dakinsu tare da cewa Alim Good night Daddy Amana ita a dole Aabid take koyawa tarbiya.

Satin Amana Biyu da fara aiki a gidan Alim yanzu sun shaku da Aabid sosai,shi kanshi Alim ya saba da hayaniyarsu a part dinsa,dama Alim indai ya dauki me kula da Aabid yafi so su dinga yawan zama a part dinsa ta yanda zai dinga ganin meke faruwa da dan nasa,shi yasa baya hana me kula da Aabid zama a part dinsa,ganin yanda yan aikin Alim ma Kansu yan gayu ne yasa Amana ta kara wayewa,amma harkar jagaliyancinta yana nan,bata ragawa kowa sai Alim,uniform dinma sai taga dama take sawa,kayanta take sawa,bata mutunci da matan masu aiki,amma duk ma'aikatan Alim maza natane mutunci sukeyi sosai,tafi yin muamula dasu,mata kuwa tsakaninta dasu sai harara,har girki take shiryawa me dadi ta rabawa mazan,watarana har kaji take soya wa ta basu kowanne me yawa,
Shi yasa idan ka dauke Alim to Amana ce ta biyu da suke girmamawa,

Amana kuma duk kula mazanta ko yatsa bata bari ko da wasa wani ya ce zai rike mata,ita duk harkar iakancin nan bata sanshi ba,ba ruwanta da shi,dan yanzu ko american film da finanan soyayya bata kaunarsu,tafi son film din yaki ko Na sojoji,tafi so taga film din tashin hankali,bata son taga film ana zaman lafiya,tafiso taga Wanda ake kashe kashe ana harbe harbe ana Sara suka,ana harba bum.to fa ka gama birge Amana

Yau Aabid tazo dauka a bangaren Alim sai taga ana film din yaki american film wani Na sojoji me taron mutane,kawai wuta ake ba daga kafa,
Kawai sai ta samu waje ta zauna,Alim kuwa da Aabid suna bedroom har 11pm tayi har Aabid yayi bacci a wajen Alim ba Susan Amana tana Palo tana kallon ba,11-30pm aka gama film din akasa 2 dinsa,duk Amana tana zaune a wajen,har bacci ya saceta ta bingire a wajen,ta wani baje skeet din uniform din nata ya tartare ya dawo Rabin cinyarta Allah yasa tana da wando tight gajere shima Rabin cinya amma da ansha kallo,
Alim yaji karar tv ya fito zai kashe sai yaga Amana ta baje a kasa tana ta bacci skert ya kara tattarewa ya kusa komawa kugu,dankwali ya kwance gashi yayi yalala a kasa,juyi ta karayi tana Sosa cinyarta tare da sa hannu ta zuge zip din skert dinta ta zareshi ta jefar,Alim ya saki baki yana kallon inda zallar baiwar kyau da kyan sura yake,cikin jikinta har yafi fuskarta fari ma kal

dashi luwai luwai ko gashin jiki bata dasu,

Can ta kara juyowa ta zuge zip din rigarta ta jefar da ita daga ita sai vest da tight dinta,tana ta baccinta,Alim duk ya diririce,maimakon ya kashe tv sai ya kashe ac ya juya dakinsa kamar munafuki ya kwanta yayi lakwas yana ta nazari,tare da tunanin surar Amana,

Da kyar ya samu yayi bacci,Amana kuwa bata farka ba sai da asuba,ganin inda take yasa ta kwashe kayanta ta arce da gudu dakinta tare da banko kofa tana mamakin yaushe ta cire kayanta,

Sallah tayi ta koma baccinta kasancewar yau Saturday ba kai Aabid schl,ba ita ta farka ba sai 11am,da sauri ta fada kitchen ta hadu da Saude ,Saude tace aikin banza dama zuwa nayi Na fada miki Alhaji ya canja min wajen aiki ya mai dani bangaren gyaran swimming pool yace daga yau ke zaki dinga yi masa abinci,munafuka abinda kike so dama kenan,an manne masa ana tsafi mayya.

Tana gama fadi ta sheka da gudu ta bar kitchen din domin tasan Amana ba mutunci gareta ba,ita Saude dadi taji yanzu ta huta da girke girke,

Amana kuwa ko ajikinta tana hada breakfast ta hada harda Alim,sannan tayi wanka,tasa uniform dinta yasha guga sai kamshi takeyi,har part din ta shirya abinci wannan lokacin sabo da Alim ta shirya masu a dining table.

Tunawa tayi da Aabid ko wanka ba tayi masa ba.dakin Alim ta kwankwasa shuru,kofar ta tura a hankali ta shiga ciki,ba kowa a room din karar ruwa taji alama wanka akeyi,kallonta ta mayar kofar toilet a bude taga kofar tare da hango Alim daure da towel iya kugu yana yiwa Aabid wanka,

Gyaran murya tayi daga can nesa tace Daddyn Aabid zanyiwa Aabid wanka,da sauri Alim ya juyo tare da zubawa Amana ido ba tare da yayi magana ba ya yafitota da hannu wai tazo,ai kuwa da sauri ta shiga kamar bazai yi magana ba sai kuma yace gashi nan Na gama masa wankan kiyi sauran aikinki,kallon Aabid tayi taga kunnensa duk kumfa,dariya ta kyalkyale dashi tare da cewa sorry Baabaaa haka akeyin wankan?kai haka kayiwa kanka,pls ka dinga karfafa jikinka kana koyon abin duniya

Komai ka wani langwabe baka iya ba,harara Alim ya watsa mata tare da ficewa daga toilet din,

Yaga alama yarinyar zata rainashi,bayan ta Shirya Aabid dinning suka fito Alim yaja sit ya zauna,Aabid ma haka serving dinsu tayi komai sannan ta kwashi nata ta koma wajen tv kasa ta zauna tare da kamo sport Chanel tana kallon wrestling.

Alim kuwa ya mai da kai sai shan kunun gyada yakeyi,ga wasu girki da ta hada wajen kala 4 bai ma San sunansu ba, dadi kawai yake kwasa,

5pm Amana ta dau wanka cikin kalar kayanta masu kama da Na wizzy ta fito,da yake Amana me kyauce shigar kyau take mata,a palon kasa ta hanyar kitchen wajen sweeming pool ta iske Alim yana hutawa,yana karanta news paper ga lemo yana korawa,

Tana zuwa tace Daddyn my boy?shuru ba amsa,Master kana yawa a kasar nan,key din mota

za a bani pls muje yawo da My Boy,Alim sai yanzu ya tuna Amana ta iya tuka mota,ba tare da yayi magana ba ya cilla mata key abin mamaki yaga ta cafe kamar namiji,tace nagode saura ka bamu kudi,ice cream zamu sha da my Boy,
Baice kala ba ya ebo kudu a aljihu bai San adadinsu ba ya mika mata,tace sai master Allah dai ya saka, tayi waje abinta ta dauki Aabid sannan ta dauki motar da ya bata key wata arniyar mota,ta bata wuta tare da fisgar motar irin Na yan tasha ta kotseta tayi gaba,yan aikin gidan sai kallonta sukeyi da mamaki,matan kuwa kamar su kashe Kansu da alama Amana ta samu fada har motar oga ta fara hawa.

Godiya me tarin yawa gareku fans dina.

AsmaBaffa
[6/27, 9:25 PM] +234 808 968 1079: ✳CIRANIN AMANA✳

50-55

By
AsmaBaffa

Wurin wani hadadden park Amana ta kai Aabid wuraren wasan  yara,sosai Aabid yaji dadi sai murna yakeyi tare da zubawa Anty Amana surutu, hadadden resturant ta kaisu sukayi ciye ciyensu,ko ina Amana ta gifta sai an kalli motar,
Ga wani hadadden tuki da takeyi,shopping mall ta shiga Aabid ta kwasarwa kayan zaki,da wasu kayan sport,schl bag new design,dasu canvas da tarkacen dai makaranta,wasu panties Na maza 3qtrs da riguna duk ta siyawa Aabid, Wasu singlet ta gani na maza latest masu tsadar gaske da boxers,Kudin ta ebo dungurugun ta siyawa Alim boxers guda biyar singlet biyar,ita kuwa kayan make up ta siya da turaruka masu saukin kudi,

Sai takalmi guda biyu da ta siya,da wasu sabuwar pcap guda biyu, ice cream ta jidar musu sannan ta je can wurin da Alim ke siyo nama,wato wajen manager inda ta taba yin aiki,sai mamaki sukeyi yanda suka ga Amana ta kara gogewa ta kara haske da kiba,ga wata shegiyar mota da tazo da ita,sun zata Amana ce tayi kudi,nama ta siya ta wuce gida,8pm suka shigo

gidan,ko kayan basu ebo ba ta ja Aabid room dinta sallah sukayi da wanka suka canja kaya marasa nauyi,sannan ta riko hannun Aabid suka kwaso kayan gaba daya har part din Alim,lokacin 8:30pm suka sami Alim a Palo yana zaman jiransu da tunanin ina suka tafi haka tun 5pm,

Ganinsu yayi da kaya niki Niki,a gabansa suka ajiye komai,a hankali yace dama kun Dade da dawowa?Aabid yace Daddy wanka mukayi da sallah,

Kayan Amana ta fara budewa ta nunawa Alim kayan Aabid gaskiya shi kanshi sun birgeshi ta iya zaben kaya,jawo wata ledar tayi ta nuna masa nata,sai yayi mamaki nata ko kayan make up din ma ba masu tsada bane,ba wani abu special da ta siyawa kanta,daya ledar kuwa mika wa Alim tayi Master kalli naka,Alim yaso gwasaleta amma yayi tunanin hakan ba dadi ayi ma abin kirki kaki yabawa,karba yayi ya duba,komai size dinsa kuma ta siyi masu tsada,
Gasu best Color nasa komai white,

Thnx ya furta a hankali,ledarta ya kalla yace amma wannan shirme kika kwasowa kanki kika dawo,next time ki kiyaye in ba haka ba baza ki kara zuwa ba,ok master cewar Amana.
Alim yace aransa jibeta kamar ta kirki yanzu kaji ana dambe da ita,kayan zakinsu ta diba tace Aabid baka shan wannan yau sai watarana watarana,idan ana shan zaki hakora mutuwa sukeyi su fara ciwo,mata iyaye a kiyaye za kuga yanzu yaro zaije schl sai a sa masa lemon kwali da biscuit a jaka kayan break,ba kudi bane,ba birgewa bace,ba kuma gata da tarbiya bace,saboda illa zai masa hakoransa su mutu da wuri,ko ya fara ciwon hakori tun yana yaro,gwara ki bashi ashirin ya siyi aya,ko taura,tsamiyar biri etc yanda akeyi da,ko ki dafa musu abinci me kyau yafi wannan kayan zakin.a kiyaye pls.

Kwashe kayan tayi ta boye icecream biyu da nama da drinks kawai ta bari,kitchen ta koma ta dauko su plate etc ta bude ta ebi nata Dana Aabid ta zubawa Alim shima

Alim a ransa yace to yau abincinmu kenan,ci yayi sosai yana kora drink yasha icecream kadan ya mika musu abinsu yana kallonsu suna ta cin nasu suma.

News Alim ke ta kalla Amana ta matsu a canja tashar ball amma shuru gajiya tayi tacewa Aabid tashi muje muyi baccinmu,ko kallonsu Alim baiyi ba har suka sauka suka bacewa ganinsa,
Washe gari Sunday da 9pm Alim ya kira Amana ya mika mata schl Uniform irin Na makarantar su Aabid green and white,ba hijab sai hula da mata ke sawa,Riga da skert,skert din irin da kadan ya wuce gwiwa abinka da lagos,
Kayan har kala biyar,sandal dasu canvas,schl bags,littafai komai ya mika mata,yace kuma Ss1 suka baki ba ss2 ba,
Murna wajen Amana ba a magana hakan ma Na gode master,Allah ya biya bukatunka ya kara buda maka,
Gobe sai kiyi shiri idan kinje office din pc zakije,wani card ya mika mata yace ki bashi wannan cewar Alim,karba Amana tayi tana ta murna.

Washe gari kuwa da sassafe ta shirya ta shirya Aabid cikin uniform ba karamin kyau Amana tayi ba, already ta hada breakfast,cin nasu sukayi suka barwa Alim nasa, brush suka karayi suka gyara sannan suka je wajen Alim dake zaune a palonsa,

Gaisar dashi sukayi sai kallon Amana yakeyi yanda ta hade a uniform,key din mota ya mika mata gashi kin iya driving ai no need driver ya tukaku,ki kiyaye ban son ayi tukin ganganci da Aabid dina.

Murmushi kawai Amana tayi ta rike hannun Aabid suka fito compound,ba motar jiya da ta tuka bace,wata motarce har tafi ta jiya kyau da tsada,

Ma'aikata kamar idonsu zai fado ganin Amana a uniform wato matsayinta har oga ya sata a schl,kuma a schl dinma me tsadar gaske irin ta dansa,ga motoci ko wacce hawa takeyi,mazan gaba daya murna suke taya Amana,matan kuwa bakin ciki kamar su kasheta haka sukaji,

Amana tana kallonsu suna shiga motar tayi wani tuki Na yan tasha ta fice daga gidan,Alim yana kallonta ta window,bai San sanda ya saki murmushi ba,tare da furta yarinyar nan bata ji ko Kadan

Tunda Amana ta cinna hancin motar schl ake ta faman kallonsu,an zata yar gidan wani shegen me kudice tazo da kaninta,kowa driver ke kawo su amma Amana ita ta ke tukin gasu daga Amana har Aabid masu kyau ne,kalar naira da Hutu,saida takai Aabid har class sannan ta wuce office din PC ta bashi card, ya kaita har ss1A tafiyar da Amana takeyi cike da gadara da takama tana cin magani an dauka Naira ce ta hudata,basu San Amana tun tana kauye haka take ba.

Kafin kace me duk mazan Ajin sun saba da Amana,matan kuwa ko kallonsu bata yi,break aka kada anje restaurant  Na schl cin abinci,Amana duk yan aji maza da mata sai da ta raba musu maltina kowa daya daya,nan da nan schl ta dauka wata yar gidan wani kusace Amana

Har class din su Aabid taje ta daukoshi ta bashi abinci da kanta Amana tana mugun kaunar Aabid bata son abinda zai bata masa rai,Aabid kuwa yanzu ya daina tsokana da ciwa mutane mutunci ya nutsu sosai,gashi Aabid yafi ma Alim haske ka rantse baturene,shi yasa yake da farin jini.

Amana har malamai take kaiwa drinks kyauta,kwananta 3 da fara schl amma har ta zama popular, kuma ba laifi tana da kokarinta,amma Amana tafi iya mathts duk wani abu Na calculation to Amana ta sanshi ta iya gifted ce,

Matan schl din tsinewa Amana sukeyi bata da mutunci bata kula kowa sai maza,guda dayace yar ajin su Amana wata Rufaida ita kadai ce suke magana da Amana sabo da Rufaida tana son Amana haka kawai,shi yasa ta nacewa Amana tun bata kulata har ta fara kulata.

Shi kanshi Alim dadi yakeji yanda yaga Amana Na kula da Aabid,ga Aabid sai kiba yakeyi yanzu kuma yayi hankali sosai.dan haka Amana ta kara daraja da kima a idonsa,Amana kuwa a schl kullum sai anyi fada da ita a schl,gashi ba a daukan mataki a kanta sabo da ta siye kowa da kyaututtukanta.

Kamar kullum Amana ta fito da mota ita da Aabid zasu je schl ta ware mota tana fella gudu,wata rantsantsiyar mota ta gani ta parker wata kyakyawar dattijuwa ajin farko ta fito daga bayan motar tana yanga da takama tazo zata tsallaka titi tana ganin mota amma sabo da takama irin ta wannan dattijuwa kawai ta hau titi tana tsaida wata mata,Amana ta Riga ta kawo da mota da kyar ta iya take birki amma duk da haka sai da ta bigi dattijuwar nan kadan a kafa,matar ta fadi wanwar,Amana da sauri ta gangare tazo tana yiwa matar sannu tana bata hakuri,matar ta rigada ta rude sosai bata gane wace kawai murya takeji,

Masifa ta fara yiwa Amana dalla matsa dabba yar talakawa matsiyata,sai faman ashar matar nan takeyi Amana Na bata hakuri amma matar nan cewa take wlh iyayenki ma sai sunyi nadamar haihuwar ki,sai Na batar dasu.

Amana haushi taji kawai ta take motar ta suka tafi schl,ta bar matar nata masifa da zage zage,da kyar driver da wannan kawar tata da take kokarin zuwa wajenta suka sata a mota suka kaita asibiti aka dan duba lfyrta suka dawo gida,matar kawai tunani takeyi a ina zata ga yarin yar nan da ta kadeta taci ubanta har iyayenta,gashi ko ta ganta baza ta gane ta ba tana rude bata ga fuskar yarinyar ba,amma zata gane muryar,motar ta tuna sai taga kamar tasan motar,kamar motar Alim danta,amma me zai kawo wata ta hau kai ba ta Alim bace amma taci alwashin nemo Amana dan ubanta,wannan dattijuwa ba kowa bace face Mum din Alim.

Amana kuwa mamakin irin masifar matar takeyi,bayan sun tashi daga schl saloon ta wuce aka gyara mata gashinta wannan karan kasan gashin tasa aka canjawa kala y koma yellow fari fari,sama kuma baki,kaji turawa an waye a lagos.

Aabid ma anma masa wani kala ya kalli sama ka rantse bature ne,dama Aabid gashin turawa gareshi yellow ba black ba,

Amana har islamiyya Saturday Sunday tana zuwa yanzu,Alim tunda yaga gyaran gashin Amana yake mamakinta kamar wata baturiya wayewar tayi yawa,na Aabid kuwa ai kasa magana ma yayi ya rabu dasu kawai,.

Suna zaune a palon kasa, Baban Amana ya kirata a waya,dagawa tayi da sauri tare da cewa Allah bar mana me gida sai Baba,ya kowa da kowa,alhmdlh cewar Baban Amana sannan yaci gaba bakya nemanmu ko, haba Baba ka daina irin wannan kasan ina ji dai kai fa cewar Amana, Baba a gaishe da Umma kace gobe zan kirata pls,Baba hope dai ka daina abin nan da kakeyi ?Allah Baba shi yasa naki zuwa Na ganku ga kudi ina samu.

Baban Amana yaji Amana tace tayi kudi sai murna ta kamashi bai damu da abinda Amana tace ba kawai ya fara haba yar Amanata yaushe zakizo Na ganki yanzu Allah ya kusa shiryata ai Amanata,zan hadaki da Ummanki,Umman Amana dake gefe taji ance Amana tayi kudi caraf ta kwace tace Amana yata yaushe zan ganki dan Allah kizo mu ganki,ki siyo min doya da manja,ki taho min da garin kwaki dan lagos,ki tahowa da kannenki kwakwar manja,da ashobe Na yarabawa zan dinga zuwa biki,

Baba ne ya kwace wayar daga hannu Umma yana harararta tare da cewa matsa banza kwadayayya,yace Amanata Nima ki siyo min leshi dinkin buba zanyi Na yarabawa maza,ki siyo wa Haladu 3qutr Na maza,ga kannenki su Badariya ko T-shirt ki siyo musu kinji,

Matan gidan da yara duk sun rude kowa yana Anty Amana ki kawo min ayaba da lemo,wasu suce naman kaza,wasu suce yohourt,Badariya yan mata kanwar Amana me ji da kanta da tashen fitsara ita ta fisge wayar daga hannun Baba tace ke Amana ni Apple zaki siyo min kin San ni ba kalar kauye bace,amma Baba yana wani wai ki kawo min T-shirt yo Allah Na tuba T-shirt ko ta su Badaru ai Na sa,kin San Baba dan kauye ne wlh,

Zanci Uwarki Badariya Jakar banza dan Ubanki Babane dan kauyen?mahaifinkine fa Allah ya kamaki shegu marasa tarbiya cewar Amana,Badariya ma ta cikin waya tace Badai ni ba kece shegiya wlh,su iyayen namu da kike tarewa Ubanme suka tsinana ma,komai mu mukewa kanmu,ba makaranta hattana sabulun wanki mu ke siya,sannan kuma muyi musu biyayya,Amana tace ke Iyayenmune fa dole mu duba darajarsu garemu,kuma dole mu bisu ko me sukayi mana,iyaye iyayene wlh amma Badariya kodai kina Jan hayakine?
Tun yaushe kuma Amana ai har wiwi ja nakeyi cewar Badariya,shuru Amana tayi.

Badariya tace ke Amana anfa kama Isa yana police station ya saci akuyar gidan shehu me alewa,Zahrau kuma ta cirewa wani yatsa daya ana ta rigima,Goggo uwar gida ita ta karbi wayar tace Amana ni ayabar da ake soyawa zaki kawo min,Amana tace oh Goggo plantain? Eh yawwa inji goggo.to shike nan sai mun kara magana kitt Amana ta kashe waya tare da dafe kai tana maida numfashi.

Sun dameta da surutu kowa nata shirme,tsaki taja a fili tace gidanmu gidanmu baza su taba canjawa ba,hannu ta daga sama tace ya Rab gamu gareka,
Kyalkyalkyal taji dariyar Alim da Aabid har sun tuntsuro kasa sabo da dariyar kauyancin yan gidan su Amana,juyowa Amana tayi taga yanda Alim yake sheka dariya sosai dimple dinshi sun lotsa yayi mugun kyau,
Sakin baki tayi tana kallonsu,ita ta manta Alim yana wajen gashi wayar a handsfree ta sata,
Tsayawa tayi ta shagala tana ta faman kallon dan bakin Alim da hakoransa yar yar ga dariyar tayi masa mugun kyau,

Saida suka gaji da dariyar suka tsaya Alim yace no wonder kike haka,Ashe a hakan kamar ma kece wayayyya nutsatsiya a gidanku,wlh Na kusa zuwa kano kece driver komai za a siya musu kar ki damu,nan ya kara sakin dariya,

Amana takaici ya kamata za a raina mata dangi da iyaye a masifance tace don't go there pls dan billahillazi ka zagi iyayena sai nayi butar malam da kai,kai akan iyayena zan iya karyaka,ka San me zaka fada min bana daukan wulakanci gwara ka koreni,dan kana da kudi muma haka Allah yaso ganinmu ehe,
Aabid ne ya matso kusa da ita zai riketa da sauri ta hankadashi baya ya fadi tim,ta zare masa ido kai ni zaka yiwa dariya a haife Na haifeka takalminta ta cire ta Zane duwawun Aabid dashi,

Sai kuka yakeyi yana bata hakuri,Alim yana gefe yana kallonsu yace kinji kunya your Boy kike duka yau,da sauri ta jefar da takalmin ta rungume Aabid tana lallashi,Mum Alim wacce ke labe

jikin kofa tana kallon komai akan idonta,banko kofar dakin tayi da karfin gaske.

AsmaBaffa
[6/27, 9:25 PM] +234 808 968 1079: ✳CIRANIN AMANA✳

55-60

By
AsmaBaffa

Mum Alim tana muzurai zata fara masifa tare da bin Amana da wani mugun kallon tsana,amma shigar Amana ta bata mamaki,domin Amana bata sa uniform din yan aikin Alim ba,kayan sawarta ne Na swagg a jikinta,Wani tunanin mugunta ne ya darsu a zuciyar Mum Alim nan take ta saki fuska da fara'a tace Alim wannan yarinyar fa? Alim yace Mum me kula da Aabid ce,ya ban ganta da uniform ba? Yanzu ta cire Mum,Aabid kuma me yayi mata take dukansa?tsokanarta yayi Mum,hmm ba a haka yarinya me raino da hakuri akasanshi,

Alim ne ya kyaftawa Amana ido wai ta gaisar da Mum,da sauri Amana tace Mum An yini Ify?hmm haka ake gaisar da manya a garinku?Baki da tarbiya ne? Amana tana zumburo baki tace sorry fa Ina kwana,

Mum ce tace hmm yanzu ai yamma ce,to ina yini?Ify cewar Mum tare da tabe baki,

Amana kuwa sarai ta gane masifaffiyar matar da ta kade ce a titi,itama Mum ta gane Amanace ta kade ta,shi yasa ta kulla mugunta a ranta,

A fili tace ke yarinya ya sunanki,sunana Amana,wanne gari? Kano state a garin wudil.murmushi Mum tayi tace good tare da cewa Alim dama Aabid nazo gani ni Na tafi gida,

Haba Mum ki zauna mana,murmushin mugunta tayi tace abinda nazo wajenka zan nemo Na samu cikin sauki shiken nan bye ta yi waje cike da shirya mugunta,

Mum murna take taga yarinyar da tafi tsana a duniya,ga laifin ta dukar mata jikanta,gata a gidan danta tana cin arzikinsa,lallai Amana zata ci Ubanta.

Ita kuwa Amana bata kawo komai ba a ranta,Hannun Aabid ta kama take ta faman lallashinsa tare da cewa master pls ka tayani lallashi,tabe baki Alim yayi yace kunfi kusa Amana keda ur Boy.

Bacci Aabid yayi a jikin Amana,kallon Alim tayi dake latsa waya tare da cewa Daddyn Alim wannan dama Mum dinka ce? Itace wacce nake fada maka Na kusa bigeta a mota tana ta fada,Kinyi sa'a da ta iya kyaleki haka ki godewa Allah,shuru Amana tayi tana tunani.bayan sati daya Alim ya samu kiran gaggawa daga wajen Mum, 5pm ya dawo gida cikin tsananin kunci da bacin rai ba a San wacce Magana sukayi da Mum dinsa ba

Amana suna palonsa ita da Aabid sunga lallai Alim yana cikin damuwa,shi kanshi Alim so yake ya samu abin nishadi abinda zai sanyaya masa rai,wayar sa ya dauko tare da mikawa Amana wayar take this kira Daddynki kuyi hira da su Ummanki,da sauran yan gidanku,

Amana cike da mamaki ta kalli Alim tace rannan fa munyi waya dasu kuma,Na sani ai ki kirasu kawai kuyi hira ungo karbi cewar Alim,shi Alim so yake yaji shirmen gidan su Amana ya sha dariya ko zai samu saukin zuciyarsa.

Amana kuwa karba tayi amma sai ta kasa amfani da wayar,karba yayi ta karanta masa number Baba yasa tare da dialing,bugu daya Baba ya dauki wayar tare da cewa Alo...Alo ..da sauri Alim ya mikawa Amana wayar ta kara a kunne tare da cewa Hello Baba Amana ce.

Hhhhh Baba ya kyalkyale da dariya tare da cewa 'yata Amanatullah wannan lambar fa ta waye? Kallon Alim tayi ya yayi mata nuni kawai tace ta saurayinta ce ,Baba number Saurayina ce,wata kara Baba ya saki Amanata yanzu a lagos kinyi farin jini kin samu masoyi,Ashe zanga aurenki a duniya,Amanata duk bakin jininki a lagos kika samu miji,murmushi Amana tayi tace Baba sai ma ka ganshi kamar bature,me kudin gaske,yeeeeeeee ahayye yan gidan su Amana suka dauki shewa da guda tuni yan gidan kaf suka yanyame Baba,Umman Amana ce ta fashe da kuka tace Allahu Akabar kabira,yanzu Yar nan duk bakin jininki kinyi saurayi,Ki gaishe mana dashi idan zaki zo ki taho da shi mu ganshi,Goggo ma ta fisge wayar tare da cewa ice ko yana bada kudi me kyauta ne?Amana tace dubu Dari Dari yake rabawa sai yan gida suka dau tafi da ihu,Haladu ne ya matso ya wafce wayar Amana dan ubanki wayar tarho zai siyo min ki fada masa, wlh kika zo babu wayar sai Na karyaki,kaji Haladu kaifa jarabane karma ka dameni cewar Amana,Badariya daga gefe tace kai Amana shegiyar gari ce,yanzu tana can tana Shanawa.

Jamila tace Amana ki kula mazan lagos HIV ce garesu karki bari ya sa miki ita,gwara ta kama Baba,Baba dake gefe samu yayi ya kwadawa Jamila mari tare da fisge wayar ,nan take matan gidan suka fara fada ana zage zagen juna,kafin kace me gidan ya hargitse ana ta cakaki,gajiya Amana tayi ta kashe wayar cike da bacin rai,

Ga kunya ta lullubeta domin Alim yasa wayar a hands free.

Kallonsa Amana tayi taga shi sai dariya da murmushi yakeyi abinsa.tare da fadin why zaki kashewa Baba waya ana hira yaci gaba da murmushinsa.

Kwanaki kadan akayiwa su Amana hutun makaranta Alim yace su shirya zasu je kano wajen danginsa for 1wk zai kai musu Aabid,su. Dameshi da son ganin Aabid,murna wajen Amana ba a magana zata ga danginta,yauce ranar tafiya Alim yace kuma a motocinsa zai tafi bazai bi flight ba,Amana ce me driving Alim da Aabid, escort suna sauran motocin,

Fitowa sukayi Amana cikin shigarta ta yau da kullum,Alim ne ya Ce ina kayan Dana siya miki aka kai dinki gaba daya Riga da skert ne kala 10 harda dogayen riguna readymade wajen 5,takalma da bags,gyale komai dai me tsada akwati guda Alim yayi mata duk wani kayan

tsaraba kuma an jibge a mota basu da matsala

In dai baki canja kaya ba wlh baza ki je ba,ko kunya bakyaji yanda kika zo lagos ki koma haka,

Akwatinta dake mota ta zuge ta dauko wani lace me tsadar gaske milk and brown,cikin gidan ta koma ta shirya sosai ta fito a yan mata,ba karamin kyau tayi ba kamar a saceta,takalmi gyale da jaka duk brown,bata iya daura dankwali ba acuci maza kawai tayi ta yafa siririn gyalen a kanta ta fito cike da takun gadara,wai ai Alim ya kusa suma yanda yaga Amana yar india,ta hadu sosai,shi kuwa wani milk wandon jean ne pencil a jikinsa sai wata T-shirt pupple, takalmi ma milk color yasha kyau,Amana fa an waye sosai key ta karba ta shige mazaunin driver Alim Na gaba ya daura kafa daya kan daya can saman gaban mortar, Aabid a bayan mota,Amana a nutse ta fara sarrafa kan mota sannan suka dauke hanya,tafiya Amana take shararawa ta gaske tun Alim yana tunanin zaiji tace ta gaji amma sai yaji shuru kida kawai takesha tana murza kan mota,Aabid yayi bacci wurin kai Uku,Alim ma sai bacci yakeyi,

Sai da sukayi Rabin tafiya har dare ya kusa yi sannan Amana ta kalli Alim tace Master yunwa mukeji ga my Boy ma sai bacci yakeyi aci abinci ayi sallah, ok kawai Alim yace tare da gwadawa Amana garin da zata tsaya restaurant din,

Abinci da sallah sukayi Amana da escort suka take kan mota har dare yayi har wurin 2am Na dare suka zo Kaduna Alim yace suyi bacci a kd gobe su karasa kano saboda kafafunsa har sun kumbura,Amana tace a'a wlh baza mu tsayaba sai munkai kano,ke engine ce wai bakya gajiya ko namiji ba kowa ne zai iya abinda kike ba,

Ae naji amma ba wani kwana a kd sai munje kano.haka suka dinga sharara gudu 4:50am suka isa kano,wajen ciromawa suka tsaya sukayi sallar asuba Amana harda yin brush a gefen titi,haka tacewa sauran ma duk saida kowa yayi brush har Aabid,Alim ma,sannan suka tsaya zasu dan huta,kafin wani lokaci Masu shayi sun fara yi,Amana har teburin me shayi taje ta zauna aka yi mata hadin kauri da indomie da kwai a wajen taci ta koshi ta shanye tea dinta Allah yasa ma mutane basu fara fitowa ba,haka tayiwa Alim da Aabid take away har mota,su kuma sauran escort sukaje duk suka sha suka ci abinda suke so Alim ya biya kudin,shi kam Alim sabo da yunwa shima cinye nasa yayi,Aabid ma Amana tayi feeding dinsa,Amana harda wanke fuska da sabulu tayi fresh,ta shafa powder da lipglow,Alim ya kalleta tare da tabe baki tare da cewa bafa saurayi zakiyi ba,dama bakin jini gareki,kar muje gidanku wlh kice ni saurayinki ne ba ruwana,

Amana murmushi tayi tace za a gani ai.ni nace kace Na fadawa Baba hakan.

Ci gaba sukayi da ta tafiya a nutse har kano cikin Tudun yola GRA,wani tsantsararren gida suka nufa nan take aka wangale musu gate suka kutsa ciki,matan gidan da sauran wasu mutanen yan uwan Abban Alim,duk suna waje sunzo tarbar Alim da Aabid,abinda ya basu mamaki mace ce driver dinsu,

Basu ce komai ba Amana ta fara budewa ta fito tare da gantsarewa tayi mika tana Hamma da salati,duk an zuba mata ido ganin ta fito ba dankwali gyalen na ta ma a hannunta yake,

Zagawa tayi ta dauko Aabid Alim kuwa daya daga cikin guards shi yazo ya bude masa kofa

sannan ya fito a gajiye,danginsa yan mata da samari kowa rungumeshi yakeyi ana masa sannu da zuwa,haka manyan iyaye ma,sannan suka koma kan Aabid,gaba daya securities din Alim sun kwashi gaisu wajen dangin Alim sannan aka basu part guda masaukinsu da masu basu abinci etc,Amana kuwa duk cikin manya samari da yan mata ba Wanda ta kalla da idon rahma,babu Wanda ta gaisar kawai gefe taja ta tsaya tana binsu da kallo,har suka gama rungume rungumensu,

Daya kanin Abban Alim ne yace Alim wannan fa?

Sai lokacin Alim ya yafito Amana da hannu ta karaso wajen,tunawa tayi yace in sun hadu da manya ta dinga gaisar dasu da wannan dalilin tace barkanku da gida tayi shuru Abinta,Alim yace Kawu wannan me kula da Aabid ce,madalla cewar Kawu,kakar Alim ce ta jawo Amana zo muje wannan ta wajena ce da kyar Amana ta danyi murmushin yake,ita gidansu can wudil take so ta tafi,

Alim ta kalla kurrr tace Daddy gidanmu zanje ni dai,nan take Alim ya watsa mata hararar data firgitata, a hankali yace haka ake gaishe da manya gidanku,zan fasa barinki kije gida wlh in kikara irin wannan,kuma kibi kaka kuje can ki zama me tarbiya kina koyawa Aabid why ke baza kiyi ba.

Haj Sameera kanwar Abban Alim itama tazo daga Nassarawa G.R.A gidan mijinta sabo da tarbar Alim,tare da iyalanta yan mata su 4,sai Alhaji Ishaq shima kanin Abban Alim shi tare suke zama da Babarsu wato kakar Alim da yaransa Maza samari manya su 4 mata 2 yara sune suka taru a gidan.

Shuru Amana tayi tabi Kaka suka tafi sashenta Aabid sai kuka yakeyi shi Anty Amana zai bi.

Kaka sai tsokanar Amana takeyi tun Amana bata saki jiki ba har ta saba da kaka, ita kaka dai haka kawai taji tana son Amana,wanka Amana tayi taci abinci ta haura gadon kaka sai bacci,Alhaji Ishaq sai fada yakewa Alim ya wahalar masa da jika tun daga Lagos har kano a mota, ka tabbata sai dai securities su koma da motocin kai da Aabid kubi flight.

Kowanne cikin Wanda sukazo baccin gajiya suke ta kwasa tun safe har 5 sannan suka tashi sukayi wanka da Sallah,Banda Amana domin hutun sallah takeyi,kuma Ita kadaice batayi bacci ba har sukazo kano,Aabid tuni yar Haj Sameera Ikram tayi masa wanka ta shiryashi,Alim ma ya gwangwaje cikin shiga ta alfarma.sunyi sallar isha an hallara ana jiran kaka da Amana amma shuru Alim sai baza ido yakeyi ina sa ran ganin Amana.

AsmaBaffa

[6/27, 9:25 PM] +234 808 968 1079: ✳CIRANIN AMANA✳

60-65

By
AsmaBaffa

Amana ta fito daga wanka a toilet din Kaka ta gama shafe shafenta sannan ta dauko Riga da wando zata sa abinda harda pcap,Kakace ta karbe kayan tare da cewa haba jikata gidan nan maza ne da yawa samari,bai dace kiyi wannan shigar ba kinji,

Babu kyau,kuma daga yau jikata idan kinga manya ki gaishesu sosai ba irin gaisuwar da kikayi dazu ba kinji,ki rusuna ki gaishesu a ladabce,nan Kaka ta zage ta dinga koyawa Amana abubuwa sosai,

Kuma Amana ta gamsu ta yarda maganar Kaka gaskiyace,ita kuwa Kaka ta tabbatar Amana tana bukatar tarbiya,da alama bata samu kulawar iyaye ba,a hankali Amana tace to Na gode kaka kuma zanyi yanda kikace,ki zama mace ta gaske me aji kinji? nan ma jiki a mace Amana tace to kaka domin tunda take arayuwarta babu Wanda ya taba cewa ta gyara halinta sai kaka,nan taji ta kara kaunar tsohuwar,

To dauko atamfa kisa a kayanki muje cin abinci,ba musu Amana ta dauko wata Riga da skert Na atamfa me kyau da tsada red ta saka ta shafa powder harda jambaki red,ba karamin kyau tayiba kamar yar India ga diri da shape ga fadin hips da tudu sosai,komai cib,

Kaka tace masha'allah,to saura daurin Dan kwali,kaka ban iyaba cewar Amana tare da dakko red gyale ta yana Dan siriri,tasa flat shoe red,suka fito tare da kaka gwanin sha'awa.

Palo suka fito karo Na farko kenan da Amana taji kunyar mutane,kowa ya zubo mata ido,Baren ma Alim da yake kallonta kamar me,karasowa tayi a nutse ta tsuguna har kasa gaban Abba Ishaq da matarsa da Haj Sameera tare da cewa Ina yini Abba,kuna Ify?fuska sake ya amsa mata,haka tayiwa su Sameera ma,mazan samari da suke ta faman binta da kallo tace sannunku Ina yini,suma sun amsa da fara'a,ganin yan matan tayi ai sa'anninta ne koma ta girmesu,ga wani kallo da suke mata Na banza kawai sai ta sharesu ta mike tsaye,daya daga ciki wato Ikram tace mu baza ki gaishe mu ba?

Amana ce ta juyo a fusace tace hey mind ur tongue bana daukan nonsense,ta juya wajen Alim abinta sauran kuwa da mamaki suka bude baki lallai yarinyar nan masifaffiyace daga magana,su kuwa mazan birgesu Amana tayi ma,

Huzaifa dan gidan Abba Ishaq dake wajen yace bakuwace fa maybe ma ta girmeku Ku Baku kulata ba, tazo gidanku sai ita zata gaisheku,Kaka da Abba Ishaq sukace kyaleshu shashashai.

Amana kusa da Alim ta koma ta zauna a hankali tace ina Aabid,A hankali shima yace Aabid yayi fushi da ke,ni baza ki gaisheni ba?

Dariya tayi tace Daddy Kakace ta koya min fa,Kallonta Alim yayi yana jin wani farin ciki da ya rasa Na mene,ga kamshinta da kyan da tayi yana wani fusgarshi,
Alim da Amana hirarsu kawai sukeyi a palon an zuba musu ido kowa da abinda yake sakawa a ransa,

Abinci aka shirya kowa ya hau dining banda Amana da Kaka su basa zama a kujera,suna ci suna hirarsu,Huzaifa ma wajen Amana ya koma ya like musu,sai hira suke sha,Dan danan Amana ta saba da mazan gidan gaba daya banda matan,

Suna gama cin abincin Alim ya cillawa Amana Key din mota muje ki kaini gidan su khaleed Frnd dina ne.cafe key din Amana tayi tace wlh ni bacci nake ji ka nemi wani driver din, tun daga Lagos ko bacci banyi ba har kano kuma kace mu kara fita,

Palon gaba daya aka cika da mamaki mace ta tuko mota tun daga lagos har kano ansha mamaki tare da jinjina mata,Haj Sameera tace ke yan mata ya sunanki ma, sunana Amana, great name,Huzaifa yace lallai sunanki Na daban ne Baby Allah sa ki zama me Amana

Kaka tace ke kyaleshi muje kiyi baccinki,shi kanshi Alim fasa zuwa yayi yaje ya kwanta shi da Aabid,cikin dare Aabid ya dinga tsala ihu shi A kaishi wajen Antynsa,
Daukoshi Alim yayi har part din Kaka ya buga mata kofa ta fito,yace Aabid ke Neman waccen yarinyar,sai kaje ka kai mata tana waccen dakin,nan Kaka ta koma dakinta Alim ya shiga dakin Amana,

Da sauri ya runtse idonsa ganinta sanye da short wando da kadan ya rufe duwawunta,sai wata half vest a jikinta ta tale kafafu tana ta bacci,
da sauri Alim ya daura Aabid a bed din ya fice da sauri tare da rufo dakin.
Da kyar Alim ya iya runtsawa a ranar,washe gari da safe Amana ta hada kayanta Dana kaka ta fito can bayan gidan jikin wani panfo daga ita sai wata doguwar Riga me hannun vest,wankin kayanta dana Kaka take faman yi,

Mutanen gidan sai dadi sukeji tana girmamasu tsohuwa,Aabid yana kusa da ita,Alim yana sama yana kare mata kallo ta window,

Kwanansu Amana uku a kano,Alim yace tashirya zasuje ya kaita gidansu,Ta gama shirinta Na tafiya Garinsu wudil sai murna takeyi,
Motocin Alim gaba daya da escort suka jera zuwa gidan su Amana cikin yan tafiyar harda Huzaifa.

Amana tana ta driving dinta sanye take cikin wani rantsatsen lace Golden Colo tayi matukar kyau,Alim yasha arniyar shadda light blue fitted,Aabid kam English wear ne,Huzaifa ma ya chakare,jerawa sukayi har garin su Amana tun a hanya Alim ya fara sa ido yana dariya kasa kasa,zasu sha kallo yau.
Ana zuwa wata majalisa Amana ta tsaya da motar tare da sauke glass kasa tace hi guys

Baaabaa Baabaa kuna sha'aninku,kallonta sukayi sosai da kyar suka iya ganewa Amana ce,Alim Huzaifa sai kallon ikon Allah sukeyi,ganin gungun samari sun yanyame motar ana ta kawowa Amana gaisuwa,haka Amana ta dinga tsayawa majalisa majalisa suna gaisawa,tace sai Na nutsu Baabaa akwai labari fa.

Har kofar gidansu ta tsaya sauran motocinma suka tsaya,Ko wa kallon irin rubewar da gidan yayi sukeyi,su Baban Amana suna waje sun zata shugaban kasane yazo wucewa,shi kanshi Baba kasa gane Amana Yayi su Alim gaba daya fitowa sukayi daga motar,mutane sun yanyamesu ana kallon turawa sunzo,wasu suce turawane zasuyi Titin kwalta,wasu suce ai makaranta zasu Gina,wasu sunce ruwan tuka tuka za ayi ko pampo,

Amana tace Allah taimaki Baba, Baba  Amana ce fa,ai Baba kamar ya suma, Da karfi yace Amana yaushe kika zama haka ko takarar Gomnan Lagos kika  fito kika ci bamu sani ba,ai Alim da Huzaifa Dariya suka kamayi,can sai ga Haladu da gudu yana haki yana zuwa ya dakumi Amana yace arniyar kasa wlh itace Dan ubanki ina wayata?

Matan gari sai leke sukeyi ta Katanga suna gulma gidan Baki sunyi kudi,Amana ta dawo da arziki harda sojoji masu take musu baya,Amana kafin ta shiga cikin gidan yan gidan kaf maza da mata yara da manya sun fito gaba daya kamar yaki,

Hamza babban yaya yazo wajen Amana yace shegiyar ban biyar Amana ta bashi hannu suka tafa tace How far man,Hamza a Abuja yake Cirani kawai sai ya juya harshe suka fara broken English pigeon shi da Amana,

Huzaifa da Alim dariya kamar su mutu,duk shuru shurun Alim kasa dannewa yayi.

Badariya yar kwalisa ita ta matso tace Banza yar kauye to ki shiga cikin gidan mana,kinzo da mutane kin barsu a waje,wajen Aabid Badariya taje tace kaga Bature amma wannan baya jin hausa,Fatar Aabid ta latsa da Sauri ta kalli Alim tace laushi wlh,dariya Alim yayi tare da cewa Badariya ko?tace laaaa dama kuna jin Hausa?a ina kasanni? Huzaifa ta kalla tace kuzo Na Baku wajen zama Ku kyale shashasha Amana,dariya Huzaifa  yayi yace antynki cefa ko? Ae yayata ce amma Allah Amana bata da mutunci kaf garin nan an sani,yanzu ta balla mutum,

Amma fa tafi kowa hankali a gidan har Baba dasu Umma cewar Badariya, dauko mana tabarma mu zauna a waje kinga muna da yawa cewar Huzaifa

Wai wanne ne cikinku saurayin Amana?cewar Badariya,Huzaifa bai San me zai ce ba kawai sai ya nuna Alim yace gashi,harara Alim ya makawa Huzaifa,

Cikin gida Badariya ta koma dakin Babansu ta dauko manyan tabarmi sababbi dal dal guda uku musamman Baba ya siya sabo da bakinsa.

Inuwar mangoro me sanyi dake kofar gidan ta shindidawa Alim da Huzaifa,suka ce ta mayar da sauran saboda guards basa bukata suna can jikin motoci,

Baba ne ya karaso wajen Su Alim a mutunce suka gaisa aka kawo musu ruwa pure water leda uku me sanyi,

Amana kuwa tana cikin gidan ana ta labarin duniya,dan ma Amana bata fiye surutu

ba,Badariya duk ta fesa cewar Alim ne saurayin Amana sai kallonsa akeyu.

Suna zaune Amana ta fito tana kuyi hakuri Na barku kuzo muje ciki Ku gaisa dasu Umma,Aabid yana makale jikin Alim suka shiga suka gaisa dasu Umma,Alim a hankali ya cewa Amana wace Ummanki? Nan Amana ta nunana musu Ummanta wata fara kwal kamar kwara,suna kama da Amana,gashi yan gidan gaba daya ba laifi suna da kyau sosai Amana ce ta fisu gaba daya,

Alim zai tafi matan manya kowacce dubu hamsim,Umman Amana dubu Dari,Baba ma dubu Dari,sai kayan tsarabarsu yace Na Amana ne ta siyo musu,su doya,manja,dankali,etc harda wayar Haladu,Apple,banana da lemo,su guava, duk abinda suke fada a waya Alim ya siyawa Amana ta basu,gida da makwafta an rude,

Alim sunyi Sallama da Amana cewar jibi za a zo a dauketa zasu koma lagos,Amana tace to ka tafi ni idan nayi 3wks sai Na dawo lagos din,Aabid dinfa? Alim ya furta,baki ta turo gaba to shike nan ka turo jibin a daukeni, Kudi ya bata yace ga salary dinki,

Kin karba tayi to wannan kyautar da kayi a gidanmu ai yafi karfin salary kawai ka barshi,ban son iyayi karba malama kina bata mana lokaci,Karba tayi tare da godiya,baku ci komai ba,tabe baki Alim yayi mungode zamuci a gida, Aabid tayiwa bye bye tare da cewa dama nasan ba ci zakuyi ba Ku yan gayune,Huzaifa yace no ba haka bane Baby Amana, wuce gida tayi aka ci gaba da labarin duniya. Alim sai wurin dare suka koma can gidan su Kaka.

Amana kuwa bata basu labarin halin da ta Shiga a lagos ba,bata fada musu irin rayuwar da tayi a lagos ba,kawai labarin duniya ta basu,haka frnds dinta maza ta ba wasu Dari biyar,wasu 1k,tunda Amana taje take yiwa yan gidansu hudubar Ilmi,cikin kwana daya duk kannenta saida ta sa su a makaranta,

Har alkwari tayi musu indai sunyi karatu to zata sai musu motar hawa,sai murna sukeyi suka sami kwarin gwiwar zuwa Islamiyya da boko,suma yayyen nata sun shiga islamiyyar Matan aure suna jira Amana ta sai musu motoci,mazan kuwa Amana tayi musu alkawarin jari,suma har sun fara nutsuwa,

Iyayensu kuwa tace Makkah zata kaisu suma wannan dalilin yasa ba shiri suka shige islamiyyar matan aure,sunga fa lallai Amana da gaske take,

Baba halinsa yana nan Na banza sai Wanda ya karu a kai,har matan aure bi yakeyi,shi yasa kudin da Alim ya bashi Amana tayi masa wayo ta kwashe kudin ta bar masa iya 20k,sauran kuwa duk ta biya family schl,

Baba yaso yayiwa Amana dukan tsiya kan ta karbi kudinsa amma sai ya tuna alkawarirrikan da tayi masa sai yayi shuru da bakinsa, yaune ranar da Amana zata bar garinsu,kananan kayanta duk ta rabawa su Badariya,su Umma ma sun samu T-shirt dai dai,Aabid ya dami Alim rigimar a kaishi wajen Antynsa ba shiri Alim ya turo driver guda daya da mota da safe da wuri yazo daukan Amana,sai kumburi Amana takeyi sai wajen 5pm sannan ta dauko akwatinta tabi driver suka taho cikin kano city.karfe takwas Na dare suka karaso gidan.

Aabid yana jin sallamar Amana ya fanfaro da gudun tsiya ya dafalfaleta,mutan gidan duk suna

Palo banda Alim Wanda sun fita gari da Frnd dinsa khaleed,
Gaishesu Amana tayi ta tafi wajen Kaka can ta ya da zango sai hira sukeyi da Kaka,har tayi wanka Kaka ta kawo mata abinci sukaci tare da Aabid,
Alim kuwa tun safe yake jiran dawowar su Amana amma shuru har khaleed yazo suka fita.Amana har tsarabar Goro ta kawowa Kaka,sai murna Kaka takeyi Goro lafiyayye me yawan gaske,Matar Abba Ishaq kuwa da Haj Sameera kayan miya irinsu su kuka,kubewa bushashiya,gyada danya etc duk Amana ta kawo musu da yawa.

AsmaBaffa
[6/27, 9:25 PM] +234 808 968 1079: ✳CIRANIN AMANA✳

65-70

By
AsmaBaffa

Tunda Alim ya dawo yaga ba Aabid yasan Amana ta dawo,washe gari da safe ma Amana bata fito ba a dakin Kaka taci abincinta,
Har yamma lis Huzaifa yaje yasa Amana tayi shiri sosai cikin wata arniyar shadda sky blue,suka fito sai kyalli sukeyi,khaleed da Alim suka gani a compound,
Da fara'a tace Daddy barka da yamma,ta kalli khaleed kadan tace ina yini tayi gaba abinta ba tare da ta jira amsarsu ba, Alim a ransa yace lallai ma yarinyar nan,
Khaleed yace wannan kyakyawarfa?yar uwarku ce? A Ina ka zama Daddy dinta?

Tabe baki Alim yayi tare da cewa Nanny din Aabid ce fa,Aabid yana ce min Daddy shine itama take fadamin,lallai ka iya zaben Nanny cewar khaleed,sai wurin 9pm Amana ta shigo ita da Huzaifa,yayi mata siyayya sosai,Alim suka gani shi kadai a Palo,ko me yake jira oho,
Yana ganin Amana ya sauke Ajiyar zuciya me karfi hade da mikewa ya bar palon,washe gari 6am escorts dinsa suka kwashi motoci suka dauki hanyar lagos, da Aabid jirgin karfe 5na yamma suka bi,Amana sai murna akeyi ana zare ido an hau jirgi,

Mintuna kadan suka sauka a Lagos wani Frnd din Alim Kamal yazo ya daukesu a airport,ya

kaisu har gidan Alim ya wuce abinsa.
Gidan neat kal kal suka samu ko ina kasancewar yan aiki sunayin gyaransu,
Tunda Amana ta dawo ta shige dakinta suka sha bacci da Aabid washe gari ma haka Alim bai ganinsu Sam,

Kwanansu Uku da dawowa amma Amana bata kara sa wani atamfa ko lace ba damunta sukeyi,kayanta ta koma sawa,yau shirin wanka sukayi Amana sanye da Wando legins tight iya gwiwa da rigar  ta tshirt armless irin doguwar nan ta kai Rabin cinyarta
Aabid kuwa dan pant ta sa masa ta jashi sukayi bangaren sweeming pool din gidan,
Alim suka gani zaune a kujera daga shi sai short ko Riga babu,yana karanta jarida yana kora lemo,towel dinsu Amana ta ajiye gefe,da fruits salad da ta hada musu,Aabid ta Goya ta shige cikin ruwan nan ba tare da suncewa Alim ci kanka ba,

Tunanin Alim Amana bata iya ruwa ba kawai sai ya hangota ta Goya Aabid tana iyo a ruwa kamar wata kifi,a ransa yace ita wannan komai ta iya kenan.
Aabid kuwa dariya yake ta bangalawa yau ya shiga ruwa,dama bai taba shiga ba,sun Dade ciki sannan ta fito zasu huta su koma,gaba daya bata sa bra ba rigarta duk ta manne a jikinta.
Alim gaba daya ya rude ya shiga wani yanayi ganinta a haka,kafe kirjinta yayi da kallo,yanda ko ya tayi motsi kadawa sukeyi,ji yake kamar ya cafkosu ya shafa,gasu shape dinsu gwanin birgewa,Amana fruits dinsu suke sha bata San me Alim yakeyi ba,Alim gani yayi Amana zata koma cikin ruwa kallonsa zai kare,kiranta yayi da sauri,
Amana! Wani iri Amana taji a jikinta babu abinda ke birgeta a rayuwarta irin taji Alim ya kira sunanta,sai taji kamar ta shide,cikin tafiyarta ta gadara da zafin nama ta karasa wajen Alim,shi kuwa Alim kallonsa yake ta sha yanda Na shanunta suke juyawa,

Ya kwashi wajen 10mnt baice mata komai ba,ita kuwa sabo da tasan yanayinsa baya magana a kan lokaci sai bata damu ba ta tsaya tana juransa,shi kuwa ba haka bane kallon kirjinta yakeyi a hankali saboda ya daga jarida nufinsa ita yake karantawa Ashe wayo ya hada kawai idonsa Na kan Amana ta saman jaridar.

Mikewa yayi daf da Amana kamar zai shige jikinta a zuwan shi tafiya zaiyi,Amana ganin kyaykyawar surar Alim yana kyalli yasa ta jin wani dummmmmm a kwakwalwarta,ta rasa gane mene domin bata taba jin hakan ba,

Alim yana sani yayi luuuu ya tafi zai fadi tare da dafe kansa yace ouch...da sauri Amana ta taroshi ya fado jikinta ragwajaf tare da sakar mata nauyinsa ai kuwa yafi karfin Amana nan take suka fada cikin ruwan gaba daya,
Sai lokacin hankalinsa ya dawo jikinsa sai ya fara tamke fuska yana cin magani tare da tsaki ya fice daga pool din,yana ta faman masifa,aikin banza daga kiranki sai ki jefani cikin ruwa,komai bakyayi A hankali kamar wata sakarai yaja tsaki tare da barin wajen cike da kunya.

Amana kuwa bata kawo komai ba tace masifaffan mutum,shuru shuru dashi sai masifa,Aabid ne yace Antyna Daddy baya masifa fa,to naji muje muyi wankanmu,komawa ruwan sukayi suna

ta wankansu har suka gama,
Yau sati biyu kenan hutun makarantar su Amana ya kare sun koma schl,Mum Alim tun safe take damun Alim kan yazo fa akan maganarsu,haka ya hakura yaje har dakin Abbansa,

Bayan sun gaisa Abba yace Alim wata magana nake jin cewar wai ka tsayar da mata za a je Neman aure,kallon Mum Alim yayi,Mum kuwa ta daka masa harara ba shiri yace yeah Abba,amma a kano take shike nan Alim ka turo min driver ka jibi za muje nemo maka aurenta,cike da takaici Alim yace to Abba ya musu sallama ya bar gidan kamar ya kashe kansa tsabar bakin ciki,

Kwana tsakani Abba ya shirya tare da Amininsa da Mum Alim,sai driver dan rakiya,flight suka bi har kano suka dauki Alhaji Ishaq sukaje can garin da za a nemowa Alim aure,

Suka nemowa Alim aure kuma an basu yarinya tare da sa ranar aure nan da 1mnth domin Mum tace bata so a day lokaci sabo da shedan,
Mum Alim koda sukaje Neman auren mutuniyar kirki ta zama tare da kaunar talaka haka ta nuna,gidan Amarya sai yabon halinta sukeyi,basu San Mum tana da dalilinta,akwai abinda ta boye a kasa.su kuwa Allah sarki sai murna sukeyi gida ya rude sabo da jin dadi zasu shiga gidan Naira.

Bayan sun dawo Abba ya sanarwa Alim komai tare da yabon dangin Amarya,Abba yace son sai watarana kafin biki ka kawo min sirikata Na ganta,domin Mum dinka tace kana sonta sosai,Asiya kanwarku ma naji yanda take yabon halinta,haka Nura da Auta Sadiq ma naji sunce sun Santa yarinyar kirkice.
Alim dai cike da mamakin makircin uwarsu yace Hmm kawai,shi kuwa Abba ya zata kunya Ce kawai.

Amana kuwa harkar gabanta takeyi kawai daga schl sai karatu,zama da kawarta Rufaida yar gayu yasa Amana ta fara dan canja halinta ba laifi,
Mum tace baza ayi biki ba kawai aure za a daura amarya ta tare,

Biki ya matso Amana a bakin yan aiki taji ogafa zaiyi aure, wannan matar yana sonta ba zabin Mum dinsa bace,nan Amana taji tarihin Alim har auri saki da Mum ke sashi yi saboda bata so wata ta ci arzikinsa sai ita uwarsa da ta haifi abinta,
Ko yan uwansa Na jini bata kauna Alim ya musu kyauta sai ta dinga nuna kyashi da bakin ciki,

Bare Abbansa bata so ko hira taga sunayi da Alim saboda kar ya bashi wani abu,Abban Alim kuwa shima me arzikine, hassada ce tayiwa Mum yawa,shi yasa bata taba yarda Alim ya auri wacce yake so,shi yasa duk wacce tasan Alim bazai taba kauna ba har a bada to ita zata nemo ta aura masa.

Amana tana gama jin labarin taji wani bakin ciki da bata San Na mene ba ya taru ya cushe

mata a zuciya,hankalinta ya tashi ta nemi farin cikinta ta rasa,a ranta saida ta tsinewa Mum Alim yafi dubu kan wanne dalili zatayiwa Daddy aure, bakin cikin Amana kenan.

Amana tana shiga Palo bata kula da Alim ba ta jefar da Jakarta a palon ta cire takalminta ta watsar cike da tsananin bakin ciki ta ja tsaki,nan ta fara zagaya Palon,da karfi tace a'a...wai mene haka ne eh....ina ruwana ma aikin banza aikin wofi,

Minti kadan ta buga kafafu tare da miko hannu kamar damisa zata damki nama tace saina ehhhhhhhhhh......shake tsohuwar nan.....can wani lokaci ta dakko ruwa ta kafa kai kwat...kwat...ta shanye tare da jefar da robar tace sai naci uwar tsohuwa wlh...tambadaddiya.....kodaddiyya.....sokayayya....me suffar hanjin ligidi.... Tayi dakinta da sauri ta fada bed dinta,Aabid ne ya shigo daga baya shi kam yaga Daddynsa wajensa ya nufa.

Ihun Amana su Alim sukaji sai karaji takeyi a dakinta,da sauri Alim ya bude dakin nata a kan bed ya ganta kawai wutsil wutsil takeyi tana karajinta tare da tsine tsine,Allah ya baki Ify cewar Alim yayi waje abinsa.Aabid yana a kafadarsa,

Ranar Amana da kyar ta iya yin wanka haka ta kwana ba bacci,sai asuba ta samu bacci,Aabid sai driver ne ya kaishi schl,amma Amana tace Sam ita bata da Ify.haka Amana ta yini da zazzabi,ga period tanayi,harda su amai tsabar bacin ran za a yiwa Daddynsu aure.

Alim kuwa tun yana damuwa har ma ya gaji gudun kar ciwo ya shigeshi a banza,frnds dinsa ma sun jajanta masa, sun tabbatar auren babu inda zaije.

Yau daurin aure saura 1wk Amana duk ta rame ita kanta bata San dalili ba,Alim kuwa ko a kwalar rigarsa indai irin wannan aure ne ya rigada ya saba dashi.

Mum kuwa burinta ya kusa cika,

Kwanaki fa suna ta ja gobe Saturday gobe daurin Auren Alim,dole ya gayyaci abokansa sosai,Amana kuwa tana Palo tana jira taga wankan auren Alim,itama ta shirya cikin shadda dark brown tayi kyau kamar itace Amaryar Aabid kuwa ya tafi weekend wajen Mum Alim,

Wani gigitaccen kamshi Amana taji ya daketa,Alim ya sakko cikin hadaddiyar shigar wata tsadaddar shadda yar gaske fara kwal,yayi Kyan da bai taba yi ba a duniya,ita kanta Amana gigicewa tayi,

Da Sauri ta mike tsaye tana wani kyafta ido sannan ta fara magana,dan Allah Dan Annabi dan Darajar Allah dan girman Allah kaje dani daurin auren naka kaji,

Pls Daddy kaje dani sosai ta damu Alim sai yaje da ita,je kiyi shiri kwana yini daya zamuyi tunda ma hakane sai Na tsaya mu taho da Amaryata.cikin tawagar angwaye dake flight harda Amana,

Amana burinta idan sunje kano taje gidansu su gaisa da yan uwanta.

Gidan Amarya kuwa an cika makil ana jiran angwaye,Abba da yan uwansa duk Suna can,Mum ma ta tura Aminiyarta Haj Talatuwa da Haj sameera kanwar Abba da matar Alhj Ishaq Aisha. Duk suna gidan Amarya ana jira a daura aure.

Angwaye sun sauka a kano sun kara haduwa a manyan motoci Na alfarma tare da frnds na kano an tafi gidan Amarya daurin aure,Amana tana kusa da Alim,sai tsokanarsu akeyi cewar tayiwa Amarya wayo,Amana dai tayi shuru ita da Alim a bayan mota Khaleed ne driver,ana ta zankada tafiya,zuciyar Amana cike da kunci,shi kam Alim ya rasa dalili jin wannan auren yakeyi daban da sauran da Mum tayi masa,baya jin wani kunci,ya danganta hakan da sabo.

Amana bata kaunar ganin garin Amaryar ma sabo da haka ta kwantar da kanta a jikin kujera tare da lumshe ido,khaleed kuwa sai tsokanar ango yakeyi yaki yin shuru,sauran motocin abokan ango suna binsu a baya,

Garin Amarya aka shigo har unguwarsu da layin gidan su amarya wani dandasheshe gida da duk unguwar babu kamarsa shi aka tsaya da motoci,mutane damkam cikin masallaci da wajensa,dangin ango duk gasu nan,har su Huzaifa, Amana bude lumsassun idanuwanta tayi don kallon unguwar Amarya,ai da sauri ta kara damke idonta ganin wani tsantsararren gida me kyau,gida Na fita kunya,ga mutane sunsha wanka,kamshi Na tashi kowanne cikin shigar alfarma,

Amana sai zare ido takeyi da mamaki tana kara bude idonta sai kallon dangin Amarya takeyi cikin suturu Na gaske,da gani sun samu harka,mamaki cike da zuciyar Amana,sai murza ido Amana takeyi.

Kallo Amana take tayi tana murje ido,ga kwalla ta cika idonta har hawaye ya fara zubar mata ta rasa meke mata yawo a zuciyarta.

AsmaBaffa

[6/27, 9:25 PM] +234 808 968 1079: ✳CIRANIN AMANA✳

70-75

By
AsmaBaffa

Amana bata gama shan mamaki ba sai da taga Babanta ya fito daga gida dauke da Alawa goro da chewgum Na daurin aure domin a kauyen haka akeyi,
Hangame baki Amana tayi domin ganin su Haladu da Hamza tare da sauran yayyenta duk sunzo daga garin da suke Cirani,mamakin Amana shine ganinsu cikin shiga me Kyan gaske,gaba daya sun canja,kyansu ya fito,sunyi fresh,to me ya faru haka,amma ai suna waya dasu Baba me yasa basu bata labarin komai ba,cikin motar da take ta kalla kawai sai taga wayam ba kowa Ashe angwaye duk sun fice an barta a ciki,su Alim ta hango sai hada hada sukeyi,musamman yanda taga Alim da danginta sai wasa da dariya sukeyi,mutumin da ba ya magana shine yake ta wasa da dariya haka.

Ana haka aka fara hudubar daurin aure,Amana sauke glass din window motar tayi dai dai da lokacin da taji ance an daura auren ALIM USMAN MUSA da AMANA SULEMAN HARKA kan sadaki naira million daya.

Amana poster tayi ta kame waje daya tare da hangame baki,shi kuwa Alim ya rasa me yake ji a ransa sai congrat akeyi masa da fatan alkhairi,
Baban Amana baki har kunne sai rabon alawa da goro yakeyi ana masa Allah sanya Alkhairi,Amana kuwa ta matsu mazan su watse ta shiga cikin gidansu taji wannan wanne irin abune,za a min aure ban sani ba,
Wani bangaren kuma wani nishadin dadi ta tsinci kanta ciki,tana ta tunanin duniya bata sani ba har mutane sun waste,angwaye kadai suka rage a kofar gidan su Amana,

A rude Amana ta gyara gyalenta siriri shara shara da ta yana a kanta bata daura dankwaliba sai acuci da tayi,gashi shaddar da tasha kowa ya ganta zaice Amarya ce,
Fitowa tayi daga motar  kamar zata tashi sama ta wuce cikin gida ko bangaren angwaye bata kalla ba,Amana doluwa ta zama data shiga hadadden gidansu,kamar a birni,ko ina yasha tiles kofofi da windows masu kyau,cikin dakuna sun sha furniture masu kyau,
Komai Na gidan Na yan gayu,dakuna ta duba bedrooms gasu nan na maza Dana mata,Dana baki,da Na Babansu Palo da bedroom,
Dakin iyayensu ma Palo da bedroom ko wacce,kakarsu ma haka.gida ya kai gida ba jin kunya,mamakinta waye yayi gidan haka,
Yan biki mata sai kallon Amana yar gayu akeyi,ana guda,shewa,tare da tsokanar Amarya,Amana sabo da tsabar gulma dan kar ace tana so sai ta fashe da kuka tare da kallon Badariya tace ke dan uwarki ina dakin Umma,nuna mata badariya tayi ta fada ciki da kuka,

Babane ya shigo dakin shima,Amana cikin kuka tace Baba ya zaka yi min haka,ayi min aure ban sani ba,ko a waya ai ka fada min,Baba yace haba Amana ta ki yafewa Babanki kinji,uwar mijinki ce tace kar Na fada maki sabo da tana kaunarki tafi so tayi abinda zai saki nishadi,kinga gidan nan mijinki shi ya Gina min,kinga kowa Na gidan nan ya basu jari me tsoka,kannenki duk ya biya musu kudin makaranta,kudi da abinci da sutura duk shi ya aiko mana sosai har yayyenki da suke Abuja da cross river yayi musu komai,ta dalilinsa gidan nan an ci gaba,ga ilmi ana samu,

Ga shi kowa yana da aikinyi,yanzu duk iskancin da jahilcin da ake tafkawa a gidan nan Nawa ya fara raguwa, Iyayenku sun fara daina zage zage sabo da islamiyyar da kika ce su shiga,haka duk maza da mata masu shaye shaye da sata da matan ma masu mugun hali ta sanadiyyar makaranta da aikinyi da suka samu duk sun daina sai abinda ba a rasa ba,

Ki duba da kanki ki gani su Hamza duk sunyi hankali,nima yanzu alhmdllh Ina ciyar da iyalaina,to Baba kaifa ka daina daya halin naka?cewar Amana,

Jan numfashi Baba yayi yace kuci gaba da min addua Amana Na kusa dainawa,kuka Amana tasa haba Baba yanzu so kake yayanmu su gajeka,mu gaskiya kana jawo mana abin kunya,

To Amanata sai hakuri ai inji Baba,shi yasa alherin da mutanen nan sukayi mana dole Amana nayi musu abinda suka bukata,amma gaskiya uwar yaron nan mijinki da Babansa mutanen kirki ne,kinyi dace,yanda suka nuna mana kauna gamu talakawa amma suka iya hada zuriya damu ai sai dai Allah ya saka,Allah sa Albarka cewar Umman Amana dake zaune bakin gado,Amana tace nidai kawai ba a kyauta min ba,

Kudin sadakinta Baba ya mika mata dubu dari shida ta dauka haladu yaje banki ya sa mata a accnt dinta Dari hudu kuma ta rabawa iyayenta da danginta,

Gidan su Amana suna da tsafta sosai saboda shi Baba Allah yayoshi me tsamtsami,shi yasa dole kowacce ta zama me tsafta a ko ina,saboda yana ganin kazanta zai iya sakin mace.

Badariya ce ta kawowa Amana wainar fulawa da yaji me dadin gaske,ta kawo mata waina da miya ta bikinta,tuwon shinkafa miyar ganye,ummanta kuma ta kawo mata danwake me zafi,

Tun anan Amana taga canji,da Dane yaushe Badariya zata wani girmamata haka,gashi abin farin ciki Badariya ta daina zuka hayakin sigari,Umma ma da ace da ce yaushe ma zata wani saurareta idan ba kudi Amana ta bayar ba gaskiya Alim da iyayensa sun taimaka musu,ko sabo da wannan dalilin ta yiwa mijinta biyayya.

Ta fara cin danwakenta kenan Badariya ta kara shigowa Anty Amana kinga booth din motar angwaye kuwa abincine irin Na hotel da kaji,da ruwan jarka ke harda lemuka sun bude a irin abin take away suna ta ci in fada miki gaskiya yan gayu ne,amma angonki bai ci ba shi,Badariya tace kinga wannan Huzaifan ya bani da yawa Na kawowa su umma,

Anty Amana wai dan Allah nima ina da kyau?kinji wannan Huzaifan sai yace ni me kyauce,nace ai kin fimu kyau yace bai yarda ba Badriya ke ta faman surutu,Amana cike da masifa tace karki dameni dallah,

Sallamar Alim sukaji Umma dake waje tace shiga mana tana ciki ai an zama daya,tana cin danwakenta Alim ya shigo ya zauna a daya daga cikin kujerun palon.

Kwanikan gaban Amana ya shiga Budawa wainar fulawa ya gani tana ta tiriri,dama shi yana son wainar fulawa,gabansa yaja kawai ya fara ci,saida yaci ya koshi ya mike yace ki gama ki fito mu tafi ina jiranki,OK kawai tace da kyar,

Saida ya fita sannan ta sauke ajiyar zuciya tare da shakar kamshinsa,
Saida taci ta koshi sannan ta mike tace Umma zamu tafi, hhhh dariya akayi sosai amarya da ango sunzo daurin aurensu tare sun koma tare,ba a taba ganin irin wannan aure ba,Amarya kamar bata da gatan dangi,

Umma wata katuwar Leda ta mikawa Amana tare da fadin Badriya ta rubuta komai a jiki,wajen Baba Amana taje sukayi sallama,Baba yace to Amana in kayi da kyau kaga da kyau,kibi Allah kibi mijinki Idan kika tsaya wuru wuru ki gani a allonki, muna kallo za a watsaki a jahannama,gidana ba a yaji,idan miji ya sakoki to ki nemi wani gidan ba gidana ba,Amana dai aranta tace wannan ai ba nasiha bace ta kirki,kai Allah shiryi su Baba,a hakanma gwara Baba ya kamanta,Umma ba wata nasiha sai wasu kwalabe manya ta wani bani a Leda,ko mene oho,

A fili kuwa kallon Baba tayi tace ai billahillazi ya sakoni ko nayi yaji dole gidanmu zan taho, ina kakeso naje,Baba ma yace aikuwa kinyi karya in kina wasa ki gwada ki gani,Baba no...zanci Ubanki Amana karki ga ina lallabaki Na fiki iya shege,Amana tace Baba Allah baka hakuri,yawwa tashi maza kuje Allah bada zaman lafiya,

Baba yanzu baza a kaini a matsayin Amarya ba?ke ya isheki Amana tafi gashi duk angwaye sun tafi mijinki ne kadai ya rage a garin nan.
Amana tana cin magani tare da kukan gulma wai dan kar ace batayi kuka ba ta fito har jikin motarsu taje Har khaleed driver yabi wata motar sun tafi cikin kano city,

Alim ne kwal a wajen,key din mota ya mikawa Amana me kuka,a ranta tace wato baima daukeni Amarya ba kenan, karbar key din tayi Alim ya Shiga gaba,ta zauna mazaunin driver ta fara tuki har suka bar garin Amana tukinta takeyi Hawayen karya nata sharara a fuskarta harda shesheka,
Har sukazo airport Amana bata daina kuka ba,Alim yana ta satar kallonta,ga driving ga kuka,frnds tuni suna jirgi ango da Amarya ma shiga jirgi sukayi khaleed ya juya gida da motar,
Amana ana lungu a kujerar jirgi har yau kuka takeyi tare da cewa Ashe tana kaunata,me sonace,Ashe kaunace zunzurutu Na dinga zaginta a banza,Ashe uwata ce nima,
Nima ina kaunarki ta kara fashewa da kuka,Alim bai gane kan zancen Amana ba,

Ashe Amana duk kukan takaici takeyi rannan da taji Mum zatayiwa Alim aure ta kwana tana zaginta kala kala,ashe ma itace amaryar,ashe Mum din Alim tana matukar kaunar Amana tunda har ta iya hada jininta da Na Amana.

Amana tunanin halin Mum ta shigayi yanda take sa Alim yana auri saki,kawai sai Alim ya kara jin kukanta tace shikenan bazanyi lasting ba,bazanyi inganci ba,
Shi dai baya gane me Amana take nufi,masu kula da cikin jirgi sai lallashin Amana sukeyi tunaninsu ko bata da lafiya,

Har suka zo lagos bata sani ba,motocin Alim Jere sun kai bakwai su suka kwashe tawagar ango,har gida wajen Mum dinsa aka rakasu,Har Amana sai wani rufe fuska takeyi saboda

kunya
Mum cike da nuna murna da farin ciki Na karya ta tarbi Amana,

Yata kiyi hakuri kinji anyi aure ba tare da amince warkiba Na yaba da halayenki matuka shi yasa naji kwadayin hadaki da Dana,kuma shima Alim ya fada min yana sonki,haka Mum Alim ta dinga shiryawa Amana zancen karya iri iri,har sai da Amana taji ta yarda da Mum,

Su hajiya Talatuwa kawar Mum sun dawo suma,Talatuwa ita kadai tasan dalilin da yasa Mum tasa Alim ya auri Amana,Aabid yana makale a jikin amarya Amana, Mum ce ta sa ma'aikata suka fito da lefen Amana Na gani Na fada har akwati 9 babu abinda babu,wasu ma a Holland Mum ta hadosu,har mota aka shigar da akwatuna,Mum ta kalli Amana tare da kallon ledar da Amana tazo da ita,da wasa da dariya Mum tace wannan kayan fa daughter,Amana murmushi ta saki tare da cewa Umma Na ce ta bani nima ban San mene ba, Mum ce ta karba tare da dubawa kayan gyara Na mata ta gani,ingatattun magunguna,fakar idon Amana tayi ta dalla mata wata uwar harara tare da maka mata banzan kallo,a ranta Mum tace za a mallakemin yarona tsinanniya zaki ga yanda zan mai da rayuwarki,a fili kuwa cewa tayi yata wannan ai sunyi araha da yawa sai su lalata miki mahaifa,ki bari ki zauna yanda Allah yayiki sai mijinki yafi sonki,Amana baiwar Allah to Mum kawai tace,

Bayan sunyi sallar isha Abban Alim ya nemi Alim da Amana yayi nasiha ta gaske sannan yayiwa Alim tasu ta sirri,Asiya ma sai yabon irin kyan Amarya takeyi har sai da Mum ta maketa,

Aabid Alim da Amana haka aka rakasu har mota suka tafi gidan Alim,kowa yana murna da fatan alkhairi banda Mum da kullum cikin kulla sharri take,
Ma'aikatan gidan Alim kaf sun sa ido suga an kawo amarya su ga kalarta su sami abin gulma,sai sukaji shuru kawai Amana suka gani da Aabid da Alim,sai suke tunanin ba yau za a kawo Amarya ba,amma wasu maza daga ma'aikata sunzo da gulmar cewar sunji ance Amana itace matar da Alim ya aura,amma aka karyatasu ba a yarda ba ganin babu wata alama data nuna Amana Amaryace,kuma sunga da safe da ita Alim ya tafi gidan biki,

Amana kuwa suna shiga Palo Alim yace ina ledar hannunki da aka baki a garinku? Mum ce tace Na bata basu da inganci Amana ta fadi,mene a ciki?Alim ya tambaya,hmm nima ban sani ba amma naji Mum tace wai kayan gyaran matane,nan take Alim ya gano wato Mum kwacewa tayi dan kar ma ko ya kusanci Amana yaji wani dadi,

Baki ya tabe tare da cewa ke kuma sai kika tsaya sototo ta karbe ko?gaki da wayo amma kuma baki dashi,sai kiyi tayi ai.ga Aabid karbeshi yayi bacci zanje Na huta

Wanka sukayi gaba daya suka kwanta baccin gajiya Kowanne a dakinsa yake,washe gari dukkansu babu Wanda ya fita,haka sai ga yan aiki sun shugo da lefen Amana gaba daya,Suna zaune sai ga Mum da sassafe tayi sallama a gidan,da sauri Alim yacewa Amana dauki Aabid ki koma dakinki,saida ya tabbatar Amana ta shiga dakinta sannan ya budewa Mum kofa ta shigo tana faman baza ido,ko gaisawa basuyi ba tace ina Amarya,yatsina fuska Alim yayi tare da tabe

baki yace Mum pls ki daina hadani da wannan yarinyar bana kaunarta,

Tana can dakinta nifa Mum duk cikin matan da kike aura mun babu wacce Na tsana kamar wannan yarinyar,bana kaunar naninta Sam,da nasan zakisa Na aureta da bazan taba daukanta aiki a gidana ba,yanzu wlh kin jawo mata masifa da bala'i aiki zata sha ta zama baiwata kawai,.
Wani sanyi da dadi ne ya ziyarci zuciyar Mum,nan take tayiwa Alim sallama driver ya maidata gida,

Wata ajiyar zuciya Alim ya saki tare da kwankwasa dakin Amana ta fito tana fitowa ya sakar mata kayataccen murmushi tare da cewa Amarya yau bazaki hada mana break ba ko hutun Amarcinne,Amana dai kunya ce ta lullubeta,harda nunawa Alim Aabid karfa yajika tare da fadawa kitchen sai Murna takeyi

AsmaBaffa

Ina godiya kwarai readers luv u all,ina ganin sakonninku ta ko ina tnx.
[6/27, 9:25 PM] +234 808 968 1079: ✳CIRANIN AMANA✳

75-80

By
AsmaBaffa

Alim suna ta game da Aabid har Amarya Amana ta gama shirya girke girkenta a dining sannan ta koma dakinta ta shige toilet ta feso wanka tare da cancada kwalliya cikin shigarta ta yau da kullum amma yau ta dabance wani burmemen wando 3qtr red da wata Riga T-shirt karama ko dankwali bata daura ba ta fito,su Alim ta hango a dining tun kafin ta karaso wajen Alim ya mata alama da hannu cewar ta juya ta canja kaya,

Tasan kayan da yake nufi dan haka ta cuno dan bakinta ta juya tana kunkuni ta canja shigar atamfa wata lemon green dinkin Riga da skert sosai tayi mugun kyau ta fito a Amaryarta,yau Amana cewa tayi sai ta daura dankwalinta nan ta fara kici ciki ta kasa kawai sai ta Dora dankwalin kawai a kanta kamar gyale ta fito haka,

Tana zuwa Alim yace ko kefa,zo...zo..da sauri taje wajensa,dankwalin ya zame a kanta,habawa nan yaga zallar baiwar gashi baki sidik yana kamshi da kyalli,
Amana kuwa gabanta sai faduwa yakeyi kasancewar namiji bai taba yi mata haka ba,

Shi kuwa Alim daurin dankwali ya shiga tsantsarawa Amana harda rera wakar barmani choge ....sakarai... bata da wayo,ai Amana dariya ta fara kyalkyalawa,Alim bai taba ganin dariyarta haka ba domin Amana ba komai ne ke bata dariya ba,
Tsayawa yayi har ta gama dariyar sannan ya daura mata daurin zamani kamar ta daura goggoro haka Alim ya Nada mata dauri,da sauri ta shiga bedroom din Alim ta kalli kanta yanda ta zama kamar sarauniya,

Fitowa tayi tare da cewa dan Allah a ina ka koyi dauri haka,ko a mata ban taba ganin wannan kalar ba,ba kin maida kanki namiji ba ta ya zaki San da wannan sakara kawai cewar Alim.tun daga wannan rana Amana ita ba abinda ke birgeta irin ta zauna taga Alim yana nannada mata dauri abin birgeta yakeyi yana bata sha'awa.sabi da haka yasa Amana kullum burinta tasa atamfa ko lace ko shadda ko material tazo wajen Alim tace Daddy ayi min dauri,shiko Alim ya zauna ya tsantsara mata dauri,kuma tayi tayi ya fada mata a ina ya koyi dauri yaki fada mata,

Amana tare da Aabid zaune a kujera tana taje masa gashi,Aabid ne yace Anty ki siyo min icecream gobe idan munje schl,Amana ce ta bige masa baki kar ka sake Na kara ji kace min Anty as from today Na zama your Momy, kunji fa Amana,Aabid kuwa ya rike gam Momy yake ce mata
Yau Amana sauri tayi kafin Alim ya fita Office tayi wanka tasha wani dakakken lace a cikin kayan lefenta ta fito main Palo Alim ma ya sakko cikin shirin sa zai wuce office da sauri tasha gabansa Daddy...Daddyn Aabid pls ayi min dauri,me zakiyi da dauri yanzu ke da Mum ke nemanki,kiyi sauri ki je wlh kafin ki shiga Matsala,cike da shagwabar da bata San ta iya ba tace to Daddy nifa kana gani ko schl banje ba yau saboda Mum tana nemana,kuma nace kamin daurin Na je kaki,kuma ma Allah ni bazan iya Driving ba yau muje ka saukeni a gidan,

Lallai yarinya baki San nufin Mum akanki ba,to ko driving karkiyi ta ganki a motata kinji Na fada miki,muje Jan hannunta yayi har dakinta,tsofaffin kayanta ya duba ya dakko wata doguwar rigar atamfa wacce take karama kuma ta kode ta jeme,yace sa wannan maza,ba musu ta yi hanyar toilet da sauri Alim ya jawota baya yace kut amma kinma raina ni dalla malama sa kayanki anan me zan gani,

Kunya sosai taji haka ta daura zani cikin dabara ta canja kayan,sannan ya dauko wani dark powder sosai ya shafa mata saiga Amana ta dawo baka baka tayi kalar wahala,kowa ya ganta zai rantse a cikin talauci take, oya yi kalar tausayi Na gani Alim ya furta,ai kuwa Amana ta wani langabe kamar Almajira, good ki yi acting ina zaluntarki,ina baki wahala a gaban Mum,karki bari Abba ya ganki a hakan,kuma zamu tafi amma zan saukeki ki hau taxi ta kaiki,duk abinda Mum zatace ki nuna wahala kike sha a hannuna,

Amana to kawai tace tana tausayin kanta haka ta sa hijab har kasa sabo da yan aiki kar su

ganta haka,cikin jerin motocin Alim suka fita sun kusa da gidan su Alim aka tsaya,Amana ta cire hijab dinta tare da yafa wani yankwanannen gyale Tsoho kalar talauci,ta fito tare da shiga taxi ta bashi Address din da Alim ya bata,me taxi ya kaita har gidan,

Sunkuyar da kai tayi har sashen Mum,tana shiga palon tayi ido hudu da Mum Alim ana mata tausa,kamar gaske Mum ta mike tsaye tare da rafka salati Yata kece kuwa, haka kika dawo?me ya faru,Alim ne ko?Amana kuwa kawai sai ta fara Kuka wiwi kamar gaske

Tace Mum baya sona,bakiga azabar da yake gana min ba,har marina yakeyi,kuma ko dakina bai taba shiga ba,yanzu kusan aikin gidan kaf ni nakeyinsa,

Ya tsaneni baya kaunata,bauta kawai nakeyi,kayan sawata gaba daya ya kwace har Na lefe,ni dai kice ya sawwake min wlh na gaji,wani dadi da sanyi ne ya lullube Mum Alim,a fili tace ki bari yata zanyi masa magana,wannan ai shirmene,ya zai watsa min kasa a ido,ina zuwa,da sauri Amana ta riko kafafun Mum tana kuka dan Allah Mum karki fada masa, ki rufa min asiri,idan kika fada masa na shiga Uku na lalace,

Mum a ranta tace baki shiga uku ba sai nan gaba,a fili kuwa kan Amana ta shafa tace ina zuwa wani daki ta shiga,Amana ta bita a hankali ta labe a jikin kofar,Mum taji ta fara waya da kawarta tana ta shewa da murna tare da bayyana irin makircin da ta hadawa Amana,da Wanda zata hada mata nan gaba,

Amana ce ta fashe da kukan gaske tana tunanin bala'in daya tunkarota da halin da zata shiga nan gaba,Mum ce taji motsi taji ajikinta Amana ce,da sauri ta katse wayar ta kira Alim tare da sawa a handsfree ta matso jikin kofa wai sabo da Amana taji bakin ciki a ranta tace Son wannan yarinyar me kayi mata haka,gaskiya kaci Amana baka kyauta ba,

Alim kuwa yasan makircin uwarsa kuma ya tabbata wannan nasihar ba tsakani da Allah tayita ba,sabo da haka Alim yace Mum na tsani yarinyar nan,bana kaunarta,bantaba tsanar wani dan Adam a duniyaba kamarta ,kema Mum kin San bazan taba son wannan ballagazar yarinyar ba,kawai biyayya nayi miki,

Amana taji komai da Alim ya fada dama kuma tasan Alim ba sonta yake ba,sai dai batayi tunanin zai ki ta haka ba,duk ta shiga rudu,komawa tayi Palo zuciyarta cike da kunci,Saboda Munafunci Mum driver tasa ya kai Amana gida har tana cewa dama saboda na ga halin da kike ciki yasa na kiraki, godiya tayiwa Mum kawai ta shiga mota,Suna barin gidan ta maida katon hijab dinta.

Fiya fiya fiya Amana ta fada dakinta tare da bugo kofar garam,1pm tayi sallah tare da addua kan Mum da Alim,ta fada kitchen tare da shirya girke girke na alfarma,

Shiryawa tayi a dining,sai ga Aabid ya dawo daga schl yana ta faman kiran Momy am back,wanka tayi masa ta shiryashi cikin kayan islamiyya,sannan ta bashi abinci tare da cewa maza ka huta ka tafi islamiyya,

Wanka ta shiga ta fito tayi shafe shafenta sannan ta bude akwatin lefenta ta zabo wani short wando pink da kadan ya rufe duwawu ya haura cinya,da wata T-shirt karama yellow,ta shirya ta baza gashinta yana sheki da kamshi,ta shafa powder da jambaki pink, tabi jikinta da turare masu matukar kamshi,

Alim kuwa ya Gaza tabuka komai tunani yakeyi me Mum zatayiwa Amana, gida ya dawo direct toilet ya fada ya fara wanka, Amana kuwa tana gama kwalliyarta Palon Alim tazo kunci yayi mata yawa,ji take kamar ta kama da wuta kawai sai Amana ta daddage iya karfinta ta kwalla da karfin gaske tace kinyi........da....yar....Halak.....ni......Amana.....Sulemanu.......Harka.......sai........Alim ne ya fito daure da towel jikinsa duk kumfa saboda magana cikin kara da yaji Wanda baya gane me akace,

Ido hudu Alim yayi da Amana wacce ta dau wankan sugar ta takarkare ta bude dan mitsitsin bakinta tana ganin Alim ta karasa maganarta a hankali da Ni....Amana... Sulemanu...Harka....Allah sai nayi mata biyayya....ina son....Surukata,kunji karyar Amana da wata mummunar kalma zata fada ganin Alim ta canja salo.

Tsaki Alim yaja ya koma ciki tare da rufo kofarsa,

Tana zaune ya fito yana kamshi cikin 3qtr da singlet fara,dining ya nufa da Sauri ta mike taje wajen, cike da shagwaba tace to basai ka tsaya nazo na zuba ma ba,Sabon iskancin da kikazo dashi kenan yau,Alim ya furta

Shuru Amana tayi Ta zuba masa abincin,sannan ta mike da niyar barin wajen,muryarsa me sanyi taji me Mum tace miki dazu zo ki fadamin,wata harara Amana ta watsa masa sannan ta karaso tana turo dan bakinta,ni kike harara? Wani wal ta karayi da idonta sannan tace ba dole na harareka ba kafi kowa sani and u are asking me,what do u want me to tell u to,

Ok marar kunya zageni yanzu fa ni mijinki ne Dole ki min biyayya,au to wacce rashin biyayya nake maka,duk biyayyar da nakeyi baka gani? A hakan kike wata biyayya,yes mana Kai ka sanni ka tuno lokacin da mukahadu a wajen yan fashi da suka taremu,a lokacin zan iya cin kwalarka na balla ma kafa,

Kuma da ace bana ma biyayya da abinda naji Mum dinka ta fada da kuma yanda kace mata a waya to da muna haduwa sai na ragargaza ma hakarkari,

Amma kawai sabo da yanzu ka zama mijina shi yasa kuma da darajar Aabid kar na illata Daddynsa amma ai da tun ranar danazo gidan nan zan kaddamar maka,

Murmushi Alim yayi tare da cewa ke ganinki zaki iya ballani to ko dan yatsa na baki isa kin lankwasa ba,baki San karfin maza ba naga Alama amma zan nuna miki,

Amana juyi tayi Hmm kai mufa mun San what man can do woman can do better,Allah ko?to mu gwada mu gani cewar Alim.da ya daina cin abinci ya mike tsaye tare da tube singlet dinsa yace in kin isa tube haka mu gani a gabana,miki miki Amana tayi,yace sannan idan har da gaskene what man can do woman can do muje toilet kiyi min fitsari a cikin kwalaba ba tare da wani ya zubo kasa ba,

Nan ma shuru Amana tayi,hannunta ya kamo karo na farko kenan,wani shock mar mar sukaji a jininsu tare da zirrr a kwakwalkwarsu, idan kin isa kwace mugani,Amana ta fara kici kici amma ta kasa, wuyanta ya damka ya shaketa kadan,yace taimaki kanki ki kwace na gani,Amana ido ya firfito tana ta kakarin amai saida ya gaji sannan ya saketa,sai murza wuyanta takeyi tana karari da tari,da kyar tace ai zan iya kwacewar kawai dan kaci abinci ne ni kuma banci komai ba,

Murmushi Alim ya saki Wanda yasa dimple dinsa dinsa lotsawa gaba daya,Amana tana tsaye ta faki idon Alim saida ta bari ya sakankance ta zagaya ta bayansa tare da shako wuyansa ta matse Kansa a kirjinsa wai so takeyi ta masa mugunta,shi kuwa Alim ji yayi ta tallafo kansa,laushin na shanunta da yaji a kansa da wuyansa shi yasa ya wani lumshe sexy eye dinsa,tare da tsotsar pink lips dinsa,Amana tunaninta zafi yaji sai kara kankame Wuyan Alim da kansa a kirjinta takeyi, ta kai 20mins a haka sannan ta dago kansa sai taga Alim ma bacci ya fara yi abinsa,zamewa tayi Wanda yayi sanadin budewar idon Alim yayi ja da gani baccine cike a idonsa.

9pm Aabid yayi baccinsa Amana tayi wanka cikin kayan baccinta na lefe sai da ts zabo wata a can kasan akwati wata yar riga fara kar iyakarta cinya me laushi,hannunta karami dashi,turaren jikin da kawarta Rufaida ta bata shi ta shafa sama sama ta sa rigarta,ta kara fesa wani turaren sannan ta kwanta,

Tayi adduar baccinta ta fara bacci amma abin mamaki tunda tasa rigar takeji wani azababben kaikayi na fitar hankali,har yan kuraje kana na suka fito mata,tun tana Susa har ta fara kuka sosai.

Cikin dare Alim yaji kuka da ihun Amana,ta hanashi bacci, fitowa yayi da Sauri ya nufi dakinta,a kasan tiles ya hangota tana ta shure shure da tirje tirje hade da soshe shoshen jikinta,ga kuka kuma tare da ihu.

Hannunta ya kama ke Ify wai burinki kullum ki takurawa mutane,Idan kika dameni part din yan aiki zaki koma.

Ba tare da ta bude ido ba ta fara Susa jikinta tana borin jini borin jini nakeyi, mikewa zaune tayi tare da makale Alim ka Sosa min dan Allah, Alim dubawa bed yayi ya hango Aabid yana ta bacci,daukan Amana yayi cak har bedroom dinsa ya kwantar da ita a bed dinsa, sannan ya fara cirewa Amana kayan jikinta,sai ci gaba takeyi da soshe soshenta ba kakkautawa,ga kuka hade da zullo duk ita kadai take ta faman yi.

AsmaBaffa

Godiya dubu gereku masoyana,ina ganin sakonni ta ko ina .
[6/30, 8:55 PM] 0mmer Farouk: ✳CIRANIN AMANA✳

85-90

By
AsmaBaffa

Tunda Amana ta shige blanket dinsa duk ya rude,ya Shiga wani hali,ya rasa dalilin da yasa yake jin haka a tare da ita Wanda bai taba jin makamancinsa a wajen duk matan da Mum ta aura masa ba,jinta yake a jininsa har bargonsa ganinta yake ita ta daban ce, a hankali Amana ta yi magana Daddynmu pls ka fahimceni wlh kazafi sukayi min ban aikata hakan ba,kasan halina kasan me zan iya aikatawa,muje schl din gobe ka tambaya kaji me ke tafiya,

Tunda Amana ta fara magana kamar tana masa rada a kunne gaba daya hankalinsa ya fara susucewa,hankalinsa ya tashi,gashi sai kara matsowa jikinsa takeyi,

Hannunsa ta rike kaji Daddyn Aabid,wani xirrrrrrr Alim yaji nan take bari jikinsa ya fara sosai,

Amana ta zata ko zazzabi ne ya kama Alim,da sauri ta sakeshi Yaya Alim zazzabi ya kamaka,Amana ita bata San kan komai ba ta dami Alim sai yasha maganin zazzabi,da kyar yaja numfashinsa yace ba...zazzzab..bi..nakeyi ba, gashi jikinka yana rawa,kirjinsa ta taba ta ji temp dinsa,ai da sauri Alim yace wayyo Allah shiiiiiiiii.....tsorata Amana tayi tace jikin ne sannu kaji ko kashinka na kirjj ya goce ne?bari na hada ma tea fuskarta dauke da damuwa,

Yunkurawa tayi da niyyar tashi taji ya riketa gam tare da fadin ina zakije muyi baccinmu kinji,Daddy to bari na kawo ma tea,no ki barshi kawai mu kwanta,to my Boy kar ya farka yaga bana nan zaiyi kuka fadin Amana,ba abinda zai sameshi,kuma Aabid ai baya farkawa ko ya farka bashi da tsoro kawai ki kwanta a nan yau,

Amana ba haka ta so ba amma bata son jayayya dashi kawai sai ta kwanta

Kamar jira yakeyi jikinsa na rawa ya matso jikinta,Amana ta tsorata zuciyarta kawai bugawa takeyi jikinta sai Mazarin tsoro yake,A hankali ya manneta a jikinsa ajiyar zuciya ya saki,tudun

mazaunanta na kan sandar girmansa kasancewar ta baya ya rungumota
Rigarta ya kama ya rada mata a kunne in cire miki wannan? Kai ta girgiza masa a'a bana so,shuru yayi tare da fara shafa kafafunta zuwa cinyarta da tasa cinyar,wuyanta ya taba dai dai kashinta tare da lasar kasan kunnenta,cikin sanyin murya yace wannan kashin wuyan naki saura kadan ya cike ranar dana fara ganinki yafi haka,

Ita dai Amana duk a takure take,cike da tsoro tace ae yanzu ai kaga ina gidanka ina cin mai kyau,inci kaji da yohourt,murmushinsa me tsada ya saki,yatsanta na tsakiya na hannun dama ya sa abakinsa yana ta tsotsa Amana a zuciyarta tace kodai maye ne wannan?shi kuwa lasarta ya fara tare da shafa wuyanta a hankali yace ina sarkarki ta rannan wata siririya tana miki kyau,Amana tace ai bana kwana da sarka ko dankunne,gashinta yaci gaba da shafawa yana kullum gashinki kamshi dame kike wankewa,Amana ta fara gajiya da wannan tambaya ta Alim,A gajiye tace shampoo na,

Damammen cikinta ya shafa a kunne ya rada mata cikinki me kyau ko kina gym? Amana ta gaji da tambaya cike da shagwabar da bata San ta iya ba ta furta wai kai Daddyn nan komai sai ka tambaya dan Allah?

Hannunsa na a kan wajen wuyanta yana shafawa yayi kasa wajen kirjinta yana hadowa yana shafo dukiyar fulaninta da suke a ciki,Amana wannan lokacin feeling wani abu ta fara kamar dadi dadi,har wani lumshe ido takeyi idan ya shafo gefen na shanunta sai taji dama ya shafosu duka,
Ta rasa gane mene wannan ke damunta,shi kuwa malamin nata a yanzu wa wuce gefen na shanunta amma baya kaiwa ciki,Amana a fili ta furta a'a ni wai lafiyata kuwa,Alim yayi nisa tsabar santi sai yaji kamar Amana tace ni ayi lafiya,

Tnx dear yaci gaba
Sai wani mika takeyi tana kara mannuwa da jikin Alim,har nishi nishi takeyi kadan,Alim ne ya juyota suna facing din juna tare da tambayar ko na cire miki rigar ga hadarine ma a garin kyafi jin dadin bacci,Amana tana tsoro amma taji tana so ya Murzata ta Riga ta fara nisa itama,
Cike da kunya ta daga mishi kai kawai alamar ae,tana sunne kai tare da rufe idonta kam,
A hankali kamar me tafiyar tsutsa ya cire mata yar fingilar rigar baccinta,ba vest ba bra a jikinta pant ne kawai,

Alim nan ya fara murtsika dukiyar fulaninta masu matukar kyau da laushi hadi da sulbi,magana yaci gaba da yi suna da kyau abubuwan naki ga taushi ko na dan sha miki?da kyar Amana ta iya furta a'a ni dai ban iya haka ba.

Haka ranar ma Alim ya murji Amana yanda yakeso da salon sa lips dinta kuwa kamar zai cire mata su sosai sukayi jajir dasu,Hakan ma bai gaji ba dan Amana taga ya haukace mata ne ta tsorata shi yasa ta fashe masa da kuka,har yanzu Amana ta hanasu bacci kuka takeyi kamar yayi mata wani abu,
Tun yana lallashi ya gaji yace ke ki rufemin baki kamar na yankaki in kika dameni zan yi

babban ma yanzu,sai kace kema bakya jin dadin kinfini jin dadin ma,dan mitsitsin bakin ta turo cike da shagwaba Allah ni bana wani jin dadi,haka kikace ko? Ae din abinda dole kake takura min cewar Amana,murmushi Alim ya saki zakiyi bayani zan kamaki,

Uhm naji idan ka kamani kar ka barni da rai ma Amana ta fadi tana fari da ido,dariya Alim yayi sosai yace ok akwai ranar bayani,

Gashinsa ta fara cukwikuya masa tana yamutsashi Daddyn Aabid wai balarabe ne kai? Shuru yayi mata,to wai kai ko dan India ne kuka dawo kasar nan?nan ma shuru yayi,tace watakil ma bature ne kai,Aabid dina yafi kama da Bature,

Cikin Muryar bacci a hankali Alim yace ki daina fada min Daddy yarona dani zakina cemin Daddy da girmanki yaushe na isa na haifi kamarki,

To dama ai dan Aabid ya koya sosai nake fada ma Daddy,amma haka kawai yaushe zan mai da miji uba,

Daddy dafa da nazo gidan nan baka magana sanda muke haduwa a gari kuwa kafi kurma kurmanta ya ,pls kiyi bacci Amana kin dameni,dama kina da surutu haka?

A'a banidashi dan kawai kayi hakuri akan an koreni daga schl ka nemo min wata naci gaba da karatuna shi yasa fa nake ta ma surkulen surutuna,

Dariya Alim ya shigayi tare da fadin kin tonawa kanki asiri ai kuma,naji to kwanta kiyi bacci gobe zamuje schl din ni dama nasan haka banza baza ki bar Aabid ki shigo blanket dina ba,

Wlh kamar ka sani nafi fa son Aabid akan ka,

Da haka bacci ya kwashesu makale da juna,da asuba sukayi Sallah suka sake komawa bacci,Amana ta Riga tashi taje ta hada breakfast lafiyayye sannan ta shirya Aabid itama shirin tayi cikin wata doguwar Riga readymade black me duwatsu Golden,yanzu ta fara sabawa da kayan hausawa har acuci tayi tare da yafa gyale golden takalmi me tsini tasa Golden da Jakarta same color,sai kamshi take zubawa ta fito rike da hannun Aabid ka rantse danta ne,

Sun fara cin abincinsu Kenan kamshin Alim yayi musu sallama,sanye yake cikin wata T-shirt ruwan toka,sai wando pencil ruwan kasa,pcap dinsa ma ruwan toka haka ma takalminsa me tsadar gaske same color,

Wata siririyar sarkar azurfa ta maza ce karama makale a wuyansa, ba karamin kyau yayi baa,tunda ya fito Amana take kallonsa, ta kasa dauke idonta,

Agogon Gucci me tsadar gaske dake hannunsa ya kalla 7am dai dai,

Amana Ce ta kalli Aabid tare da zabga masa harara,Aabid Wanda ya Riga da yasan me Momy Amana take nufi,da Sauri ya furta Daddy ina kwana,

Fuska sake Alim ya Amsa masa,bayan sun gama komai Amana ta mika masa kanta Daddy daura min dankwali,ba tare da ya kalleta ba yace ban iya ba ki dage ki koya da kanki,pls Daddy ka dankwalin ta rike a hannu tare da yafa gyalenta kawai tace muje,Amana kwas kwas take tafiya da takalminta me tsini kamar zata fadi kasancewar bata saba da shi ba,suna compound takalminta ya gurde saura kadan ta fadi Alim ya riko hannunta da karfi ta fada kirjinsa suna shakar kamshin juna,Aabid har ya kai jikin mota,Wai wai Allah ya taimakeni da tuni naci kasa fadin Amana,rankwashinta yayi a kai ai u r too stubborn,kara ta saki tare da kura masa ido

kasanfa da zafi Amana ta furta,ke da kike namiji mace me kamar maza kwari ne babu,to idan ni namiji ce kenan kai dan gay ne tunda kana eh yane dani,

Karki kara dangantani da gay uban me nakeyi dake abinda dan Dane kawai nakeyi sai kuka da kike damun mutum dashi,dariya Amana tayi ai Kaine Allah danma mijina na ne kai nake kyaleka amma sai ka dinga sawa ina jin wani abu da ban taba sani ba,kuma ka dawo kamar damisa na Neman nama ni wlh tsoro kake bani,dan dai kawai Baba yace nama biyayya ne,kasan me Baba yace?girgiza mata kai Alim yayi alamar A'a.

Dariya ta karayi hmm waifa cewa yayi kar na sake na koma gidansa idan nayi yaji,kuma ko an sakeni na nemi wani gidan ba nasa ba,jiba dan Allah mutum da gidansu,idan Mum dinka watarana ta koreni dole na koma can ko?

Tunda take surutunta a compound Alim yake kallon Amana sama da kasa cike da shauki,ga wani kyau da tayi masa,a hankali ya furta ki daina tunanin zata koreki,ai ni nake aurenki,ki tabbatar duk abinda kika gani ko kika ji kin fada min,saboda a dau mataki,hannunta ya rike hade da murzawa muje ko,

Duk abinda su Alim keyi a compound Saude na kallonsu ta bangaren yan aiki.a fili Saude ta furta kamar a kunnen Hajiya,cikin jerin motocin Alim sun kai goma suka shiga cikin schl din,sai kallonsu akeyi har office din pc,.

PC jiki na rawa ya gaisa dasu Alim,takadar ya mikawa pc wacce ya kori Amana, cike da izza ya furta yimin bayani kan wannan,

Jikin PC na mazari ya kwashe yanda sukayi da Mum ya fada masa, tunda Alim yaji Mum ce ya cika da mamaki,kawai sai ya ce Aabid yaje class sannan yaja hannun Amana suka bar schl din,wata makarantar Alim ya saka Amana suka bata ss2 sannan suka dawo gida,

Amana zaune a Palo ta zuba tagumi sai tunani takeyi kan me tayiwa surukarta ta tsaneta haka,Alim ne ya fito sanye da short wando da singlet ya iske Amana zaune ta zuba tagumi,karasawa wajenta yayi tare da janye hannayenta yan mata me ya faru,jiki ba kwari Amana tace ba komai idonta ya ciko da kwalla,habarta Alim ya tallabo gashi kamar zakiyi kuka meke damunki? Kuka ne ya kwace mata ta fada jikin Alim tare da kankameshi tana ta kuka,tausayinta ya kama Alim ya shiga shafa gashinta yana dan jijjiga bayanta kamar jaririya,sai da tayi me isarta sannan ta share hawayenta ta mike zaune,hada ido suka hada da Alim sai kuwa Amana ta kyalkyale da dariya ta kara fadawa jikinsa ta boye fuskarta a kirjinsa,

Dago fuskarta yayi tare da kura mata ido wani sabon hawaye ya gani a fuskarta ya gangaro kadan,a hankali Alim yace fada min Ify me ya faru?

Da kyar ta iya furta shike nan na kusa zama bazawara,Mum zata sa ka sakeni ni an lalata min rayuwa ta na zama bazarawa,Alim ne ya kalleta to mene bayan ma ko rayuwar aure bamuyi ba,idaan ma mun rabu wani zaki aura ki manta dani,idon Amana jajir tace to ai kuma shike nan ni bazawara ce kuma sai dai na auri Tsoho me mata,

Murmushi Alim ya saki ai wasu matan sun fi son Tsohon ma,baki Amana ta tabe cike da

shagwaba tace taoho me ciki katoto ina zansa rumbun cikinsa,gashi da matarsa yafi son uwar gidansa,ke da kike kyakyawa cewar Alim,kyan banza har wani kyaune dani,komai kyanka maza su ina ruwansu,ci ma mutunci zasuyi wasu har da duka,ai kuwa wlh Daddy ko indai miji ya min ba dai dai ba na masa warning yaki jiki to inba sai na fasa masa kai da tabarya,in samu in karya masa wuya,matarsa ta zaneki ai cewar Alim,mikewa tsaye Amana tayi kut..ai kuwa wllh da sai na cire mata hanci,kasan karfi na kuwa?

Alim ya girgiza kai taya zan sani tunda bamu taba dambe ba,to kaja bakinka ka tsuke mutumina dan kar na gwada a kanka,dariya Alim yayi waye mutumin naki kai mana,yawwa dan Allah dan yimin Sandar rake kaji Daddyn Aabid,mene kuma sandar rake? Alim ya tambaya,a kafada zaka sabani kamar ka dauki jaririya kana zagawa sai kace Sandar rake sai nace Azo a siya,oya tashi muyi ta janyo hannun Alim sai kawai ya mike tsaye,Amana ta zata karfinta ne ya mikar da Alim tsaye ta kalleshi tana tsalle kamar zata buga ball ka gani ba ka gani ko ai na fada ma karfi gareni if not taya zan iya mikar dakai tsaye.

Cak Alim ya saba ta a kafada cikin sigar shagwaba tace Daddy to kace sandar rake,Alim baiyi magana ba da kyar ya iya furta ina zan kaiki?muje bedroom dina,har kan bed dinta Alim ya jefa ta dakin yabi da kallo ko ina tsab tsab gwanin sha'awa kwanciya yayi kusa da ita cike da shauki ya jawota jikinshi,a tsorace ta ja baya tana ya Alim muje sweeming pool,janshi tayi har pool ta famjama cikin ruwa,tayi tayi ya shigo amma yaki,yana bakin wajen a zaune daga shi sai short,

AsmaBaffa
[6/30, 8:55 PM] 0mmer Farouk: ✳CIRANIN AMANA✳

90-95

By
AsmaBaffa

Amana ruwan ta fara Watso masa tana tsalle da ihu cikin ruwa tare da facaka,fitowa tayi daga ita sai yar Riga karama ta manne a jikinta dukiyar fulaninta a ganinsu a rigar saboda ba bra jikinta,wani dan guntun wando short ne a jikinta,

Alim ya shagala da kallon ta bai San sanda ya mike tsaye ba,tana zuwa ta zagaya ta bayansa ta tura shi cikin ruwan,itama ta fada ciki yeeeeee na masa wayo na turashi ciki,cike da

murmushi ya jawota jikinsa a cikin ruwan,

Babu wani bata lokaci a cikin ruwan ya matso ta jikinta sosai tare da hade bakinsu waje daya ya fara tsotsa hannayensa kan kirjinta yana murzasu,Amana yanzu kam abin kara gaba yakeyi dan yanzu Alim ya murza jikinta yafi komai dadi a wajenta,

Gani takeyi baza ta iya rayuwa ba tare da Alim ba yanzu,ji take ya zame wani bangare na jikinta,amma idan ta tuno da kudirin Mum sai hankalinta ya tashi,idonta a lumshe tana karbar ruwan sakon da Alim ke watsa mata,bakinta kamar zai cinyeshi, itama ta shiga taimaka masa tana mayar masa da martani cike da kunya,abin da Amana takeji ya kai karshe, saman kirjinta Alim yake shafawa sosai

Hannunsa ta riko da kanta tana fitar da numfashi sama sama kallonta yake da sexy eye dinsa wanda suka koma ja,kasa tayi da kanta sannan cike da kunan rai tace stop it,ka daina taba ni.

Amana bata gama gigicewa ba sai a karo na  na farko da Alim yake mata wani irin salo da ko a film bata da labarin irinsa,kafafunta sun Gaza tsaiwa ganin haka yasa Alim daukanta cak suka fito daga ruwan,

Tunowa da Mum yasa Amana ta kwace jikinta ta koma dakinta da gudu ko kayan bata cire ba ta kwanta a kasa tana ta faman fushi tana kumbura,shigowa yayi ya iske tana kunci,saman bed ya zauna

Cike da nutsuwa ya furta nasan Abinda kike ma wannan fushin,kiyi hakuri ki daina  muyi magana sai musan ya za a bullowa Alamarin,haba jaruma duk juriyarki ki fara gazawa akan abinda bai kai ya kawo ba,cikin kuka tace to to Mum dinka sawa zatayi ka sakeni fa,dama tace so take taga na wulakanta a gidanka,ban san me nayi mata ba ta tsaneni,

Naji to mike ki zauna muyi magana,har kan bed suka zauna tare da kwantar da kanta a kafadarsa kamar bazai ce komai ba a hankali yace me yasa kika zama marar juriya yanzu,kinason zama dani?kai Amana ta daga ae sabo da Aabid dina bazan iya rabuwa dashi ba,kallonta Alim yayi sai yaji haushin kalamanta wato ma sabo da Aabid baza ta iya rayuwa ba shi ba,a fili yace sai sabo da Aabid ko? Kai ta daga masa yes, what of me?kai ai baka sona,taya kika San hakan?bakinta ta turo to ka taba cewa kana sona ne? Kuma ma waye zai soni a haka ni ba wata hadaddiya ba

Murmushi Alim ya saki tare da lakace mata hanci kinfi kowa haduwa ma kuwa kawai bakya abunda ya dace mace tayi kinga da ace kinayin abuuwan mata da sai anyi mamaki,sai kin zama star, to dan Allah ya zanyi na koya ni kasawa nakeyi ka taimaka ka koya min, hancinta me matukar tsini ya ja kar ki maidani dan daudu mana ina namiji me na iya,

Akwai dai wata mata da take koya irin wannan zan kaiki wajenta

Sannan zan canja miki schl amma a schl zaki dinga sa uniform saboda kar Mum tayi bincike,zaki daina driving sai dai kije a taxi,zan hana ma'aikata shigowa part dina ke zaki dinga yin komai sabo da kar Mum ta sa mana dan leken asiri,

Idan kinji door bell kar ki bude sai kin leka idan ba ni bane ko su kamal Frnd dina karki bude sai kinsa katon hijab kin rufe kwalliyar jikinki sabo da tsaro,ki kiyaye sosai bazan boye miki ba kiyi taka tsan tsan da Mum,nan Alim ya kwashe tarihinsa Dana gidansu da halayen Mum,da kudirinta kan Amana ya fada mata komai kaf,
Amana kam ta sha mamaki tana ganin family su ne kadai da matsala Ashe sauran mutane ma akwai,kowa da tasu matsalar,shauki ne ya kwashi Amana ta kwashe irin iya halin rayuwarta kadai ta fadawa Alim sai kuma sama sama da ta fada masa abin dariyar yan gidansu,

Amma duk wani halaye na iyayensu marasa kyau Dana yan uwanta bata fadawa Alim ba iya na mutuncin ta fada masa saboda mace me fadar laifin iyayenta Dana yan uwanta a gaban miji to tana zubarwa da kanta mutunci tana rage darajar iyayenta da danginta a idon miji,sai kaga mijin yana wulakanta danginta da iyayenta saboda ta gama fadawa miji halayensu na banza,da anyi abu sai mace ta kwashe ta fadawa miji
ko a cikin yan uwanki wacce kikafi yabon halayenta wajen miji zakiga a cikin danginki yafi mutuntata..

Monday Amana ta fara zuwa schl a taxi,sai taje schl take sa uniform a office din PC dinsu Ngozi,Aabid yasha kuka Daddynsu ya canjawa Momynsa schl,
Tuni Amana karatu yayi nisa sosai a new schl,
Gashi weekend tana zuwa gidan wata me gyaran jiki tana koya mata kula da miji,gyaran jiki da duk wani abu da ya danganci mata,
Rufaida kawarta har ziyartar juna sukeyi

Sosai Amana ta fara canjawa yanzu ta fara abubuwan mata masu ji da Kansu,yayin da Alim kullum take kara shiga zuciyarsa, Aabid ma yana samun tarbiyya Da kulawa sosai wajen Amana.

Saude tuni ta kaiwa Mum Alim gulmar cewa Alim son Amana yakeyi sosai yanzu ya canja mata schl ma,gashi Amana tayi kiba Da kyau,sosai Saude ta fadawa Mum karya da gaskiya, Mum kuwa takaici kishi hassada da bakin ciki ya gama kamata,jira kawai takeyi Abban Alim yayi tafiya zuwa wata kasar sanan ta fara cin uban Amana
Amana an fara zama yan mata tuni yanzu kalar tafiyarta ta fara canjawa,ga girke girke ta kara koya gyaran jiki da kula da miji,bangaren boko ma karatu yana ta tafiya haka islamiyya ba a barta a baya ba.

Kamar kullum ta dawo daga makaranta a compound taci karo da Saude tana waya bata San da wa Saude ke waya ba amma Saude Na ganin Amana ta kashe wayarta tana nuku nuku,gaba daya Saude ta gigice.
Amana bata yi wata wata ba ta rike hannun Saude gam gam ta fisge wayar, call History ta duba ta dauki number da akayi waya yanzu tasa a wayarta sannan ta danna kira still hannun Saude rike Dana Amana,Amana tayi mata ruko tsauri,

Danna kiran number tayi a wayar Saude taji bugu daya matar ta daga,Muryar Mum Alim taji

tace Saude ina jinki kince har yanzu wannan yar iskar yarinyar tana zuwa schl ko?Amana tana ji ta mannawa Saude kiran a kunne tare da cewa yi magana ko Na karyaki yanzu,Saude ta San Halin Amana ba shiri tace Uhmmm...ahmm......Haji...ya ....zan....kiraki akwai matsala,

Kashe wayar Amana tayi ma'aikata suna kallonsu Amana taja Saude part din Alim tare da jefata wani dakin ta danna key,sandar bishiya me kauri kamar kulkin yan sanda Amana ta samu,tana sauri kafin Alim ya dawo ya hanata jibgar Saude,Ashe dama itace munafukarsu,
Shiga dakin tayi ta kulle daga ita sai Saude Amana ta canja kaya zuwa Dan short din wando da T-shirt tayi kyau haka ta fara jibgar Saude ka rantse aikin Dan Sanda takeyi,

Saude kuruwar kuka kawai takeyi,amma Amana ba tausayi tana jibgar Saude tana fadin maganin irinku kenan dattijan banza munafuka,bazan taba daga miki kafa ko in saurara miki ba kika sani kuka,kika sa Mum ta sa aka min sharri aka koreni daga schl,zaki kashe min Aure ki rabani da Mijina kisa Na zama bazawara,dama tuntuni ina sa ido akanki duk abinda kikeyi ina kallonki,dama bari nayi sai na kamaki,kuma wlh a dakin nan zaki ta rayuwa ba fita ba shiga,baki San wace Amana Suleiman Harka ba,wlh har hajiyan darajar Alim takeci da Baku isa kun ko da nuna ni da yatsa ba.

Saida Amana tayiwa Saude jina jina sannan ta kwace wayar Saude ta kulleta a dakin gashi window akwai ragar rodi ba dama mutum ya iya fita.

Amana Na fitowa Alim Na sallama,Oyoyo Daddynmu cewar Amana kamar yau ta fara ganinsa tahowa Alim yayi da Niyyar rungume Amana amma da sauri ta ja baya tana dariya,Aiki nayi fa ya Alim jikina maiko da zufa,

Bashi kika ci,ae jeka ina zuwa,kitchen ta shiga ta fara girke girkenta har ta gama ta shirya a dining,Alim yunwa tasa ya ja kujera ya fara ci ba jira,Aabid ya dawo kamashi tayi ta wankeshi tas ta shiryashi yaci abinci ya huta sannan ya wuce Islamiyya,

Wanka tayi sosai sannan ta shirya cikin wani riga da skert Na lace dark brown da milk,tayi kyau matuka,sai kamshi takeyi taci kwalliya lips yasha janbaki red,
Room din Alim ta shiga da sallama,dankwalinta a hannu,

Yana zaune a sofa Amana ta karasa kusa da Alim ta wani turo mazaunanta saitin fuskarsa sannan ta zauna a cinyarsa, wai su Amana anwaye za a nunawa Alim bariki,sosai ta bawa Alim dariya,
Ido daya ya kanne tare da dage mata gira daya yana cije lips,jikinsa ne ya fara rawa idonsa ya koma ja harda hawaye kamar kwalla ta taru ciki,

Da sauri Amana ta daga cinyar Alim tana kallonsa Ify kake kuwa zazzabi ne ya dawo,shuru Alim yayi tace Kuka zakayi? Wai mene ke damunka? cikin sigar rada Alim ya jawo Amana ta kwanta a kirjinsa yana shakar kamshinta itama haka sannan ya furta kece matsalar,
Tana saman kirjinsa ta dago da kanta suka kurawa juna ido cike da shauki,a hankali ta zaro

harshenta ta lashi nasa cike da kunya ta sauka daga kan kirjinsa da gudu zata bar wajen jawota Alim yayi ta fado jikinsa, sannan yace ga iya shege ga kunyan tsiya ko? Dariya tayi tana rufe fuska tare da cewa Daddy Allah kunyarka nakeji sosai.

a hankali Alim ya hade bakin su waje daya yana aikin tsotsarsa tare da aika mata zafafan murza a jikinta,da kyar ta kwaci kanta,zata arce ya riketa yana maida numfashi sama sama,
Mene zaki gudu kullum ko romance baki bari nayi Na kirki why?
Cike da shagwaba tace to ni wai...so kake haka kawai ka maidani bazawara ka sakeni,ok wannan shi kike ganin masalaha,mufita ce wannan? Ae ai sakina zakayi watarana,
Hmmm baki da wayo ciki da haihuwa kadai zaisa mu kasance tare da juna ki bari Na baki Baby ajiya shikenan,

Kuka ta sa ta hada kanta bango wlh bazan yarda ayi min ciki ba aje a sakeni a banza nasha wahala,ok haka kikace?ae din cewar Amana, to shikenan ni kuma wlh ta karfi zan miki fadar Alim,dariya ta kyalkyale dashi har wani karfi gareka malalaci irinka ni da Na fika karfi wullu....tayi masa gwalo,kuma nace bazanyi cikin ba ehe tayi fari da ido harda murguda baki,

Dariya Alim yayi to naji sarkin karfi zo kiji wata magana muhimmiya,kusa dashi ta zauna sannan ta rike yatsunsa tana wasa dasu,
Alim ne ya fara magana jibi zanje London 2wks zanyi wani aiki zanyi ba dadewa zanyi ba,

To ka tafi dani dan darajar Allah Na hau jirgi naji irinsa,kin San Mum dai ko?matsala zata faru fa,au eh hakane kash mu an takura mana dande kawai Mum ce dole ayi mata biyayya cewar Amana,Allah kaika lafiya ya dawo da kai lfy dan Daddynmu,amma kafin Na tafi ai za a baki ajiyar Baby ko?
Nifa bana so gwara ma ka cire a ranka, yawwa Daddy Kasan..ki daina fada min Daddy Na gaya miki tam,to ba yanzu zan daina ba sai nan gaba,

Kasan Na kulle Saude A room Na jibgi shegiya,nan Amana ta bawa Alim labarin komai,da kyau cewar Alim ki kulleta karki budeta idan tana gidan Dole sai ta bawa Mum labarinmu,idan na koreta ma dole Mum sai tasa Na dawo da ita,best solution a kulleta kawai,
Ai Daddy kullum sai Na jibgeta da safe shine first breakfast dinta,da lunch sai dinner,dariya Alim yayi yace ayi mata a hankali,ai so nake Na koya mata hankali fadin Amana,

Muje Na ganta cewar Alim tare suka shiga har Alim Saude tayi miki miki,Amana duk tayi mata jina jina,hakuri ta shiga basu tana rokon Alim,Alim yace tunda ke munafuka ce matata kadai ta isheki sai yanda tace dan haka ba ruwana,Amana sabo da Saude Na wajen taje ta rungume Alim kam tana shinshina shi,Ruhina muje ka bani ajiyar Babyn nan Na matsu naji kukan jaririna,suna fitowa ta sawa Saude key sukayi gaba,Alim yasan karya Amana takeyi ba wani Baby da take nema,riketa yayi har room dinsa,da kyar Amana tana rusa ihu ta gudu daga room din ta bar Alim da wahala saboda matsananciyar sha'awar da ke damunsa.

Alim Mum da Abba da sauran mutanensa yayi musu sallama zaiyi tafiya ranar tafiyarsa

London Amanace ta kaishi Airport Amana harda kuka,da kyar ya lallasheta.

Amana da Aabid suna zaune a Palo taji karar door password ma"ana suna da baki,hijab ta nemo kato tasa sannan ta bude kofar,Mum Alim ce ta bayyana tunda tasan Alim baya nan kome tayi Alim bai sani ba bare ya fadawa Abbansa ya dau mataki kanta.

Yatsina fuska ta shigayi tana watsawa Amana kallon banza,cike da ladabi Amana tayi mata sannu da zuwa ta tsugunna har kasa tana gaisheta amma ko amsawa Mum batayi ba,

Mikewa Amana tayi taje ta kawo mata kayan motsa baki,sannan ta koma dakinta ta canja shigar rashin tarbiyarta ta da,wandon wizzy kato da riga T-shirt,gashinta ta baza ta fito,asalin tafiyarta ta da da komai shi ta fara acting.a zuciyarta tana dama darajar danki kikeci ni danayi gadon rashin tarbiyar ba duka ba zagi zanyi maganinki. Siyasa zan miki kuma sai nayi nasara da yardar Allah.

AsmaBaffa

Godiya masu comments daga yau zaku koma kullum page 1 zan baku.
[6/30, 8:56 PM] 0mmer Farouk: ✳CIRANIN AMANA✳

95-100

By
AsmaBaffa

Tunda Mum taga Amana ta fito ba hijab sai tayi tunanin dama can wannan kayan ne a jikinta,nan Mum taji sanyi a ranta ganin Amana bata canja ba yanda take da haka take yanzu sai haske kiba da kyau data kara,ta tabbatar Alim bazai taba son mace me kamar Amana ba mace kamar Namiji,Alim dinta da yake son classy girl ma.

Kallon Amana tayi shekeke tare da yatsina fuska sannan tace ke yanzu sabo da dabbanci,kauyanci da Jahilci har yau baki canja ba?
Me Dana ya rage ki dashi amma jiba shigarki,to ki jini da kyau in zaki canja ma ki canja dan idan baki canja ba sawa zanyi dana ya sakeki,
Dama Mum hanya take so ta nemo Wanda zata kafa hujja ta takurawa Amana da cin mutunci iri iri,
Ran Amana yayi mugun baci ta fusata da niyyar cin mutuncin Mum Alim,tunawa tayi surukarta ce fa kamar uwar tace,tunawa tayi mahaifiyar Mijinta ce wanda ya sota ya taimaketa,yaso danginta,ya tallafi danginta da iyayenta,ya canja musu rayuwa,mijinta Wanda takeson kasancewa dashi har karshen rayuwa,

Itace ta haifeshi da bata haifeshi ba da bata sameshi ba,kuma ita tasa danta ya aureta duk da cewa akwai manufarta amma ta taimaketa komene Na jin dadi ya sameta Mum da Alim sune sula a yanzu,
Tunani tayi idan ta wulakanta uwar mijinta kamar tayiwa uwarta ne, domin uwa uwa ce,ko uwarta akayiwa dole taji haushi Ashe idan tayiwa ta Alim shima dole bazai ji dadi ba,ko ya saketa ma ko ya tsaneta.

Shawara ta sake nan take ta fara kukan karya ta marairaice,ta dawo kalar tausayi,saukowa tayi ta durkusa gaban Mum tace kiyi hakuri Mum ba laifina bane,Alim baya kaunata,shine yace kar ya sake ganina da kaya irin Na mata ya tsaneni,baya kaunata,ni da namiji duk daya a wajensa sabo da haka ma ya sani a schl wai dan Na daina yini yana kallona,rannan ma amai ya fara yi daya kalleni,kara rushewa Amana tayi da kuka dan Allah Mum ki min rai ya sakeni Na huta,London din nan ma ban San ya tafi ba a wajen yan aiki naji labari.

Rannan ma saida ya mareni sau 5 ,wani dadi da farin cikine ya lullube Mum,amma sai a fuska ta bata rai amma Alim baya kyauta min kiyi hakuri zan yi maganinsa,

Mum ce tacewa Amana kira min Saude za muyi magana kwana biyu banji ta ba ina son bata sako,Amana murmushi tayi cike da ladabi tace ai Saude ta tafi kauye tun shekaranjiya yayanta ya rasu,

Ran Mum a bace tace amma wannan shashasha ce amma ai sai ta sanar min nayi mata alheri,Amana tace Allah sarki ai Daddyn Aabid yayi mata komai.

Mikewa Mum tayi cike da jin dadi Na ganin Amana cikin wahala,Ashe Saude duk karya take mata gashi nan Amana bata canja ba,har yanda take magana tana cijewa irin Na yan jagaliya.

Har mota Amana ta raka Mum,tana tafiya ta dawo tana sheka dariya,tare da fadin tsohuwa ki taka a sannu Na fiki iya shege,ke karamar kwaruwa ce,
Room din da ta kulle Saude ta shiga da bulalarta saida ta kara Zane Saude tas sannan ta bata abinci da ruwa ta kulle kofar ta fito,
Yau Amana dauke Aabid tayi suka koma dakin Alim nan sukayi komai Na shirin bacci suka

kwanta,tana kwanciya Kiran Alim ya shigo wayarta ta Skype wato video call,

Faskekiyar wayar ta ta dauko tana murmushi ta danna ta daga tana murmushi me kayatarwa Alim ne kwance cikin blanket,wani sanyi dadi hade da Niima ya mamaye zukatansu,Daddynmu kaje lfy?ya hanya? Lfy Almdllh ya kike ina Aabid ?gashi yana bacci yau room dinka zamu kwana,missing u Baby cewar Alim,a kunyace Amana tace me too,hey karfa ki fara min wannan shirmen kunyar banso,hope dai kunyi Sallah ko?Aabid yayi,what of u? Ai...ai..yau...uhm...kaga...bana Sallah,shine sai kinmin nuku nuku,nuna min pant dinki Na gani, Na jikina ko bana jiki Na ba?na jikinki mana,ni dai bazan iya ba,kefa matata ce kinfi so Na kalli Na turawa ko?da sauri Amana tace a'a,yace to nuna min kinji Dear,

A hankali ta dage rigar baccinta iya gwiwa ya kalli pant dinta pink color same color da rigarta,nan take Alim ya fara shiga wani Hali,a hankali yace Baby pls nuna min boobs dinki kinji,ka bari mana ka dawo pls amma ai hankalinka tashi zaiyi ka kasa control Amana ta fadi cike da shagwaba.ke zakiyi control dina.to how can I help u? Kiyi min duk abinda zaki min da hannu sai kimin da baki,

Kuka Amana zata fara yace kin San Allah indai bakiyi ba ina dawowa kishiya zan miki ba abinda ya dameni,

Baki ta turo Allah baka isa ba,badan ta so ba ta cire kayanta tas daga ita sai pant haka Alim yake ta kallon abarsa,

Dole yasata tayi romancing dinsa da baki tana ina shafa maka kaza,ina maka kaza haka har ya samu nutsuwa domin Amana ta dabance,

Haka bacci ya kwashesu gaba daya.

Kullum Alim sai sun kwana suna waya da Amana,kullum Suna zuwa schl dinsu,haka Kullum da kalar salon dukan da Amana zata yiwa Saude,

Saude ta rame tayi baki gaba daya Amana ta sauyawa Saude kamanni,a haka ma tana tausaya mata babbar macece ce.Saude kullum a magiya da tuba take yayinda a zuciyarta ta rike Amana cewar idan ta kubuta sai tayi maganin Amana.sai ta tashi Amana daga aiki.

Yau Amana da ta shiga wajen Saude kafafun Saude kawai ta jibga ta fito,yanzu Saude tuni ta nada Amana shugaban mugaye Na Nigeria gaba daya.

Mum Alim kuwa hankalinta yaki kwanciya da Amana.

Kamar kullum 1:30am Amana da Alim suna ta video call,Alim yace next wk zan dawo Baby nayi missing dinki,bazan iya zama ba,Amana kuwa kamar an mata kyautar Aljanna sabo da Murna.

Kwana sukayi suna hira,

Ranar da Alim zai dawo ranar Abba ya tafi Ethiopia wurin company sa zaiyi kamar 1mnth,Mum sai murna takeyi,Abba na tafiya Mum ta sa driver ya dauki Asiya kanwar su Alim aka kaita airport wai ta zaga dangi,

Har gida Mum tazo ta kara ganin Amana da mummunar shiga,Mum tace kai bazan iya barinki a gidan nan ba,gwara ki koma gaba Na sabo da Alim yana zalintarki,gaban Amana ya yanke ya fadi amma sai ta daure tace Allah Mum zan iya manage,no bazan yarda ya dinga cutarki ba,Amana tace Allah da dai kin barni din,Mum tace Allah muje gidana kawai,Amana ta kara cewa Allah da kin barni,a,a jeki ki shirya mu tafi ban son musu,haushi ya kama Amana a fusace tace to da an bari ya dawo ko Iya,haba tsohuwa ya kike hakane wai eh? Lallai Na tabbata baki da tarbiya to ko Alim bai isa ya ja dani ba, yaufa zai dawo Mum, ke dallah muje ni.

Cike da takaici Amana ta shirya akwatinta tsab har guda Biyu,sannan ta ba da key tace wa wani guard ya kula da saude kar ya sake ta fita,

Tuni Amana ta turawa Alim text labarin komai,Aabid ma an gama shiryashi,Amana a ranta tace kin jawowa kanki tsohuwa a gidanki za a buga game din zan canja salo bari Alim ya dawo.

Sunje gidan Mum amma abin mamaki sai batace Amana ta canja shiga ba,samu Amana tayi ta kebe waje daya ta kira kanwarta Badariya marar m a waya ta zayyane mata komai,kuma tace karta fadawa kowa a gidansu.

Wata ashariya Badariya ta lailayo tace turo min kudi nazo Lagos billahillazi sai Na juyar mata da brain din ta,mu jinin Sulaimanu harka ba a ja damu a kwana lafiya,

Dariya Amana tayi kunyi hutu ne Badariya,munyi Hutu mana yo Allah Na tuba akanki Amana ai saidai a mutu, ta Sanadiyyarki rayuwarmu take tafiya dai dai yanzu yo a kan a taba ki ai gwara Ethiopia ta kama da wuta dan uwar babarta wlh,ke in ban yo gayyar su Haladu sun rugugu da ita ba Allah dau numfashina.

Ni ban San ya akayi kika lalace ba,kika zubar da makaman yakin ba Amana,ke da kamar kanwar fir'auna kike wajen rashin mutunci amma kika kyale wata uwar miji yo Allah Na tuba dan kawai Allah ya shirye mu ne fa.Amana tace bari Badariya ai da tuni Na ragargazawa shegiya kashin kirji.

Baza ki gane ba Badariya kawai ki bani accnt din Haladu Na tura miki kudin motar zuwa,an fada miki ni yar kauyece ina da accnt dina,OK ki tura min sai Na miki transfer ko,

Jibi zan taho insha'allah,gadar zare zamu hada mata.

Sallama sukayi da Amana.

Amana ta rasa inda zata sa kanta ga Alim zai dawo ko kwalliya batayi ba Na tarbarsa kuma gidan Mum zai zo direct ya ga Amanansa da yayi missing,sai duba lokaci Amana takeyi.

Mum ce ta shige zugar motocin Alim taje taro Danta da kanta daga airport,

Tana tafiya Amana tace duk abinda zakiyi sai dai kiyi me dattin dankwali, wanka ta shige a room din da Mum ta bata ita da Aabid,wanka ta fesa sosai,Sallah la'asar tayi tare da adduoi sannan ta shirya cikin wani material me taushi da tsada sea blue color,Riga da skert ne, tayi kyau har ta gaji,jambaki purple tasa tasha powder,

Shape dinta ya fito sosai,mazaunanta kamar zasu tsaga skert ta fito,haka boobs dinta ma,fatarta sai sheki takeyi.

Kamshi kawai take bulbulawa,tana gyara gashinta taji karar motoci tasan Daddynsu ne ma

ya dawo
Cike da zumudi ta leka ta window,hangoshi tayi a tsakiyar securities, Mum ta rike hanunsa ta kankame shi.

Amana ce ta fito Palo ta zauna a kujera cike da gadara tana kada kafafu,tana jin Sallama ta mike ta fara oyoyo Daddyna ta manta da wata Mum a gefe da sauri ta fada jikin Alim,Alim yaga yanda annurin Mum ya canja gaba daya,da Sauri ya ture Amana ta fadi kasa ragwajaf,fuskarsa a murtuke ya watsawa Amana kallon banza tare da jan tsaki,sannan ya juya wajen Mum yace Mum why zaki kawo wannan sharar gidanki? Bana son ganinta.

Mum bata San sanda murmushin dadi ya kwace mata ba sabo da farin ciki ta rasa inda zata sa ranta,amma a fili kallon Amana tayi tace tashi Yata,kiyi hakuri,Alim zan saba maka wlh,

A zuciyarta kuwa cewa tayi kaga matsiyaciyar yarinya da kyau kamar aljana,gaskiya nayi gangancin aurawa Dana wannan yarinyar,wai ma ya akayi basirata ta kwace haka.
Mum Mamaki takeyi dama Amana ta iya daukan wanka haka,wani bakin ciki ne ya mamaye zuciyar Mum kar Alim yaso Amana fa.

AsmaBaffa

[7/3, 8:06 PM] +234 806 534 5129: ✳CIRANIN AMANA✳

105-110

By
AsmaBaffa

Masu comments da masu Neman ci gaba naku ne wannan page din.

Alim harga Allah bai San meke faruwa ba bai San kulla tsiyar da Amana sukewa Mum dinsa ba,saboda basayi a idonsa sai baya nan,gashi babu wata sheda da zai gane,shi yasa Mum ta kasa fada masa sabo da bata da sheda ita Mum tace tafi karfin kowa sabo da tana da kudi,
Ba sai ta fadawa Alim ba da kanta zatayi maganinsu,

Badriyya ce ta daure Mum a jikin Bed sannan tace Asha bacci Ify hukunci muke miki me sauki sabo da darajarki ke babba ce kuma Babar Alim Allah ya gani bamu cuceki ba yes.
Fitowa Badriyya tayi da niyar shiga dayan room din taji maganar Amana tana ta yiwa Alim magiya,shi kuwa sai lallabata yakeyi ta yarda,Badriyya ce taje jikin kofar tace wlh ki rufewa mutane baki aikin banza ke kadai aka taba yiwa aure,kina ta wahalar da bawan Allah,daga ciki Amana tace zan fasa miki....mhuuuuuu kawai Badriyya taji, bakin Alim ne cikin Na Amana ya hanata karasa maganar, da gudu Badriyya ta bar wajen,

Abin haushi Amana iya romance kawai ta bari akayi ta hana komai,Alim har ya fara jin haushinta,cikin dare Allah sarki Mum har tayi bacci a daure Badriyya ta je ta kwanceta ta maidata kan gado ta rufa mata bargo ta bar dakin.

Washe gari Badriyya ta Riga kowa tashi tana Palo a zaune shuru ba Wanda ya fito yan aikine kawai suke ta gyare gyare har 10,sannan Mum ta fito,Mum ce ta kurawa Badriyya ido tana balla mata harara,
Dariya Badriyya tayi tace ina kwana,yana gidan ubanki da uwarki cewar Mum,Badriyya tace tofa,komawa Mum tayi ta dakko gyale ta hau mota ta bar gidan zuwa gidan kawarta Talatu.

Alim ne ya fito cike da fushi fuska a daure kamar zai tashi sama gam ya buga kofar,Badriyya tace da alama Amana bata yarda ba, ina kwana yaya Alim,murmushi yayi tare da zama kusa da Badriyya yace Sis ya kk,Ify lau,
Naga kana fushi Ify?ko Amanace? No Ify kawai wani ne ya bata min a waya,ok Good,tana so ta tambaya tana jin kunya,

Amana ce sanye da rigar bacci ta fito itama cike da fushi kamar zata fashe tana tafiya a wani slow,ganin haka Badriyya tayi tunanin an wuce wajen,
Mikewa tsaye Badriyya tayi ta kwala ihu eho....kwallo a raga wlh,fadawa jikin Amana tayi tana murna,tureta Amana tayi ta koma kusa da Alim a kunne take masa rada dan Allah kayi hakuri zan yarda kaji,idan da gaske ne muje yanzu,no ko gobe ko jibi sai Na yarda kaji,

Matsa to karki kara kulani kuma ko Na tafi bazan dawo ba,mikewa Alim yayi ya bar gidan gaba daya,Badriyya tana gefe tana kallonsu,yana tafiya Amana ta kama kuka sosai da kyar Badriya ta lallasheta sannan suka koma daki,

Amana yanzu duk chance din da kuka samu baki yarda ba ai? Gaskiya kina zaluntarsa kina son mutum to ko ni da ban taba aure ba Allah bazanwa mijina gardama ba idan nayi aure,idan baki da lafiya kiwa girman Allah ki fada mana mu sani.

Kina ganin uwar mijinki kin San halinta fa,to Badriyya tsoro nakeji gaskiya naje sai ina da ciki ko Na haihu tasa ya sakeni,
Hmm nidai shawarata kome zai sameki ki dauka kaddarar kice baki da wata dabara,abinda Allah ya kaddara shi zai sameka sai dai karfin addua,dan haka kawai ki yarda sannan muci gaba da addua kawai shine mufita,to ance da zafi fa,Badriyya tace see u har kece zaki ji tsoron abu ke da kike da juriya kalli fa damben da kikayi a duniya,bama son iyayi kawai ki fito min a yar sulemanunki ya zaki wani dinga min iyayi da shagwaba.wani maganin mata da Umman Amana ta bayar a kawo mata su Badriyya ta dinga dirkawa Amana.

Yaushe kika canja haka Amana kinga tafiyarki da yanda kike komai yanzu ba kowacce macece zata yi ba,kin zama yar gayu ga iya tafiya da yanga saima in kinawa ya Alim shagwaba tab,kefa kin fiye shirme cewar Amana.

3pm Alim ya shigo gidan ya Tarar da Badriyya ta matse bakin Amana tana ta yi mata duren maganin Matan da aka bata a gida ta kawo kuma ta tabbatar Amana ta shanyesu,shi yasa tace dole sai ta cika alkawari.fada ne ya kaure a tsakaninsu amma Badriyya tsabar naci saida ta tabbatar Amana ta shanye,Amana ta tashi da niyyar lakadawa Badriyya dukan tsiya Alim ya riketa ram kallonta kawai yayi yasa ta gane mummunan gargadi yayi mata lakwas tayi.

Alim yace Badriyya ta shirya da yamma zai kaita yawo ta ga gari,nifa Daddy baza kaje dani ba? ae bazanje dake ba,shikenan cewar Amana,tausayinta yaji Amma yasan idan Amana ta bisu to dole suyi fada da Badriyya tunda Badriyya akwai tsokana,Amana da saurin fushi da zuciya.

Har yamma Mum bata dawo ba,Alim ne cikin shiga ta fitar asiri yasha kyau,room din Alim ya shiga Badriyya sanye da hijab tace yawwa ya Alim kaga ta hanani nasa kayanta kuma nawa Na yan kyauye ne,
Da kansa ya zabowa Badriyya kayan sawa cikin kalar Na Amana,Shiryawa tayi tayi kyau sosai dama Badriyya ma tana da haske da kyanta,
Har mota Amana ta rakasu zasu wuce tace baza kamin kiss ba yau,eh din cewar Alim,kai dan Allah Daddyna,
Zarab Badriyya tace wai Daddy ke wai me yasa har yau jinin kauyece ke ana sa sweet name kina wani Daddy local u.

Badriyya Na rantse sai na  yi maganinki ina magana kina samin baki,ka gani ko Daddy Allah kayi mata Fada zan zaneta,ta fada din cewar Alim ke yar kauyece da mecece ke komai baki iya ba.ke zo mu tafi daga yau ma kece ta karfen tawa,
Motar Driver yaja suka tafi tunda suka fita suke ta zaga gari yana kaita wurare da yawa dama

ita Badriyya tsabar shige shigen yan birni yasa ta waye tuni sai abinda ba a rasa ba,

Kayan ciye ciye ya siya musu iri iri sannan suka dawo gida,Mum har yau bata dawo ba,Amana tana sallar isha suka shugo,Alim Mum ya kira a waya yaji ko ta dawo amma taki dagawa har text ya mata ba reply,

Badriyya dakinta ta wuce tayi wanka da sallah,Alim dama shi ya tsaya a masallaci yayi tasa,

Amana tana idar da sallah ta haura kan gadon kusa da Alim,hijab ya cire mata wow ya furta domin Amana wani wando creazy jean ne a jikinta pencil blue,da rigarta black tayi kyau kamar a saceta ta baza gashin sai kamshi takeyi,hugging dinta Alim yayi tare da sinsinata,Amana tace sannu da zuwa ina uwar rikici tayi? Taje Sallah ai kin fita rikici cewar Alim,ki daina yi mata fada pls,bata da kunyane fadin Amana,Alim yace banaso kinji Na fada miki indai kina mata masifa zamu bata dake kuma kin San halina,to Badriyyan ai kanwatace kaji ikon Allah Amana ta fada tana wani narke masa, ahaf 2 mnths fa kika bata kacal,amma dai Na girmeta.

Mikewa Alim yayi ya shige wanka a mota ya dauko 3qtr da singlet ya shirya,Amana ta gyara masa gashinsa,kira mana Badriyya musha Dariya,bazan kirata ba shike nan ko hira baza muyi ba ka dauketa kunje yawo kun Dade yanzu zaka ce tazo ta takura min da zancen banza.

Bari naje da kaina to,kumburo baki tayi cike da shagwaba tace bari naje ai bance bazanje ba ko,cike da tafiyar ta ta takama da yauki ta je ke kizo malama cewar Amana,Badriyya tace ke yane eh nima fa Na iya jagaliyancin nan kar kiga nazo wajenki ki dinga rainani da kadan kika girmeni fa,Amana tafiya tayi da niyyar shako Badriyya amma sai ta zille ta fada dakin Amana da gudu,ya Alim kayiwa matarka fada kagani ko,

Kyaleta bata isa tayi komai ba,kayan ciye ciyen da suka siyo Amana ta baje musu su uku suke ta faman ci suna hira wasa da dariya,

Kofa aka banko ba sallama,Momi ce ta dawo,kallonsu tayi taga Amana da Badriyya a ranta tace tsofaffin yan barikine wannan yara anyi kwarkwararrun yan iska nan wajen,shike nan Alim dina Na shiga uku Na dauko ruwan dafa kaina.

Badriyya ce ta faki idon Alim tayiwa Mum gwalo,cinyar kaza ta daga sama wai dan ta gani taji haushi,rumtse ido Mum tayi da karfi ta rasa wace tafi wata iskanci a cikin su Amana,A ranta tace Amana tafi muguntа da karfi,bakuwa Badriyya tafi iya shege da rainin tsiya,idonta a bude yake,Mum a ranta tace da Badriyyace tazo Cirani da yanzu ta tabbata an koneta da tyre mota a lagos.

Amana tace sannu da Zuwa Mum,Alim ma haka,Badriyya tace Mum an dawo lfy munyi kewarki Mum kin Dade a shagwabe tace wai ina kikaje baki je dani naga gari ba,

Tsaki Mum taja tayi gaba,Alim haushin Mum yaji bata kula kanwar matarsa abin sonsa ba,shi Alim akan Mum ta kulashi gwara ta dinga mutunta Amanarsa da danginta.

Badriyya cewa tayi ya Alim bari inje muyi hira da Mum naga kamar Na mata laifi,ok kawai Alim yace,Badriyya tana shiga dakin Mum da sallama ta zauna kusa da Mum,hada ido sukayi badriyya tace how far? Badriya kure karshen turancinta tayi tace Mum ni as u see so no fear no

mercy,mu da kike ganinmu duk yan gidanmu creaminal ne,mu a gidanmu aka sauke container iskanci Na Nigeria sannan muka sanmuku.

Mu da kike ganinmu mu sassara mutum ba komai bane,Anty Amana da kike gani darajar ki take gani da tuni tayi guduwa guduwa dake,

Wlh nayi miki gargadi Yau idan Na ganki kusa da dakin Amana wlh ba daureki kadai zanyi ba sai Na miki abinda baza ki manta ba har ki koma ga rabbil samawati kinji Na rantse da zatin Allah Badriyya tana fadi cike da bala'i.

Ke wacce irin uwar mijice ko kunya bakya ji,

Mum tsorata tayi ta kasa magana haka har Badriyya ta gama cakakinta ta bar dakin,tana tafiya Mum tace shegu yan daba zanyi maganinku sai Na fanshe abinda kuka min kan iyayenku.

Badriyya tana fitowa ta kwankwasa Amana ta leko tace gudnight Anty pls ki bari asa kwallo a raga,rankwashi Amana ta zubawa Badriyya,lekowa Alim yayi tare da kyaftawa Badriyya ido cewar shirye shiryen fara wasan ake,

Dariya Badriyya tayi tace Ya Alim ina tuna ma no fear no mercy no daga  kafa,make sure u Bararraka her,am waiting for u early in the morning call me make I gasa her with Hot water, abeg don't wash her I wl do the job,make am turara her with steaming water duk sunan da Badriyya ta kasa fada sai ta fada da Hausa.

Daga Alim har Amana Dariya suke ta kyalkyalawa Badriyya ta zabgo turanci harda broken (pidgin) english ita ga yar lagos.

Kofa suka kulle suna ta faman dariya kamar tababbu,

Badriyya zagaye takeyi a Palo sabo da kar Mum tazo ta bata wasa,

Ai kuwa Mum ce ta fito da zafin Nama zata je dakin Amana,Badriyya ce   ta riketa ram,Mum tace dan ubanki sakeni a yau sai an saki yar uwar taki, a Daren nan Na rantse sai kun bar gidan nan,

Kara surar Mum Badriyya tayi ta kaita can wajen compound har garden inda ba wanda zai gansu ta daure Mum a bishiya,abin shocking ta dakko dan karami wanda ta siya a kano city wajen wasu kantin yan china na electronic da suke saidawa masu gyaran wuta,

Harshen Mum ta zaro ta ta rike sannan ta danna shocking stick a kai,sai ga Mum ta hada gumi tana rawar banjo kirkirkirkirrrrrrr yayin da Alim da Amana wasa yayi wasa, wasa ya dau dadi,harka tayi harka ita kanta Amana taji ta dau chargi,wasa na kyau Amana ta kasa yin komai na ganin ta hana zura kwallo a raga,babu kwari babu kuzari Full light ta kawo sai Maida martani takeyi itama tana nunawa Alim kwarewarta,

Abinda ya kara birge Alim yanda Amana tayi mugun iya sarrafshi,yanda Amana take da kuzari haka take sarrafa Alim yanda ya kamata,ko hugging idan Amana tayiwa Alim sosai yake Jinsa zam zam saboda Amana jarima ce,

Sucking down Din Amana Alim yakeyi yayinda Amana ta haukace wa Alim gaba daya,

Alim rada yayiwa Amana mine akwai dadi ne?
Tana kukan dadi tace Baby kaci gaba tare da jawo hannayen Alim gaba daya ta daura kirjinta.

Mum ta galabaita tasha wahala hannun Badriyya ko motsi batayi sosai,Badriyya daukan Mum tayi ta dawo da ita room dinta,tare da kwantar da ita a Bed dinta ta lullubeta tace sai da safe kuma kika fadawa wani gobe wlh taki ta kare,kuma kika sa Alim ya saki matarsa kafin mu bar gidan sai mun yankaki.
Mum da kyar tace tsinannu Allah ya isa kuma zaku gani wlh,

Ga dinner nan readers ku sharbi dadinku lol love u All.

AsmaBaffa
[7/3, 8:06 PM] +234 806 534 5129: ✳CIRANIN AMANA✳

110-15

By
AsmaBaffa

Yau kar Ku sa Rai da dinner,ina kaunarku masu comments.

Amana ta gama fita daga hayyacinta amma Alim yace Na Fiki susucewa domin Alim ji yake kamar yau ya taba aure a duniya,sai yaga lallai yaune first night dinsa Na gaskiya domin yau ne yake shirin farawa da wacce ya dade yana kauna,

Bakinsa ya hade Dana Amana a hankali yake wara cinyoyinta yana shirin shigarta kenan ta matse kafafunta tana magiya dan Allah kayi hakuri kaji,da kyar Alim ya iya furta karya kike yarinya kinji Na ma rantse wlh wlh yau bazan taba kyaleki ba ko Mum ce tazo a gabanta zanyi idan kika ga Na kyaleki to Allah ne ya karbi rayuwata.

Allah ya gani Na tausaya miki kuma Na miki uzuri nayi hakuri gwara ki tsaya Na biki a hankali ko jikinki ya fada miki,kara manneta yayi a jikinsa,Amana kam tayi suman kwance

Tana ji tana gani yaci gaba da sarrafa ta,ta karfi ya ware kafafunta ya bankareta gaba daya kamar bankararriyar kaza,a hankali ya jefa kwanlonsa a raga,a hankali yake binta,Amana sarkin juriya jaruma duk da azabar da takeji batayi kuka ba kuma ba yakushi ba cizo,amma irin yanda ta kankame Alim jikinta Na karkawar azabar da take sha,rikon tsauri tayi masa iya karfinta,

Alim kuwa rikitibar sa yake sha kawai sambatun da yake ya zarta tunanin me tunani,abin nasa ya wuce hankali kamar hauka sabon kamu,cikin sambatunsa yace ke da kishiya sai dai hurul ein,badan sun zama dole a aljanna ba da nemi Alfarma a barmin iya ke kadai kin isheni.

Amanata Na baki gidana dake unguwar Ogeota lagos,Na bawa ummanki kujerar maka,da Badriyya yar aljanna me hadin Alheri,

Badriyya Allah ya mata albarka itama Na bata kujerar makka,dani dake duk zamuje Saudiya,Haladu Na daukeshi aiki a company Na Na kano tare da Hamza,

Na dau Nauyin bikin Badriyya idan ya tashi ni zan mata komai da komai,kuka Amana ta fara yanzu kam juriyarta ta kare,Alim ya fara lallashinta amma shi dadin yayi masa yawa kawai sai shima ya fara kuka wiwi to yarasa a inda hankalinsa yake kam,a kukan ma yazo har yafi Amana yi dan nasa sautin sosai yake sheka kayansa da ace da mutane a Palo da gaba daya sai sunji Alim,

Amana shuru tayi tana jin azabarta ga Alim sai kuka yake yana ta baje kolinsa wannan shine kura da cin duka gardi da kwace kudin

Alim cikin sheshekar kuka yace ....I love...u....I can't do without u Mine,

Ban San ya zan fasalta irin kaunar da nake miki ba,tuntuni nake sonki,karya na miki nake boye miki,sonkine dalilin da yasa nake kai Aabid wajenki,sonki yasa Na kawoki gidana,ke ko Mum baza ta iya sani in sakeki ba,da Na sakeki gwara Na hau titi mota ta markadeni,

Stile ya canja tare da fadin Badriyya tafi kowa a wajena cikin danginki,ke har nawa dangin Badriyya ta fisu Matsayi,kuka Amana ta kara saki tace ni naji mun gode dan Allah ka kyaleni haka,amma ina saida Alim ya Dade yana ta abu daya yaji shi komai zam zam sannan ya hakura badan ya so ba shi baiki a kwana a haka ba.

Duk ac dake tashi bai hana Alim hada zufa ba,shuru sukayi kowa yana maida numfashi,saida

ya huta sosai sannan ya mike tun a lokacin Alim sai wani dariyar dadi yake har yayi wanka ya tsarkake jikinsa Murmushi kawai yakeyi ya fito yana ta kamshi ya fesa body spray ya sa nightwear dinsa yazo ya dauki Amana itama tun a Daren ya gasata sosai sannan ya mata wanka,tayi Na tsarki Bedsheet ya canja tare da kwantar da ita sannan ya bude kofar ya fito zai kai bedsheet washing machine ya wanke, Allah sarki Badriyya ya hango a kujera ta kafa ta tsare har barci ya kwasheta a kujera.murmushi ya saki yace kema Allah baki miji Na gari yarinya baki san dadin harkar ba ma kina hada Alkhairi ina ga kin sani,

Wucewa yayi ya wanke yadin gadon ya shanya ya dawo,time ya duba har 4am tayi,sabo da Mum kar ta sa musu ido da safe ya daure ya gyara komai har room din kamar ba ayi komai ba,

Alwala yayi ya dinga nafeela ba ji ba gani,Amana ya fara yiwa addua sai Badriyya ta biyu,yana zaune har asuba tayi, yayi sallar asubarsa da azkar sannan ya kwanta kusa da Amana dake ta kwasar bacci ya kankame Abarsa tsabar maitar Alim zigidir suke baccinsu cikin blanket,ko juyi yayi to sai yayi dan murje mujensa,

Da sassafe Badriyya ta koma dakinta tayi sallah taci gaba da baccinta,Mum kuwa tana yin Sallah ta sakko kasa ta fara dukan dakin su Amana da karfi kamar zata balla kofar,
Alim yaji sarai yasan itace yaki budewa yaci gaba da baccinsa,ita kuwa Mum yi takeyi bata fasa ba,Alim haushi yake ji Mum zata tashi Amanarsa daga bacci haka kawai,kunnen Amana ya toshe da tafukan hannunsa dan kar ma ta farka,spare key Mum ta dakko ta zura rashin sa'ar daya Alim daya manta ya zare key din ya ajiye saman wardrobe, haka Mum ta dinga gwada spares keys har ta bude kofar su Alim,banko kofar tayi,tana zuwa ta daga tsawa Alim.....shuru Alim yayi ya kama baccin karya,kasa hakuri Mum tayi cike da bala'i ta yaye musu blanket tab babbar magana saura kadan blanket ya sauke kasa cikin zafin nama Alim ya rike bargon kam tare da cukwikuyeshi a jikinsu iya cikinsu zuwa saman kirjinsu ne kawai ya bayyana,dole taga kirjin Amana,

Da badan Alim ya rike ba da tuni ta gansu tsirara,bakin ciki ne ya kama Alim takaici ya addabeshi,amma ko kunyarta baiji ba saboda Mum tana ta zubar da darajarta,
Lullube jikinsu yayi sosai amma Mum ko a jikinta tace ubanme kakeyi har yanzu baka je masallaci ba,ka wani kwanta ka tashi ka shirya lokacin office ya kusa,
Shuru Alim ya mata,tace wlh zan kwada ma mari Alim,ubanme kakeyi ka like a gindin mace zaka watsar da aikinka,ka tashi ka fito wlh ko Na sa kayi abinda baka so,

To kije zan tashi ai cewar Alim kuma kin San time din Dana ke zuwa office Mum amma yanzufa akayi sallar asuba,ae ka fito Na gayamaka wlh aikin banza aikin wofi,ni zaku mayar yar iska Mum ta fadi tana kumfar baki tare da ficewa,minti biyar ta kara dawowa ya Na jika shuru ne?kazo Na baka abinci ka tafi, wanka zan shiga cewar Alim,uwarka kakeyi a kan gadon wai,
Amana tana jinsu tace pls tashi kaje kar ka jawo tayi fushi dakai,Fushin iyaye bala'i ne ga dansu,jeka kayi wankan a room dinta,banaso wani abu ya sameka sanadiyyar sabawa iyaye,idan ya shafeka ya shafeni Na shiga masifa nima,

Baki da lafiya fa wa zai kula da ke,jeka pls zan kula da kaina ga sister tana nan fa ka San halin Badriyya dole zata min komai kana da wakiliya jeka,duk maganar nan da Amana takeyi idonta a rufe yake tana cijje lips,

Kiss ya Manna mata a saman lips sannan ya dan shafa boobs dinta sannan ya fito daga cikin bargon rigar bacci da pant ya dakko a akwatin Amana ya sa mata sannan ya fita.

Yana fita ya ga Mum manne jikin kofarsu tana musu labe yaji haushi sosai ransa bace ya fito ya wuceta ya haura sama dakinta,Dadi Mum ta kama ji tana murmushi tabi bayan Alim yauma a gabanta Alim ya shirya ta mika masa wani sabon dinkin shadda me tsadar gaske fara kal,dinkin fitted ne yayi kyau sosai sai shekin amarci yake,

Yana so ya koma wajen  Amana amma Mum abinci ta bashi yaci ta rakashi har Mota sai da taga motocin Alim sun bar gidan sannan ta dawo ta shirya Itama ta fita unguwa ko ina zata je oho masu aiki ta fadawa sai dare zata dawo,

Badriyya ce ta fito tasha kwalliya kayan Amana tasa doguwar Riga baka readymade, a dining ta zauna tana kwalawa masu girkin gidan abinci,abinci taci kalar da takeso tare da tambaya ina Mum,Ibr yan aiki suka bata ta fita sai dare,

Alim ne ya shigo da sauri domin yaji Mum tace zata fita sai dare zata dawo Ashe bai tafi office ba labewa yayi a hanya yana ganin tafiyarta ya umarci securities dinsa suka dawo gida,

Badriyya ya iske a dining ta gama cin abinci kenan da sauri taje wajensa badai a gidanka ka kwana ba?adduoi ya fara zabgawa Badriyya da bata gane kan zancen ba,tace ya Alim kaga kyan da ka kara kuwa,murmushi ya saki yace baza ki gane ba kanwata, ko dai kwallo cikin raga?Badriyya ta tambaya,Alim yace ai sis penalty Na samu masu kyau,Allah sarki Amana ta tsufa amma shine kaki kirana nayi mata wanka,

Dariya Alim yayi yaushe zan barki kiga sirrina wajen danake buga kwallo,kinsan ma Anty ba barinki zatayi ba,ni ba Antyna bace kawata ce she is my frnds,ok muje kiyi mata wankan to,har daki suka shiga da Alim,Amana bacci takeyi da kyar tayi sallah ta koma bacci,

Badriya tsalle tayi ta fada bed din ta matso wata babbar kalma da ta iya a turanci tace felicitation (congratulation) Amana sannu,farkawa Amana tayi idonta ya kawo kwalla,da Sauri Alim yaje ya rungume Abarsa yana lallashinta,kukan ta fara sosai,shewa Badriyya tayi tace ahayye ayyiriri wannan kukan Alkhairi ne,bama son shagwaba idan zaki tashi ki tashi malama,rada Badriyya tayiwa Amana a kunne today ma in the middle night zamu jefa kwallonmu .

Kuka Amana tasa cike da shagwaba Murya kasa kasa tace ya Alim ka ganta ko,sis Zamu zaneki kina takura mana fa,Amana tana jikin Alim suna kan gadon Har Badriyya,kara rada mata Badriyya tayi zamu ganki da tirtsi bulli cikinki katoto wullu,amai shaaa,tofar da yawu,Amana idan kin isa tashi ki Bini da gudu yanzu Na gani ko ki zaneni idan kin isa,

Kuka Amana ta kara saki Daddy kajita ko,kyaleta zanyi maganinta cewar Alim,Badriyya ce ta kara kama kunnen Amana tana mata rada ya dagargaza wajen ko?

Rankwashi Alim ya zubawa Badriyya tashi ki tafi marar kunya,kije Huzaifa yanzu zaizo daga kano ki koma Palo ki tarbeshi kafin nayiwa mine wanka.

Ya Alim wai Huzaifan nan kyakyawa da kukaje dashi gidanmu a kauye?yes shi Wanda kuke ta surutu tare cousin dina me, Ok to bari naje palon.
Wanka Alim yayiwa Amana ya shiryata har kwalliya shi yayi mata, simple doguwar riga ya sa mata,suna kamshi,abinci ya bata a baki tana ci tana goge kwalla,
Magani ya bata tasha ya ja hannunta suka dawo Palo,har Yau Huzaifa baai karaso ba,Badriyya ta gaji ta koma dakinta ta kwanta.

Badriyya akwai barkwanci da surutu ga tsokana,Amma akwai sanin ya kamata,gata da son yan uwanta,ga hangen nesa,itama fara ce kawai haske Amana zata fita,kuma da kyanta bata da makusa ko kadan,
Huzaifa ne ya shigo da sallama,Amana tana kwance jikin Alim dake karanta jarida,hannu ya mikawa Huzaifa suka gaisa,malam tun dazu muke jiranka ka shanyamu,wlh flight ne suka kara mana time kafin mu tashi,driver Alim ne ya kaiwa Huzaifa akwatinsa dakin Alim Na da,

Amana ta gaishe da Huzaifa yana tsokanarta Amarya yane kalau kike kuwa? Lafiyanta kalau shagwaba ce ta motsa yau cewar Alim,
Badriyya Alim ya kwalawa kira sweet sis,shuru ba amsa,Darling sis?shuru nama, Hadin Alkhairi? Badriyya tanaji ance hadin Alkhiri tasan da ita ake,fitowa tayi a nutse,dariya Huzaifa yayi au Ashe ma kawata ce a gidan naku,kallonsa Badriyya tayi tace dan duniya dan duniya hayakin wiwi ko hakayin Benson ne?
Ai Na daina kulaki baki da kirki ko kira babu,wai ace yarinyar nan har number ta na baki fa amma hmmm,

Murmushi Badriyya tayi tare da cewa kai dai bari ya Huzaifa labari sai an zauna,bari tukin tumbinka ya dauka,kice akwai labari?of course ta fada tana wal wali da ido,dariya Huzaifa yayi yan mata bakya sanya tace ai mune on top in bamu tafiya bata ja.

AsmaBaffa
✳CIRANIN AMANA✳

115-120

By
AsmaBaffa

Gaba dayansu hira sukeyi a palon banda Amana dake lafke a jikin Alim tana ta wasa da Dan gemunsa kadan tare da tura yatsanta Na tsakiya a bakinsa,aikin dake jikin shaddarsa a kirjinsa ta koma yin wasa dashi,Huzaifa da Badriyya ne suka kalli juna suna kafta ido tare da gulmar Amana,

Alim yana kallonsu yace munafiki dai baiji dadin halinsa ba,dariya sukayi gaba daya,daukan Amana yayi yace kuci kanku mu munyi room,

Room Alim ya koma suka kwanta da Amana sai take taken Neman kari yakeyi,a sanyaye Amana tace kawai ka dakko wuka ka yankani ka huta da wannan azabar da kake shirin karamin,kyaleta Alim yayi to Na hakura amma ki daina jagwalgwalani tun dazu kike tabe tabe a jikina,

Huzaifa wanka yayi suka yi lunch yasa Badriyya ta shirya,key din mota ya karba suka bar gidan yawo suka tafi,

Amana da oganta suna Bed yaki bari ma ta motsa ko nan da can,Aabid ne ya dawo daga schl yar aiki ce ta shiryashi sannan yayi knocking kofar Amana,Alim ne ya bude kofar daga shi sai short Daddy ina Momy? Tana bacci my son jeka kaci abincinka ka huta ka wuce Islamiyya, shagwaba Aabid ya fara shi Momy Ce zata bashi abincin da kanta,zan mareka Aabid ka iya ci da kanka fa get lost baza ta fito ba,

Cikin fushi Aabid ya nufi dining,Alim ya rufe kofa harda sa key a kofar,Amana tana daga kwance ta fara masifa wlh ka daina korar min da,ina jinka fa ya zaka takurawa my son,

Barko ya rufa musu tare da manneta a jikinsa zo nan kiji,Romancing dinta ya shigayi sosai har sai da ya samu nutsuwa,

Sai yamma lis sannan su Huzaifa suka dawo,

Mum ce tare da gungun yan daba ita da Aminiyarta tana basu address gidan da zasuje suyi mata aiki ko su Amana zata sa a kashe mata Oho,

Huzaifa ne kwance saman gado sai tunanin Badriyya Frnd dinsa yake,ya rasa inda zai sa kansa sai gizo take masa a idonsa,ya kasa zaune ya kasa tsaye,har jira yakeyi gari ya waye ya samu ya fadawa Badriyya abinda ke ransa,

Mum ta dawo gida cikin dare,12:30 Na dare ta fito ta fara bugun kofar  su Amana,wannan time din Huzaifa da Badriyya ne suka fito,Huzaifa ne yace Mum Ashe kece ma,tsaki ta ja tare da gallawa Huzaifa Harara saboda dangin mijinta ne,ita kuwa Mum babu Wanda ta tsana a duniya irin dangin Mijinta,bata kaunarsu,

Alim ne ya fito sanye da jalabiya,batayi magana ba kawai ta fesawa Alim Kyakyawan mari tace wuce ka tafi gidanka,wannan tsinaniyar yarinyar ce tasa kabar gidanka ka dawo nan ka

tare,
Alim dafe da kunci Amana ta fito a fusace ta kama lailayawa Alim kumatu tana hura masa da bakinta,
Babyna kayi hakuri komai lokacine,rayuwace kaddararka ce kaji zo ka tafi kaji,

Kan uwarki ce kaddara,ubanki da uwarki ce kaddarar,Annamimiya karuwa tsinanniya tambadaddiya wlh ki bani 2 days sai kinji a jikinki,zakiga yanda zan miki,an fada miki kaunarki nakeyi to ban taba kaunarki ba aura miki Alim nayi domin naga kin wulakanta a duniya,kin koma Bazawara kin lalace shegiya jaraba,kaya,ja'iba,kwarababbiya,makira,talakawa matsiyata da ubanki kwarto me Neman mata da Matan aure,yayan zina,yayan mazinata shegu marasa asali,saura kadan Ku fara ganin hukuncina.

Badriyya ce tace ko a jikinmu kanki akeji,Kai Alim koma ciki kaida Anty Amana Body no be rock,body no be tree and Body no be firewood kuje Ku Dora daga inda kuka tsaya i will Handle the case cewar Badriyya,
Alim kuwa juyawa yayi fuska ba rahma zai shiga dakin Amana,Mum tace idan ka taka daga nan Allah ya isa Alim ban yafe ma ba,nono Na daka sha ban yafema ba shashasha shanyayye,

Daga Alim har Amana hawayene ya fara kwarara a idonsu,Alim har kasa yakai yana rokon Mum,Mum tace ai tsinuwar bata fara aiki ba tukun sai kaki yin abinda na saka,yanzu Na yafema son bazan taba tsine ma ba,amma idan kana son farin cikina to a wannan satin wlh wlh kaji Na rantse Qurani izu sittin idan baka saki Amana ba to sai Na tsine maka kabi duniya Mum tana kumfar baki tare da kafe ido.

Badriyya da Huzaifa sunyi suman tsaye yayinda Amana kukan da take ya tsaya cak idonta ya bushe,tsawa Mum ta dakawa Alim ka tafi gidanka kar Na kara ganinka a gidan nan saida takadar wannan tsinanniyar ta nuna Amana.

Ba tare da ya furta ko ehemba ya ja hannun Huzaifa zo mu tafi gidana kawai,Badriyya Alim ya kalla yace kin San komai sis handle the case pls kiyi komai daya dace,Amana ya kalla idonsa jajir kamar zai sa kuka ido ya kaftawa Amana never mind nothing wl.....

Mum tace nothing din kutmar ubanka Alim fice ka bani waje stupid kidahumi me kwakwalwar kifi,akwati huzaifa ya dakko tare da mannawa Badriyya kiss a goshi princess sai gobe,shekeke Mum ta kalli Badriyya da Huzaifa tace haka aka iya,nan akafi karfi inba kazanta ba ubanwa zai tsotsi fatar mutum ko bakinsa shedanunun kutmar uwa kawai,tuni su Alim sunyi gaba,dariyya Badriyya tayi sosai ta kalli Mum tace hhhhhh Ashe dama yar kauyece ko kiss bakyayi kidahuma lallai Abba yayi kokari Ashe kawai lafkewa kikeyi a bed,rabone kawai ya rantse kika haifi yara,shi yasa Ashe kasurgumar jahilace ke sai yau Allah ya tona ki,

Amana ce ta damko Mum yayinda Badriyya ta fada toilet ta cika baho da ruwa ta fito Mum sai wutsil wutsil takeyi tana dura zaki iri iri na banza.
Amana ce ta daga kafafun Mum tayi tsaiwar wata kanta suka dilmiyya a ruwan yayin da

Badriyya ta hau jibgar Mum ba ji ba gani,Amana kuma tana danna kan Mum a ruwa tana zarowa, Mum ihu da kuruwa takeyi tana Neman agaji,

Badriyya tace sai kin janye kudirin Sakin da zakisa danki yi,dan kankanin lokaci Mum ta fita daga hayyacinta amma duk da haka cewa tayi wlh sai Dana ya sakeki saki uku ma shegiya,

Shocking stick Amana ta dakko Na Badriyya,suka kwantar da Mum suna jibgarta suna danna mata shocking ,wuka Badriyya ta dakko tana sheki da kyalli ta dora mata a wuya,ta nuna Mum tare da mika mata waya tace kira danki Alim wlh kice kin janye kudirinki Na saki,wlh idan kuma kikace munyi miki Wani abu wlh Ethiopia ma sai sunji labari,Amana tace matsiyaciyar uwa me suffar kwadin ruwa

Tsorata Mum tayi taga su Amanafa ba Imani garesu ba,ba shiri ta kira Alim,bugu daya ya daga tace kaci sa'a Na janye kudirin saki,Badriyya ce ta kwandala mata torchlight a kanta,kara ta saki Alim ta waya yace lafiya Mum?Mum tace no bigewa nayi kuma Na baka izini kullum kazo kaga matarka sau daya a rana,ai Alim sujjada yayiwa Allah yana ta zubawa Mum godiya sannan ya kashe wayarsa,

Labari ya bawa Huzaifa sukayi ta Murna,Amana ce ta cisgi gashin Mum tace ba sau daya a rana zaizo ganina ba sai yanda ya ga dama,

Badriyyace tace haba Amana kefa muguntarki tayi yawa bakisan ayi abun hankali ba,au dan uwarki nice marar hankalin?to da mece? Sabo da Allah ta hakura ta janye kudirinta sai kice sai an kara ni wlh bana son haka,

Sai Na daina tayaki fadan ma,au to ni Na kawoki shashasha marar kunya marar tarbiyya,yawwa bakuwarmu Mum tacewa Badriyya,kafa Badriyya tasa ta Make bakin Mum tare da cewa fadan yan Uwane....ohhhh Mum ta kwalla kururuwa.

Ai wlh Na Fiki tarbiyya cewar Badriyya ta fadawa Amana,zan tattakaki ni mate dinkice?Amana ta fada tare da fara masgar Badriyya,Badriyya da bakar zuciya tsalle tayi itama suka kaure Suna ta Chinese tare da tattake Mum da kafafunsu garin kokawa,Amana tace dan kinga ina kyaleki,Badriyya tana haki tace ni amfada miki kyaleki zanyi,

Mum tana ganin haka ta sulale ta tsere dakinta harda sa key tana yanzu idan rashin Imaninsu ya juyo zuwa zasuyi su karasani,shegu sai karfin tsiya kamar samudawa.

Amana ana ta kokawa har taji ciwo a kafa jini Na fita,Badriyya kuwa lebe ya fashe sosai harda goshinta,rashin sa'a akayi Amana ta bige saitin gabanta da jikin sink na ruwa da ake Brush da wanke hannu,

Faduwa tayi ta kama kuka a kasa tana kuka tare da dafe wajen domin an mata famu sosai,

Badriyya Na gefe tana haki tausayin Amana ne ya lullubeta wajenta ta tsugunna tana ta lallashinta,sannan ta cire mata doguwar rigar dake jikinta, Amana daga ita sai bra da pant,

Ruwan zafi Badriyya ta Tara cikin baho me zafi rau ta zuba gishiri,pant ta kama zata cirewa

Amana,Amana ta bige hannunta cike da shagwaba tace Allah sai na fadawa Mijina,Dariya Badriyya tayi tace inye kaga masu miji, wlh Amana kin iya shagwaba dole Alim ya manne miki.

Allah gasaki zanyi zan rufe idona wlh trust me Badriyya ta furta tana cirewa Amana Pant tare da rufe idonta kam tana baki da kamata Amana nice taki babu yanda zakiyi kuma nasan baza ki iya wanka da kanki ba tunda kinyi famu,
Idon Badriyya a rufe ta cirewa Amana kaya ta tsomata a ruwan zafi tare da dannata a ciki ta bude kafafunta,ihu Amana takeyi amma Badriyya ta kafa ta tsare tace dama nasan wlh yanda Ya Alim ke kaunarki bazai taba yi miki gashi me kyau ba gwara da Allah ya kawoni lagos.

Amana tana ihun zafi tace zan mareki,dariya Badriyya tayi kimin shuru ko yanzu na jibgeki kar ki jawo na kara famu,
Saida Badriyya ta yiwa Amana gashi da ruwa har sau Biyar tana zubarwa tana sake sabo,wata Ni'imace da karfin dadi suka dinga ratsa Amana.
Amana tace sis wlh kin iya wa ya koya miki?Badriyya tace wajen kawarmu Bilkisa ta gidan Baba Tsoho,itace take mana lecture akan aure idan mukaje wasa gidanta,har kawata Maimuna ni na gashe shegiya minjinta ya mata daga daga.

Allah shiryeki cewar Amana, Badriyya tace rufe min baki ba gashi kin amfana ba,yanzu zauna cikin Bahon na miki wankan sabulu kuma kafin na bude idona.
Ba musu Amana ta zauna aka cudeta tana Badriyya kiyi a hankali mana zaki cire min fata,
Da Allah uwar kwailo duk karfinki kina badani.

Dai dai kirjin Amana tazo Ba ruwan Badriyya ta dirjesu da soso sosai,kara Badriyya ta saki kutmar....shege Alim dole yayi mukus a bed munafuki... Ashe rashana yake kwasa,fusge soson Amana tayi fita zan karasa kina tabawa Alim sirrinsa, wlh saina karasa ko na fama miki ciwonki,da sauri Amana ta bata soson mayya kawai ungo.
Tas Badriyya ta wanke Amana tare da daura mata towel sai lokacin Badriyya ta bude idonta. Har daki ta kawo Amana ta bata mai da nightwear sannan itama tayi,Alwala sukayi suka jero nafeela da karatun Qurani da sauransu sannan sukayi ta jera adduoi wa komai da ya damesu na duniya Dana Lahira.
Yau bed daya suka kwanta suna hirar zuminci,sai tausa Badriyya kewa Amana tana kwantar mata da hankali.

Asiya kanwar Alim tayiwa Abbanta waya cewar ta fitar da miji Sadiq yayan Huzaifa kenan dan kanin Abban Alim dake kano,shima kanin su Alim auta dake karatu a Cairo ya kammala karatunsa gaf yake da dawowa shima tace ya samu matar aure yar Adamawa state ce Zahra tare sukayi karatu amma Mum tayi tsalle ta dire tace wlh bai isa ba ita zata zabar masa mata.
Itama Asiya tace bata yards da zabin Asiya ba domin Saddiq ma'aikacin Gomnatine bashi da gadon arziki da Gomnati ya dogara ita kuma tace dole itama Aliya ta auri zabinta wato Sageer dan gidan Gomnan Kebbi tubabben Bayarabe ne,
Kuma baya da haka ma Mum bata kaunar dangin mijinta.

Babu magiyar da Aliya da Auta basuyi ba Amma Mum ta kekasa kasa taki abinda ya tashi hankalin dan autanta da kuma Aliya,Aliya tana can kano taki dawowa sai kuka takeyi,dan Uwan Abba kuwa sai tausarta yake yace addua itace mafita sabida idan aka matsa to Mum zata tsinewa yaranta wanda hakan barazana ce ga rayuwarsu.

AsmaBaffa
✳CIRANIN AMANA✳

125-130

By
AsmaBaffa

Ina matukar godiya fans duk naga sakonninku na Kuma Ji yanda kuka nemeni na gode da nuna kaunarku. Kuyi hakuri ba kuji ni ba,ina kaunarku sosai ina jinjina muku.

Page din nan naki ne MARCYCOOL my sweet and lovely sis.

Basu zarce ko ina ba sai gidan Alim direct Amana Jan Badriyya tayi har cikin Palon part dinsa nan take Badriyya ta sukukuce wajen kallon asalin haduwa, Badriyya batayi kasa a gwiwa ba tace Amana yanzu wanna kata'in gidan ne gidan mijinki, anan kike zama?ina Kallon gidan Mum Alim hadadde Ashe akurkin(cage)kazane ban sani ba,Amana dariya Kawai tayi yanda Badriyya ke zuba kauyancinta, Badriyya taci gaba Amma Mum ta cuce ni da tuni anan aka saukeni ko?

Kaf saida Amana ta zagaye gidan Tana nunawa Badriyya komai na gidan har sukaje part din

Ma'aikatan gidan mata sai gulma Sukeyi Ashe oga Amana ya aura, Badriyya har yanga take musu ita ga kanwar matar gidan,

Sama suka hau a part din me gida Alim Sautin kidane ke tashi a manyan speakers dake girke a Palon Alim,Huzaifa zaune yana chat Alim yana latsa computer system,Badriyya kamar idonta zasu zubo tsabar kallon tsaruwa, volume suka rage a nutse suka karasa suka gaisa da Juna suka zauna,Alim kamar zai cinye Amana saboda Kallo,Huzaifa ma rudewa yaya ganin su Badriyya an dau wanka,

Alim ne ya radawa Amana baby kinyi kyau,wani yarrrr... Amana taji a cikin jininta sakamakon irin salon da Alim yayi wajen mata

Magana cikin kunne, nan take ta lumshe Ido,kasala ta sakko Mata,ba abinda takeso kamar tajita rungume jikin Alim musamman yanda kamshinsa ya cika mata hanci me dadin gaske,

Bari mu shirya Cewar Alim,kai kawai ta gyada,Huzaifa ma ya mike ya nufi shiryawa yana bin Badriyya da mayen Kallo.

Amana taja Badriyya zo muje kiga Saude yanda na kulleta,me gadi ne ya bude musu Dakin da Saude take suka shiga,Saude Tana ganin Amana ta fara lailayo manyan zagi Tana watso musu,

Haushi Badriyya taji tace kinji ko Amana, Saude tace tsinannu gadon tsiya, bakar haihuwa, haihuwar gefen kwalta, haihuwar tsakar Rana,wacce da Rana ubanki yayi cikinki,wlh nice ajalinki Dan ubanki Tare da Danno ashar lafiyayya.

Amana ta harzuka tace ki daina zagin iyayena nasan darajarsu,Saude tace Ubanki Ma yaci Uwatas, Uban Uwarki na fada yan tsinannu.

Amana tace Baba me gadi dauko min sandar nan me kamar kulkin yan sanda,aifa Baba da gudu ya kawo ya bar wajen,Amana ta mikawa Badriyya sanda jibgi rabonki Sis,Badriyya tace yanzu naji manana wannan shine aha...

Shiga Tayi ta Fara lugudar Saude,Amana kuwa kofar ta rufe musi Tana jin yanda Badriyya ke tafkar Saude,Saude kuwa bata fasa zagin da take ba.saida Amana taga lallai Badriyya zatayi kisan Kai sannan ta koma ciki Badriyya wai wanne hauka ne haka ki kyaleta haka ai dukan yayi yawa kina ganifa ko magana Saude ta Kasa,

Badriyya tace yo ni ina ruwana idan zata yini to wlh zan kwana akan zagin iyayenmu, Amana tace banason musu fa ke halina dake banza ce baki san kadan ba,Badriyya ta kalli Amana wlh kin lalace Amana, wai ke kikewa wani fada akan dukan wani.

Naji muje Kawai komai Ai sai ana hangen nesa

Sandar ta kwace ta kira me gadi ta bashi kudi da yawa sannan tace ya bata abinci da ruwa yaci gaba da tsare Saude.

Saude wacce ta gama jikata bayan su Amana sun tafi tace shegu ammafa wannan kanwar ta Amana har tafi Amana mugunta, saidai dukan Amana yafi zafi Domin duka daya na Amana shine goman na Badriyya.

Suna komawa Ciki Alim ya fito cikin shiri ya dau wanka na kece raini cikin pencil jean brown

da riga Sea blue irin color na kayan Amana.
Yasha kyau suma taci Kudi sai shining yakeyi hade da kamshI.
Wani agogon Gucci ne me tsadar gaske a hannunsa,

Huzaifa ma ya hade cikin kanan kayansa black nd white,Alim ya kalli Amana wacce ta ke satar kallonsa domin ya mata kyau. Kamar dazu ina wanka naji ihu a gidan nan cewar Alim
Huzaifa ma yace nima haka wlh naji kuma na Mace,Amana sun san ihun Saude Ne Amma sai tace munje ai masu aiki matane wai sunga ga kadangare shine suke ta ihu amma an fitar dashi.

Huzaifa yace kai mata kenan Alim yace lets go zamuyi Missing flight,akwatunan guards Suka zuba musu a mota nan Suka wuce sai Airport dake Lagos.

Suna cikin Airport kafin a fara musu screening wata kyakyawa yar gayu bahaushiya suka hango ta taho tana yanga tana taku dai dai hade da juya mazaunai irin na yan duniya.
Alim ta kafe da kallo wanda shi bai ma san da ita ba domin Amana yake ta faman Kallo yana lallabata ta sha fresh milk tunda ba wata lafiya ce da ita ba.
Amana kuwa da Badriyya kallon wannan matar sukeyi Badriyya ta kama kunnen Amana ta mata Rada yanda ba wanda zaiji,Kalli wannan Amana wlh mijinki take kallo zatayi miki snatching,Amana itama ta yiwa Badriyya rada bar shegiya zanyi maganinta, Badriyya a basu show...
A basu show Sis,
a dauko manana yar Sulemanu Harka
CIRANIN AMANA

130-135

Official

By
AsmaBaffa

QUEEN MERMU WANNAN PAGE NAKINE,HAFCYCY DA SUBBY GODIYA

GAREKU,OGA ASY BAN MANTA DA KE BA,INA TA WAJENA MAMAN WALEEDA ALLAH YA BAR KAUNA.
SAURAN READERS MA NA GODE

Har cikin garinsu kauyensu Badriyya ta kaisu, hamdala sukayi Allah ya kawosu lfy, a gurguje suka kwashi kayansu Amana ta sallami taxi Man ya tafi,kafin kace me anyi dandazo ana kallon yan gayu su Amana,kamar bakin larabawa ko indiyawa

Cikin sauri da zafin nama suka fada cikin dan gidansu me kyau,duk yan gidan tasowa sukayi ana tururuwar rungume su Amana,Amana hannu ta bawa yayyenta mata da maza manya da yara suna tafawa tas tas tare da share hawayenta,a tsakar gida bisa katuwar tabarma babba suka yada zango,

Cike da mutunci suka gaisar da iyayensu da kakarsu Iyya babar Sulemanu Harka wato Iyya.

Tambaya sukayi Ina Baba?Umman Amana tace suna asibiti daga nan zasu biya gidan me dori na Hausa,

Iyya tana sharar kwalla tace ai abokansa me Unguwa da Iliya su suke ta dawainiya dashi sun hana kowa zuwa sun dauki nauyi anjima zuwa dare zasu dawo daga asibiti.

Gwaggo tace ai wlh wannan tsinanannun yan Daba ne,

Iyya tace jarabar duniya asara ai basu da imani ko kadan,addua tsinuwa na dinga tsine musu kenan har ranar da mala'ikan mutuwa zai zare numfashi na

Gwaggo tace ohhhh Allah ya rufa mana asiri da ta kare akan Sulemanu shi kadai maganinsa kenan ishara ce Allah ya nuna masa tunda yaki tuba.

Umman Amana tace wlh kuwa in banda kwala min touch light da sukayi a ka ba abinda suka min,daya matar Sulemanu tace hhhhh ai ni dadi ma naji da suka masa haka yanzu kinga yayi karatun tanutsu ba kwartanci,

Matar cikon ta hudu n itama dariya ta kyalkyale da ita tace wai kunga wani mari da suka fesa min na zata Wlh duniyar ce ta kife kif,Sakina karamar kanwar su Amana tace ta saki dariya tace gwaggo kinga abinda ya bani dariya wai katon cikinsu zaiwa Iyya fyade wai Iyya wacce ta rigada ta yi expired,

Dariya gaba daya aka sheke da ita,Hamza ya zubawa Sakina rankwashi yace Iyya ai sweet zatayi kika sani ko danta ita ya gado

Iyya ce ta fashe da kuka sosai tace Allah ya isa tsakinina daku,kuma wanda ya kara min turanci to ubansa yaci uwatas tsinannu uwarku kuka zaga,kuma dana Sulemanu ba abinda Zai sameshi aniyarku ta biku

Iyayen ne wato matan Harka su 4 suka ce heeeeeee can ga su gada, dan naki wanne zalince ne Bai mana ba ai hakkinmu ne ya kamashi,

Amana tace ya isa haka pls ice ko dai Baba jikin da sauki,duk suka ce Alhmdllh Badriyya tace good,iyayen sukace kai Ku dinga turancinku can mu me muka sani

Hamza yan crossriver gaba daya pidgin English suka koma da su Amana,kb wanda ke bin Hamza yace you girls are chilling woo,u dey enjoy oooo,Hamza yace I swear come see enjoyment no be small thing Sis,

Isa ne ya shigo yana budawa tare da yin doro yana kobarewa yayi hugging din Badriyya yace ahhhh...this girl I know u no dey carry last look at ur skin.
Kallon Amana yayi yace easy easy Baba cutie u r still shining wooo,Amana tace stop this nonsense joooo...a done big now,a be house wife, no joke abeg that useless thing has past Man,
Badriyya ce tayi katsalandan tace wait guys just gist me how things goes, abeg stay quite stingy girl cewar Hamza, dariya sukayi gaba daya Badriyya tace I have a story for u guys, kowa saurarenta yakeyi sannan tace am in love ,tafi suka dauka gaba dayansu yan ciranin gidan da sauran yara wanda suke schl suna tsintar turancin
Isa yace a bamu musha ya hadu, Amana ce ta fara magana,gaskiya a tsaya a tsaya shuru kowa yayi har iyayensu dake zagaye dasu a hankali ta furta tunanin mijina nakeyi u knw am a married woman ,heeeeeee suka fara ihu,Hamza yace shegiya u done fall

Kwanjin Isa Amana ta buga da sauri ya dafe wajen yace wlh har yau karfin ki na nan wai,Haladu da shigowarsa kenan dauke da danyen kifi headphone makale kunnensa yana Shan Sauti ai ganin Amana yasan dole kudi yazo kawai sai ya fara casa rawa yana slizing kamar wani Michael Jackson,dariya sukeyi Badriyya tace u too funny.

Alim kwance yana numfarfashi na zazzabi ya fita daga hayyacinsa,10pm wayarsa ta shiga ruri ba tare da ya duba me kiran ba ya jawo ya daga tare da karawa a kunne Jin Muryar Amana yasashi Jin sanyi a ransa,cike da karkarwar sanyi yace hello,nan take Amana ta rude Jin Muryar jariminta ba lafiya,
Cike da kulawa tayi kasa da Muryar tare da shagwabe murya tace dear ya najika haka are u ok,kara narke mata yayi Baby pls come to me i need u badly,
A rude Amana tace sweet Alim me ya sameka pls,a hankali yace kawai ni kizo Baby fever na damuna I missed u,missed u much more dear amma ya kamata ka Kira doctor kaji,
Uhm no Amana zan warke
Kara lankwashe murya tayi kamar zatayi kuka tace oh dear pls bana son rigima kawai ka kira doctor kaji,to baby Allura fa za a min kuma bakya kusa bare ki rikeni ki lailayamin,
Uhm kaji rigimarka ko mine,

Kaci abinci?no bazan iya ci ba I am missing u Amana
Rokonsa Amana ta fara dan Allah kaci ka taimaka min kaci abinci Dan darajar Allah kaji,ka tausaya min Babyna kaji,wani shauki ne ya kara shigar Alim ya kara narke mata zanci kadan to, cikin wani salon Muryar da bata San tana dashi ba tace tnx oya tashi kuma kar kashe Ina ji zaka ci sannan ka kira doctor,pls ki kyale doctor ban son Allura fa kamar zaiyi kuka ya furta,

OK to shike nan tunda bara ka kira doctor ba mun bata na daina kulaka ma,
Uhmmmmmm kamar zaiyi kuka yace am sorry Baby,
Ban hakura sai kayi abinda nace oya get up,Babyna bakya tausayina ko?I will kill u just do as I said ok
Tana jinsa sai shagwaba yake zuba mata tana lallabashi har yaje wajen Mum ta bashi Abinci yace doctor ya kawo masa magani yasha yayi wanka ya kwanta sannan Amana ta kyaleshi tace goodnight My Alim muuuuuuuuuahhhhhhh ta watsa masa kiss ta waya sunfi 10,
Alim yace ohhhhhhh u are killing me honey I wish u r here with me hmmm da sai na kwana ina wasan kwallo,wani dariya Amana tayi me Jan hankali ta fara shagwaba uhmmmm....banda rigimafa Mine night sweet dreams,pls kiwa Baba sannu da jiki ina nan zanzo kinji ko?to ba matsala Allah kawoka,haka sukayi sallama.

Washe gari Alim waras ya warke shiri yayi sosai tare da daukan wanka na gaske domin zuwa Airport dauko Nura da Matarsa.
Mum,Alim,da Abba ne suka tafi dauko Nura,Asiya ma tazo daga Kano domin taron babban yayansu,
Wani kyakyawa chocolate ne da matarsa black beauty tare da yarsu yar kimanin 3yrs suka karaso jikin motocin su Alim,
Nan suka dinga Murna da gaisawa,Mum sai hararar matar Nura takeyi da kyar ma ta amsa gaisuwarta,hakanma dan taga idon Abba ne,
Nura dan wanka mota suka shiga sai gida inda suka ci suka Sha ana ta fira,Asiya sai surutu akeyi,
Washe gari Autan Mum ma ya sauka shima ya gama schl kyakyawa kamar dan India dan yafi Nura haske amma Bai kai Alim ba,gida ya kacame ana ta murna da hira,
Bayan Mum da Abba sun tashi suka fara tattauna Matsalar uwarsu
Dan Auta yace Wlh ni bazan yarda da wani auren dolen da Mum zata yi min ba,Nura yace hmmm ai na rasa wanne haline da Umma zuciya ba Imani,Asiya tace ai ni shi yasa na koma wajen Abban su Huzaifa kusa da masoyina ni kam bazan yarda ba wlh.
Alim wanda magana bata dameshi ba,yace Ku kenan nifa fisabilillah Ku duba komai a kaina ya kare,aure nawa tayi min.
Yanzufa Amaryace Dani Amarya pls kuji fa ta hanani sakewa na rasa yanda zanyi yanzu taje duba babanta ba Ify amma Mum ta hanani zuwa cike da shagwaba ya karasa zancen kuma wlh ni dai I need my wife firewood ne ni ko rock Amaryafa guda,
Dariya sukayi Autan Mum yace hhhhh bros mun ganoka dama ai kai kawai son ehhh...
Zan mareka ban son iskanci ni sa'anka ne,Nura yace kyaleshi bro shi ai Bai San dawar garin bane.
Tsaki Alim yaja to ni dai a bani shawara guys body fa ba dutse bane,Mum ce ta katsesu Body yaci kutmar ubansa duk naji me kuke cewa kuma wlh Ku kiyayeni babu dan iskan daya isa ya ja Dani,ni na tsuguna na haifeku banzaye,ke kuma Asiya kyaleki nayi kika zauna a Kano wajen wancan tsinannun wlh ki kiyayeni dakikiya.
Huzaifa dake gefe yayi kus baice komai ba dan ya gama shiri gobe yakeso ya bar gidan nan ya gaji da jarabar Mum ta safe daban ta rana daban haka ta dare ma.

Dan Auta ne ya fara kunkuni yana turo baki Bai aune ba yaji Mum ta zuba masa rankwashi a kai.

Mikewa Alim yayi cike da bacin rai ya koma gidansa shi da Huzaifa suna shirye shiryen yanda zasu bullowa Mum ayi mata wayo Alim yaje wajen Amana

Domin ko ya fadawa Abba to tsine masa Mum zatayi.

Amana da Badriyya zaune gaban Babansu sai kuka sukeyi yanda suka babansu raga faga komai sai dai ayi masa kafafinsa a karye hannunsa daya ma a balle,jikinsa duk raunuka an canja masa kamanni,

Cikin rauni Baba yace Yayana kunga yanda Allah yayi dani ko?

Nasan wanda ya min abin nan Amma bazan fada ba sai nan gaba idan Allah yaja kwanana,na jawowa kaina wayyo duniya oh.....Amanata na dauko ruwan dafa kaina, lallashin Baba sukeyi,Baba yace kayya yara ni na siyo da kudina,Amma Amanata kinfi kowa a wajena ke kadai zan fadawa wanda suka sassarani haka.

Da dare daga Sulemanu sai Amana nan ya fara magana Amanata ina so ki sani bake ba komawa lagos Allah tsinewa lagos,tir da halina na turaki Cirani na amfana dashi ta wanni fannin na jawowa kaina masifa,inaso ki sani duk son kudina yau na hakura naga duniya,don haka baza ki koma lagos ba,ba aure ba ko tattabarace ke karewar aure na yankeshi

Tari Harka yayi yace Allah kawo mijinki wallahi sai ya sakeki bake ba komawa hannunsa,

Idan kika koma lagos to ban yafe miki ba duniya da lahira gaban Amana ne ya yanke ya fadi nan take sai hawaye takeyi,yace Uwar mijinki ita ta zo da yan daba tasa sukayi min haka,duk kuma nasan irin ukubar da take gana miki,

To aure anyi kenan na dauka yan mutuncine shi yasa na basu ke Ashe shegiyace.

To bari mijinki yazo sai ya sakeki,

Amana tace Baba ya akayi kasan itace?

Baba yace tare da yan fashin suka shigo dakina da ita,ta rufe fuskarta da zasu tafi ta budemin fuskarta na ganta kiri kiri harsai da ta tabbatar na ganeta sannan ta tafi cikin mota.

Amana taji wani bakin ciki amma tasan ba laifin Mijinta bane,

Amana tace Baba ina son mijina kayi hakura za a daukar maka fansa,Baba dake kwance rashe rashe ko ina a daure a jikinsa,yace kaji wofi banza da gadamar daukan fansa nayi da tuni ban fadawa su Hamza ba sunwa shegiya fata fata,yo Allah na tuba ko ke nasa ai nasan sai kin mata rugu rugu kin ramamin,

Amana cikin kuka tace Baba wlh ina son mijina ni dai,Baba yace soyayya taci ubanta,uban soyayyar tattabara ma taci uwarta.

Wato so yasa kin canja ko kin Zama lusara ina alfahari dake ashe kin lalace.

To mijin naki zaizo ya sameni dan ubansa tashi ki ban waje.

Cikin kunkuni Amana ta fito.

Yau kwanan su Amana 3 a garinsu yaune kuma Iyya kakarsu ta fara Amai da gudawa cholera zuwa magriba Iyya tace ga garinku nan,sunyi bakin ciki sabo da zaman tare ba wasa ba amma basuyi kuka ba domin sunce ai Iyya taci duniya dama ya kamata ta wulla.

Ana zaman makoki su Hamza sune kan gaba,kwana daya kacal Hamza yace an rufe zaman makoki ai Iyya ta cancanci ta wuce.

Badriyya tace wlh amma kalli Baba da rashin godiyar Allah wai harda kuka Ummansa ta mutu,Haladu yace ke rabu dashi da Allah tsufane eh...

Amana tace su Iyya yanzu tuni nasan walakiri ya mata guduma daya,don fa Iyya ko sallah bata iya ba, kb yace ai Iyya ta wuce guduma sai dai a kafa mata Kusa Allah wlh.

Amana ce ta janyo jaka ta zaro kudi ta mikawa kb gashi Baabaa ayo mana cefane,Haladu yace easy wlh Anty Yau dan Allah a bani 3k zanwa my one and Only hidima,Amana tace sai Bro ai mu inde akan har kar Love ne to gwara jari ya karye don mun San darajarsa ga 5k ayi manage.

Haka suke ta abinsu Amana ta canja sosai Amma haka take biye musu tana raha da tuna baya ana har kar eh..aha..da ita hakan ba karamin nishadi sukeyi ba.

Alim ya je ya kokawa Abba amma kar ya fadawa Mum domin tsine mishi zatayi, dan haka Abba yace Alim ya tura Adamawa zai masa wani aiki Huzaifa kuma zai koma Kano,har Mota Mum ta raka Alim tana masa addua,Huzaifa ya mata sallama amma a wulakance ta amsa ta wuce.

Alim da Huzaifa jirgin kano suka hau sai kano,

Suna sauka gidan su Huzaifa suka huta, washe gari da safe da wuri ko Amana bai fadawa ba tsabar zumudi suka dau wanka shi da Huzaifa Sai garin su Amana.

Huzaifa ke driving,

Alim waya suke da Amana amma bai fada mata ba cewar suna hanya ba har suka gama soyewa a waya.Mum da Abba da yan uwansa duk sunyi waya suna yi masa ya Adamawa kawai sai yace Ify shi da Abba ne kadai suka San inda Alim ya tafi.

AsmaBaffa

A dinga yi ana sharhi readers yana kara kwarin gwiwa fiye da tnx etc.love u all.

✳CIRANIN AMANA✳

135-140

Official

By
AsmaBaffa

WANNAN PAGE DIN NA SADAUKAR MIKI MARCYCOOL ALLAH YA BAR ZUMUNCI

Suna kan hanyar garinsu Amana yau Alim cikin nishadi yake kamar yayi tsuntsu ya afka garin shuuut,sai nishadi yake,
A kofar gidan Sulemanu Harka suka gyara parking din jibgegiyar motarsu hadaddiyar gaske.
Haladu tun a majalisa yace wannan irin motar sai dai bakin Amana,dan kaf unguwarsu itace me harkalla da masu kudi shi yasa ma suna parking shima ya kara so wajensu‹ tun daga takalmansu da suka zuro kafafu waje kasan sai kusoshin Nigeria,
Tun kafin Alim ya fito bude motar kawai kamshinsa ya cika layin,

Haladu sanye da 3qtr da armless yayi kyau hannu ya mikawa su Alim suka kashe cike da mutuntawa saboda kaf yan gidan su Amana babu me duhun kai,kowa ya waye saboda suna fita wasu state din,ko wankansu irin na yan birni sukeyi musamman yanzu da Alim ya musu hanyar samun kudi da ilmi.

Palon baki Haladu ya kaisu palon yasha kujerun da Alim yasa musu,su Sakina sun gyara shi tsab sai kamshin turaren wuta yakeyi me dadi haka gidanma ko Ina fes fes yana kyalli.

Haladu exotic da malt sai holandia da ruwan roba duk ya cika musu a gabansu‹ Alim wanda ya matsu ya ga matarsa yace Ina wife Dina first,murmushi Haladu yayi yace na tura a kirata wai taje gidan wani frnd zata gaisar da Mum dinsa makwafta ne ana mutunci da iyaye sosai,

Nan take mood din Alim ya canja,kishi ya cikashi Mum din frnd ba ma mace ba Mum din wani ba Mum din wata ba,
Kasa Zama yayi ya jawo waya yana danna Kira yace Ina zuwa ya fita can waje,kofar gida

yana huci tare da Jan tsaki zai kirata a waya.
Rashin sa'a bata shiga,minti kadan ya hango ruhinsa Amana ita da kanwarsu Sakina suna tahowa ta wani lungu, tsananin kyan da yaga Amana ta kara yi shi ya ja hankalinsa tare da kafeta da Ido,
Arabian gaunt ne jikinta tayi rolling dankwalinta black and pink.

Tun daga nesa Amana ta hango sahibinta,wani farinciki ya mamaye zuciyarta,cike da nishadi take karasowa,kishi yakeyi maza na kallar masa murmushin matarsa,gashin kansa ya shafa,

Wani wajen da ake charging a jikin gidan su Amana su ne suke kunna DJ kida na tashi me matukar dadi wakar Hausa kamar a taka rawa,
Nan ya kara musu wani nishadi Amana tun daga nesa ta kashe Alim da mugun kallon kauna tana aika masa da wasu sakkoni,
Alim ya kasa dauke Ido,
Tana zuwa kusa dashi sai ji tayi ya rungumeta tsam so tight,
Kunya taji kar a ga rashin kunyarta a fili

Kafin kace me yara sun zagayesu ana ta kallansu wasu na cewa yan iska ne....yan iska ne,
Wasu kuma suka ce yan film ne....laaaa Alquran ga yan film,harda masu leke ta saman katanga
Da kyar Amana ta kwance kanta cikin dabara don taga Alim kiss yake shirin manna mata ga shi sun kwashi yan kallo,Allah yasa an San yan gidan Sulemanu Harka ba mutunci garesu ba shi yasa ake tsoronsu sun wuce raini.

Hannun sa ta ja har cikin gidan ya gaisar da su Ummansu sannan yaran gida suka gaisa sosai,ya musu ya jikin Baba da ta'aziyar Iyya,su Baba an tafi Hospital sai wurin magrib zasu dawo sai sun jira. ya Dade cikin gidan wajen yan uwan Amana ana ta hira dashi shi kam yasha dariya sosai, Huzaifa kuwa yana can da Badriyya suna hirarsu,
Amana dakinta ta ja Alim da yake gidansu ba wani kunya ko wani sa'ido musamman ga mata da miji
Suna shiga Alim ya jawota jikinsa,daga nan ya fara lalubar bakinta yana ta tsotsa,tana shafa wuyansa ta baya domin hannunta na sakale a wuyansa,
Kallonsa tayi cike da shagwaba tace I missed u,kan bed suka zauna sannan ta dan zamo kadan ta risina Ina kwana,ya hanya,
Sai sannan ya balla mata harara bana amsawa Ina kikaje?
Narkewa tayi lalle fa naje kalli ma ta miko masa hannayen da kafar,
Sai kuma na biya gidan Maman na Marsiyya muka gaisa domin ta tallafamin lokacin da banda shi,magana take amma hankalin Alim yana kan kirjinta, yana kallon yanda suka kara cikowa, waye kuma Na Marsiyya?Alim ya tambaya,tace makwafta ana gaisawa da Babarsu kuma tana so na ta karasa zancen tana

Kallon sa, ta kalli inda Alim yake kallo wato boobs dinta kunya taji tace kai yaya Alim Mene

haka?
hannayenta ya rike yana kissing din lallen da aka mata
Kinyi kyau my wife I love u.
Kansa Amana ta kamo a hankali ta kwantar a saman cinyarta tare da shafa sumarsa tace Husband karka damu trust me kasan bazanyi wani abu Bad ba ko Ina naje naga kamar ranka ya baci.

Cikin shagwaba ya furta ni dai pls ki daina fita ko kofar gida idan kina son farin cikina.
An gama ya Alim,me kake son ci? Tuwo nake so idan akwai idan babu ma kiyi min wani.babu sai dai na yi maka,
Ok ayi min to zanci kallonsa tayi tare da yi masa kiss a goshi ka fiye shagwaba Allah ya Alim, har kafi mace kamar dan jariri haka kake.jawota yayi jikinsa sosai yana murmushinsa me sa Amana Sandarewa saboda kauna,ya shiga mirza boobs dinta yana wani shidewa itakam lumshe Ido tayi tana jinsa kasa hanashi tayi suka shiga romancing gani tayi Alim zai wuce gona da iri murya can kasa ta rada masa a kunne tare da shafo cikinsa tace bari nama girki ko? Uhmmmmm ya furta tare da tura kansa cikin wuyanta yana shakar kamshinta amma dai ke zaki dafa min da kanki nayi missing girkinki
Fari tayi da Ido tare da yin wata Mika me Jan hankalin da Namiji ta furta wa zan bari ta dafa ma abinci,wannan hakkinane Ina kissing kaci girkin wata mikewa tayi tare da barin dakin,
A bed din Amana ya kwanta nan take bacci me dadi da nishadi ya kwasheshi.

Amana ana kitchen duk mutan gidan kallonta sukeyi suna mamakin Kula da miji irin na Amana,
Sakina ce ta shigo tana kuka sosai ta samu gaba daya yan gidan suna zaune a katon palonsu banda Baba da Badriyya,Baba na asibiti Badriyya na wajen Huzaifa
Sakina ta rushe da kara rushe musu da kuka,Amana cikin hasala tace dallah malama yi mana shuru wlh ko naci Ubanki banza doluwa katuwa dake kina wani mana kuka kin Zama budurwa fa,
Kb ne cikin takaici yace Amana Mene haka halina dake hauka da saurin fushi baza ki tambayi dalili ba,
Amana da masifa tace rufemin baki kb wlh kasan halina bani da mutunci yanzu dan nayi laushi ne da Baka isa ka fada min haka ba,kar fa kaga ka girmeni wlh ba ruwana bazan raga maka ba,kana jinta tana kuka mijina yana bacci idan ta tasar min shi fa,Isa da dariya yace yaro ne shi eh an tasheshi din,Haladu dan zamani yace kin birgeni ki Kula da abinki, Amana tace to dan Allah ma yanzu wlh da kyar na samu na lallabashi yayi bacci idan ya tashi rigima zai min ta karasa da shagwaba,

Hhhhhhhh kowa dake gidan ya kyakyace da dariya harda Sakina me kuka.
Hamza yace ke kikeyin Abin wlh amma ni nakejin kunyar abin,ke yanzu ko yar kunya babu ko?
Umman Amana tace ai banzace wai ita a dole yar birni ta waye,Gwaggo tace. Munji labari har rungumeshi tayi a bainar nasi.

Hamza ya kalli Sakina uban waye ya taba mana ke fada min wlh ya gane kurensa yau,
Sakina kuka taci gaba dayi harda shidewa Amana a fusace ta make bakinta har sai da ya fashe tace ohhh zaki tace Babyna wlh kika sake ya tashi ban gama masa abinci ba sai na tattakaki a gidan nan.
Sakina dafe da baki sai Hawaye takeyi,
Hamza yace ki bita a hankali mana ke fada mana Mene?
Sakina tace saurayinane Mohd mukayi fada yace ya fasa aurena wai na fiye masifa ta kara fashewa da kuka kuma wlh Ina sonsa wayyo....karshena yazo...ni mutuwa zanyi.

Yaya Isa dan Allah tunda abokinkane ka bashi hakuri ko gidansu can cikin Kano city ka je ka bashi hakuri,
Ke.....ke...ke....hold there abeg wanne irin in bashi hakuri sai kace dole ki kyaleshi Allah ya baki wani ai sai ma ya raina mu yaga kamar andamu dole ya aura karshe kisha wulakanci,c cikin kuka tace dan Allah ya Isa,
Isa yace ke zan kwada miki mari wlh kinma rainani sau nawa Ina zaunar dake ina baki shawara cewar idan kin San kina son Mohd ki rikeshi sosai ki gyara wannan masifar taki kika ji ke a dole budurwa dole ya so ki ko ai gashi na kinwa kanki.

Kuka taci gaba da yi ,Amana wacce ta fito daga kitchen rike da wani bowl tace a'a ke tashi ki tafi can kofar gida wlh ko ki koma dakin uwarki kiyi ta kukanki ya dan iskanci zaki tasar min Baby yana bacci,
Shuru Sakina tayi tana kunkuni.Badriyya ce tayi sallami tabi Sakina da kallo ke ga yar iska ko kinzo sai kuka kike ma mutane kina firgita min Huzaifa kina cika masa kunne shashasha ta ja tsaki,kb dake cin indomie yace ki taya jaje saurayinta ne ya fasa aurenta Mohd abokin Isa,
Fuskar tausayi Badriyya tayi tace eyya sorry kinji Sis rashin masoyi ba dadi kamar nice ace Huzaifa ya daina kulani ai daji zan shige kawai.

Sakina tace ni dai Allah a San yanda za a dawo min dashi ehe
Harara Amana ta watso mata,Badriyya kitchen ta shiga tace Amana ki dafa da Ya Huzaifa fa,ae ai dama dashi nakeyi kira min Haladu pls na aikeshi,Amana yayanki ne fa Haladu amma zaki aikeshi,ina ruwanki to kawai ki kira min shi.

Yara yan makaranta sun taso suna ta surutu Amana da masifa ta fito kai kuyi min shuru mijina Bacci yake kwakwaran Motsi Amana ta hana yaran nan suyi  har ta gama girkinta ta fesa wanka ta dan dasa kwalliya cikin doguwar rigar materal fitted gaunt tasha kyau hips komai ya fito das das ta Jere abinci a gefen bed sannan ta tashi Alim ya shiga toilet din dake cikin room din domin yin Alwala

Saude kuwa tana kauyensu bayan ta samu nasarar guduwa daga gidan Alim ko me take aikatawa oho ta ya Saude ta gudu sai mun koma wajen me gadi za muji labari
Amma dai Saude ta murmure ta dawo fes da ita tana harkokinta can kauyensu dake Gombe state.
Alim kamar gidansu yana shigewa toilet saida yayi wanka da soap din Amana,yayi Alwala

da sallar Azahar,Amana kuwa period takeyi ma
Zaune yake kan katuwar sallaya abinci Jere a gabansa ga Amana tasha wanka tana aika masa da wasu sinadaran kallo masu rikitarwa.
Wasu flasks masu kyau ya bude wow....ya furta miyar danyar kubewa ce tasha kifi da tuwon danyar shinkafa,wani flask ya bude farfesun kaji sai kamshi ke tashi sai wani glass Bowl kankanace a yanke da fork spoon ciki
Ga wani zobe yasha kayan hadi a glass juck har ya fara kankara,sai ruwan roba,yanda aka kawowa Alim haka aka bawa Huzaifa ma,
Alim ya manta ma tare suke da Huzaifa ma

Amana zagewa tayi ta cire masa rigarsa ta shadda daga shi sai dogon wandonsa wai kar mistakenly miya ta bata masa riga hehehe love

Alim kamar gidan ubansa ya wani kwanta a kafadar Amana tana ta ciyar dashi saida ya koshi sosai sannan a karshe ta bashi kankana yasha,
Brush ta kawo masa sabo ya tsaftace sannan ya dinga kora zobon,
Amana kuwa abincin itama taci ta kwashe komai ta gyara room din tare da kara wanke toilet din ko Ina kamshi yakeyi,
Alim saman bed yajata suka shige sai wasanni sukeyi a ciki.
Huzaifa yaga Alim shuru yaki fitowa sai mamakin rashin kunyarsa yakeyi a gidan surukai, Badriyya tace ai mu nan gidan ba ruwan wani da wani,lallai rayuwarku tana birgeni a gidan nan kowa harkarsa yakeyi cewar Huzaifa.

Har magriba Baba Basu dawo ba,Huzaifa har ya fito jikin mota suka hadu dasu Baba sun dawo an kwaso Baba kamar kayan wanki yana ta numfarfashi,har dakin Baba yaje suka gaisa harda yar hira sama sama sannan ya masa ya jiki,Baba yana nishi yace ina wannan dan marasa mutuncin dan uwanka mijin Amanata
Huzaifa ya sosa kai Baba yana dakin Amana yanzu ma jiransa nakeyi ya fito mu tafi kar dare yayi,
Sanda Baba ya jawo a kusa dashi ya rafkawa Huzaifa a kansa nan take wajen ya kumbura,dan ubanka fitar minshi daga gidanaa na tsaneshi,Huzaifa dafe da kansa yace Baba lafiya kara daga sandar yayi da niyyar kwala masa Badriyya ta fado dakin ta tare tace ni ka dakeni Baba akan ka daki wannan me sukayi maka?

Huzaifa ne ya janye Badriyya yana bawa Baba hakuri suka fita,
Amana ne suka fito tare da Alim kamar zasu hadiye juna,sallama yayiwa mutan gidan kaf tare da yi musu kyautar ruwan kudi,Huzaifa kuwa Badriyya ya kashe da kudi sai Haladu da Sakina.

Huzaifa yacewa Alim malam dan Allah ka shiga wajen Baba ka fito mu tafi dare nayi mana,
Murmushi Alim yayi, Amana tace karka damar min miji dariya sukayi gaba daya.
Suna shiga Baba ya dinga zagin Alim da Bala'i. Yace kuma dole ka sakar min yata gadon tsiya, Amana ce take kuka haba Baba wannan butulcine,Baba yace Butulcin Ubanki akan sun bamu yan kudi da yi mana wannan gidan.gidan banza gidan wofi nan fa Ba irin cin mutuncin da

Baba baiwa Alim ba,Alim sai hakuri yake bashi tunda shi Bai San dalilin zagin da Baba ke masa ba.

A hankali yace Baba kayi hakuri amma bazan iya sakin matata ba,

Baba sai da yaja nishi sosai sabo da azaba ciwo yace da yake uwarka ce ta haifa min ita ko kai nafika iya shege na fika tantiranci,ka tambaya kaji gogaggen dan duniya ne ni nafi karfin uwarka ma.

Amana cikin kuka tace Baba wai Mene haka dan Allah,Jan hannun Alim tayi muje kawai na bika mu koma Lagos.

Baba yace kije gidan uwarwa kai na fiku tasha wlh,kaje ka kawo min takardar yata kuma saki uku tafi ka bani waje ke kuma na fada miki idan kika kuskura kika bar garin nan namu to ban yafe miki ba,

Amana tace Baba iya garin nan ko ka yarda na fita na zagashi yace ae iya garin nan zaki zauna,ko gidana zaki bari to ki zauna iya garin nan kiyi ta yawon duniyarki amma a anan garin.

Shi Baba ganinsa ya kafawa Amana tarko,Alim yace Baba na tafi Allah kara Ify ya zaro damin kudi ya ajiye masa,Baba ba kunya ya karbe tare da Jan tsaki

Amana suna fitowa waje tacewa Alim sallami Huzaifa ya tafi gida ni kuma ka jirani muje wani gida a garin nan tunda Baba Bai hanani fita a nan ba.

Haka kuwa Huzaifa ya tafi Amana ta dauko kaya a hand Bag Babba tace muje,Alim yace nifa tsoro nakeji kar Baba yayi mana wani Abin,

Dariya Amana tayi tace rana zafi inuwa kuna both Mum naka da Babana ai kawai muyi me dalili mu rufta kawai Baaaba komai ta fanjama fanjama.

Dariya Alim yayi tare da lakace mata hanci,taja Hannun Handsome Alim suka Sha kwana ta wani lungu.

AsmaBaffa

Tnx all

CIRANIN AMANA

140-145

Official

By
AsmaBaffa

QUEEN MERMU AGAIN,THS PAGE IS FOR UUUUUU

Corner su Amana sukesha kawai ba ji ba gani har Alim ya gaji yace gaskiya honey a tsaya am so tired daga cewa ba nisa nan nan sai Shan corner mukeyi da layika,
Kafeshi tayi da Ido duk ya jigata saboda Sam Bai Saba da wahala ba,gashin kansa ya hargitse harda bige kafarsa domin wajen ma ya dan yi jini kadan,
Lazy kawai kamar ba Namiji ba,yanci zamu karba wajen iyayenmu Amana ta furta tana kada masa idanuwa,murmushi Alim yayi kinga karfa wani yazo wucewa ya kallar min farin da kike min da ido am gealous,
Kuma taya zamu karbi yanci a haka wai ma ina zamu‹hope dai baza mu Dade ba kinsan Aabid dina yana can Mum zata kara lalata minshi da wasu halaye kina gani yaron yanzu kullum boyeshi takeyi a room dinta ko ganinsa bamayi a gidan makaranta ma ba kullum take bari yana zuwa ba,yaron kafin na zo nan na ganshi duk ya rame,idan yace Momy ko Daddy Mum makeshi takeyi,wlh na rasa yanda zanyi da Abin ga Aabid saurin girma gareshi...

Nasan komai fa ba sai ka fada min ba Allah zai kawo mafita kaji sai hakuri,kwalla Alim ya share da sauri kar Amana ta gani,ita kuwa Amana ta gani amma sai tayi kamar bata gani ba,Naushinsa tayi kadan a kirji ba shiri ya saki kara ouchhhh.....be a man,u have to be strong fa muje ta kama hannunsa oya muje kawai,
Sun kara tafiya me Nisan gaske kamar zasu bar garin sannan suka isa wani dandasheshen wani gida dan karami harda gate yasha tiles da flowers.
Gidan ta kwankwasa wata dattijuwar mata ta bude tare da fitowa nan take matar ta washe baki tare da cewa barka da zuwa Hajiya,
Amana tace yawwa suka gaisa,matar Sa'adatu tace Hajiya lafiyar gidan kikazo dubawa domin nasan mun biya kudin hayarmu
Amana tace Sa'adatu wannan miji nane shine me gidan nan mun dawo zamu zauna a

saman benen tunda dama iya kasan na Baku haya nace Ku dinga hawa kuna gyara min sama kar a bar mana gida da dirty,

Murmushi Sa'adatu tayi tace hakane komai yana nan tsab a part dinku wato upstairs,bari na kira mijina,

Malam Salisu ne ya fito suka gaisa cikin mutunci sannan Amana ta masa bayani ta kama Alim suka haura sama part dinsu,domin gidan part biyu ne,kasa 3 bed room ko wanne da toilet,sai Palo kitchen da toilet,saman ma haka take komai da komai. Sa'adatu da Malam Salisu sai yaransu 3 babbar macece yar 20yrs Iklima,kamal da Yahaya suna part din kasa.

Alim shi kam mamaki yakeyi Amana yaushe take da gida bari su huta zai tambayeta, Suna shiga abin mamaki latest dubai furniture ne a saman yasha Alatu,sosai an kawata part din da kaya na Alfarma amma komai a rufe da ledarsu.

Amma Sabo da Sa'adatu na gyara shi kullum ta kulle da key kal kal komai suke sai kamshi ko ina ke yi kasancewar Sa'adatu me tsafta ce.suna shiga ya shige bedroom kalar bed din sun birge Alim tafiya yayi da niyyar fadawa bed din domin ya gaji caraf Amana ta damkoshi tare da jawoshi baya tare da kakkabe masa rigarsa wai zai bata jikinsa,

Ledar dake lullube da katifa ta kwaye nan ta leka kasan bed din fes dashi Sa'adatu na daga katifa ta share da moping,sip ta bude ko ina bedsheet ne kalakala sun kai 5 masu kyau ko wanne room da kalolinsu,duk ta da musu turaren ajiya a ciki sai kamshi sukeyi,share room din tayi tare da moping cikin zafin nama dan babu abinda babu a part din na amfanin gida komai Sabo kamar sabuwar Amarya nan ta shimfida bedsheet wani Mai kyau na gaske,room freshner ta fesa da turaren wuta ta kunna, toilet ma ta kara wanketa fes fes, kafin kace me room din ya dau kyau, palo ta fito Alim ta hango a tsaye yana ta layin gajiya sai rufe ido yakeyi gashi Amana ta hanashi zama wai zai bata kayansa,

Ido suka hada ta kashe masa ido daya tare da jan hannunsa ta kaishi har kan bed din riga ta cire masa da wando daga shi sai tight da singilet sannan tace oya slip kafin sallar isha bari na kara sa aikin,sai binta yake da kallo wani farin ciki ya cika masa zuciya.

Ficewa tayi haka tabi ko ina a upstairs part dinsu ta cire ledar kayan ta gyara komai ta share ta goge ta kunna kamshi sannan ta kunna Ac ta duka dakunan kasancewar da wuta tuni gida ya dau kamshi,waje ta fita ta siyo taliya spagetti da kayan miya hade da danyen kifi harda indomie da kayan shayi da wasu abubuwan na amfani da babu,direct kitchen ta shige kamar kitchen din Amarya komai na harkar kitchen akwai kayan abinci ne kawai babu fridge ta kunna ta zuba lemuka da ruwan robar da suka siyo sannan ta fara girki, ko gas babu sai kerozine da ta siyo ta cika katona resho ta,ta kunna miyar jajjage tayi tasha kifi ta dafa taliya sai coffee da ta hada ta cika musu flask ta shirya abincin a dining sannan ta gyara kitchen din kamar ba a ciki tayi girki ba,toilet ta fada a dayan bed room din wanka tayi sosai,

Ba sallah takeyi ba tana fitowa gashinta ta busar da hand drier da ta taho da ita a jakarta sannan ta shafa lotion dinta ta shirya cikin wata gaunt iya gwiwa me dogon hannu peach color toilet ta koma ta wanke kayan data cire tare dana Alim data cire masa ta Shanya su.

Zama tayi ta rangada kwalliya sai kamshi takeyi sannan ta dauki jakarta ta koma dakin da Alim ke ciki,tana shiga ta tadda shi ya tashi sai mika yakeyi da salati bakinsa dauke da addua

Sabulu da sabon soso ta kai masa toilet sannan ta dawo ta zauna kusa dashi ta zo zata rungumeshi Alim ya buga tsalle ya ja baya,

Tana dariya tace Ify? Murmushi yayi yace rana ta dake ni dazu ga tafiya munyi da kafa nayi dirty ai sai ki shafi dirty na,

Amana tana murmushi ta karaso kusa dashi suna facing juna tace see u kaji kamshin da kakeyi kuwa zaka ce kayi dirty,babu me cewa kayi wani tafiyar kasa,come here joooo ta afka tare da hugging Alim harda cusa kanta a kirjinsa tare da manna masa kiss normal babu wani canji saima kamshi da yakeyi,

Brush da toothpaste ta mikawa Alim to maza yi wanka ka fito tare da mika masa towel ya shige ta rufo masa kofar.

Wasu sabuwar farar jallabiya da sabuwar singlet da boxers ta dakko cikin wanda ta siyowa Alim da taje cikin Kano hospital kai Baba shine suka je ShopRite ita da Sakina sai ta ajiyesu da nufin idan ta koma lagos zata bashi.

Yana fitowa ta mika masa mai me tsada da kamshi ya shafa sama sama,turarukanta ta mika masa ya shafa sannan cike da mamaki tambayoyi cike a zuciyarsa yasa kayan da ta bashi dai dai shi kamar an auna yayi kyau sumarsa sai sheki takeyi,comb dinta ya karba ya taje kansa,

Tunes ce ke kwakularsa Bai gama Shan mamaki ba saida Amana ta jawoshi Palo saman dining food flask hadaddun gaske nan suka ci suka Sha suka godewa Allah,

Kwanikan ta kwashe suka koma Palo ya jawo Amana jikinsa suka kwanta a kan 3seater suka mamuki juna domin a kan jikinsa ta kwanta,

Ga plasma TV Amma ba a hada kayan kallonba

Gashin Amana dake matukar fidda kamshi ya fara shafawa a hankali kana ya fara magana kasa kasa Amana tashi zaune muyi magana,ba musu ta Mike tare da Zama suna gugan juna,yace tambayarki zanyi duk wannan Abubuwan ina kika samosu wai I mean gida,food,kayan jikina etc.

Murmushi tayi sannan ta Mike tace ina zuwa bedroom ta shiga handbag ta bude ta ebo wasu takaddu guda uku ta fito dasu ta zauna kusa da Alim tace Babyna ba Abin mamaki bane,

Wannan gidan daka gani gidanka ne,sanda ina gidanka ina Kula da Aabid dina kana bani kudi masu yawa haka duk wata a accnt dina kana biyana kudi kafin a daura mana aure

Numfashi ta ja tace to da kudin da kake bani na sai maka wannan gidan har kayan dake ciki dalilina kuwa ko Mum tace ka sakeni nasan baza ka iya ba idan ma ka sakeni kaga sai na fada ma na dawo gidan nan da Zama har Allah ya dai daita komai,Ko iyayena basu San da gidan nan ba,Badriyya da Ya Hamza ne kadai suka sani domin su na turawa kudin nace su sai min gida,to sai suka ga wani ya gida wannan wai baya son gidan garin ya masa kauye da yawa shine suka fada min nace su siya min da shedu,

Takardar shedar gidan ta mika masa da sunan Alim da komai a jiki daya takardar ta kara

mika masa ga wannan shi kuma takardar kayan da aka zubane gashi,kayan sawa dana Baka shekaran jiya munje kai Baba hospital Kano city na siya ma da niyyar na Baka idan na koma lagos suna cikin akwati da yawa gobe zan dauko ma a gidanmu

Abinci kuma kana bacci na siyo kayan dafawa na yi mana duk cikin kudin da ka bani dazu a gidanmu,

Mamakin Amana ya cika Alim gaskiya Amana macece ta gari duk da basu da kudi amma gashi Abin duniya Bai dameta ba,da wasu ne ai iyayensu da yan uwansu zasu bawa komai har cutar mijin zasu dingayi

Firgigit ya rufe bakinsa sakamakon Amana data hade masa su waje daya.

Mika mata takardar yayi yace wannan gida ni Alim na mallakawa mata ta halak malak shi ga takaddu rikesu,

Amana cike da shagwaba tace Allah Baka isa ba yaro dankwali yaja hula,kaza ta janye zakara kayi gida a garinmu wooooo

Dariya Alim yayi yace bazan karba ba kukan shagwaba Amana ta fara dole sai ya karba ita me zatayi da gida,ai bata fatan ta zauna ba a gidan mijinta ba,dole Alim ya karba sabo da rigimar Amana,sallar isha yayi da nafeela yaja Amana suka fada Bed nan Alim ya shiga romancing dinta ya fara magana da.....

Mum ce zaune gefen Abba ga su dan Auta,Abba ya kalleta yace Ina Nura ki fada masa gobe ya dauki matarsa su koma gidansa an karasa masa ginin gidansa anyi komai,nan take Mum ta hade rai tace yanzu duk Fadin gidan nan Alhaji sai kace sai sun koma gidansu fisabilillah,Aabid ne ya shigo room din tare da Islam yar gidan Nura,

Mum ce ta dauki jikokinta tace ai Ku muna nan tare daku ko? Aabid cikin masifa da kuka yace ni Bana sonki Momyna new Anty nake nema da Daddyna,make masa baki Mum tayi ta jefoshi kasa Ku fita yan iskan yara kunyo halin iyayenku.

Abba ne ya jawosu jikinsa ya fara lallashinsu sannan ya fara balbale Mum da masifa sosai,Dan Auta yace gaskiya Mum wlh bakya kyautawa ki dinga dubawa dan Allah.

Zakinsa Mum tayi ya tashi ya bar dakin amma Mum tace dole Nura da matarsa ma a gidanta zasu zauna baza su taba komawa gidansu ba,matar Nura har kuka tayi tace dan Allah Mum kiyi hakuri ai nan Mum ta kurma ihu da kukan karya tace matar Nura ce ta zageta babu wanda ya saurareta.

Yau kwanan Amana da Alim Uku a gidansu dake garin,sun siyo kayan abinci komai da komai,sannan Amana ta dakkowa Alim wasu kayansa na wajenta,itama ta kwaso nata Sulemanu Harka da yan gidan ba wanda Yasan a inda Amana take kwana domin idan tazo duba jikin Baba zasuyi hira da yan gidan da iyaye har Ummanta amma ba wanda ya taba tambayarta a ina take Zama,Badriyya kadai ce ta tambaya  Amana ta bata labarin komai,Badriyya tace Good gwara haka,Huzaifa ma ya sani sai dariya yakeyi mace ta rike Namiji.

Da ATM card din Alim suke cire kudiin da suke amfani dashi Amana ta San code number dinsa komai tare sukeyi soyayya suke Sha kawai danma Amana na period ai maybe da tuni tayi ciki.

Sati daya tsakani Mum ta samu Abba tace ya kamata Alim ya dawo gida haka nifa ban yarda da yaron nan ba,masifeta Abba yayi ya fara ki yayeni wlh zan baki mamaki shashasha uwar Banza,

Tsaki Mum taja tare da ficewa ta fara neman Number Alim cike da fushi,

Alim kwance kan cinyar Amana suna kallon news kiran Mum ya shigo,ya kai hannu zai daga Amana ta kwace wayar tace karka daga ka jirani zuwa dare zamu kirata back.

Murmushi Alim yayi yace nasan bakya fake mission Allah kaimu.

Waya ta daga ta kira wani dan daba dan wiwi tace ya Akayi Sa'idu kunkuru Amana ce mu hadu A shagon Bilya No sleeping no sitdown ka gane? Cikin muryar daba yace an gama Baabaa sa'a dai chau wlh ba yawa.

Tana gama waya Alim ya fara kishi da masifa,da kyar ta shawo kansa ta ganar dashi dalilinta sannan yayi shuru.

Da dare kuwa ta jashi har shagon no sleeping no sitdown wasu tantiran yan kwayane da wiwi.

Ko Ina kallon Alim akeyi dan gayu bature

Suna zuwa Kunkuru yace fada min matsalarki,nan Amana ta musu bayani suka Sha dariya,wayar Alim ta dauka tare da dan nawa Mum kira ta mikawa kunkuru,

Cikin muryar Basawa Bilya Kunkuru ya ce Hello Iyya danki Alim ya mana yawa yanzu zamu cika masa aiki,Mum taji murya kamar ta mugyanbo ta fashe da kuka tace dan Allah karku taba min dana ko nawa kuke so za a baku wayyo na shiga uku,

Duk Mum ta rikice,Amana ce ta amshe wayar tare da canja muryar katon gardi tace Hajiya kuyiwa danku zaman makoki kawai ba kudi muke bukata ba,munyi kidnapping dinsa zamu aikashi Can,Mum ta fashe da kuka Amana tace Baabaa ba yawa a fede min shi.

Alim ya tafi duniyar tunanin da mamakin Amana yaji kwanya masa mintsini ba shiri ya rafka kara,sai Mum ta kwalla kara ta cikin wayar ta fara kwalawa yayanta da Baban Alim kira.

Abban Alim.....Nura....na shiga uku Nura.....Ku fito kuji shike nan Alim wayyo ina zan sa kaina na shiga uku dan Autana Ku fito.

Kit Amana ta kashe wayar Alim baki daya ta cire simcard din tasa sabo a ciki,tayiwa su Kunkuru sallama tare da basu kyautar kudi.

Sun kusa zuwa gidansu a dan wani lungu me duhun tsiya Alim ya manne Amana a jikin wata katangar gidan wasu ya fara tsotse bakinsa baji ba gani,Ya bita da mirza dukiyar fulaninta,sun fita daga hayyacinsu sosai a lungu wani dan tsoho yazo wucewa ya kunna torchlight me mugun haske ya dallesu da ita nan take tsoho ya saki salati da karfi harda kuka ya fara shike nan karshen duniya yazo tamu ta kare shegu tambadaddu,kara haskasu yayi yaga ko

kallonsa basuyi ba sai kara salo sukeyi Amana ta juye Alim ya koma shine a jikin katangar, sai sakin kalamai sukeyi wa junansu na tsantsan kauna

Tsohonne ya kara matsawa ya dallesu sosai Allah ya shiryeku watsatsu iyayenku nacan kunzo nan kuna lalata tir daku,Amanace ta juyo tsoho yace munafuka maza ki bari ya lalataki ki kaiwa Ubanki cikin shege har gida,akan kinganshi Bature Nasara asarar duniya shine kika tsaya yana wannan tabargaza dake...yiiiiiiii......tsoho ya fashe da kuka yace wlh Ku bar nan ko nayi maka ihun kwarto,Alim yace matatace fa,ai tsoho kururuwa yasa yace karshen zamani yanzu karuwarka har ta Zama matarka yanzu daurawa kanku aure kukeyi,Amana zatayi magana tsoho ya kurma ihu ga kwarto ai nan danan jama'a suka fito ta kudu da arewa da sanduna,Alim shi nufinsa su tsaya sai ya kare kansa,Amana ta tartare skert tace wlh baza su saurareka ba dukan tsiya zasuyi mana a kauye ne fa ba lagos ba Arewa fa ba kudu ba.

Zo mu gudu wlh kafin musha sanduna, Alim yace oh God ni da matata wai wannan ai sa Ido ne,Alim yaga mutanen da gaske suke Bai San sanda yaja hanun Amana ba suka arce sai a palonsu suka tsaya suka kulle ko Ina da key suna haki

Mutanen har kofar gidan su Alim suka ja birki tsoho ne ja gaba yace asararru Ku fito in kun isa,Amana ce ta leko tare da Alim ta saman bene ta haskosu da torch tace Baba tsoho kun gammu wullu,Alim yayi dariya tare da rungumo Amana su Baba tsoho suna kallonsu sai tsotsar juna sukeyi,

Tsoho ya kwalla da karfi in kun isa Ku fito baku cika marasa Kungs ba ai,Alim ya kwala da karfi shima yace Baza mu fito ba kuma dole mu kwashi duniyarmu,Tsoho ne ya kada kai yace Allah yana kallonku zaiyi maganinku ne duniya zata ladaftar daku karuwai.

AsmaBaffa masu comment tnx alot love u.
✳CIRANIN AMANA✳

145-150

Official

By
AsmaBaffa

MAMAN WALEEDA INA KIKA BOYE NE?

WANNAN PAGE NA 'YAN ASMABAFFA FAN'S CLUB NE DUK WACCE TAKE WANNAN GP TO PAGE DIN NAN NAKUNE LOVE U ALL.

Alim dai mamakin sa'ido na yan kauyen yakeyi Bai Saba ganin hakan ba Sam,
Sabo da haka ya dage dole sai ya ganar da tsohon nan gaskiya kar ya kala masa sharri
Alim ya kwallo da karfi Baba tsoho ka fahimceni mana matata ce pls ka gane,tsoho dai ya kara haskesu yace kai ni nan dan zamani ne harda hada dan turancinsa kalleni da kyau noti a small boyi ni big ne zaka mai Dani gara, uwarka ka yiwa ba ni ba shegen yaro,
Tsaki Alim yaja tare da dafe kai Amana tace ka kyaleshi kaima kasan fa ba ganewa zaiyi ba,
Tsoho yace kinyi da uwarki Abinda yasa muke yiwa irinku Wa'azi Ku tuba Ku daina saboda idan Allah ya tashi kamaku sai a hada da mu na gari wanda bamuji ba bamu gani ba wlh baza mu yarda da Ku a cikin garin nan ba,indai na isa sai nasa an koreku daga garin nan muna ji muna gani Ku jawo a kifar da garin ko ayi mana girgizar kasa,to Ku sani billahillazi la Ila ha illahuwa saina nemi me gidan nan wanda ya baku haya ya koreku ya tasheku da gidan nan,mu Malam Salisu dake kasanku mutumin kirki ne.Amana ce ta janye Alim,haka tsoho ya gama surutunsa ya tafi.

Kitchen Amana ta shiga Alim ya bita ciki suka fara girki tare,Alim Bai iya komai na girki ba kawai batawa yakeyi,
Garin yanka Alaiyafu ya yanke a yatsansa sai jini shar....Amana kamar itace ta yanke kwace wukar tayi ta kama yatsan toilet ta kaishi ta wanke masa hannun ta sa masa hydrogen ta manne masa da plaster,
Kallonta kawai yakeyi ji yakeyi kamar ya hadiyeta ya huta yanda take matukar Kula dashi.lips ta cuno masa shi kuwa ya miko nasa ya manta kiss,murmushi sukayi taci gaba da aiki a kitchen yana zaune a gefe yana kallon ta idan ta juyo suka hada Ido sai ta cunno masa lips ta turoshi sosai shi ma ya miko nasa sai muahhhhhh..... zuba masa kunun Aya tayi da ta hada yana tasha tana aikinta
Waist dinta ya rungumo ta baya da hanu daya daya hannun kuma yana Shan kunun ayarsa,
A hankali yake magana ayi sauri a gama girkin nan,mene kake sauri yunwa?hmm kema fa

kin sani tun kafin ki bar lagos rabona dake nazo nan kina period da kyar nake manage,kin gama kin hana min abina har kinyi kusan 4 days da gamawa ya karasa kamar zaiyi kuka.duk sai taji tausayinsa domin iyakacinsu romancing yana so haka zai hakura saboda tace tana Jin zafi kuma karyar Amanace kawai wai itama dan aji ta ja masa amma ko ita watarana tana so musamman Idan ta kalli kyakyawar surar Alim dinta me tsananin kyau da haduwa.

Bayan ta gama girki abinci suka ci tayi gyare gyarenta,fitowa tayi ta shiga bedroom dinsu Alim ta gani ya fito a wanka yana shafa Mai ba komai a jikinsa,

Amana dai wani yarrrrr yarrrrr take ji a jininta ,nan take taji tana matukar bukatarsa,sha'awarsa taji wacce bata taba jiba a rayuwarta, tsayawa tayi tana ta kallonsa kamar mayya,tongue dinta ta zaro ta lashi lips dinta sai lumshe Ido takeyi tana ta kallonsa,sai ta fara sosa wuya idan ya juya har dogon wuya takeyi wajen leko kirjinsa etc

Yana kallonta ta mirror amma bai Kula ta ba domin ta dan bashi haushi dazu a kitchen yace yana bukatarta ta shareshi ko kulashi ba tayi ba,

Rigar wankansa ya mayar harda kara daureta ya rufe jikinsa kirjinsa kadai ya bayya,Matsowa tayi tana soshe soshe Him.... uhmmmmm...uhm kallonta yayi tare da lullube jikinsa da towel yace Ify?

Uhmmmmm ba komai,dayan Bed room din ta wuce tayi wanka tare da sako wasu shegun kayan bacci masu Jan hankali tasha kyau tana bulbula kamshi,

Saman bed ta hango shi shima cikin shirin baccinsa ya mike kafafu sai danne danne yakeyi a system,

Jiki a mace tana karairaya hadi da lumshe Ido tana fari,Alim ya kalleta sama da kasa sai da ya girgiza ta gama tafiya da imaninsa,

Sha'awarta ta dawo masa sabuwa fil amma ya daure ya shareta,gyaran murya tayi hade da Zama kusa dashi tana ta binsa da kallo tana ina ina tace um.um..ta sosa kanta taci gaba baza...baza...kayi bacci yanzu ba?

Alim ya kalli yanda take kallonsa idanunta sun canja tsab ya ganota yasan me take so amma ba tare da ya kalleta ba yace kwana zanyi ina aiki yau,

Magana tayi tace to..to..to naga Alama tana ta zaune taki kwanciya sai satar kallonsa takeyi,

Kashe computer yayi Amana na ganin haka tayi Hamdala a ranta,bai kwanta ba sai ya zauna cure a bed din,Hannunta ta mika a hankali ta kama wasa da kafarsa,

Dauriya kawai yakeyi,gajiya Amana tayi matsa jikinsa cikin sigar shagwaba tace am in...in....the...mood kaji kayi wani abu sweet mana,ta kare zancen tana shafa hannunsa,matsawa yayi gefe yace dazu da nace I need u me kika ce min?sai yanzu zaki neman da yake bukatarkice I hope zan iya miki yanzu amma na gaji kin makara

Jiki a sanyaye ta Mike zata bar dakin tare da cewa ahhhh.....ok.....never mind ta fara tafiya ya fisgota ta fado kansa flat ya mata ya fara kissing dinta dama Amana jiran kadan takeyi ba bata lokaci suka gigita Kansu kamar mayunwata,Sosai Amana ke enjoying din abinda Alim ke mata ta bada hadin kai ta dage tayi iya yinta,ta gama baje basirarta a kan Alim,ta mishi abubuwa masu rikita hankali wanda ya Sha mamakinta yanda ta tafiyar dashi,gata gwarzuwa ce akwai juriya da jajircewa na ganin ta bawa Alim abinda yake so ,shima hakan take

Yau su Alim harda kwallar dadi da farin ciki,bai taba Jin makamancinsa ba,Amanansa ta

dabance sai da yayi round 3 ya kyaleta hakanma kawai kyaleta yayi dan kar ya shiga hakkinta Bai sani ba domin Amana Idan zaiyi sau 100 baza ta nuna masa alamar ta gaji ba sai ta daure,duk da cewa itama tana da karfin sha'awa kuma uwa uba tana Jin dadin harkar kasancewar mijinta ya hadu ta ko ina,style iri iri sunyi shi,tasha sambatu wajen Alim itama haka,saida suka nutsu ya shiga sa mata jerin Albarka,wanka sukayi tare da tsarkake jikinsu sai nafeela da sukayi da adduoi suka fada Bed hade da manne juna sai bacci.

Sulemanu Harka jiki yaki dadi duk yanda za ayi anyi masa ana ta kashe kudi amma kafunsa sunki doruwa,sai ma kara lalacewa sukayi yanzu kullum sai an fitar dashi an Shanyashi a rana a kofar gidansa,

Yauma yana kwance a tsakar gida sai numfarfashi yakeyi ya tambayi Badriyya ke ina Amana ta ke zaune a garin nan?Badriyya tace Baba nima ban sani ba tana dai zuwa dubaka kuma ta ebi kayan sawa ta tafi,duk kusan ta kwashe kayanta na sawa,

Baba yaga bashi da kudi kudinsa ya kare gashi ba fita yake ba ba Ify,ga ba Amana ba mijinta babu me bashi domin ko sanda Amana na lagos har kudi take tura masa.

Baba ya kwalla kara yace Wannan kwai gantalalliyar yarinya akan wannan shegen yaron ta bar gidana saboda nace baza ta koma ba,

Indai Namiji ne gata gashi na yafe mata taje tabi mijinta akan haka harda barin gidana,to ni dai na yafe mata ta koma dakinta yarinyar kirki ta gari bani da kamarta ga biyayya tafi kowa Jin tausayi na da bin umarnina,matansa da yaransa ya Tara ya fada musu dalilin barin gidansa da Amana tayi,babu wanda ya kulashi sai Umman Amana tace Baka kyauta ba kayi butulci,nan dukka gidan Akayi caaaaa akan Baba,yace to kuzo Ku dakeni Ku huta

Isa yace Baba matar da kake zargi itace Umman Alim wlh ba ita bace Baka ganeta ba,ni naga matar ganin idona,Babar Alim fara ce waccen kuma Baka ce,

Ka bari ayi bincike tukun amma mijin Amana mutumin kirki kalli yanda ya mai damu mutane,

Nan Sulemanu Harka yace to latso min waya ka kira min Amanata,Hamza ya fara kira amma bata shiga har Number Alim duk basa shiga,

Da dare Alim Zaune a saman kujera Amana na kasa magana ya mata honey yau mu dan fita mu zaga gari mana,

To bari mu shirya ko,wanka sukayi fes dasu suka hade cikin shiga me matukar kyau sannan suka kulle wajensu suka fito,da yake akwai wuta ko Ina da haske ba laifi,

Sunzo tsakar gida su shiga Wajen Sa'adatu suka gaisa sai ga Yarta budurwa Iklima ta fito sai kallon Alim takeyi taga baiwar cikar zati

Mum gaba daya ta rasa sukuni sabo da rashin Alim,gashi Abba yaki saurarar zancenta yace karyane dansa yana nan lafiya,

Su Nura ma shareta sukayi kowa ya kama harkar gabansa,matar Nura shanawa sukeyi da mijinta saboda Mum tana cikin damuwa bata kulasu,Matar Nura ke Kula da Aabid sosai.Mum kuwa kullum kuka takeyi harda Jin haushin Abbansu Alim shi ya cuceta ya tura mata da yaro aiki wani state.

Amana na kallon yanda Iklima yar Sa'adatu take kallonsa ta faki idon kowa ta dallawa Iklima harara,radawa Alim tayi tashi mu tafi tare da tamke fuska wai haushi,a hankali yace mu dan zauna ayi hira ko ma Saba dasu,Amana tace pls kaga ni Bana son wani sabo,mu kadai zamu dinga rayuwarmu.

Me za

Muyi a wajensu dama mutuncin makwaftaka yasa muka shiga,

Sa'adatu ce ta fito dauke da lemo da ruwa amma Amana tace sun koshi tafiya zasuyi,Sa'adatu tace da kun zauna munsha hira?Amana tace zamu dawo watarana ai,Alim yace to Mene mu zauna mana Amana cikin Jin haushinsa tace ko second Biyar bazan kara ba tashi mu tafi kawai ai yawo zamuje.muje to ya Mike sukawa matar sallama Amana tasa Alim a gaba kamar danta,suna fita Iklima tace Mama wlh wannan matar tasa masifaffiyace kuma kamar itace mijin yanda take abu ta gama mallake bawan Allah, wa ya sani ko asiri ta masa da ganin Alama,Sa'adatu cikin fada tace ina ruwanki dasu ki iya bakinki,Iklima tace ai naga ta gama mallakeshi wlh har ya bani tausayi.

Alim suna fita Amana tace Allah ya taimaki yarinya watarana ta gwada min hauka kamar yau ta gane shayi ruwane da kanta kamar kwallon kwakwa,Alim yayi murmushi ke ki kwantar da hankalin ki ke kadai ce ba Kari don ta kalleni sai me ni kinga na kalleta ne?to me yasa zaka ce mu zauna?nufina mu dinga zumunci,to bazamuyi dasu ba karma ka jawo na koresu daga gidan nan.

Sorry sarkin zuciya ni dai ki huce  kar mu koma gidan ki hanani Harka,da wasa Amana ta dalla masa harara sunan Babane fa Harka,sorry na manta I swear

Dariya Amana tayi tare da rungumeshi tsam haba dai ai kome zaka min bazan hanaka komai ba,ba wannan shirmen ai sai kace yarinya marar tunani,idan ana Jan fada haka ai aure baya lasting duk fadan da zakuyi da mutum matukar baza Ku raba makwanci ba to dole a shirya da wuri bare har ya kai ga saki,kiss ya manna mata tare da shafa wuyanta a rungume da juna suke

Suna tsaye sai ga Baba tsoho yana takawa da kyar ya dawo daga masallaci ya kara biyowa ta wannan lungun me duhu,wannan karan tsohon masifa yakeyi a hanya sosai,Alim yace laaa ga tsohon nan  na ranar nan mun ga ta kanmu

Tsoho Ashe yaji me Alim yace yace bakuga ta kanku ba sai Allah ya damkeku da kansa,

Yau ba ta Ku nakeyi ba domin kun Zama Bala'i sai sadaka,

Amana tace Malam me aka maka yau kake fada?yace kedai bari karuwai wlh wasu yarane suka bata min  tsoho ya fara basu Labari wai wasu Samari ne a masallaci kullum sai sun dagashi bayan an idar da sallah saboda bashi da karfi da kyar yake tashi ma,

Kawai sai rannan matarsa ta haihu gobe suna shine ya bada Sanarwa a masallaci gobe za a rada suna matarsa ta haihu samarin nan suna jin haka suka saki dariya tare da cewa ah....tsoho Ashe kana da karfi yanzu har matarka ta samu ciki ta haihu ta wlh baza su kara dagashi ba sai dai idan ya kasa tashi ya kwana cikin masallaci tunda har  yasan zai iya wata ciki,ai kuwa su Alim suka dinga dariya,Amana tace Baba dai dai sukayi wlh gwara haka,

Tsoho yace ai gwarani ba dan iska bane irinku,karuwai shedanu,Amana tace wlh Tsoho muna da aurenmu fa,yace ban yarda ba ko sama da kasa zata hade bazan yarda ba kuna da auren

zaku dinga bin lungun masu shegen duhu ba kunya ba komai,
Da Allah kar Ku kara min takaici wai yanzu ace yaronka Bai jawo ma magana ba wasu a titi na kwararo su dinga sawa zuciyarka na tafasa.
Dariya suka karayi tsoho yace kwayi da wani marasa mutunci.
Alim ne ya zaro kudi masu yawa ya mikawa tsohon Baba ga wannan ka siyi rago ko
tsoho yace wuuu...rufani ka sayani dannan niiiiii na karba kudinku na haramci inma cin hanci ka bani wato dan na dinga rufa muku asiri kuna shekewa to ni Bana karbar cin hanci,bazan rufa muku asiri ba,zan karba na gode kuma amma kar kusa rai zaku zauna lafiya a unguwar nan sai na sa me gidan ya koreku,tsoho ya karbe kudinsa yana godiya,wata mata tazo wucewa Ashe tasan Amana nan suka gaisa sosai,tsohon nan har ya fara tafiya ya dawo yace Delu wato ke kike daure musu gindi ko har gaisawa kukeyi?Delu tace kaji tsoho da sa Ido to har duwaiwai na hada na daure musu karewarta,tsoho yace Bana ja'in ja da matar wani yayi tafiyarsa yana masifa wlh sai ya tonawa su Amana Asirinsu.

Delu tace tsohon nan sai hakuri ta wuce,su Alim suka tafi yawonsu sosai suke Jin dadin yanayin.

Saude ce zaune a wani rubabben dakinta dake kauyensu tana waya tana faman sheka dariya,ba a Jin me suke fada sai dariya r Saude kawai kake ji.
Alim da Amana sun Dade suna zaga garin har 10 na dare sannan suka dawo gida hannunsu rike da ledar da suka siyo gashashiyar kaza da yogourt.
Suna shiga cikin gidan Amana tace ayi rige rigen zuwa Palo,ai kuwa Alim yace 1,2,3 go suka zura da gudu Amma Alim ya Dade da shiga Palo sannan Amana ta karaso ciki tana nishi tare da kukan shagwaba ni... ban yarda ba Allah,dariya sukayi gaba daya suna ta faman haki,ta fara masa rigimar sai ya goyata,haka ya goyata har saida ta fara bacci a bayansa sannan ya samu Ify,
Dole ya tasheta suka ci namansu da wanka sai bacci,
2:30 Alim ya farka da rigima ya fara tashin Amanarsa Babyna Baby,cike da maganar bacci tace naam mene?cikin kulawa tayi magana tana mayen bacci ruwa zaka Sha?yace ae Mikewa tayi zaune zata bar kan bed ta kawo masa ruwa,cike da sha'awa yace honey naki nakeso fa,dukan wasa ta kai masa sukayi murmushi nan suka karashe Daren suna ta faman raya sunna.

AsmaBaffa

Ina godiya masu sharhi kune nawa.

✳CIRANIN AMANA✳

150-155

Official

By
AsmaBaffa

ZAUREN QUEEN MERMU DA TASKAR FIDDAUSI SODANGI WANNAN PAGE NAKUNE. TNX ALL.

Bayan 3months Mum Alim ta shiga damuwa,zuciyarta dankare da bakin ciki,haka Sulemanu Harka komai sai dai ayi masa baya iya komai ya rame yayi baki ya tashi daga aiki,gashi Bai yiwa yaransa abinda ya kamata ace iyaye sunwa yayansu ba,bai sauke hakkinsu ba,ya gama zubar da mutuncinsa duk da cewar suna masa komai da ya dace amma basu damu dashi ba ko ya mutu ko yayi rai harkokinsu sukeyi domin mazan ma sun koma state din da suke business wasu kuma sun dawo Kano da kasuwanci duk cikin tallafin Alim gashi Hamza Babban yaya da kb sun samo matan aure a city har an musu engage,
Badriya ma maganarta da Huzaifa tana tabbata sai karfi takeyi,

Alim ne yayi shiri da safe da wuri yace zaije banki ya curo musu kudi,cikin shadda dakakkiya yake dinkin fited yasha kyau har bakin titi Amana ta rakashi ya shiga taxi drop ya wuce
Ta dawo ta gama komai na gidan tana Jin zazzabi kadan kadan har ta kwanta tana tunanin rayuwarsu ita da mijinta,
Gaba daya jinta take bata da lafiya kawai hijab dinta tasa ta tafi hospital sabi da ta tsorata this mnth bata ga period ba,kuma Alim yace mata indai unguwa ta kama da lalura to ko baya nan taje kawai ya yarje mata,
Karamin asibiti taje a cikin garin saboda yana da girma garin nasu,ana aunata ciki ya bayyana a jikinta wata daya,magungunan da aka rubu ta mata ta siya ta wuce da result a hannunta tana

ta murna,ta matsu Alim ya dawo ta bashi labari,

Kasa hakura tayi tun a hanya ta danna masa kira a waya cike da nishadi shauki na kwasarta tace my Man yaushe zaka dawo? Alim yace nan da 3-4hrs na biya ta wani waje,

Amana ta saki murmushi tare da furta Allah dawo min da kai lfy,murmushi Alim yayi cike da zallar

Kauna ta gaske sannan a hankali yace Ameen sai na zo me zan kawo miki?anything kawai cewar gogar,sallama sukayi ta koma gida tare da bajewa a 3seater.

Alim Bai dawo ba sai 9pm ya kwankwasawa yayi tare da murda handle,Amana ta fito daga kitchen tasha kyau da sauri ya jawota jikinsa yayi hugging dinta yana murmushi sannan ya mika mata ledar hannunsa,

Wani dan kyakyawan saurayine ya fito fit daga bed room din su Amana yana sweetheart kin barni ina t faman jiranki kiyi sauri muyi abinda za muyi kafin dare yayi nisa ina da aikin yi ....kamar gaske saurayin nan ya tsaya cak yana hangame baki yace dama cutata kikeyi kin San kina da aure kika ce nazo,

Da gudu saurayin nan ya nufo Amana tare da kwasheta da wawan mari yace kin cuceni Allah ya isa ban yafe ba nayi tarayya da matar aure.

Ya bude kofa ya fice fit,Yana barin gidan wata dalleliyar mota ta tsaya gabansa ya shige suka bar garin gaba daya.

Alim kamar gunki haka ya tsaya yayi poster sai hawaye da suke ta bulbula kamar famfo daga idonsa,Amana kuwa da ledar da Alim ya mika mata da result na ciki na hospital ta saki a kasa,

Kafin kace me ta sume sharab a wajen,

Alim kuwa innalillahi kawai yake maimaitawa sannan ya shige bedroom ya tattara nasa ya nasa kaf,ya fito ganin Amana har yau a sume sharab a kasa kallo daya ya mata ya tsugunna tare da daukan result din hospital dinta ya duba hawayensa ne suka karu kamar ba Namiji ba ya zauna ya dinga rusa kuka,

Yana why....why.....na bar yan uwana da iyayena duk sabo dake,Mum dina ban San wannan Hali suke ba,sai yanzu Alim ya gane kuskuren biyewa shawarar Amana da yayi sabo da so ya rufe masa Ido,Mum dinsa tana can cikin bakin cikin rashinsa har cuta tayi sabo da son da take masa,ta dauki cikinsa,ta raineshi amma yanzu ya gujeta duk da Mum Nada babban laifi amma uwa uwa ce baza ka biyasu abunda suka maka ba,sune sular zuwanka duniya Harka hadu da wata,

Amma yayi fushi da Mum dinsa ya barta saboda matarsa kuma yasan dole tana cikin wani hali tunda duk tafi kaunar Alim cikin yaranta,

Kuka sosai Alim yakeyi,ashe Amana dai Amanarsa take ci,yana ta shirme akanta yana biye mata,bai taba zatan zata aaikata haka ba,tunani yayi sosai da karfi ya furta no.no...nooooo...baza tayi haka ba,

Amma Sam zuciyarsa ta hanashi tunani bare wani bincike,ji yayi ya tsani Amana gaba daya baya kaunar ya bude Ido ya ganta,sambatu yakeyi sosai idonsa jajir jijiyoyinsa sun tashi rada rada ji yake kamar ya kashe Amana ya huta,

Ya yarda a gaban ko waye zai iya zubar da mutuncinsa kan Amana domin ya faranta mata,

A titi,a lungu,a kwararo,a bainar jama'a duk saboda yayi proving dinta yanda yake sonta,dan

yasa taji duk duniya ba kamarta tafi kowa sa'ar miji,har ana ce masa kwarto sabo da ita,

Abinda watsatsun yan mata keyi a boye a titi yayiwa Amana shi tana matarsa amma duk wannan Bai hanata neman maza ba,

Ashe makaryaciyace,ta yaudareshi,mikewa yayi da niyar tafiya

Amana ta ja dogon numfashi ta farfado,zumbur ta Mike tare da rike rigarsa tana kuka wiwi kamar ranta zai fita,da kyar tace pls....ka...sau...rareni...dan Allah wallahii ban sanshi ba,kayi tunani da bincike sharri aka mana kasan muna da makiya,hannu biyu Alim yasa yaci kwalar Amana tare da girgizata da karfi ya makata jikin bango ya shaketa sosai tana ta kakari,... sannan yace ohhh makiya ko......da karfi yace makiya Mum ce makiya ko?Amana ta kasa magana sai hawaye nan Alim ya jefar ta kasa ta zube rigip,juyawa yayi tare da cewa kar ki sake ki nemeni,kar naga kafarki a gidanmu bana son ganinki na tsaneki,

Inda kika San zamu hadu kar kibi ta layin coz idan na ganki cikin karaji ya karasa I will kill u.

Result din ciki kuma ki haihu ayi DNA test idan har nawa ne zan karba.ya bude kofa baram ya kara makota ya bar gidan,

Direct airport Alim ya wuce ya bi flight sai Lagos inda akafi wayo.

Amana kuka takeyi tana salati sallah tayi tayi addua sosai hawaye kuwa yaki tsayawa a idon Amana,bata San wannan tsinanne ne ya hada mata wannan sharri ba.

Tattara nata ya nata tayi itama cikin dare tana zabga kuka ta bar gidan ko su Sa'adatu bata yiwa sallama ba,tana fita ta fara tafiya a kasa wani Almajirin kusa da gidansu ya biyota yana dan Allah Anty ki bani sadaka dare yayi banci komai ba,wani takaici ne ya kara kama Amana ta kara harzuka ta hayayyakowa Almajiri da masifa cikin kuka kai dalla karka dameni ka kyaleni naji da matsalata,da wannan matsalar dana shiga gwara na kwana 3 banci komai ba,dallah matsa ta furta tare da tallafewa Almajiri keyarsa ta jefa masa  Dari Biyar,

Tana yin gaba ta hadu da karamar kanwarsu Zaliha ta siyo sugar a kanti na gobe da safe,Zaliha tace Amana kece da dare yau me ya sameki Baba yana ta nemanki har ya rasu ma naga su ya Haladu suna ta kuka da Umma,ai Amana kafa tasa tayi short da Zaliha,

Ta kara gaba,Zaliha ta gama kukanta ta bi bayan Amana suka shiga gida,tun daga tsakar gida taji kukan su Haladu da gudu ta fada dakin Baba,Baba ne a kwance yana ta suma yana farfadowa ya suma yafi sau saba'in gashi yace Baza a kaishi asibiti ba,an tafi dashi yace duk wanda ya kaishi asibiti Bai yafe masa ba,haka aka dawo dashi,

Amana kan Baba tayi tana kuka ta cakumeshi tana Baba dan Allah karka tafi ka barmu muna sonka Baba,

Farfadowa Baba yayi tare da damke hannun Amana ya fara magana da kyar Amana...ta....da yan uwanki Ku yafe min ban muku tarbiyar kirki ba na sabawa Allah da yawa kin min Wa'azi naki ji ga yanda duniya tayi min juyin wainar Asabe,ki rokar min matana iyayenku su yafe min,gwaggo uwar gidan Baba tana sheka kuka tace mun yafe maka   Allah Baka Ify,

Sauran matan ma suka ce sun yafe suma ya yafe musu domin irin zagin da tsinewa Sulemanu mijinsu da suka dingayi kullum a maimakon suyi masa addua,

Tari Baba yayi yace Amanata ki koma dakin mijinki na yafe miki ki yafe min kin Sha wahalar rayuwa na turaki Cirani saboda kina min Wa'azi kaico na,

Badriyya tace Baba mun yafe maka dan Allah kar tafi ka barmu muna sonka,muma munyi maka laifi sosai bamuyi ma biyayya ba,Sakina cikin kuka tace Baba wa zaimin kayan daki idan ka tafi wayyo gashi na samu miji gatana ya kare bango ya fadi,kayan daki Baba gashi ko secondary ban gama ba,Sadiya wacce ke Aure a Gaya Ig tace Baba gashi su Hamza sun fara kudi Amana ta auri me kudi karka tafi baka dangwali dadi ba Baba,

Kb ne yace baku da hankali Ku ta abin duniya kukeyi ko,Baba ne ya fara tari ba ji ba gani sannan ya lafa,Amana ya damko yace ga Amana nan na daura mata nauyinku gaba daya saboda nayi Imani duk abinda zan muku Amana zatayi muku shi domin tafi kowa hankali,kyauta,da son zumunci,Amana ke ce wakiliyata ki rike min Iyalina ki maye gurbina,ga yayyenki Maza da sauran Ku hadu kuyi zumunci Ku tallafi juna,ku Manyan maza abinda Allah ya hore muku Ku tallafi yan uwanku Ku hade kanku babu yan Ubanci duk da nasan dama bakwa nuna yan Ubanci Ku kara akan Nada,

Ku Zama masu hakuri,juriya,hankali da nutsuwa duk fitinar da kukeyi da kuyi kokari Ku daina saboda nasan kun daina Amma a kara jajircewa duniya ba matabbata bace,hakuri da yafiya shine komai Ku rike wannan komai akayi muku banda daukan fansa Ku Zama masu yafiya da kawaici,a tsare mutunci, amma kar Ku bari a rainaku ko ubanye Ku taka masa birki.

Baba ya kara Suma ya farfado ya Dora da nasan Amana da saurin zuciya kike dan Allah ki dinga salalawa ga maza nan zasu tayaki Ku Kula da kanku,ga takaddun dukiyata nan nayi rubutu na fitarwa da kowa gadonsa yana nan rubuce a cikin littafin nan,Amana nafi yarda da ke me adalci ce dauki ki rike a hannunki,Amana dai sai kuka kawai Baba sai nauyi yake Dora mata Bai San ma Alim ya gujeta ba a lokacin da take  bukatarsa.

Baba yace Ku kuma matana wacce taga zatayi aure to tayi aurenta amma ta barwa yayana a cikin yan uwansu ban yarda a rabamin kan yayana ba su zauna tare su so junansu zumincinsu yayi karfi,

Kuci gaba da min addua ko Allah zai karbi tubana ya yafe min,na barku da alheri.

Nan Baba tari ya turnukeshi yana ta murkususu Bai kara minti biyu ba yace Amana ki tallafi zuri'ata tayi kyau,ta gyara,abinda banyi ba kiyi musu kiyi iya kokarinki ki bar sauran ga Allah,

Gaba dayanku Maza da mata Manyan Ku tallafawa Amanata Ku Kula da kan....k...luf Baba ya cika Allah ya karbi rayuwarsa cikin wannan dare,

Sunyi kuka sunyi Addua mutane sun girgiza da wannan mutuwa,

A daren aka hada gawa akayi komai,washe gari Aka fito da gawa akayi mata sallah aka dauka akayi hanyar Makabarta a hankali akaji kamar makara na motsi, a tsaya a tsaya a kace Makarafa na motsi dubban jama'a suka fara guduwa sun firgita,

Liman da wasu tsirarine suka karasa kan makara tare da yayan Sulemanu suka duba Gawa sai akaga Baba ne yake motsi yana magana Badai asibiti zaku kaini ba a mai Dani gida ko na tsine muku,yana makyarkyata yace ina Amanata iceko tana Kula da Iyalina,ina su Hamza kai ...kuna tallafa mata kuwa,matana fa sunyi aure?karfa su auri kowa ina son matana ina kishinsu, idan sukayi aure to nima za a bani Hurulein

Ina littafin da dukiyata take ciki ne Ku raba kuwa?na bawa Haladu buhun masarata

Biyar,Amana a bata sabon injin murzar taliya dana siyo rannan hhh
Ai su Hamza murna da gudu suka suri Baba suka koma gida ana Bai mutu ba Bai mutu ba,gawa taki rami gawa taki rami Allah wlh sai Baba.
Suna dawowa karfe Biyun rana Baba ya kara margayawa wannan mutuwar gaske ce domin Har doctor suka dauko ya auna ya tabbatar musu ya rasu, haka suka kara sabon kuka da komai aka kai gawar Sulemu Harka aka binne.

Amana kuka kamar ranta zai fita sauran kuwa har sun fara Hakura,Amma Amana itakam ba iya kukan mutuwa take ba,kukan rabuwa da masoyinta takeyi,ga nauyin da Baba ya daura mata,ga kuma ko secondary bata gama ba,bare ace tayi karatu tunda ba miji ta nemi aiki ta cikawa Baba Burinsa,

Ga cikin dake jikinta gashi Alim baima yarda nasa bane,ga bakin cikin sharrin da aka mata ga mutuwar uba duk ita kadai,shi yasa gaba daya ta kusa zarewa,yan uwa duk sun hadu da aluma masu zaman makoki ana ta yiwa Amana nasiha an zata kukan mutuce kawai,mutane sai ace Allah sarki Amana duk tafi shiga damuwa ai sun shaku da Babanta duk yafi sonta dole tayi kuka mutuwar tafi taba ta,

Tun Amana na kuka ita kadai a daki har ta fito waje ta kalli bishiyar da Baba ke Zama sanda tana Budurwa tazo ta wuce tana bouncing tace ai sai Baba Allah bar mana tsoho,yanda Baba ke ji da ita komai Amananansa,
Alim dinta ta tuno ta tabbatar da suna tare da tuni ya lallasheta ya sata nishadi da tuni ya zame mata gurbin uba,amma yanzu Babu me lallashinta,ya tarairayeta ya bata farin ciki ya tallafi danginta da iyayenta,shine gatanta,iyaye kuma duk lalacewarsu katanga ne,nan take Amana ta kurma ihu a kofar gidan ga maza masu zaman makoki su Hamza suna ciki,Amana ta fadi a kasa ta fara burbuwa tare da cewa wayyo Allah Bango ya fadi katanga ta rushe,gatana ya kare,gatana wayyo gatana,duniya kin juyamin Baya,kin juya min up side down,wayyo uwata wayyo Ubana...mijina...mijina shikenan nima.

Su Hamzane cikin hawaye suka riketa tare da danne kirjinta saitin zuciyarta domin wani numfashi yakeyi zuciyarta zata buga,
Da kyar aka samu numfashinta ya dawo normal,magana ta fara Ya Hamza a haka rami nima a binneni,nima dan girman Allah ku harbeni,zuciyarta ta nuna tace ku fasa min nan da Bullet,
Haladu dauko wuka a samu wani ya yankani dan Allah masifar danake ciki tafi karfina,

Kb da Isa ta kamo tace dan Allah ku farke min ciki mene Amfanina,kuka ta kara fashewa dashi,haka suka shigar da ita gida Amana ta fita daga hayyacinta,
Zazzabi tayi sosai sai hakuri ake bata,yau Kwana hudu da rasuwar Baba,Amana ta dan gana ta daina Kukan rashin Baba sai na Kukan rashin  Alim,amma duk da haka idan taga abokan Baba da wani abu daya shafi Baba sai kuka mutuwar ta dawo mata sabuwa.
Kamar yau Huzaifa Badriyya ta fada masa rasuwar babansu dole ya taso Abbansa da kanwarsa Saddiqa suka taho ta'aziya,bayan sunyiwa su Hamza sai suka jera Baban su Huzaifa a gaba,Huzaifa da kanwarsa Saddiqa suna baya haka suka shiga har cikin gida domin Yiwa

mata ta'aziyya,Amana tana ganinsu haka mutuwar Baba ta dawo mata sabuwa ta dora hannu aka tare da kwallawa da karfi wayyo wasu suna da Uba mu bamu dashi wayyo Ubanmu...ga wasu yan gata da Ubansu nan ma da kyar aka lallasheta,sai kuma tashin Alim ya fado shima,ganin Huzaifa suna yanayi da Alim sai ta fara Hawaye,

Tana ta kallon su Huzaifa kamar bata sansu ba,

Huzaifa bai sai me ya faru ba,yace Madam sai hakuri na sanarwa mutuminki yace min yaji kin yayanki ya fada masa dashi Akayi ta'aziyya zuwansa ukku ma,

Cak Amana ta tsaya da Kukan wato har ta'aziyya yazo ko nemanta baiyi ba da gaske ya hakura da ita,nan hawaye masu zafi suka zubo mata,

Ta kara wajen Haladu tace wai Alim yazo ta'aziyya?

Haladu yace dashi aka raka Baba har makabarta a mutuwarsa ta karshe, dashi akayi sadakar Uku,cewa yayi kar mu fada miki bai son ganin kukanki,

Amana a ranta tasan dan kar ya ganta ne ya tsaneta,

Amma kuma taji wani irin dadi da farin ciki tare da da ran Allah sa ya dawo gareta watarana,nan kuma tayi dariya hadi da hawaye,Amana bamu sanki da kuka ba ko ya kukace readers?

Huzaifa ne ya fito zasu tafi Su Abbansu na Mota da kanwarsa shi kuma Huzaifa sun tsaya a soro suna ta hira da Badriyya cike da so yana lallashin Badriyya,Amana ta hangosu a cikin mutane a fili ta furta ni bani da masoyi babu me lallashina sai kuka tare da tuna yanda Alim ke ji da ita.Ummanta ne suka fara mata fada sosai,kamar akanki aka fara mutuwa Allah ya hana Yiwa mamaci kuka haka,idan ma ganinki wani abu to ki sani Baba ba dawowa zaiyi ba kukanki ba gata bane a wajensa,masifa kike kara masa,daki Amana ta fada taita Kukanta.

Kwanan Baba Bakwai da rasuwa yau Alim yasa Abbansa,da Nura tare da dan autansu suka je sukayiwa yan gidan su Amana ta'aziyya,

Lokacin Amana ta kule a daki tana ta zazzabi da kuka,sai jin labari tayi Alim ne ya hana a tasota,wai zai dawo.

Ga abinci sun kawo musu Mota guda da kudi masu yawa sannan suka tafi,

Haladu ya ce Amana kai mijinki na sonki kinga yanda yake barka kuka kamar mace ke kyace babansa ne ya mutu,kb yace ai wannan Kukan Uba bai cancanci ayi masa ba sai dai Uwa,Isa yace kutmar Uba guy nan mace ne,kb yace a macen ma ta gaske,Hamza yace mamakin danayi mutum kai ba ubanka ba amma kafi yayan cikinsa kuka,

Haladu yace kai Burauba naga kuka wajen yaron nan kasan yaran masu kudi yayan Hutu ne inda kaga mace haka suke basu saba da gwagwamarya ba,wai guy nan daga cewa Amana ta suma tana kuka ta rame tayi duhu kawai ya barke da kuka shima yo ko uwatace ai bazanyi kuka ba bare mata,akan wata mace ka kama kuka,

Hamza yayi dariya yace ai kabewa ne,Isa yace ai mugun tumatir ne wlh.ammafa yana son Amana da ka ambaci sunanta za kaga ya kafe ka da ido ya shiga wani hali sai kwalla kuma kwal kwal,

Kb yace ai da ace ban san Amana ba da cewa zanyi asiri tayiwa guy nan,Hamza yace gaskiya Uwarsa ta haifawa Amana da Allah ya tsare ta haifawa Wata da,

Suna tsaye suka ga Amana yif tayi kasa ta sume saboda tsananin tunanin Alim,surarta sukayi Sai asibiti.
Kwananta uku aka sallameta tare da garga din Likita cewar a kiyaye damuwa zata mata illa kwanan nan,
Suna dawowa gida aka rufarwa Amana da nasiha cikin kuka tana share ido tace ku nutsu na baku labarin mece damuwata,

Kaf Amana ta kwashe ta fada musu tun farkon Haduwarta da Alim da irin zaman auren da sukeyi da soyayyarsu,da Mum Alim abinda take mata,da kuma gidan da ta zauna tare da Alim a garin,da sharrin da aka mata,sai rasuwar Baba,mata har Amana suka taya kuka,sun san Baza ta aikata haka ba,Hamzane yayi magana Lallai ko waye aka masa haka dole ya yarda kar kuga laifin Alim,

Da gani har yanzu yana sonki sai yanzu muka gane dalilin da yake barka kuka,
Zamu tayaki da addua Allah ya bayyana gaskiya,Haladu yace Insha'allah zai dawo da kansa wajenki ki raini cikinki Allah raba Ify,Umma tace shi yasa kike ta kuka haka,gwaggo tace Allah ya shige gaba,sauran matan sukace Ameen,Amana sai hawayene ke sintiri a fuskarta,ana ta mata Nasiha,Badriyya tace wlh ko Saude ko Mum ne zasu kala miki wannan sharri na sani Allah zai saka miki.

Alim kuwa kwana yakeyi ba barci saboda tunanin Amanarsa tsananin sonta,da abinda kuma ya gani wai kwarto fasiki Amana taci Amanarsa,shima yayi kuka yayi bakin ciki yana wani Hali ya rasa inda zaisa kansa,shike nan cikin zazzabi,baya cin abinci,duk ya rame sosai,kamar yau yana kwance a gidansa domin tunda ya dawo gida bai taba ko kwana a gidansu wajen Mum ba,yauma kwance yake zaman bed zazzabi ya rufeshi a hankali ya furta I missed u me yasa zaki zalunceni,bayan ina sonki zaki ha'inceni?why Amana.haka yayi ta sambatu,

Mum tayi farin cikin ganin Alim dinta gashi ya dawo shi kadai ba tare da tsinanniya Amana ba. cewar Mum
Abba da su Nura sun tambayi Alim ina matarsa sai yace ya dan barta a gidansu ta huta Sabo da rasuwar Babansu zai dinga zuwa can yana da gida a garin nasu a ciki ya sata.

Aabid kuwa yana gidan Nura sunyiwa Mum wayo sun daukeshi.

Amana ta gargadi Badriyya kar ta fadawa Huzaifa komai tsakaninta da mijinta.

Kwana biyu laulayi Amana ta fara sosai zazzabi,kwadayi ga yawan sha'awa da takeji kuma sha'awa r Alim kadai take ji,s ai ciye ciye kullum na kwadayi yan uwanta Maza da mata su suke kula da ita sosai,kafin tace tana son abu sunyi mata,sai abinda take so suke kawo mata,kowa lallabata yakeyi dan hankalinta ya kwanta,ta rame sosai sai fari data kara kwal kwal da ita,
Yanzu bata da matsalar komai sai ta rashin Alim,sha'awarsa,sai nauyin da Abba ya dora mata har yau bata sauke ko daya ba,

Sati Uku da rasuwar Baba sai kuma wata sabuwa Umman Amanace ta bijiro da wata tsiya rigima sabuwa fil ta baro.

AsmaBaffa

Readers a dinga Afwa idan anga mistake,ba lallai Allah ya hada komai abinda kake so ba,idan kunga abinda bai muku ba kuyi hakuri story a haka yazo,kuma ku dinga nutsuwa a ko wanne acting da akayi a wannan novel ko wanne page akwai sakon dayake isarwa a dinga gane abinda ake rubutawa ana masa kyakyawar fahimta ta gaske.na gode kwarai
✳CIRANIN AMANA✳

155-160

Official

By
AsmaBaffa

ANTY SUMEE INA GAISUWA WANNAN PAGE NAKINE.MARAICIN SO FANS INA GODIYA KWARAI.

Umman Amana ta tsiro da wata tsiya Inda kwata kwata take ta jin haushin Amana saboda taga yanzu bata da kudi,bata Auren me kudi komai sai dai su Hamza suyi mata,yan kudin da take dasu duk ta karar dasu a gidan tana yo musu cefane idan mazan basa gida gashi ta biya sauran yara kudin makaranta,gashi mutane da yawa sunzo wai suna bin Sulemanu Harka kudi kafin ya mutu ya ranta,sabo da haka kudin bashin da ake bin Mamaci dubu dari tara akayi lissafi,

Gashi sauran mazan gaba daya sana'arsu batayi karfi ba ga kula da gida,

Gashi wanda sukayi aure ma ko wacce rurowa sukeyi a gidan ake tallafa musu,ga yara masu tasowa cincirundo,shawara suka hadu iya manyan gidan babu kudin da za a biya Bashin mamaci kuma ya zama dole,Amanace ta bada takaddun gidan da suka zauna da Alim aka siyar dashi aka biya bashi,

Sauran canji akayi bukatun gida,bayan kwana biyar wani yazo yace shima yana bin bashin dubu dari biyu Amana ta bada sarkar Gold dinta har guda Hudu da Alim ya siya mata nan ma aka siyar aka biya,bayan sati biyu wasu suka kara zuwa wannan yace dubu hamsin,wani ashirin wani talatin,haka mutane suka dinga zuwa su Hamza suka nemo sukayi karo karo aka gama biyan bashin Baba kaf,kowa na gidan a gida tattalin arzikinsa yayi kasa basu da wani karfi,gwara ma su Hamza ba laifi,dole suka jinginar da maganar aurensu.

Kullum Umman Amana haushin Amana takeji wai ta kwashe kudinta ta biya bashin Baba ita kadai arzikinta duk ya kare ita bata bata ko kwandala ba,kuma Amana yanzu da su Hamza take shawara har meeting sukeyi,

Amana ga halin da take ciki ga kuma Umma kullum cikin hantararta da zaginta takeyi tana jifanta da muggan kalamai,idan readers baku manta ba Umman Amana ko koko safe a da bata bawa Amana sai dai ta siya,ganin Amana Allah ya buda mata ta samu kudi tana auren me kudi shine Umma ta sakko take kula da Amana,yanzu Amana Babu ba mutunci,dama ita Umma me bata shine nata,idan kana bata to a cikin yayanta kiri kiri zata dinga nuna banbanci.

Yauma gaba daya family na mirgayi Sulemanu sun Hallara a babban palo ana shawara,banda iyaye a meeting din,

Amana zaune take a tsakiyar Palo ta dararararrashe ta sangale kafafu zaman masu ciki sosai ta rame idan kunga Amana za ku sha mamaki ta rame sosai,kana ganinta sai ka tausaya mata Sabo da Amana kullum sai tayi Kukan rashin Alim tayi addua tayi ba dare ba rana,

Da addua aka bude taro Hamza yace da Amana sayyada a cika mana da addua kinfi kowa Ilmi,ai kuwa akayi addua sannan aka kawo littafin wasiyyar Baba daya bari na gadon kowa gwara a bawa kowa hakkinsa dama Umman Amanace tace wlh sai an dakko an raba gado domin duk anyi tunanin Sulemanu ya tara dukiya ne a boye shi yasa har yayi littafi guda ya raba gardamar gado,

Page din farko na littafin aka bude ga abinda aka gani da Babban baki ya sa wani abokinsa ya rubuta masa domin Harka baiyi boko ba Badriyya ce me karantawa.ga abinda ke rubuce.

AMANATA INA KAUNARKI,Amana na jin an karanta haka ta fashe da Kukan tuna Baba,NI SULEMANU HARKA BABAN AMANA NA BAWA A CIKIN DUKIYATA DA ALLAH YA MALLAKA

MIN NA BAWA AMANA SANIYATA WACCE NAKE KIWATAWA A GIDAN ABOKINA ME GARI,SANIYAR BATA HAIHUWA ITA KADAI CE ABINDA NAFI SO A CIKIN DUKIYATA,SABO DA HAKA SANIYA TA AMANACE KAR TA SIYAR DA ITA TA YANKA TA IDAN ALLAH YA BATA HAIHUWA TA DAGARGAJI DADINTA.dariya kowa yayi harda Amana me kuka,

Page 2. HAMZA NA BAKA TINKIYATA DA RAGO KA YANKAWA AMARYARKA RANAR BABBAR SALLAH ASHA DABGE,hhhhhh nan ma aka dau shewa da tafi tare da cewa Allah yaji kan Baba.

Page 3. KABIRU KB DAMIN GERO SHIDDA KA SIYAR KA KASHE KUDIN,

ISA KUMA WAYATA TA CELLULA DA AMANA TA SAI MIN,

HALADU KUWA BUHUM MASARA BIYAR,

BADRIYYA TOLO TOLO GUDA UKU,

SAKINA BARGONSA NA BACCI DA RADIO DA YAKE JIN LABARAI,DUK SUNA GIDAN ABOKINA ME GARI IDAN BAI BAKU BA KU SHIGAR DA KARA.

MATAN AURE KUWA KO WACCE A BATA RIGARSA DA WANDONSA DAYA DAYA,

SAURAN YARAN GIDAN KUWA KAI KUNCI UWAKU GABA DAYA GA SU AMANA NAN DUK ZASU KULA DAKU KAR KUCE BAN BAKU KOMAI BA CIKIN KAYAN SAWATA KUMA A RABA MUKU DAYA DAYA KOMA ME ZAKUYI DASU KUYI.

second to the last page kuwa na matansa ne,

KO WACCE CIKIN MATANA NA BATA KYAUTAR IYA DAKIN DA TAKE CIKI TA ZAUNA HAR IYA RAYUWARTA,SAURAN GIDAN KUMA KAR WANDA YA SIYAR GABA DAYA NA YAYA NANE,WACCE TAGA ZATAYI AURE TO BA BATUN SIYAR DA DAKI DOLE SAI DAI CIKIN YAYAN WATA KO WANI YA SIYA

LAST PAGE KUWA FATAN ALKHAIRI DA ADDUA YA ZAZZAGAWA IYALINSA,

Gaba dayansu sai da sukayi hawaye na tunowa da Baba,Umman Amana kuwa wani uban tsaki taja tare da cewa aikin banza akan wannan ya bata lokacin to wlh ni yola state zan koma cikin city wajen yan uwana su rikeni mahaifina,duk kun hanani ci gaba a garin nan.

Dan haka wanda yaga yana da kudin siyen dakina ya siya ya bani ko na kira wani a waje bare ya siya,

Amana hawaye da takaici ya isheta,tace Umma zan siya,Umma saida tayiwa Amana kallon banza sannan taja tsaki tace naji dumus,Kb Amana ta kira gefe tace kb ku samu a siyi dakin nan banda kudi hanuna kun san komai dai,kb yace akwai ragowar kudin gidan ki a hannuna ina ga zai siyi gidan,

Amana ta dawo cike da Ladabi tace Umma nawa kudin dakin? Umma tace sannu azagwai uwar Iya, wa ya sani ko da gaskene abinda kika aikata nasan ubanki kika gada shi kwarto ke kuma fa ?ai dole ayi gadon tsiya,wannan mijin naki yaron kirki Amana amma sai da kika nuna hali ya

sako ki gaki ga gidan nan ai ki zauna,
Muna zaman Ify yaro na mana kyauta kika watsa kanki ya sakoki ga ciki dan Allah baki ji kunya ba?

To ko kin sayi dakina dan ubanki dole ki bini mu tafi yola na dinga dora miki talla,mene amfaninki wai ku masu Uba ko?
Amana dai bala'in da take ciki kadai ya isheta ta saba da hali Ummansu tunda yanzu bata da kudi,
Shi yasa Amana kamar ba ita ba duk tayi laushi tubus ta gama karaya da lamarin duniya,cike da ladabi tace to Umma amma Baba yace in ba aure ba kar mu rabu da yan Uwa,  da karfi Umma tace iyyeeeeeee to wlh sai kin bini,sana'a za muyi mene amfaninki,
Nan Umma tayi kudin daki Amana ta siya sannan Umma tace dauko kaya mu tafi,kowa dake gidan yaji ba Dadi,nan Mutuwar Baba ta dawo musu sabuwa kowa kuka,
Musamman Badriyya da suka shaku da Amana ga bikin Badriyya da Huzaifa ya kusa,domin Huzaifa ma har tallafi yake kawo musu idan yazo sai Badriyya tace suna tare da Alim a lagos ita kuma Amana ta boye kanta,Sakina da Badriyya rana daya za ayi bikinsu saboda mazajensu masu hali ne sunce sun dauki nauyin komai na biki.

Amana bata so bin Uwarta ba amma gudun bijirewa iyaye dan kar ta maimaita yanda ta bijirewa Baba ta bar gidan da ita da Alim duk da cewa iyayen sune masu laifin amma duk da haka saida masifa ta afka musu shi yasa taji tsoron bijirewa Ummanta

Duk yan gidan ne suka taushi Amana suna ta kwantar mata da hankali,Badriyya da Haladu harda kuka yanda Amana ta fita daga hayyacinta gaba daya,

Haka tana ji tana gani tare da sharbar kuka ta hada kayanta tas tabi Ummanta,amma abin mamaki Umma ta bar kannen Amana wajen su gwaggo wai su rikesu Amana tallafa mata za tayi da talla.
Tun a tasha,Amana kuka kawai take shike nan an kara nesantata da Alim,kuka kamar ta kashe kanta,Umma tace kiyi kukan jini ma ke kika jawa kanki,

A mota ma kuka takeyi ana ta kallonsu,to Amana ko wa zai taimaka miki oho.yanzu ba kudi basu Hamza ba Alim baki da kowa sai Allah.

Yanda Amana take wannan halin haka Alim ya shiga sanadiyyar rashin Amana kusa dashi ya yarda itace rayuwarsa,shima ya rame sosai da kyar yake fita ma,yan uwansa da iyayensa sun rasa gane kansa,yayin da Mum ta Nemo masa wata yar kawarta Zainab wai Abba yayi masa aure ko zai samu nutsuwa,Abba kuwa ganin halin da Alim ke ciki sai ya yarda,
Har zance Mum tace sai yaje wlh,Alim yana zuwa yaga Zainab wata tambadaddiya marar tarbiyya nan take yaci mutuncinta tun daga sama har kasa yayi tafiyarsa,wannan dalilin yasa aka dage biki sai nan da 6mnths,

Saude kuwa ana can Ana Wainar siyarwa tare da ci gaba da kulle kullen tsiya.

Ranar da Amana tabi Umma suka tafi ranar da yamma Alim yazo gidan shi da Huzaifa,dalili kuwa ranar kawai yaji ba abinda yake so ya gani a duniya irin Amana,

Waya yayiwa Huzaifa wai yana so ya gaisar da iyayen Amana mata yayi musu alherin saboda yanzu basu da miji,ai kuwa Umma bata da rabo Alim Mota guda yasa aka kawo gidan ta kayan abinci,sai kallon yan gidan yakeyi,sai ya faki ido ya share Hawaye,gaba daya suma sunga ya rame,inda

Su Hamza suka birgeni ba wanda yayiwa Alim maganar Amana ko kadan,sai Baza ido yakeyi yaga Inda Amanansa zata bullo yayi tozali da ita ko bai mata magana ba zaiji sanyi kuma zai rage radadin sonta da yake daminsa,

Amma duk da haka yana cike da bakin cikin Amana taci Amanarsa ta zalinceshi gashi yana sonta Amma dole ya hakura da ita,maybe ma ta manta dashi tana ta rayuwarta cikin Jin dadi,a hankali ya furta Allah sarki ni..a fili .

To Alim dai yana ta baza idanu Ba Amana ba labarinta,tunowa yayi da Badriyya mutuniyarsa me handling case dinsa,

Komawa yayi wajensu ita da Huzaifa yace sorry frnd zanyi magana da kanwata for some few minutes,

Sun kebe waje daya shi da Badriyya Alim yace Sis wannan yarinyar fa? Badriyya tace wa kenan a hankali yace Aman...kasa karasawa yayi saboda yanda zuciyarsa ta kare,takaici yake son taso masa haka ya daure,

Badriyya ta lura da hakan sai tace oh...Amana ai sun bar gidan na....kafin ta karasa Alim yace Badai aure tayi kan aure na ba?Badriyya tayi dariya kamar bata San komai ba tace haba aure ba aure ba kawai Ummanta ce ta takura mata sai sun tafi Yola garinsu tayi mata talla.

Talla?Alim ya kwala da karfi yace to wlh bazai yiwu ba Sam,nan ya fara fada ni nake da iko da abata,

Badriyya batace komai ba sai tace ai na tausaya mata in ka ganta baza ka ganeta ba ta rame sosai kullum cikin kuka take tace wai sharri akayi mata aka rabaku gashi tana da ciki har ya fara girma,kasan me Baka ga bakar wahalar da take Sha da cikin nan ba,yanzu Amana ko maganar kirki ta daina sai da dalili,

Fiya fiya fiya Alim ya kama fyalla sauri kamar zai tashi sama,mota ya bude tare da fadawa ciki ya dinga bakin ciki da share kwalla na tausayin Amana har ya gaji yace ko mene ke kika jawo,ke kika jefa mu cikin masifa...nan take zazzabi ya rufeshi da ciwon kai mai tsanani cikin motar ya kudundune saida Huzaifa ya kaishi asibiti sannan suka koma gidansu Kano kenan.

Amana sun sauka lfy,wani gida suka shiga da Alama nan ne gidan su Umma,gidan Bulo ne ko siminti babu,daki biyu ne rak,ba mace a gidan iya Baban Umma ne kawai wato kakan Amana kenan,shi kadai yake rayuwa saboda tsabar masifar tsohon,masifaffe ne number daya,sabo da haka mata basa Zama da shi,haka Umma ta masa bayanin Amana da ita,zasuyi Sana'a,

Malam Nuhu yace to gwara da kukace zakuyi Sana'a ni dai kwandalata bazan kashe muku ba,gida dai gashi nan Ku zauna a waccen dakin baya Ga wannan ba zan yi muku abun sisi ba,

Amana dai tunda ta gaisheshi kala batace ba,tana rakube a bango kamar marainiya,tana tunanin Umma Babanta ta gado, Umma ce ta dan sai musu abinci har Malam Nuhu sukaci dan kadan dashi baifi mutum daya ba,

Amana kuwa bata cin shinkafa da miya amai takeyi da tashin zuciya amma Umma tace iskancine wlh baza ta sai mata komai ba,ga yunwa tana ji gashi bata da ko sisi,haka taci abincin tana ci ta fara Amai sosai Ai kuwa Malam Nuhu ya fara sauke Bala'i wannan iskanci ne wannan?yanzu haka ma cikin shege ne kuka gudo min nan za a cuceni, Umman Amana tace Haba Baffa da kai fa aka daura mata aure.

Amana ta ebu ruwa zata kuskure baki ta wanke hannu datt
ijon yace karki bata min gida kimin asarar ruwa ubanki ne ya sai min?kai gaskiya ubanku ya Sha wahala daku to wlh baza a zo a hanani walawa ba a gidana,

Amana kwalla ta share tare da tsugunawa tace kayi hakuri,kallonta yayi tsab yace iyye ke baiwar Allah yaushe kika daina harkar niganci da jagaliyar ne?Allah da iko yaushe haka ta faru?amma wanda ya aureki kamata yayi a bashi kyautar sarkin hakuri,yo ni da nine yausheeeeee tabbb,badan halin ki ba ebi ruwan kadan amma ki shiga bayi ki wanke hannu da baki ba a tsakar gidana ba bar ganin gidan ba siminti ba a lalata min gida,hakan Amana tayi ba tare da tacewa Malam kala ba,saboda tasan ma idan tayi magana to bakar magana zatayi domin ta kai wuya saboda halin da take ciki ga duniya ta bata darasi shi yasa bata cewa komai,kun San shi karatun duniya dole sai ka jishi,kuma ba iya kunne ne ke ji ba duk gangar jiki ce ke karba sosai.Amana sarkin zuciya ji take kamar tayi ta dukan Malam har ya suma,dan darajar Umma ta kyaleshi amma da sai ta nuna masa ita wace

Washe gari Umman Amana ta siyo gero ta fara kunun siyarwa ba na markade ba na daka su surfa ita da Amana su daka ayi Amana ta dauki katon botikin paint a kanta ta fita can wata majalisa,bata so gudun fushin Umma ta hakura, Amana kar A manta fa,dama can ta Saba da sana'a talla ne kawai bata taba yi ba amma duk aikin wahala tayishi kuma gata da zafin nama ba bata lokaci tunda tasan dole tayi ko dan abinda zasu sa a bakin salati bare ma ta San Umma ba kyaleta za tayi ba kuma bata son yi mata musu heeeee su Amana anji jiki fa da dane na tabbata Umma baza ta iya juya Amana ba,sai gashi yau Amana har mamakin wai ita Amana akewa abinda aka ga dama,da ace da dane har Baban Umma Malam Nuhu zata ci Ubansa. duniya kenan.

Amana kam yau satinsu Biyu da zuwa Yola,suna zuwa har gidajen sauran yan Uwan su Umma suna zumunci,

Amana tana zaune da waya a hannunta zata kira Hamza Umma ta kwace wayar kawo siyarta zanyi na kara jari,Amana shuru tayi ta zare sim dinta ta mikawa Umma dalleliyar wayarta sannan ta fashe da kuka sabo da wayar taka rage zafi da ita wajen kallon hotunansu tare da Alim sai taji sanyi a ranta ta samu nishadi to yau Umma ta kwace wayar ma amma duk da haka ba iya sim ta cire ba komai na wayar ta mayar kan Memory ta zare Memorynta ta hade ta daure a Leda tasa a bag dinta,

A banza Umma ta siyar da wayar Amana duk tsadarta,yayi dai dai da Alim wanda ya kasa

hakura da Amana,ya shiga matsanancin Hali kullum sai ya Sha maganin bacci yake iya bacci kawai ya yanke shawarar kiran Amana ko muryarta zaiji ya rage zafi,canja new Sim yayi tare da dan nawa Amana kira amma ya makara wayar bata shiga,Badriyya ya kira itama ta gwada bata zuwa,yace Badriyya pls bani Address din inda suke a Adamawa,Badriyya tace wlh duk gidan basu sani ba amma dai gwaggo tasan sunan local government da suke a can da unguwar amma bata San wanne gida bane,tsaki Alim yaja yace kinga Illar rashin Zumunci wannan ba zumunci bane yanzu idan wani abu ya sameta kuma baza Ku sani ba‹ ya kamata ace ko kishiyoyi a dinga zumunci ana sanin asalin inda kowanne ke zaune Sabo da irin wannan. yanzu wannan me yake nufi kenan kuna Uba daya baku san inda yar uwarku take ba ku bakwa shiga harkar kowa gashi abin har yan Uwa na jini ma wannan ba dai dai bane,

Haka Alim ya dage ya dinga bala'in da masifa ya dinga saukewa Badriyya kwando kwando yana ta nuna mata illar rashin zumunci wasu kuma zumuncinsu ma sai suna Uwa daya Uba daya da iya su suke zumunci.Sai da ya gama yana huci kana yace hadani da gwaggo ta fada min Unguwar da Ig din,
Bayan an fadawa Alim komai sai kuma ya fara jin dadi da nishadi kamar wanda akace masa ga Amana a gabansa,

Amana ce suke ta daka geron kunu,sanye take cikin kayan da ta saba dasu wata falkekiyar riga tshirt saboda cikinta ya dan fito sai jean trouser fari tayi kyau ba laifi Sabo da yanzu yawan addua yasa ta dan rage damuwa duk da cewar kullum sai tayi Kukan rashin Alim,amma yanzu ta danyi kiba kadan Sabo da cikin ya sata yar kiba da kyau yanzu,

Yanzu ma tana dakan geron ta tuno Alim sai hawaye tana yi Hawaye na bin kuncin ta,Malam Nuhu dake gefe yana jin radio ya mike yau ga kwarzababbiyar yarinya yar iska ke zan koreki fa daga gidana kullum cikin kunci da kuka ko uwarki aka yimiki iyeeee nace Ubanki aka miki? Ke kenan a gidana kullum cikin shigar yan iska kike kina nuna tsaraici,shi yasa ma ga badayanki zubin karuwa shaddar kasuwa ce dake wannan anya jikata tace ba musaya akayi ba,Umma dake wajen Murhu haushin Babanta taji yana zagin yarta sai taji tausayin Amana kuma,mikewa tayi tace ajiye dakan muje ciki muyi magana ba musu Amana ta shige daki tsoho ya dauki Salati yace Hauleeeee Hauleeeee yau ni Ubanki zaki nunawa kin haihu niiiiiiiiii....sai ya saki kuka.

Umma daki ta samu Amana kwance bisa tabarma tana sharbar Kukan takaici tayi rashin Uba da miji yanzu da Ubansu ya na raye duk Lalacewarsa ai gidansa zata zauna,a da suna ganin Baba bai musu rana ba bashi da amfani a garesu sai gashi tun ba a je ko ina ba mutuwarsa tasa sun ga rashin Uba babban wani abune a rayuwa,

Da da Mahaifa sai Allah Umma ce ke lallashin Amana tace kiyi hakuri kinji tashi ki siyo abunda kike so yau kici kinji,Amana bata ce komai ba,Umma ta rasa abinda zata cewa Amana ta sata nishadi Umma gani take yau kudi zata kashewa Amana sai tace Amanan Baba ko za kici mitimis?saida Amana tayi murmushi,Umma taci gaba zan kashe miki kudi ko mene fadi kinji,shuru Amana tayi tare da goge hawaye,Umma tace Aya fa? Dan tamatsitsi?dabino?awara?gurasa?ko dan silif zaki siyo flour kiyi? Amana tace ni kaza nake sha'awa dan Allah Umma ki sai min a ribar da muka samu,Hangame baki Umma tayi tace yo

ina kudin kaza yake ke Amana wannan ai zalincine da mugunta har Kaza fa?

So kike ki karya jari canja wani kinji yar Baba,Amana kuma a duniya kazar take son ci,haka tasan Umma ba siya mata zata yi ba,sai ta hakura tace Umma to ki siya min kasar calabar da Aya.

Umma tace ko kefa zauna da kaina zan siyo miki ma,A mana insha'allah sai mijinki Alim ya dawo da kafarsa ya nemeki har ki ja masa aji da yanga ko?kyalkyal Amana ta kyalkyale da dariyar Jin dadi tare da furta ai Sai Umma,Amana sai nishadi Umma bata taba birgeta ba irin yau,tunda Umma ta ambaci Alim ta gamawa Amana komai a duniya.

Umma kuwa mamakin Yarta takeyi yanda take matukar son Alim haka,

Umma tace tab Amana ni kuwa me Alim yake miki ne kike sonsa haka?ko kanki bakya so haka,Amana cike da fara'ar da ta Dade rabonta da yin irin ta ta fara magana Umma baza ki gane ba komai Alim yi min yake Umma komai da kika sani,Umma tace komai? Amana tace komai Umma bazai fadu ba ina fada miki Umma Mijina karshene a komai da kika sani wasu suka rab....sai kuka wiwi Amana ta fara,sannan tana murmushi sosai ga hawaye tace Umma Allah uban giji ya daidaita ni da mijina,Umma Alim mutum ne,Mijina yayi Umma nayi dace,hawaye ya kwararo mata taci gaba da sambatu Umma Alim abin so ne dan ina Jin kunya ne da kullum sai na dinga baki labarinsa abubuwan da yake min.

Umma harda kwalla tace kullum zan dinga tayaki da addua yata.
Fita tayi da kanta ta siyowa Amana Aya da calabar harda Rabin kaza gashashiya sai da Umma ta siyo mata,Amana bata zata ba Allah sarki Uwa me tausayin yayanta.

Nan Amana ta zauna a tabarma ta dinga Garza,
Umma na kallon ta da tausayi.

Kusa da gidan da Amana suke makwaftansu akwai wani Deeni kwaro tantirin dan iskan gari ne,tunda yaga Amana ta fita tallan kunu yaji a duniya Bai taba sha'awar mace ba irin Amana,a ransa yace ko hannun Amana ya shafa sosai to ko ranar ma dan ta shi ya mutu,
Sabo da haka duk unguwar ake ce masa na me Kunu ko hannunta ka shafa sai ya karasa musu da ko yau namutu.

An fara Zafi sosai a Adamawa nan su Amana suka dawo suna kwana a tsakar gida,Amana tana can karshen gidan kan tabarma ta shige cikin net dinta sabo da sauro
Umman Amana ma tana tsakar gidan farkon gidan cikin Net,haka Malam kuwa yana can cikin daki,

Cikin tsakar dare Deeni kwaro ya taka katangar gidan ya dane tare da lekowa a hankali,sai yaga mata biyu saboda duhu gashi baya so Amana ta farka tayi ihu ya kasa shafa jikinta,haka ya shiga gidan ta saman Katanga sadab sadab ya shige cikin Net din Umman Amana ya zata Amana ce, kawai ya ya kara shigewa jikin Umma sosai ya fara shafa jikinta,Umma cikin bacci taji ana shafata ta manta Sulemanu Harka ya rasu cikin magagin bacci tace

uhhmmm......Sulemanu....Sulemanu a'a....a'a mene haka Sulemanu,kaji jarabar taka ko,Da gudu Deeni kwaro ya fito fit kamar walkiyya Umma ta dawo hayyacinta ta jawo rigarsa baya ai kuwa Deeni kwaro ya cire rigar cikin zafin Nama ya barwa Umma a hannunta ya tsallake ta Katanga ya fece,

Umma ta fara kuka da kurruwa Sulemanu ya jawo mana yayiwa matan wasu wlh dole ayiwa nasa wani tsohon zan samu na aura kafin wani ya min Illa ohhh yau na gane da saurana Ashe saurayi haka na bi na ai sai aure,

Tashin Amana tayi tace tashi dan Ubanki mushe kina can wani zaimin fyade,bazan iya zaman nan ba wani satin zamu koma gidan Babanki gwara gidan Mirgayi wlh ina gama takaba zan samu sakarkarin dattijo na aura domin ubanku ya jawo mana sai mun tsare mutuncinmu.

Amana sabo da murna harda tsalle da kyar ta iya bacci sabo da murna zata koma wajen yan uwanta,murnar Amana dayace tasan dole bikin Huzaifa da Badriyya Alim zai zo ko don Huzaifa to dole ta ganshi ko taji sanyi.

Malam Nuhu kuwa dadi yaji zasu bar masa gidansa wani satin.

Alim duk abin duniya ya masa Zafi shirye shiryen bikin Huzaifa sukeyi kuma shine kan gaba shi ya tsaida dashi zuwa Adamawa neman Amana.

Washe gari Amana ta tashi fes cikin tsananin murna,karin Jin dadi n Amana Umma tace ta daina talla kudin da suke dashi ya ishesu har su koma gidan Baba Mirgayi.

Yau Amana ta fita siyo kayan miya a hanya garin tsallaka kwalabati kafarta ta goce ta fada katon Kwalabati marar ruwa cikinta ya bugu sosai nan take cikin ya juya sai jini ya yanke mata sosai yake ambaliyar fita daga kasanta,Amana ihu takeyi tana wayyo Allah dana dana zai mutu na shiga uku dana wayyoooo dana kar ka tafi me kama da ubansa,kai nake sa rai zan haifa na dinga ganinka kamar babanka 'yata ko dana me kama da Alim dina,

Gudan jinin Alim,zarota mutane sukayi da kyar ta kara dafe cikin taci gaba wayyo dan Halak dan Alim,wlh Alim ne yayi cikinka mijina Alim a gidan aurenmu,Ka tallafamin kaine shedata da zan wanke kaina wajen babanka,

Deeni kwaro ne ya taho da gudun tsiya masoyiyarsa ta samu matsala yace mahaukata kun tsaya my love tana gabanku shinfide cikin wani Hali kun kasa kaita asibiti sai kallonta kukeyi kuna kallon daga inda jinin ke fitowa kuna Jin dadi kuna kissima surart a zuciyoyinku,to gurin yafi karfinku,daga wanda yayi mata cikin sai nine kadai zan San wajen nan,

Amana dai ta fara fita daga hayyacinta sai nishi takeyi tana Dan Alim...shedata...dan Alim Habawa ai tuni Deeni kwaro ya Sureta tare da tare napep sai asibiti.

AsmaBaffa

Tnx alot readers.

CIRANIN AMANA

160-165

Official

By
AsmaBaffa

Dukkan yan AsmaBaffa fans club godiya gareku da jinjina.love u all

Da sauri Deeni ya shiga da Amana cikin wani private hospital nan danan akayi emergency da ita likitoci suka rufa a kanta,komawa Deeni yayi tare da sanarwa Umman Amana da Malam Nuhu,a sukwane suka rufta asibitin,Umma sai kuka takeyi tana ohhh na jawo miki,na jawo miki masifa Amana Ashe kaddarace ta kawoni na daukoki nan Adamawa,

Deeni ne ya biya kudin asibiti da komai da aka bukata domin Deeni kwaro akwai neman kudi baya talauci..

Duk iya kokarin da likitoci sukayi dan ganin Cikin Bai fita ba amma abu yaci tura domin tun kafin ma a kara so asibiti ciki ya zube,dan haka suka mata wankin ciki,sai allurai da magunguna na Karin jini da sauran abubuwa,Deeni Kwaro kuwa maltina carton 3 ya kai da madara peak ta ruwa kwali biyu,sai kuma kullum da kalar naman da yake kaiwa asibiti wajen Amana.

Amana kuwa bata magana sai yanda akace da ita,da ance yi zata yi bari zata bari,kai ko gabas kace kalla zatayi,arewa,kudu,

Sai hawayen da basa tsaya a idonta,tasan yanzu ita da Alim sai a darul salam dama da cikin ta dogara idan ta haifa dole zaiyi ko kama da Alim sai ya San da gaske shine Ubansa to gashi ya zube.

Umma kuwa ko a asibitin gasa Amana takeyi sosai tana gyara ta cike da tausayi,
Satinsu guda aka sallamesu,Deeni kam yayi Namijin kokari,sai yanzu ya gane lallai son Amana yakeyi,kuma yaji labarin tana da aure,hakan yasa ya tattara soyayyarsa da kwadayinsa ya kara gaba dan karma ya dinga ganin Amana yana Jin wani abu ya koma daga gida sai wajen aiki,sanadin hakan Deeni kwaro ya daina halayen banza ya samu shiriya Sanadiyyar Amana me Kunu,Amana ma batasan yana yi ba,sunje dai har gidan su Deeni sunyi Godiya sosai,sai lokacin Maman Deeni ta basu labarin Deeni da komai har shiryuwarsa sanadin Amana,ai nan take ya birge Amana ta dinga yi masa fatan alkhairi,Amana ta bashi Address dinsu na gidan Baba.Deeni dai ya karba kawai amma bazai je ba tunda Amana Nada aure, kuma ga kunyar shiga net din Umman Amana da yaya satin Amana biyu cif da yin Bari yanzu kam Umma gyarata tayi sosai a saboda Shan madarar rakumi da sauran Abubuwa yasa Amana ta maida jikinta tayi sumul sumul tayi kyau na ban mamaki sabo da kayan da Umma ke bata tana ci da Sha na gyara,

Itama Amana saboda kullum cikin sa rai take zata hadu da Alim dinta yasa take yarda da gyaran sosai,kai ba kace Amana ta taba aure a duniya ba yanda ta kara komawa kuma gashi kullum dai sai tayi kukan rashin Alim amma a hakan ba laifi ramarta kadan ce ta rashin mijin ta.
Saura kwana Uku su koma gidan Baba Sulemanu Umma ta samu Amana tace na dauki Number Hamza dake littafi jiya na ari wayar Malam na kira shi mun gaisa sosai duk sunce a gaisheki,bikin Sakina da Badriyya Saura kwana 5 biyar a fara kinga zamuje a dai dai,Badriyya tace na fada miki ta kai miki dinkunanki cikin Kano za a yo miki,wai ya cikinki na basu Labari ya zube da abinda ya faru,sunyi jaje sosai,
Murmushi Amana tayi tace Umma bari naje gidan su Nusaiba ayi min dilka da halawa,Malam Nuhu shi ya bawa Amana kudin,Amana kuwa gaba daya kwana Ukun nan a gidan gyaran jiki take yini,ko ina ta gifta kamshi take bari me dadin gaske,skin dinta tayi smooth sai sheki da kyalli takeyi,duk wannan Alim takewa tanaji wai ko zai ganta ya ganta bata lalace ba ya ganta har yanzu fa za a je da ita,yaga bata ci baya ba,kuma duk sabo da tsaro bata San ya ta Allah zata kasance ba ko Alim zai yi tunani ya daina zarginta ya maida ta wajensa kunga kenan a shirye take,dama kuma kun San Amana bata son raini akwai son har kar wanka da gyara hade da tsabta.

Umma tace kinga gobe zamu tafi ko zakiyo lallen bikin?Amana tace a'a Umma salon ya goge ma da wuri kenan ai sai naje can zanje har cikin Kano city ayi min na kece raini,
Duk sabo da Alim Amana ake wannan cakarewa.

Ta wani bangaren Amana tana Jin haushin Alim sosai yanda ya manta da ita duk zaman da sukayi,ya kasa tunani akan abinda ya gani,ya zargeta,har ya yarda zata iya cin Amanarsa,
Uhmmmmm Amana ta furta a fili tace Namiji kenan me manta alkhairi,ka shekara kana aikin me kyau rana daya ta baci ba mutunci...wai ni Alim zai yarda Ina bin maza,wai Alim ya gujeni ya manta Dani,lallai a duniya anything is possible shuru tayi tana ta tunani,
Maybe idan Alim ya ganta ma ko kallonta bazai yi ba ya manta da rayuwarta,wani Hawayene ya zubo mata masu Zafi,ganin Umma na kallonta yasa tayi sauri ta fada daki ta kwanta tana ta shesheka har bacci ya kwasheta.

Alim kam bangarensa sai duai domin yafi Amana shiga kunci yaje Har Adamawa ya gama bulayi baiga Amana ba ya dawo ya dage da addua sosai na tabbata da Alim Bai rungumi addua ba shima da tuni ya haukace ya zare.amma a haka idan ka ganshi sai ka dauka bashi da matsala haka Addua take da yawan karatun Qurani yan uwa mu dage da Addua karatun Qurani shine magani.Alim gaba daya sun rankaya sun taho Kano bikin Huzaifa aboki kuma dan uwa.

Baban su Huzaifa part guda ya warewa Amare da kawayensu haka angwaye da abokai nasu daban duk cikin gidansa sabo da Amare Sakina da Badriyya ba a cikin Kano suke ba su kuma angwaye a cikin birni suke saboda dinner kala uku da angwaye suka shirya yasa Abba yace Amare da kawayensu su taho gidansa angwaye ma haka har mijin Sakina sabo da shima sanadin zuwa zance suke haduwa da Huzaifa har zumunci ya kullu tsakaninsu tare suke shirye shiryen komai,Alim kuma shi ya shirya musu party har kala biyu,Abban mijin Sakina ma ya shirya musu daya.don haka duk shagalin biki gidan su Huzaifa za ayi shi,daurin aure ne kawai za aje gidan Amare a dauro,su kuma iyaye mata suna can zasu Kula da jamaarsu ta gari.
Alim sabo da zaman mutuncin da sukayi da Amana da kuma sonta da yakeyi yasa kaf mazan da matan gidan da yara yayi musu dunkuna na alfarma manyan mazan kala Uku uku yaran kala biyu biyu,har iyaye har Umman Amana ya bayar da nata a Dinka a ajiye mata,Amana kuwa ya Dinka mata har kala Goma da takalma da jakankuna da mayafai tsakaninsa da Badriyya sukayi sirri yace tace wai Huzaifa ne ya Dinka mata itama kar ta fada shine,Badriyya tace to bakina kanin kafata,a halin yanzu Huzaifa yasan Alim da Amana basa tare amma duk ya tambayi dalili ba wanda ya fada masa har Badriyya kawai sai ya kyaleta.
Kayan abincin biki kaf Alim ne ya saukewa su Hamza shi da kudin kayan dakin Amare,amma Sam Angwaye sukace kar a kawo Amare da cokali sunyi komai nasu.
Alim ya karbi kudin ya siyawa Hamza da Kabiru kb fili kato guda biyi a Na'ibawa Kano,sun Hamza harda kukan dadi za a koma City,
Yacewa su Haladu ma za a basu nasu suyi aure shi kuma Huzaifa yace zaiyi tallafin Gina gidajen nasu,Ishaq Saurayin Sakina yace shi kuma zai zuba musu furniture,wannan murna kawai sukeyi suna cewa duk A sanadin Amana suka hadu da wannan alkhairi,Ciranin Amana ciranin alkhairi,ta yo musu hanyar arziki gaba daya gidan,domin ta hanyar su Alim kadai Alkhairi ke fado musu,

Allah sarki Amana ana nan ana Jin dadi ta sanadinta ita kuma tana can ma ba ita ke Jin dadin ba haka ikon Allah yake.
Saura kwana biyu a fara biki misalin karfe biyar Amana da Umma suka kwado Sallama cikin gidan Baba Sulemanu,
Kaf gidan suna nan ana ta shirye shirye,nan kowa ya tashi da ihu ana rige rigen rungume Amana,Mazan kuma suka tafa tas tas da Amana suna ta kashewa ana dariya,da karfi Amana tace surprise no going back sai ihu yeeeeeee,Amana ta rike kugu tare da juyawa ta furta look at me ? Ya kuka ce heeeeeee wlh a basu wuta,Amana tace ai da girma ya fadi gwara na kwana da yunwa,nan suka hargitse da murna yara da manya Amana ta dawo gaba daya,kowa sai cewa yake I missed u Sis,yaran gida suka hada baki we missed u Anty Amana,murmushi Amana tayi tana daukansu daya bayan daya tana ajiyewa,

Nan fa aka fara labarin bayan rabuwa daga nan suka bawa Amana labarin komai na yadda suka shirya biki,suka bata labarin yadda Angwaye da iyayensu suka taimakesu sosai da kawo agaji,a karshe suka fara bata labarin kaf alkhairan da Alim ke musu,suna fada mata Amana kuma bata San sanda Ruwan Hawaye ke bulbula a idonta ba,

Yana yin wannan taimakon a danginta amma Bai taba tambayarta ba lallai badan ita yakeyi ba don taimakon Allah yakeyi,ba komai hakan ma an gode masa cewar Amana.

Lallashinta akayi sosai harda su Gwaggo,Umma kuwa tuni ta sa kayanta a dakinta ta yi sallah ta huta ta fito wajen kishiyoyinta sukayi hira sannan ta basu hakurin abinda tayi,sannan tayi musu godiyar Kula da yaranta da sukayi,

Gwaggo tace ba komai ai daki har yau nakine tunda yakice ta siya,mukan munji dadinmu arziki sai bunkasa yakeyi ta hanyar mijin Amana nan suka bawa Umma ma labarin,umman Amana ta saki baki tare da cewa ohhh....rashin rabo ya sa na tabi ina ta Shan wahala,iyyyeeeee kuce sai cin jar miya da zaki,Inna tace ah mu sai Sam barka Allah ya kai gaban Annabi,wannan yaro Allah masa Albarka,Hajiyayye kuwa daya matar ta shanye hannu tare da bugar cinya tace ai dadi ya barki baki ga yanda muka canja ba harda dunkuna naki yana wajena kala Uku Alim Bai manta dake ba harda ke,

Umma ta rike haba tace oh kinjiiii na gudu na bar ladana,to ai ta faru ta kare yanzu mun dawo kenan,gwaggo tace af wa yagaya miki barni gabas take gane min hanya yar uwa cewar Hajiyayye.

Amana kuwa Badriyya ta jawo akwati guda na kayan Alim da ya dinkawa Amana,Badriyya kuma ta cika alkawari tace Huzaifa ne yayi mata Amana tayi mamaki tayi godiya sosai.

Tace dan Allah ki fada masa idan kunyi waya to kawai Badriyya tace,

Badriyya a cikin wayoyinta biyu ta bawa Amana daya tasa sim dinta da memory wayace me kyau,sosai yanzu gidan Sulemanu suka kara nutsuwa suke zumunci,suka samu zaman lafiya ba a ware kowa.

Dama sai ba wani wasu zasu gyaru,ranar da wani ke kukan babu wani shi kuma ranar yake samun nasa kudin.

Sai yaba kyan da Amana tayi akeyi,kowa kallonta yakeyi har yan uwanta mamaki sukeyi,Amana ta kara gogewa ta Zama mace sosai,

Wannan bacin ran da ta shiga yasa ta Zama miskila,bata magana irin da,ba fada ba masifa,amma duk da haka me Hali baya fasawa watarana sai an dan gwadashi,

Alim kam rashin Amana da halin da yake ciki yasa ya tashi daga miskili, shuru shuru, mararar magana, ya dawo kasurgumin masifaffe number daya,abu kadan zaka masa ya zage yaci mutuncinta,ko maganar arzikice sai ta koma fada a wajensa,kullum cikin hade rai da bakin ciki yake,

Ko Aabid yanzu tsoronsa yakeyi da yayi abu zai ci Ubansa,Duk yan gidansu basa ma ganin fara'arsa,bare Mum da yake gani ita ce ta jawo komai.

Mum kuwa bata zo Kano biki ba sabo da bata son dangin miji,tace ranar yini zata zo a flight ta koma da yamma.

Ana gobe Amare zasu dawo Kano a fara biki angwaye tuni ma sun fara zuwa domin wasu duk daga kasar waje suka sauka,sai na wasu state duk sunzo,Alim yana cikinsu sun cika a Palo yana kwance a 3seater baya magana duk hirar da sukeyi,bacci kuwa ya daukeshi Bai Dade da bacci ba ya fara mafarkin Amana,Yana ta dariya a mafarki yana washsh....Amana zaki kasheni,sai yayi dariya yace my wife I love u,do u know what? Can yayi shuru sai sukaji yace I missed u,

Mika ya karayi ya ci gaba da mafarkinsa yana ta furta I love u.......I missed u......sai hawaye zirrrr zirrrr ta idonsa suna ta gangarowa yana I missed u kuka na kara yawa,sai yi yake ta yi,yayan Huzaifa Ahmad ne ya danawa Alim duka tashi banza na mamajo,zumbur Alim ya tashi yana taba fuska alamar Bai San ma yayi mafarkin ba,sai da ya nutsu ya tuno mafarkin Amana ya kara yi dama kullum aikinsa kenan,da masifa yace mene haka zaka tashe ni,Ahmad yace to dan iska kaje can wajen Amana ka sauke gajiyarka da kwadayinka zaka zo nan kana mana kukan banza da wofi,mayen mata kawai manniru,kwana dayan ma baza ka hakura ba,me yasa Baka taho da ita ba kasan Baka iya Zama saida ita,Alim ya cika tam amma ganin mutane sai ya share zance sai tsaki da yaja kawai yana turo bakin shagwaba kamar mace,Ahmad yace Allah....sannu Ayu....mu zaka kawowa iskancin shagwabarka nan to bada mu ba kaje can gaban Amanan ka mata, Huzaifa yace pls Babban yaya a kyaleshi haka.

Gobe dai za a fara party daya dan haka Amare da kawaye yan makaranta hadaddu Sabo da Badriyya duk kawayenta yan cikin birni ne bata kula na kauye,Sakina kuwa nata duk yan makarantar boarding schl dinsu ne,sai da suka zabo gogaggun yan wanka da masu kyau hadaddu su suka gayyata dinner saboda kar a lalata musu party,tuni Ishaq ya turo abokansa aka ebi Amare da kawayensu da wasu manyan ma da zasu dinna,Hamza ma yana da Mota yanzu zai tafi da kb,Isa da Haladu, Alim ne yace dole sai sunje dinner har dinkin dinner ya musu.

To fa Badriyya da kawayenta da sauran yan Uwa yan mata suna cikin kano gidan su ango Huzaifa,suna part dinsu maman Su Huzaifa rakanas ta dauko musu me lalle da kwalliya,dama Amare sun kashewa jikinsu kudi sunyi gyara sosai,Amana ta rasa me zata siyawa Amare gudun mawa kawai ta je gidan Me gari aka bata Saniyarta ta gado ta sa aka girba saniya da wuka,aka gyarata ta karbi motar Hamza aka zuba nama a buhun huna,ta figi motar Hamza sai cikin birnin kano,wani waje da akeyin kwangilar hada take away takai tace ayi dambun nama lafiyye a zuba a abin take away unique color na alfarma,

Zoben Gold na Alim da ya taba bata ta cire ta ba dashi jingina hhhh jinginar zobe huuu Amana aka bata kudin da niyar idan ta samu kudi zata basu su bata zobenta zoben Alim ne baza ta iya siyarwa ba,baza ta iya rabuwa dashi ba,haka ta karbe kudi ta biya masu dambun nama,computer Laptop dinta ta Nemo ta siyar da ita nan ta kara figar kyakyawar motar Hamza ta tafi Saloon da lalle cikin city,

Sai dare aka gama mata,a daren sabo da rashin tsoron Amana ta koma garinsu Wudil,

Amana fa ta fara daukan haske shining kawai takeyi,ga lalle ga gashi yasha gyara,washe gari Badriyya sai waya take radowa Amana tayi sauri tazo a fara kwalliya da ita,Amana kuwa kwalliya ta cancada kai kace yaune party, Hamzane yace kiyi amfani da matata Amana kije da

ita kawai ni zamu yi Amfani da ta friend dina tafi tawa girma sosai kinga muna da yawa kuma zan kai su little Zaliha ma.
Tnx Bro cewar Amana.

Akwatinta guda tasa a bayan Mota,t a cokala takalmi me shegen tsini cikin kayan da akace na Huzaifa ne a cikinsu tasa wata arniyar atamfa baka da green,dinkin riga da skert yayi mugun da Meta fam,da kyar take mitsi a ciki,ga takalmi da gyale siriri na daukan magana malam,ta sha kyau kamar a sace ta kamar wata yar shugaban kasa,
Dama ga tafiyar Amana tun asalin ta takama da gadara ce,

Sai zuba kamshi takeyi gashin ta glass a fuskarta brown yayi mugun mata kyau gashi sake a gadon baya.
Wajen masu take away ta nufa tuni an gama mata komai nata na take away yayi kyau shi kanshi plastic da marfinsa da aka zuba dambun naman a ciki abin kallo ne,Bare ledar da aka sa plastic din a ciki wai wai,buhunan take away ta zuba a Mota,sannan ta sa kati a wayarta,sai canjin kudi sababbi dal dal yan dari dari da ta canja rapa biyu,ta zuba a pose din dake hannunta Direct gidan su Huzaifa ta nufa da motarta,

Yan mata da samari sai sintiri sukeyi a gidan,wasu tsakanin mata da mazan ma har sun saba da juna sai shagali akeyi tare,musamman aka dauki dj aka sa a tsakar gida zai dinga kida kwana da yini har a gama biki,Alim duk wacce ta shige sai ya kalleta ko Amana ce ,amma Amana shuru,ko yaushe yana tsakar gida ko zai ga tazo amma shuru,Shine ya kutsa wajen Badriyya wai lallai sai ta kira Amana tayi sauri tazo ayi mata kwalliya,Badriyya shine fa take ta faman kiran Amana,
A waya.

Dama in baku manta ba Amana tasan gidan su Huzaifa,Alim yana zaune a farar kujera a tsakar gida gindin bishiya ga dj na tashi wasu na rawa wasu na hira,wasu matam gulmar Alim sukeyi ga wani me kyau ga haduwa kamar bature,wasu suce dan india ne,musamman kawayen su Asiya da kannen su Huzaifa yan iyayin tsiya yan kwalliya da daukan wanka,har fada sukeyi wai ina marar mutunci matar yaya Alim ne,gwarzuwa me tuko Mota from lagos to kano,sun ga Alim ba fara"a yanzu shi yasa basa tambayarsa Amana,wasu yan matan kuwa cewa suke mutum baya kula kowa sai ya dinga fitowa yana wayon kallon yan mata,
Wasu sukace munafukin banza ba fara'a baya kallon ko wacce da mutunci kamar yaga kashi to uban waye ya sa ya fito waje.

Amana ce ta danna uban Horn a kofar gidan,me gadi ya wangale kofa,ta shararo motar cikin gidan da Alim tayi tozali.

Sorry masu karatu bakuwa nayi yau shi yasa ban gama typing da wuri ba,n asan kun jirani,gashi ku karba na wullo muku.........

AsmaBaffa
✳CIRANIN AMANA✳

165-170

Official

By
AsmaBaffa

INA GAISHE KU MAKARANTA CIRANIN AMANA.

Da Alim tayi tozali ya harde a kujera ya tsirawa gate ido,tuni gaban Amana yayi mummunan faduwa,da kyar ta iya parking din motar sannan tasa hannu a saitin kirjinta ta dafe tana maida numfashi ga mugun sabon Son Alim da ya taso mata,tunani ta shiga na abinda ya faru a baya, Hawaye ke neman kwace mata a hankali ta maida kukanta tare da furta ah...Oh God ....bazanyi kuka ba...karki yi kuka Amana ke me dauriyace,amma duk da haka saida hawaye kadan ya fito tasa yatsa tare da dauke hawayen,sai da ta daidaita kanta sannan ta bude kofa tare da zuro kafarta daya waje,bata ma son ta kalli bangaren da Alim yake bare ya mata wani wulakancin tunda yace duk hanyar da zata hadasu kar ta sake ta bi ta wajen,sannan yace mata ya tsaneta,amma kuma dole sai ta wuce ta gaban su Alim sannan ta shiga cikin gidan part din Amare,

Alim kuwa kalle kalle yakeyi yanda Amana zata bullo bai kawo itace a Mota ba domin bata da Mota amma sai kallon motar yakeyi yana tuna inda ya san motar,

Alim a ransa yace wannan kamar motar Hamza,gashi wata kyakyawar kafar mace ya hango

kamar ta yar India,takalmin kawai ya gani ya gane takalmin da yasiyo ne a London ya kaiwa Badriyya ta bawa Amana,wannan kenan Amana ce tazo da motar Hamza tunda dama yasan Amana ta iya driving,yes itace Alhmdllh cewar Alim.

Amana kuwa kasa fitowa tayi saboda da gudun kar tayi kuka,amma haka tayi shahada ta fito gaba daya da kyar saboda yanda dinkin ya tamke mata ko ina cip cip,tuwon mazaunan nan gasu sunyi dam sosai,

Ko mayafi bata yafa ba yana hannunta saboda taga cikin gidane kuma tayi ne Sabo da Alim yaga fa ba ta tashi takeyi ba wai irin ta manta dashi ma wanka take dauka shiga takeyi yanda taga dama,bayan kwalliyar duk dan shi akayi,shi kuwa Alim yaga duk kayan da ya siya matane a matsayin na Huzaifa,sai farin ciki ya lullubeshi,ga wani kyau na ban mamaki da Amana ta karo,da gogewa tare da zama hamshakiyar wata yar budurwa,

Ka rantse bata taba aure ba,

Nan take kishi ya tasowa Alim za a kalli Amana ga maza,to wai ma ina cikin dake jikinta tambayar Alim,ko ta zubar dashi lallai ma yarinyar nan zanyi maganinta,

Yana ta magana a zuci ji yake kamar yaje da gudu ya rungumeta,yama rasa inda zaisa kansa,Amana kuwa juyawa tayi tana fito da buhun hunan take away,da akwatinta,mayafinta na rike a hannunta tana ta tunanin Alim,ji take kamar taje itama ta rungumeshi yanda taga ya kara kyau da haduwa yar ramace kadan jikinsa ita ma sai kayi masa farin sani za kace ya dan ragu kadan,Amana a ranta tace uhmm dan gayu wannan uban daukan wanka da yayi haka kamar zaije dinner,

Ya wani zo ya zauna cikin mata sai kallonsa akeyi,awai dan a kalleshi an fada masa kowa ce zata soshi dan yana da kudi da kyau ya wani zo sai tallar kansa yakeyi,salon wai ace ana sonsa tsaki taja a hankali,kaji fa Amana to ina ruwanki.

Buhu buyu ta dauka tana tafiya das das kowa mata da Maza sai kallonta akeyi,Alim kuwa dafe kai yayi yana hadiyar yawu,yace lallai yarinyarnan kalli yanda take wani bawa mutane show kalli Maza sai kallonta akeyi lallai zan gyara mata zama wannan ai tangal tangal ne da aure kaji Alim to ina ruwanka da ita kaida ka tsaneta,

Garemu matan Aure,zawarawa,yan mata,karki bari mijin ki ya dinga dawowa yana ganinki bakya daukan wanka kamar zaki party,bazawara da budurwa ko kun rabu da mijinki ko saurayi ki sani bafa mantawa yayi dake ba ko ya daina sonki yana nan yana sa miki ido yana bibiyar halin da kike ciki,kinci gaba ne ko kin lalace,namiji yana bakin ciki yaga sun rabu da mace taci gaba,tafi da haduwa kyau da komai da komai,yafi so yaji ance ai naga wance rannan baka ganta ba ta lalace ta rame ta fige,duk kwalliyar wance tab ai kasa ganeta nayi a hanya,ta dawo abar tausayi,ko kuma shi wanda kuka rabu ya ganki da kansa,kin lalace murna zaiyi ba zai damu ba,cewa zaiyi ma wa ya gaya mata,da tana jin dadi a gidana tayi min kaza na kori shegiya gwara haka gashi ai yanzu ta dawo abar tausayi,ai Baza ta samu kamata ba,tayiwa kanta,yanzu ni aka bani wannan me zanyi da ita,ai gidansu wuya suke sha etc.idan kuwa ya ganki kinci gaba,idan yana sonki sai yayi dana sani tayu ma ya dawo yayi ta naci ki koma,ya rude a kanki zaman da kukayi tare ya dawo masa,ko labari yaji saiya nemi ya ganki face to face

ya ganewa idonsa,idan budurwace sai yaji takaici ko bai aure ki ba,idan matar aure ce zai kara dinga kaunarki,dan karamin neman aure sai kiji ya fasa,ko ya auro ma yasan kin fita,kowa yana son gyara,tsafta,kwalliya etc duk da cewa suma mazan suna da matsala,amma mata shine ur eye woooo a kara dagewa a daure a cire kyuya da son jiki kiyi iya yinki,

Amarya Sakina ce ta fito ita da ango Ishaq wai yazo kawo mata abinci ta kasa cin abinci shine yazo da take away sai da ya tabbatar taci ta koshi ta rakoshi zai tafi kafin zuwa after magrib dinner party,

Da Amana suka ci karo,dariya Sakina tayi oyoyo Anty muna ta jiranki ba dadi ba kya nan,to banza take away na tsaya daukowa laaaaa hado mana kikayi? Yeah cewar Amana,Nan Sakina ta dinga godiya Suka gaisa da Ango shima harda godiya,

Sakina ce tayi magana to ki mayar cikin motar kinga ko an kai ciki sai an kara fitowa fa dasu dole ga mutane,Amana tace af hakanefa na manta kinsan ni ba kawaye ne mata dani ba,sannan bikina ban samu gatan haka ba ban san ya abin yake ba,bari na maida,ango dai tuni ya hau mota ya tafi,Sakina ta dauka bari na tayaki...Amana tace commot abeg Amaryace ke ba aiki ai,matsa ko na makeki,Sakina ce ta radawa Amana ga mijinki can kamar zai cinyeki da kallo,kinga kalli yadda yake ta muzurai,kamar kishi yakeyi fa,Amana tace zan mareki Sakina ban son shirme na fasa kaiwa motar ebi ki kai ki zuba,

Kai Amana saurin zuciya da fushi yana nan dai,kyaleta Amana tayi ta koma ta kai kayan cikin Mota da kanta ta dauko trolley dinta ta juyo kenan taga Alim a bayan yana huci kamar zai daketa har ta tsorata sai ta tsinci muryarsa yace gyara parking din motarki zan fita da tawa,Amana itama a fusace tace duk filin nan bai Isa ka dauki Mota ba sai na gyara parking?Alhmdllh Alim ya furta a ransa saboda dadi hade da sanyi da yaji a ransa Amana tayi magana yaji muryarta,

Cike da masifa ya kara cewa ko bazaki janye bane?Amana shuru tayi don taga kamar zai daketa yanzu kuma bata fada,kawai sai ta shiga motar ta janye ta can lungu ta fito a fusace fuuuuuuu ta ja akwati ta wuceshi.

Badriyya sai murna takeyi Amana tazo Sakina har ta fesa mata Labarin Alim da take away na Amana da ta musu,

Bayan Amana ta huta saiga Asiya kanwar Alim tazo tana cewa Badriyya wai ina matar Ya Alim ne?

Da sauri Badriyya ta nuna Amana dake kwance saman gado tana faman tunanin Alim,

Anty Amana ina yini cewar Asiya Amana ta amsa cikin fara'a da sakin fuska,Asiya suna kama da Alim sai take ganinta kamar Alim,kallon Asiya takeyi tana ta murmushi tana jin sanyi a ranta,sai suka fara hira, har muryar Asiya kamar ta Alim,Amana sai hira take kakalowa,Asiya tace muje wajen su Abban Huzaifa da Mama ku gaisa da sauran dangi,Amana ba musu ta yafa mayafinta tare da kara gyarawa suka wuce,da dan Auta Kanin su Alim suka ci karo Asiya tace Bro kaga matarfa ya Alim na san baka santa ba lokacin kana schl,Amana a ranta tace wannan yama fi kama da Alim dina,gaisawa sukayi sosai yana ta tsokanar Amana ashe matas ce ma,gaskiya na iya zaben me kyau,suna tsaye saiga Nura ma Babban yayansu shida matarsa

da yarsa sun dawo daga shopoing,Asiya tayi sauri ta nuna musu Amana suka gaisa harda hira sosai da sosai saboda Nura akwai nutsuwa, Amana a ranta ta ce lallai ai wannan Nuran ma sunfi kama sak da Alim. matarsa ma sai jan Amana take da barkwanci,tambaya Amana tayi wai ina dana ne Aabid?

Nura yace yana wajen Maman Huzaifa yana ta bacci,ok kawai Amana tace taja Asiya suka wuce cikin part din su Huzaifa,Da sallama suka shiga palo da Alim suka fara hada ido yana saman kujera yana cin snacks da Icecream a gefe,

Huzaifa Ango yana gefensa,mama tana zaune tana jira lallenta ya bushe,ga sauran yan Uwa mata nan gaba daya cike dam a palon amma Alim yana ciki yana cin abu sunki tashi,,tsugunawa Amana tayi har kasa ta gaishe dasu kaf cikin mutunci,Mama da fara'a ta tarbeta tana yata sai yau kika zo muna ta jiranki,dariya Amana tayi,Alim a ransa yace wayyo ta kasheni da murmushinta,

Tambaya Amana tayi ina Abba da yar tsohuwa kaka kenan idan masu karatu baku manta ba,Tace tsohuwa tana daki da bakin ta har danki Aabid yana wajenta,Abba kuma yana sama ke Asiya rakata ta gaida kowa,

Sun mike sunje ko ina sun gaisa da kowa cikin mutunci sun dan dade suna hira da kaka tsohuwa Aabid bacci yakeyi,kowa na dangi sai da aka nuna masa Amana suka gaisa

Fitowa sukayi amma still Alim yana palon kusa da Mama,Huzaifa kuwa ya koma jikinta ya nanike ya kwanta a cinyarta,kowa ya shigo sai anyi dariya Ango kamar Amarya me jimamin rabuwa da gida,

Mamace ta kalli Amana dake shirin fita tace zo yata,dawowa Amana tayi tare da tsugunawa har kasa,duk wanda yasan Amana a da sai yayi mamakin canjawar halinta yanzu har Alim,Mama tace zaki dawo dakina da kwana ne? Da sauri Amana tace a a zan zauna wajen frnds,Haushi Alim yaji a ransa yace da kin dawo nan ai nafi ganinki,Huzaifa yace Anty tafi son cikin yan mata,hararar wasa Amana ta cilla masa,

Yana dariya yace to mene na harara,kowa yayi mamaki ana cewa matar Alim ce amma anga basuyi magana da juna ba sai kallo da yake binta dashi kamar maye yana shan Icecream,

Mama ta fuskanci kamar da matsala tsakaninsu Amma sai kowa ya share tunda ba wanda yasan komai akai,Mama tace to ga dakin mijinki ko can zaki zauna dan iyayi dakinsa shikadai ne ko angon ma su biyu ne amman wannan marar kunyar Mama taja kunnen Alim tace dakinsa daban kullum yana cikinmu,yaki bari mu sake,dariya akayi banda Alim da Amana, Umma duk bata sani ba Alim ne ya tura Asiya ta kawo Amana su gaisa da danginsa shi yasa ya dawo palon ya zauna Sabo da ya kara ganinta,

Mama tace zauna yata,Amana kallon dakin tayi kaf ba space kujera 2seater ce kawai ta rage me dama dama,itama Alim ne a kai ya wani kwanta,Mama tace zauna kusa da wannan kwadayayyen Alim kenan,Amana bata son tayi musu,gashi bata so a gane halin da suke ciki da Alim tunda shima ya boye,Mama tace gyara musu su zauna mana, Asiyace taje ta fara Zama sannan ta jawo Amana ta fada kujera suka sa Alim a tsakiyarsu,

Tofa an Dade ba a hadu ba.

Jikinsu ne ya gogi juna,wani uban shock ne da faduwar gaba ya shigi masoyan biyu,
Haushi Alim yaji kar ma tace ya damu da ita,itama Amana haka,Alim ya matso jikin Amana ya bangajeta da kafada tayi gefen kujera haushi taji a ranta tace dan yana Jin haushi na sai ya bangajeni,gyara Zama tayi,ya kara bangajeta,Amana a ranta tace kai Kai kai da Zafi fa Bai isa ba saina Rama wlh ina ruwana dashi,Amana ta matso itama sosai ta bangazo Alim Bai zata ba ai kuwa ya rikita jikin Asiya,
Asiya tana kallonsu tayi murmushi,Alim a ransa yace halinta Ashe yana nan,nan ya samu ya kara turota tare da kara hade rai,Amana ta kyaleshi ganin mutane kara bangazota yayi,Ai kuwa ta samu ta sa hannunta iya karfinta ta turashi jikin Asiya tana nishi da cijewa,kuma sunyi mukus suna ta faman ture turen juna,haka suka dingayi sai kallonsu yan biki keyi suna dariya,mitsini Alim ya kwanyawa Amana a cinya da sauri ta sosa waje tasa kafa ta take masa kafa tare da murzawa,Alim yaji Zafi amma ya cije, hannu yasa ya yakusheta a wuya har wajen yayi danja kadan,Mama tace wai me kukeyi haka Ku tashi ku barmin Palo iya shege a cikin bakina sai ture ture kukeyi da yakushe yakushe, Ku fice Ku karata can,mikewa sukayi gaba daya Amana fuska ba rahama Alim ma haka,Asiya dariya ta cika mata ciki wannan soyayya haka.

Suna fita tsakar gida Alim ya taho da sauri Amana ta matsa gefe amma saida yazo ya bangajeta ya fara tafiya,da gudu Amana Ido cike da kwalla ta bishi tare da cafko hannunsa ta ganya masa cizo da karfi kamar kura tayi hanyar part din yan mata,

Alim sai da ya saki kara,a fili yace sai na balla yarinyarcan ina wasa da itane,ina ruwana da ita zanyi maganinta.

Amana kuwa daki ta fada tana ai wlh kana min zan rama kaji mutum ina ruwana dashi saboda yana neman na masa rashin kunya ya ci min mutunci shi yasa yake tsokanata to ni kuwa bazan kyaleshi ba sai na rama karma yace tsoron sa nakeyi.

Ana ta shirin dinner Amare sunsha kyau,yan mata da samari kowa walkiya yakeyi,ana ta iba ana tafiya can,Amana ma ta shirya cikin tsadajjen lace light blue da red,gogoronta red,jaka da takalmi red,jambaki red,sarka dan kunne agogo duk red,pose dinta ma red,tasha kyau na gaske,dinkin fitted gown fadin kyan da Amana tayi bata bakine,

Har wajen kaka tsohuwa taje har an shirya Aabid,kowa yaba irin kyan da Amana tayi akeyi da wanda ya Santa da wanda Bai Santa ba,Aabid na Jin muryarta ya dago kansa da sauri tare da rugowa da gudu ya daka tsalle ya dane ta,dagashi sama tayi suna ta dariya,Momy ina kika tafi bana ganinki? Amana tace unguwa naje nan suka dinga surutu tare,sai ji tayi gaba daya har an tafi tana nan,Aabid ta dauka tayiwa tsohuwa sallama,tana fita Alim ma ya fito cikin shiga ta alfarma kamar wani dan sarki,yasha kyau sai kallon juna sukeyi kowa na yaba shigar dan uwansa,Alim cikin shadda Fara kal yake komai fari yayi kyau na gaske,suma taci kudi,kamshi da kyalline kawai ke tashi,
Tunawa Alim yayi ai sunyi fada da Amana basa shiri da sauri ya dauke kai ya juya,Itama Amana a hankali tace au jaka ni kamar muna shiri na wani kalleshi,to wanne ma kyau yayi shi

din me, me ya hadani dashi tsaki taja ta wuce motarta ta bude tare da sa Aabid a gaba,Aabid ya fito fit yace Momy ga Daddy can motarsa tafi kyau muje a tasa,Aabid ya kwalawa Alim kira Daddy ka jiramu muje a taka,Amana tace to bazan shiga motarsa ba dalla wuce muje,Alim ma yaji me Amana ta fada shima magana yayi da dan daga murya yanda zata jishi ko kinzo ba daukanki zanyi a motata ba,ko kinji nace zan daukeki dama,da masifa Amana tace oho ko kace ma ba shiga zanyi ba ehe,kuma a daina kallona za a cinye min kurwa to tawa daci gareta kurwata kurrrr ta karasa tana huci,.

Alim shi dariya ma ta bashi da birgeshi,kinga na kallekine?baki kyau ba dai,ga masu kyau can sun tafi party,Da masifa Amana ta hayayyako me zasuci da kai ragowar mata,woooo ragowar mata an gama da kai sai ragowa zasu samu,mata nawa ka aura me auri saki,ina fada ma watarana wata sai ta harbeka kowa ya huta,

Dariya ta kusa kwacewa Alim sai ya kara mazewa ya tamke fuska yace haka na gani shi yasa kike bin abokaina kina fada musu su bani hakuri na dawo dake,

Kugu Amana ta rike tace kalleni tsaf na wuce ajinka Malam ai kai na gama da shafinka na jefa a shara masu kwashe shara sunzo sun kwashe ka an zubaka a katon rami.sai yanzu ma nakejin haushi kaina na auri Kazami yan... yan... yan.....tana yatsina fuska ta kara da cewa ko kyau babu,yanzu ma da kasan munin da kayi da baka je dinner ba ta tsaya tare da murguda baki,

Alim dariya fa yake tayi a zuciya ya samu abinda yakeso,da sauri yace wannan kuma karya kikeyi yarinya,kuka ne ya tahowa Amana tayi sauri ta maida shi tare da jan kwafa ta shige mota,Aabid Bai San me sukeyi ba har ya gaji da jira,kowanne ya figi mota ya hau titi suna tafiya idan Alim ya figi mota ya wuce Amana sai Amana ta cisga ta wuceshi itama,

Idan masifa ta ciyosu sai kowa ya danna mugun horn,yanzu Alim zai wuce Amana ya sauke glass kasa ya zo saitinta da mota ya fara mata gwalo,itama kuwa ta tako da karfi ta masa gwalo wullo wai dan ta tura masa haushi da yawa ta dallaro harshenta ta barshi a haka,tana kaga kaga suna hada Ido ta glass tace nafi karfinka baza ka iya Dani ba,na Riga na maka nisa na wuce ajinka,ta ce woooo wulluuuuuu, ta zuge glass tana haki cike da masifa tace nayi maganinsa ai Bai isa na kyaleshi ba,bazai ja Dani ba,

Alim kuwa yana rufe glass ya dinga dariya kamar me har suka karasa wajen dinner.tare suka tsaya Amana da Bala'i ta fito wai irin kar Alim ya rainata.
Alim kuwa ya shirya me zai taokaneta dashi.

AsmaBaffa
✳CIRANIN AMANA✳

170-175

Official

By
AsmaBaffa

MARCYCOOL JINJINA GAREKI,

DUK MASU SHARHI WANNAN PAGE NAKUNE,SANNUNKU DA KOKARI INA MATUKAR JIN DADI,KUNA KARA MIN KARFIN GWIWA.

Amana rike da hannun Aabid sauri tayi ta shige wurin da ake event din,wow wuri ya hadu sosai Dinner Baban Ishaq angon Sakina ce yau nasa da ya hada musu aka fara yi,Amare zaune da angwaye sunsha kyau,wurin ya cika da mata da samari dangin Amare da Angwaye,ga kawaye da abokai,wanka iya wanka,mata iya mata maza iya maza a wajen nan ba a magana.

Aabid kuwa da gudu ya tafi wajen Nura da matarsa da yarsu,Amana ana tafiya kwas kwas sai kallonta ake ta faman yi musamman maza,

Ta wuce zata zauna Ashe Alim yana bayanta duk inda tasa kafa sai yasa,sabo da kida bata ji tafiyarsa ba,Amare harda dagowa Amana Hanu suna zaune,Badriyya ta dagawa Alim babban yatsa shima ya daga mata tare da murmushi,Sakina ta masa inkiya da Ido,nan take Alim ya bar kusa da Amana wajen Asiya yaje tana zaune ita da Ahmad yayan Huzaifa ,Alim fuska ba wani walwala ya furta Asiya tashi ki janye min wancen Ku zauna tare,

Dariya Asiya tayi tace yaya Da Alama Allah laifi kayi mata shi yasa kabi ka nacewa mata ka kyaleta ta huta pls,

Zan mareki kije kiyi abinda nace,Ahmad yace kai masifaffe mufa ka ishe mu da wannan matartaka tunda tazo yanzu duk gidan biki gulmarku akeyi iskancinka gaban kowa yi kakeyi Ayu kawai.

Kana surikin nawa? ai an kusa bikinka idan naga dama sai na hanaka kanwata ka rufawa kanka asiri cewar Alim, Asiya kuwa tuni ta cika Umarnin Alim zaune ita da Amana dan auta ma wajensu ya dawo yana fadawa Amana wai ga wata can dan Allah taje ta hadasu ko zata soshi,Amana tace dan yaro dakai to ba Dani ba,dariya sukayi,Alim yana kallonsu yana ta Jin dadi.

Amarya Badriyya da Huzaifa MC ya kira su fito fili ana bukatarsu,Amana ce ta fara mikewa ta shiga fili, Amana bata rawa bata taba yin rawa ba saboda kar a rainata wai hee baya ga haka ma bata iya ba.

Yan Dari Dari ta fara lika musu, cikin takun isa da birgewa sai ga Alim yazo ya fara likawa Amarya da Ango yan Dubu Dubu shima yana liki

Kallon Amana yake yi idonsa na kanta suna hada Ido sai ya maka mata harara itama kafin kace me ta rama harda murguda baki,

mutane ne suka zo yuuuu mata da maza suka lullube wajen kowa liki yakeyi,wani Namiji ya fara likawa Amana kudi sosai,Alim takaici ya kama shi,Amana juyawa tayi ta dinga likawa Saurayin nan kudinta,Alim kamar ya hadiyi zuciya ya sheka lahira,

Kafin kace me ransa yayi bakinkirin,har idonsa ya canja color tsabar bala'in da yakeji,

Yana ta likinsa Bai fasa ba cikin zafin nama ya samu ya shige tsakiyar Amana da saurayi ya musu kerere a tsakiya tare da ci gaba da yiwa Amare likin Naira.

Amana Jin kamshin turaren Alim yasata lumshe Ido nan take ta fada tunanin rayuwarsu sanda suna tare yana nannadeta cikin kirjinsa ta shaki kamshinsa da dumin jikinsa son ranta

Matsowa yayi yanda zata ji shi cikin bacin rai muryarsa har rawa takeyi nace ki fita  bana so me kikeyi haka kinawa kato liki for God sake, ko kallonsa Amana batayi ba,cikin karajin da Amana ce kadai zata ji ya furta zan yi maganinki ki bar ganin Ina wasa dake akan wannan bazan miki da sauki ba.

Amana ba walwala ta furta sannu Ubana Sulemanu kai awa?mene hadina da kai ta fada tana Balla masa uwar harara,haka kikace?cewar Alim,Amana ta kalleshi up and down tana fari da Ido tace wacce grass ce kai ko nace wanne weed ne? Wanne ruwan kwatar ne?wacce shara ce?

Me likawa Amana kudi tuni kudinsa suka kare yayi waje kuma yana jin fadan da sukeyi da Alim a ransa yace saurayi kayi asarar budurwa sai dai ka koma wajen Bazawara Amma wannan Budurwar yar dagwas gwas ni zan kwaceta.

Alim da ya tuno me yayi sai ya tuna fada sukeyi ba kishinta yakeyi ba ina ruwansa,

Sai ya canja magana da cewa taimaka miki nakeyi saboda bakiyi kyau ba abin kunyane aga ana miki liki ke baki ga dariya ake miki ba,Amana taci gaba da masifa Alim kake ko wa?ka sakar

min mara nayi fitsari pls nace bana yinka kaje ka nemi irinka yanzu nafi karfinka ehe yawwa asakar min mara nayi fitsari,, murmushi Alim ya saki wanda ke kara masa kyau, Amana a ranta tace mijina me kyau, Alim ne ya katse mata tunani  da cewa idan naki fa?

Itama ta fara magana kasan ni ai kasan Halina ko na gwada ma? ni da kake gani na ba mutuncine dani ba,ni abin kunya idan ya ganni to guduwa yakeyi saboda uwar gidansa tazo Amana ta furta cikin fushi kamar bata taba dariya ba,Alim yace hmm wanda kikewa ne suke kyaleki yarinya,Amana ta maida martani gaka nan Babban yaro brolas kajin gidan gona girman dare daya.

Gadan gadan ya nufi wajenta da niyyar damkota amma Amana da sauri ta sauka kasa tace idan yau za a kwashi wani zuwa hospital yazo ya biyoni ya gani, masu rawa da liki suka ci gaba da yi,

Amana tsakaninta Da Allah fada akeyi gagarimi, yanda take jin haushin Alim sosai ba mutunci,shima Alim haushin Amana yakeji baiga ciki jikinta ba,sannan ta wani manta dashi ta kara kibarta da kyau,da aurensa a kanta tana ta yawo inda taga dama.

Alim yaga Amana da gaske takeyi karta kunya tashi a mutane sai ya fasa ya koma ya zauna Amana taci gaba da shagalin bikinta,har aka zo cin abinci inda kowa zai tashi yawa kansa serving abinda yakeso,ana ta karbowa,Amana ta ebowa Aabid,little Zaliha,da Ikkram din Nura,

Komawa tayi zatayi serving kanta fara Eba tayi  Alim yazo ya wani faffake wajen,Amana bata kulashi ba ta samu ta matsa,  kara faffakewa yayi, lekawa tayi tana dogon wuya zata ebo ta wani cokalo bakin masifa,duk inda ta nufa da niyyar ebowa sai Alim yaje yayi blocking wajen,

Alim haushinta yakeji yanda ake kallonta ana yaba surarta, cokali me yatsu tasa tare da yakuso hannun Alim ai kuwa fatar hanun ta kwarzabe kamar yakushin damusa, ta eba tayi gaba.

Dinner tayi kyau da dadi,bayan an tashi duk an watse gida,su Mama sun tafi da Aabid,Alim ya fito ya hango Amana zata shiga Mota shima zai shiga tasa ya murde mata kunne  sosai ya,Amana haushi ya isheta ta sai kawai ta shareshi ta shiga Mota ta figa ta hau titi,Alim ma haka,

Gani tayi Alim zai wuce ta tayi masa Over taking tare da sauke glass tana masifeshi dan jagaliya baka iya tuki ba ka koma ka koyi mata,Alim ma ya leko ya kwalla da karfi idan na raina kasuwa ko sautun Cincin bazan yi ba,

Amana tace dan kauyeeeeee,Alim yace daga birni nazo nazo ai,wai yayiwa Amana gori,

Nafi karfinka dai ni na wayar da kai,

Alim yace ai kin iya daurin dankwali yanzu,Amana tace ance maka da can iyawa kayi? ,Alim yayi maganar yan daba yace kya nuna mana Zara,ai mune Zara yar nan,

Ni ba karamin tantirin dan iska bane,Amana ta kwallo itama da karfi tace ai kuwa nima ba karamar tantiriyar yar iska bace kai dukkan mu ba kananan tantirai bane,Maganar ta irin ta nigogi tayi Baaaaba kana yawa,Alim yace motar aroceee,Amana tace dan mafiya me kudin

tsafiiiii motar da ka siya da kan dan jariri.

Suna karasowa cikin gidan kowa ya Parker tare da fitowa zata wuce part dinsu,Alim ya kama yatsanta ya lankwasosu baya ta kwalla kara ta kwala masa jakarta,tana haki tace azzalumin mutum ni ba wasa nake da kai ba
Tafiya Alim yayi ya kyaleta yace yarinyar nan da gaske take amma na kyaleta daga yau ya furta cikin fushi.

Amana kuwa ciki ta shiga tayi wanka ta canja kayan bacci ta kwanta gefen Sakina da Badriyya.
Badriyya ce ta Mike ta fara magana Anty Amana ina kika tsaya haka kin San har 2am yanzu fa,banza Amana ta mata,Badriyya tace dama tambayarki zanyi dan Allah first night da Zafi?Allah tsoro nakeji,
Amana tayi dariya tace sanda kika dinga zuga Alim kina hadamu daki ki kulle kin nemi shawarata?
Ki kyaleni naji da abinda ya dameni pls,
Juya baya Amana tayi ta fara tunanin Alim yanda zata daina kulashi ko yayi magana ta daina kulashi,ita zai rainawa hankali ya mata laifi ko yayi tunanin lallashinta saima wani hade mata fuska da yakeyi tare da gwada mata mungunta.

Washe gari bayan Anyi sallar Asuba rana ta fito kadan kowa ya koma baccin safe,12pm Amana ta tashi daga bacci wanka tayi ta shirya cikin doguwar Rigar material Golding color tayi kyau Sosai kamar a sace ta,Amare da kawaye duk sun dau wanka anci ansha,Amana bata ci komai ba ta wuce wajen Maman Huzaifa tare da gaisheta da sauran dangi,Aabid ne yazo tare da makaleta,cike da kunya Amana tace Mama abinci nazo nema,Mama tace ke duk kowa yaci yasha sai yanzu kika fito ana jira a kawo lunch duk an wanke komai tare da gyarawa,shiga kitchen ki hadawa kanki,
Kitchen ta shiga ta dafo indomie da kwanta ta dawo Palo kusa da Mama zata fara ci Alim ya fito cikin 3qtr da Riga T-shirt yana kamshi,Mama tace girman lagos aikinka kenan yawo cikin Mata kaine nan kaine can ga shigar arna, Amana sau daya ta kalleshi ta dauke kanta gefe,
Matsowa yayi tare da gaisar da Mama kana ya kurawa Amana Ido tana cin Indomie Aabid yana gaida Alim ya zura da gudu ya bar wajen ya hango yara na wasa,
Alim kuma ya tsuguna ya dauke plate din Amana yayi tafiyarsa da abincin,Mama ta saki baki tace Alim zan bata maka wlh dawo mata da abincinta,Alim yace Mama yunwa nakeji fa,to ita kuma fa?Sai ta dafa wata Mama tace sai dai ka dawo kuci tare sai ta kara dafa muku wata Ku kara,
Amana tace ni na koshi kyaleshi,a'a baki isa ba cewar Mama spoon biyu kikayi fa, Mama ni bazan ci dashi ba Kazami ne fa Amana ta fada da azababbiyar shagwaba wacce tayi sanadin zukewar numfashin Alim, ajiye Alim kuci cewar Mama, cikin yan uwa duk suna palon,Alim ya jawo sallaya ya zauna yana masifa yacewa Amana sai ki sakko kasa ai kamar wasu yara, Amana gudun kar tayiwa Mama musu ga dangi za a gane basa shiri kawai ta sakko kasa ta zauna Mama harda mika mata pillow ta zauna tana hade rai,
Mama tace Asiya ta je ta dafa musu wata kafin su cinye wannan,

Asiya taso a kyaleta itama taga fadan su Alim amma haka ta wuce kitchen,

Fork spoon dayane Alim ya fisge a hannun Amana ya dinga cin indomie da sauri da sauri wai dan yafi ci da yawa Amana ta rasa ,Amana ta finciko cokalin a bakinsa yasa hakuri ya rike spoon din gam, da kyar ta zaro cokalin itama tai ta ci da yawa ya kwace cokalin tare da tattaro indomie gabansa,yana ta ci,Amana tace Mama kinga zai cinye du,Mama tace wai kai wanne irin mugu ne?bata spoon dinta taci,Amana ta warce itama ta sharba,Alim yace Mama kalli kazantar da takeyi wlh zata lalata abincin,Mama tace to kema baki dai dai ba bashi cokali yaci,Alim ya kwace yaci da yawa Mama tace kaima kayi zari ka bar mata plate din sai an kawo wata Alim yace haba Mama ko romon ni fa ban sha ba,Wata a cikin dangi tace to kai kaci girma mana akan Indomie kamar mayunta ku bari a kawo wata mana wlh Mama ke kike kulasu,ji nake jiya suka gama iskancin ture ture da yakushe yakushe,
Amana tace Allah ni bana kulashi shine yake takalata,cokalin ya dan buga mata a goshi,Mama tace ah...kema da halinki duk halinku daya,ni ban san Alim da haka ba sai yanzu,

Asiya ce ta kawo musu lafiyyar Indomie tare da mikawa Alim cokalinsa daban,
Nan kowa ya fara ci sai gwaren cokali sukeyi a plate,ka daina cimin gabana,cikin rada Alim yace tab wannan maganar tafi karfina kin jin nace ina nema zan....Amana tayi shuru har ya fassara mata magana. Suna ci gaba da ci Sai ta ebo yasa cokali ya kwace,Amana ganin mutane yasa ta kyaleshi,da yaga taki kulashi kuma so yake ya sata bakin ciki sai,ji tayi kawai ya turo plate din jikinta Indomie ta zubo mata a gefenn cinya ta bata mata kaya Amana kwalla tab a idonta tace Mama kin ganshi ko wlh kar na rama aga banyi dai dai ba,na gaji da halinsa sai yana dukana yanzu ma kina kallon can ya mareni kaji Amana da karya, wata dattijuwa tace abin naku iskanci ne kawai ,Mama tace kai ku rabu dani na gaji da halinku,Amana tace Mama shine fa yake ta min abu,jiya ma haka ya dinga dukana,har marina yayi a wajen dinner da zamu dawo,Wata  a cikin yan biki tace wai ba mata da miji bane? akace mata da miji ne,matar tace iya shegen banza da ya kuke zama a gidan auren? Wannan ai sai kusa mutum hawan jini,

Mama tace Alim ka kiyayeni na fada maka,Kanwar Abban su Alim ce tazo tace Mama yaranan ina kallon gangancin da sukeyi da Mota a titi zasu je dinner suna ta fada ta windon Mota,mutane suka saki Salati,kunya Amana taji ta mike ta bar palon,Alim ma haka,mutanen wajen suka ce wannan matar tasa yar nema ce naga a tsaye take itama,amma Alim da miskili ne ta koya masa sun zama daya,wasu sukace wannan Yara da kuruciya suke abin dariya,fadan nasu duk ba fada bane.

Amana suna waje a zaune da mata da Maza kawaye da angwaye ana ta hira,Alim shi da wani frnd dinsa suka zo wajen kusa da Amana Alim ya zauna cikin hira Alim yace ai shi yasa akace mata duk sunfi yawa a wuta,Amana tana ji tasan da ita yake zaraf cikin dagewa da masifa tace ai wlh wannan karan sai dai ayi kunnen doki Maza rabi mata rabi,Mazan gasu nan duk azzalumai,

Alim a fusace yace kinji nayi magana dake zancen mu mukeyi zaki sa min baki,Amana ta shareshi,Alim ya kara cewa ai idan mace ta isheka to ka karo aure,Amana tace wace zata

zauna da kai da baka san komai yanda duniya take ciki ba,duk mutane wajen shuru sukayi ana jin fadan su Alim,Alim yace dadin abin dai Aljannarku na kasan kafafunmu,Amana tace idan mun zo shiga ku take,ke da ke nake wai? Alim ya mike tare da Barin wajen yana masifa

9pm aka fara shirye shiryen tafiya dinner,Hamza ma duk sunzo kuma sun karbi motar hannun Amana suna kai kawaye,Amana data shirya ta fito cikin shiga ta gaske,ba kowa a tsakar gida duk an gama tafiya sai kakar su Alim kawai ta fito zasu tafi da Alim tana ta tsokanar Amana,Alim ya fito fes cikin rantsatsiyar shiga,kaka taja Amana wai dole su tafi tare,Amana taki yarda Amma kaka ta matsa mata,dole ta bude gidan baya a motar Alim ta shi ga ba walwala,Alim ma fuska ba rahma,ya zauna gefen kaka,Asiya ta fito ta shige gaban Mota,

Bai ce komai ba driver yaja Mota kamar abin arziki sun danyi nisa da tafiya, Alim da Amana sunsa Kaka a gefe karshen mota Amana a tsakiya Alim a gefenta

Alim ya leko da kansa ya kurawa Amana ido,dagowa tayi suka hada ido aí kuwa ya mata gwalo itama ta rama,

Bayan minti daya yace Anjima idan mun dawo zamuyi magana ta fahimta yayi zancen ne ba wasa da gaske,Amana tabe baki tayi tana so tace bata da lokacinsa Amma kuma Kaka na wajen da Asiya,kawai sai tace ba time,

Pls kinji?tayi banza dashi kamar bata ji ba,yace am talking to u fa,tayi banza dashi,

Nan ya zuro hannu tare da latsa cikinta ina abina?

Amana ta kwadawa Alim duka a hannun,Kaka tace yau naga fitsararre,Dariya Alim yayi ya Mika hannu again Kaka ta bige hannun,Amana ya kara rukowa hannu pls ki bani time,Amana ta rike hannun Alim ta garza masa cizo sai suka fara kokawa da hannaye, Kaka na kallonsu suna ta yakushe ya kushe,Alim ya kara tafkawa Amana mintsini,tana haki da Hawaye tare da cewa ka mintsinen?

gyara zama tayi suka fara kokawa sosai,garin fada suka tugewa Kaka dankwali Kaka tana mene haka ku bari Ify?saboda taga Amana harda kuka,Alim kuwa yi yakeyi Amma dariya ta cika masa ciki yanda Amana ta zage,Kaka ta daura dankwalinta,Amana tace Kaka kiyi hakuri kinga dai laifinsa ne ko,Kaka kuwa manne kanta tayi a jikin kujera tana gefe suna ta faman yi,Amana tace kai kai kai kai dannamin kashin wuya uhmm....zaka gani Amana ta Yakushi Alim ta cijeshi yayi kara da karfi,Kaka ta matsa sosai gefe suna ta yi,ganin haka kaka ta rabasu a tsakiya ta zauna a tsakiyarsu wai ta shiga tsakani, sai gashi sun tsallake kaka Alim ta gaban kaka ya zuro hannunsa sai ya taba cikin Amana,Ita kuma taki yarda shine suke ta faman kokawa,

Amana ta rike hannun Alim kamar kunama sai fasa masa cizo takeyi yana ta kwalla kara,Kaka tace yawwa jikata yi maganinsa,

Alim ya karbe hannunsa da kyar yasa dayan ya cirewa Amana gogoron da tasha wahalar sakawa ya ja gashinta da karfi,tayi kara Kaka ta sa hannu biyu tare da Dukan Alim ka haba ka bar yarinya ta sake,Driver da Asiya dariya kawai sukeyi saboda kowa ya kalli abin yasan ba fada sukeyi ba,

Amana tace nafi karfinka ko banza na cijeka da yawa kaifa me ka iya yimin ta karasa tana

hakki kamar tayi tsere.
Alim ganin Kaka ce shi yasa baya Jin kunyarsa

Alim yace sai na ballaki kika kara yi min magana,Amana tace na gaba yayi gaba na baya sai labari,gobe i yanzu na tafi gida ina zaka ganni kuma kafin na tafi sai na tabbatar dana yi maganinka.

Ina ma da ne yaro da kagane shayi ruwane,Alim yace kanki ake ji,
Har aka je cece kuce akeyi,amma Kaka tasan da wata a kasa idan sun koma gida zata hadasu taji me laifi acikinsu,

Amana da Alim ba wanda ya kula wani har akayi party suka dawo gida,Kaka tace kuzo muje dakina zanji dalilin wannan shirmen da kukeyi a matsayin fada.

Suna dakin Kaka zaune a kasa Kaka tana saman Bed tace ke fada min jikata mene matsalar ke da mijinki? Amana tace ki tambayeshi,Alim yace ke dai ki fada,k a fada dai kai da akayiwa laifi,Alim yace in zakiyi bayani kiyi,bazanyi ba nan suka fara cacar baki,ita Amana mamakin Alim takeyi har yaushe yake da baki haka yanzu,

Alim ne ya gyara zama tun farkon haduwarsu da Amana da halin Mum da abinda Sulemanu yayi musu da sanadin rabuwarsu duk Alim ya kwashe ya fadawa Kaka yace Amma kaka sirri pls kinji iya mu dake,Kaka tace kaine da laifi baka kyauta ba,kasan da halin Mum Dinka dana Saude amma ka zargi matarka ba tunani ba komai,kayi kuruciya Alim ga matarka ta gari,kuma yanzu gashi kasan kayi laifi ba bincike ba komai maimakon ka fara bata hakuri da lallashi sai ka dinga fada da tsokana da yakushi,

Ke kuma jikata nasan yayi laifi bai kyauta ba kiyi hakuri ki dauka kaddarace,nan Kaka tayi musu nasiha sosai tayi musu fada sannan tace kar na kara ji da gani ya wuce daga yau,Amana a ranta tace tab yaci banza ma kenan wlh Bai isa ba,a fili Amana tace ya wuce Kaka insha'allah bazai kara faduwa ba,

Alim wani sanyi yaji da dadi a ransa marar misaltuwa,Amana ma taji dadi da sanyi sosai zuciyarta wasai saboda Alim baya zarginta yayi tunani ya San ta gari ce ita,

Alim ne ya kalleta tare da cewa Kaka kice ta biyani cikina,Kunne kaka ta toshe tace kai ban son shashanci,to wlh ta fadi inda ta kaimin ciki cewar Alim,Amana tace ciki ya zube ka auri wata ta haifarma ta Mike tare da ficewa,Kaka tace sai kayi aiki da lallashi fa,
Kaka yarinyar nan taurin kai gareta,nasan baza ta taba kulani ba shi yasa kika ga ina tsokanarta da fada,nasan tana da saurin zuciya shi yasa nake mata abinda zatayi magana in ba haka ba nine zan Sha wahala,
Koma me ta maka kai ka jawo ba tunani ba komai ka yanke hukunci cikin fushi,Kaka kishine wlh da shedan amma nasan Amana ba yar iska bace a virgin na samu abata cikin kwali a like,kaka tace tashi ka tafi marar kunya,

Fita Alim yayi tare da tunanin ta yanda zai bullowa Amana ta hakura,washe gari da rana Mum Alim ta sauka tana gadara da takama,

Amana ce ta shigo palon Mama tana neman Aabid,
Mum Alim ta gani zaune tana latsa waya,har gabanta Amana taje tare da tsugunawa har kasa ta gaisheta cikin ladabi,Ify kawai tace ta dauke kanta cike da mamaki dama jarabar yarinyar nan tana makale da Alim lallai aiki Bai kare ba,dole ta aikata lahira kowa ya huta.

Amana dama tasan abinda Mum zata mata kenan kawai sai ta Mike,Alim ta gani a bayanta ya harde hannaye yana ta murmushin Jin dadi an girmama uwarsa.

Ta gefen sa Amana zata wuce ya rukota tare da hadata da jikinta,wani so da shauki hade da shock sukaji gaba dayansu,Amana Hawaye ya cika idonta Alim ya kai bakinsa a kunnenta tare da cewa am so sorry ki yafe min kinji,missed u kwace jikinta tayi tare da ficewa daga dakin,Mum ta kalleshi tace kayi asarar halinka jibi yanda take tureka kana manne mata,Alim ficewarsa yayi baice komai ba,

Amana kuwa room ta koma tana share hawaye sosai ga wani sabon son Alim da yake azalzalarta,
Alim ma kasa Zama yayi ya rasa inda zaisa kansa matarsa yake so,kuma taki hakura
A ranar duk yanda Alim yaso suyi magana da Amana abin yaci tura,sam Amana taki ma yasan inda take,
Last party ma da zata je babu yanda baiyi ba ta kulashi ko ta saurareshi suyi magana ta kirki amma taki yarda
Duk hanyar dayabi ta tosheta, kukane kawai Alim baiyi ba,
Haka aka gama biki sannan suka dawo garinsu har Amare washe gari aka daura Aure tare da kai Amare abinsu shar komai yayi a gidansu.

Amana ta dawo gida washe gari da safe wanka tayi ta shirya tare da komawa baccin gajiya,Alim yazo gidan gaba daya sai da yabi dangin Amana da iyayenta wai su bata hakuri ta saurareshi,su kuwa kaf Alim nasu ne musamman yanda yake kyautata musu ba musu suka kwantar masa da hankali harsu Umma.

Gaba daya manya da yara tare da iyaye suka dungumo dakin Amana tana bacci suka tasheta,Amana gabanta ya fadi da ta gansu gaba daya,nan fa suka zauna zasu fara magana.

AsmaBaffa

Happy sallah to u all
✳CIRANIN AMANA ✳

175-180

Official

By
AsmaBaffa

Maza da mata iyaye harda yara ne suka sa Amana a tsakiya suka fara caccake ta, me fada nayi me masifa nayi me nasiha nayi da masu lallashinta yan yara kenan,
Amana tana jinsu a ranta tace lallai Alim ya gama siye dangina da kudi amma ai nafi sonsa daku ina son abina kuma nafi Ku farin cikin dawowar mijina wajena,a fili kuwa sai Amana ta fashe musu da kuka, Gwaggo ta hangame baki tace yau naji shashashar yarinya ana nema miki gata kina shirme, Umma ta hayayyako yo dan ubanta ma laifinsane ki duba sharrin da aka kulla miki har yau gaskiyar abin Bai fito ba amma ya dawo wajenki a haka zai mai dake amma kin tsaya shirme,

Hamza yace akwai me kaunarta irin wannan bawan Allah idan wani ne a take a wajen zai sakeki,yana da kudi ga mata nan ke kadai ce mace,
Kb ya fara ai ni wlh tana kin komawa wata rangadediya zan Nemo masa ya aura,Amana ce ta dago tare da gallawa Kb harara,Isa yace ga kannenta da yawa ai ya halarta ya rabu da ya mu bashi kanwa, Amana ta sigar wasa ta daki Isa a kirji,Haladu yace munafunfun ana so ana kaiwa kasuwa wai ke jan aji ko?

Wayar Hamza ce ta dau ruri Badriyya ce ta kira tana fada masa yanda Alim ke kiranta a waya ita da Sakeena akan su tayashi lallashin Amana.
Umma ce tace duk kuyi shuru zan yanke hukunci yanzu Amana dolene ki koma wajen mijinki jibi nace ya dawo jibi ya tafi dake kuma Umarni ne na baki a matsayina na mahaifiyarki,yanzu ma yana palo ki tashi ki shirya kije ko yanzu na turoshi nan,
Amana kamar zatayi kuka tace haba Umma wai mene haka.
Gwaggo tace kai kuzo mu fita karki koma idan kinga dama,mazan ma sai da suka tsaya tare da yiwa Amana nasiha sosai sannan suka fita,

Suna fita Amana ta Mike tsaye tare da daka tsalle ta fada kan Bed ta jawo pilo ta kanka me tana ta dariyar Jin dadi tare da furta Alhmdllh,ta kara mikewa tsaye ta daka tsalle tare da furta jibi sai lagos ko da kafar katako ne Allah kaimu,towel ta daura ta fada toilet,

Umma kuwa ganin Amana shuru taki fitowa taje wajen Alim kawai sai ta sa Kb ya rakoshi har dakin Amana,daga bakin kofa Kb ya juya,Alim daya shiga ciki karar ruwa yaji a toilet yasan itace take wanka,jikin kofar toilet din ya karasa tare da cewa na shigo? Amana tana jin muryarsa tace ya salam kai Umma,ji tayi ya kara magana nazo muyi wankan?Amana tayi banza dashi da wasa ya murda handle Amana cikin fada tayi magana basai ka shigo ba pls.
Murmushi Alim yayi tare da komawa kan bed ya kwanta yana shakar kamshin Amana.

Tana sani taki fitowa daga wankan ya dade yana jiranta har bacci ya daukeshi sosai sannan ta fito, saida ta leka fuskar sa taga bacci yakeyi sosai,ta fara kare masa kallo sanye yake cikin farar shadda dinkin Maza fitted domin Maza ma yanzu dai dai su suke dinki sai ya dan damesu,
Harda sa hula domin shi ba sosai yake sa hula ba Amma yau harda hula dai dai shi ya wani coko ta gaban goshi sawar yan gayu na zamani duk gashinsa me uban yawa gasu nan waje,yayi kyau sosai komai fari dama shi akwai sa farin kaya,

Murmushi tayi a fili tace dan duniya kenan harda bacci a hankali ta cire masa hular tare da ajiyeta gefe,kafarsa ta kalla duk rabi a kasa karfinta tasa a hankali gudun kar ya tashi ta gyara masa kwanciyar saida ta hau dashi bed din sosai,Amana da karfinta to, Amma duk da haka tasha wahala dama tasan Alim din nata idan ya fara bacci to sai ka saceshi bai farka ba,

A nutse ta shirya tsab cikin riga da skert na material black tayi kyau matuka nan ta fara Barin turaruka a jikinta harga Allah a zuciyarta dan Alim tayi kwalliyar Amma a fili wai sai tace badan shi nayi ba dama nayi niyyar kwalliyata,idan zuciyarta ta tabbatar mata dan Alim tayi sai ta karyata,tunani Amana tayi ta shiga kitchen ta dafa masa abinci amma kuma idan ta shiga kitchen kwalliyarta zata baci duk da cewar da Gas suke amfani amma ai aiki zaisa kwalliyar ta lalace tun Alim bai gani ba,

Fasa shiga kitchen tayi tace idan ya tashi na hada masa,wata zuciyar tace idan yaki tashi da wuri fa har sai kwalliyar ta baje,tace kai bari na tasheshi na masa wayo ya gani sai ya koma baccinsa,

Toilet ta shiga tare da ebo ruwa a hannunta ta yarfa masa a fuska zumbur ya bude ido tare da mikewa ya zauna,
Kallon Amana yayi gaba daya kwalliyar Amana ta tafi da hankalin sa sai kallonta yakeyi bai ce komai ba,
Amana ta kara tamke fuska irin ba wasa ta kara gyarawa tayi tsaiwar daukan hoto ta gama Zuko da matso kyau tare da kallon saitin Alim,tunowa tayi baiga bayanta ba sai ta juya tare da kallon mudubi tana neman wani abu a kan Mirror dan Alim ya ga bayan,Alim kuwa ai tuni ta gama kashe masa jiki da kwalliyarta sha'awarta ce ta taso masa,

Sai da ta tabbatar ya kalli bayan ma sannan ta juyo tare da tamke fuska ta furta malam lafiya ka sani a gaba,nayi maka kara,na maka tauna,nayi maka hadiya ina jira naji me kazo yi a gidanmu harda shigo min daki ka kama bacci?

Shuru Alim yayi baice komai ba,Amana ta kara magana jibeka simi simi kamar mutumin kwarai,Alim dai baice komai ba,Amana tayi mamaki shi da yake tsokanarta ma,

Alim a hankali ya furta am so sorry abinda na miki kiyi hakuri kinji,Amana wani tausayinsa taji kamar tace ta hakura amma sai ta daure tace ka daina bani hakuri haka ya isheni me zaka ce Dani yanzu na yarda,kai harni zaka Zarga,da masifa Alim yace taya bazan zargekiba ko kece kika shigo kika sameni wata tayi min haka exactly abinda na gani ya zakiyi? Dole ki shiga kokonto,ni waye da bazanyi laifi ba?Sufi neni?dan Adam ajizine Kuma na fada miki na baki hakuri uncountable ya kikeso nayi kashe kaina zanyi?na biki na biki ok to zo ki cinyeni ko ki yankani,ko sati biyu bamuyi ba da rabuwa sai da na nemeki,ranar da Baba ya rasu zuwana nawa?ance miki da bana sonki zanzo inda gidanku yake ne?abinda yasa ban ce a kira min ke ba nasan kina cikin wani Hali kuma banson ganin damuwarki tunda Baba ya rasu,ki tambaya zuwana nawa gidanku bakya garin nan,kafin ma ki tafi Adamawa, ni fa ko a waya kin nemeni? Ko text kin taba yi min na tunanin wanke kanki ko kimin bayani ko kiji halin da nake ciki,ko namiji shine marar aji?shi ba mutun bane? Gidanku nazo ki fada min abinda kika ga dama kuma dole ki koma gidana yarinya amma kisan me zaki fada min banson raini ya karashe fadan da kinyi kyau dai badon halinki ba,

Amana dake tsaye sannan ta fara nata itama ka dakeni ka hanani kuka,daga yin abu Baka tsaya ka saurareni ba kayi tafiyarka,harda zazzagina kuji sharrin Amana,

Alim yace kiji tsoron Allah yaushe na zageki?Amana ta gwada muryar Alim tace haka fa kace ke din banza ni nafi karfinki talaka,wawiya,doluwa,bahuwa,kuchaka kuma saina ballaki idan na kara ganinki sai na karya miki wuya,

Salati Alim ya saki sannan yace kiji tsoron Allah,Amana ta kara hade rai tana Hawaye Alim yace to mene na Kukan kuma?,Amana tace ai kaci mutuncina da yawa dole idan na tuna nayi kuka,Alim dai sharrin Amana ya isheshi yace to yi hakuri kinji.

Ni Bazan hakura ba yanzu cewar Amana,Alim yace to sai yaushe? yayi maganar cikin sigar lallashi,Amana tace sai an gano wanda ya kulla min sharri,tsaki Alim yaja ke ban son shirme fa dole ki hakura kinji na fada miki, Bazan hakura ba to dolene,mikewa Alim yayi tare da furta bari na mike kika tsawona,tunkarota yayi sosai da gudu ta fice tare da cewa ka jira na sanmaka abinci amma ban hakura ba

Kwanciya Alim yayi bacci ya kara dauke shi,ya dinga yi har Amana ta gama hada masa jullop din taliya tasha hadi sosai,tana zuwa ta ciji yatsansa ya tashi firgit tare da rike wajen,

Kallonta yayi kana yace bashi kike ci,

Toilet din ya shiga tare da dauro Alwala sannan ya zauna yace to zuba min abincin tace ka zuba da kanka mana ai ban hakura ba bare na fara yima hidima,kyaleta yayi ya zuba abinsa tare da hada tea yaci yasha,

Amana ta kalleshi tace kwadayi anzo ana cinye mana shinkafarmu da taliya bai san sanda dariya ta kamashi ba sosai,Alim yace yimin kudi na biya mana,banza ta masa tana danna wayarta yace me kikeyi a waya Ba tare da ta dago ba tace Charting,idan da namiji ne wanda ba muharraminki bane bada yawu na ba, tashi ka tafi gidanku gaskiya ka takura min, basai kin koreni ba ya furta tare da mikewa tsaye

Kudi ya zaro Bundle biyu na yan dari biyar biyar yace dauki daya kallon kudin tayi dama bata da ko sisi sun kare a biki,hannu tasa ta kwace duka bundle biyun duka nake so kuma ka biyani kudin da ci da kaina da nayi yunda da aurena a kanka ka barni nasha wahala kasan hakkinka ne ka biyani duk kudin dana kashe,kudin sabulu da omo,kamo hannunta Alim yayi suka zauna gefen bed sannan yana murmushi yace sai ki fada min dalilin kenan na fushinki tuntuni na biyaki ashe da dalili to fada min komai na biya,Amana sai yanzu tayi dariya sannan tace dan kadan ne ma fa,banda wannan kudin da ka bani saboda wannan kyauta ka min,Alim yace ina Jinki,Amana ta gyara zama tace kudin Kukan  dana sha da wahalar da ka bani na bacin rai,Alim yace daya,tace kudin ci da kai,kudin rainon ciki kafin ya zube,kudin kayan kwalliya dana siya nayi amfani dasu baka nan,kudin zirga zirga ta zuwa unguwa kasan dole zan kashe kudin Mota, sauran na yafe maka basai ka biya ba,

Dariya Alim yayi cikin jin dadi yace to ki jira zaki ga Alert ya mike zai tafi,Amana tace na manta kudin mintsini da Yakushi,sai kudin gyaran jiki kafin na bika mu koma lagos.

jagira (eye liner) baka da ja sun kare ka siyo,ko kuma kaga fuska ba kwalliya, jambakina sun zama tsohon yayi a siyo wasu, sannan sai ka sake min lefe zan koma kuma duk ka bayar dinki a dinka da kana nan kaya ka bani 2wks sannan kazo mu tafi,Alim yace an gama indai zaki koma ai shike nan,Amana tace kuma ka Aiko min da Mota ko na dinga hawa mashin dan acaba kasan kauye har yau ana hawa machine cinyata ta gogi ta dan achaba ba ruwana ni,

To karki hau dan Allah Huzaifa zai kawo miki Mota,Amana tace kuma aikin hajji da za aje bana sai ka biya min na sauke farali,Alim yace wannan me sauki ne, yawwa nima nasan me kudine mijina Amma kazo sai cutata kakeyi kana jin dadinka kai kadai cewar Amana
dariya Alim yayi sosai yace to zamuje,

Amana tace na karasa yafe maka sauran laifinka to,dariya Alim yayi sosai sannan ya jawo Amana jikinsa tare da rungumeta kam kam,

Baby so kike ki karar min da kudi ko?,Amana cikin shagwaba tace me teku tasan anyi dan an ebeta da cokali? Murmushi yayi tare da yi mata rada Baby danyi min kiss kinji,Amana tace naki din Ai dane muka dafawa jaka shayi ,Alim yana sheka dariya yace ina kika samo karin magana haka ni ban taba ji ba,

Amana tace ae mana kalli dai jaka wato donkey Amma a dafa mata shayi ai an bata dadi kuma gatan yayi yawa shine nima nace ai dane muka dafawa jaka shayi,

Murmushi Alim yayi tare da furta i love Amanata tare da kankameta i missed u,a hankali Alim ya hade bakinsu waje daya yana faman tsotsa kudin dake hannun Amana ta watsar daga hannunta tare da kara kankame mijinta,sosai suka shiga mirzar juna kamar zasu cinye kansu, kan bed suka fada Alim ya shiga zare mata kayan jikinta one by one,da kyar Amana tace ka bari na koma lagos dan Allah,Alim yace ina so ni dai ki kyaleni,zan fasa yin hakurin to naki yafe ma cewar Amana,Alim yace bakya tausayina dama na sani,to ka bari mana na kara warkewa

har yaushe nayi Barin cikin ma da za ka kara min wani,ka bari idan na koma lagos sai kayi,na hakura to ai tunda bakya so nasan ko bari naji dadi Baza kiyi ba Allah kaimu ki koma zaki fada,

Gyara kayansa yayi itama ya mayar mata da zip dinta sannan ya mike tace to karka manta da motar kuma kudin gyaran jiki kwandalata Baza tayi ciwon kai ba don bani nace ka koreni daga gidanka ba sannan lefe Sabo in ba haka ba bazan ma kwalliya da masu kyau ba ehe,

Alim yayi murmushi tare da cewa Amma a Adamawa kika koyo rashin Imani ko?haushi ka bani da har ka iya zargina shi yasa Sabo da na huce zan ci ma kudi nima,zance kayi aka baka ni?a sadaka ka aureni tsabar gata ranar da aka daura aure ranar na bika muka tafi ba wani tarzoma,

Alim yace to naji fadi kudin gyaran jikin Amana tace salon na fadi kadan saboda da zan iya tausaya maka,kawai ka bayar da abinda kaga dama,au na tuna ribbom dina ma suna bukatar canji,

Check Alim ya zaro tare da rubuta mata check na million biyar ya Mika mata karba Amana tayi ta duba,sannan tace laaaa ashe da gaske kake zaka bani,ungo abinka ni wasa nake maka to,
Alim yace bazai karba ba,Hh dama tsokanarka nakeyi ai sai dai nace Allah kara budi ubangiji ya biya ma bukatunka nan gaba ka bani 20million kace Amanata gashi a siyawa Yara a Icecream, murmushi sukayi gaba dayansu,har Mota ta rakashi ya tafi cike da jin dadin samun nasara.

Tun daga ranar Amana gyaran jiki takeyi kawai da sauran shirye shirye sai zumudi da jindadi takeyi,bangaren ogan ma haka yana can sai da ya canja komai na gidansa,kayan sawa kuwa na Amana da Rabin nasa duk ya bayar dasu ya canja mata sababbi kamar sabuwar Amarya,Yanda Mum taga Alim ya wani rude gaba daya kullum cikin farin ciki yake har yayi kiba ya kara fresh ta zata sabon aure zaiyi har murna takeyi ta zata Zainab din da ta bashi ya aura ita zai kawo,Abba da sauran yan uwansa duk sun san Amana ce zata dawo,

Asiya ma Abba ya tsai da ranar bikinsu ita da Ahmad yayan Huzaifa,murna wajensu ba a magana,Mum kuwa bata murna dan kawai Abba yafi karfinta ne,

Bangaren Amare su Badriyya ana can ana cin soyayya da angwayensu,
Sati biyu kenan yaune Alim yawa Amana waya ta shirya gobe zasu tafi,
Amana sai murna akeyi a boye, Umma tace Allah yasa dai uwar miji ta barki lafiya,kar kiji komai Umma kawai addua ce taku,
Musamman Amana ta figi mota taje lalle tare da tsantsaro saloon,dama tuni Huzaifa ya kawo mata motar hawa a cikin nasa ya bata daya Sabo da Alim ne ya bashi Umarni ya kai mata.

Amana ta kashe kudi sosai haka su gwaggo dasu Umma duk sunyi mata nasu suma,
Washe gari da sassafe sai ga Alim Sabo da tsabar zumudi,Amana lokacin ma ko bacci bata

tashi ba,bayan sun gaisa da mutan gida,Umma tace shiga tana ciki,harda ledar take away a hannunsa,yana shigewa Umma tace gwaggo yau naga rashin kunya zumudin yayi yawa kamar wata Amarya.

Gwaggo tace kema kya fada wannan uban sammako haka ko kasar waje zaije ai sai haka,kamar zai tashi sama kai irin Sulemanu harka suna da yawa a kasar nan cewar Inna dayar kishiyar, Amana tana cikin bacci tajita a sama an daga tare da direta a kasa,da kyar ta bude ido tana kallon yanda yayi mugun kyau,

Kije pls kiyi wanka ba kallona zakiyi ba sauri zamuyi muje gida,flight zan canja mana Baza mubi na 5pm ba yayi dare da yawa,

to naji ka zauna banfa ci komai ba ma,to nidin naci ne? kiyi sauri dan Allah mu tafi gida, janta yayi har toilet ya Suri brush tare da zaunarta a wata kujera tana layin bacci idonta a rufe yace bude bakin mana ai kuwa ta bude yayi ta yi mata brush a hankali ya gama,

Ki bude idonki mana haka sai wani bacci kike,a hankali Amana tace zaka bata kayanka da ruwa fa,kamota yayi suka fito taki bude idonta wai bacci takeyi ita,fresh milk ya dura mata a bakin tare da bata chips da egg,ina ka samo abinci?da abina nazo nasan zaki bata min lokacine,haka ya dinga tura mata tana cinyewa shima yaci,suna gamawa yace wanka je ki shirya ko na miki,kuma ki bude idon haka mana kiyi sauri,

Wanka ta shiga tayi sannan ta fito tana goge jikinta,ta fara sha mai duk jikinta,tazo kafafu Alim ya fisge man kamar wani engine ya karasa shafa mata,kayan ta dauko ya kwace ya dauko pant yace to dafani kisa, Amana ta dafa shi ya sa mata da towel dinta a daure,

Cire towel din asa bra,haba a'a ni dai ka sa min akan towel din sai na zame towel din haka akeyi,kamota yayi yanda tace haka ya sa mata ita kuma ta zame towel din ta gyara sosai ta kara daura abinta,

Rigar tasa fitted Gown readymade Brown color,tasha kyau ta shirya ta dauko hand bag da katuwar akwatinta na abubuwan da take bukata duk shirye ciki,wanda zata bayar ta bayar dasu,sai wata katuwar Ghana must go na tarkacen kayan gyaran jiki da wasu abun,

Wannan kayanfa?Amana tace nidai kawai a samun a mota dasu zan tafi kuma dole ka dauka,

Alim yace Bazan iya daukan Ghana must go ba wlh tayi local bari muje cikin kano sai a canja wata kalar,Amana tace yanda kaga yafima saukin dauka nidai ga mijina bazan dauki kaya ba,Dariya Alim yayi sarkin son girma,

Yaran gidan ne suka sa kayan a Booth Amana ko kuka da canja fuska babu tayi musu sallama tare da cewa sai munyi waya,duk abunda ya faru a dinga fada min ta waya,

Na tafi a mana addua,

Har mota suka rakata sannan ta Mika musu hannu daya bayan daya suna gaisuwar sallama.

Alim kuwa kudi ya basu masu yawa suna ta godiya driver yaja mota Amana da mijinta suna bayan mota,

Suna zuwa kano ya canja wata tsantsareriyar jaka ya cire Ghana must go ya jefar suka je gidan Badriyya da Sakeena suka musu sallama har gidan Abban Huzaifa sunje sannan suka wuce airport sai gasu a jirgi sai lagos......

AsmaBaffa

Love u all
✳CIRANIN AMANA✳

180-185

Official

By
AsmaBaffa

Kuji dadinku readers ina godiya.

Tun a jirgi Alim ya fara mutsu mutsu yana takurawa Amana,ta kasa kafarsa yasa yana faman gogata a kan ta Amana,
Amana ce ta juyo tare da kafeshi da ido tana aika masa da wani kallo mai tokare zuciya,

Shima ogan nata ba a barshi a baya ba wajen aika nasa,
Kwanto da Amana yayi a jikinsa sannan ya fara magana ko dai baki hakura ba baby?
a hankali ta furta me ka gani? Naga sai wani shareni kikeyi,to bakuwa ce ni yaushe na saba da kai da har zan saki jiki,ban ganeba duk zaman da mukayi zakice wani bamu saba ba,
to wai ni shike nan baza ka barni na huta ba,da ban sanki da mita da korafi ba amma yanzu ko rainani kikayi ban sani ba,y a za ayi na rainaka ya Alim,gashi nan kinyi ma yanzu wai Alim ma ba ko Dear,honey etc kawai Alim.

To kayi hakuri na daina,suna haka jirginsu ya sauka suna fitowa taga motocin Alim masu matukar kyau da bata san dasu ba,suka shiga sai gidan Alim,masu kwasar gaisuwa saiyi sukeyi har suka shige part dinsu,
Duk inda suka shiga sai Alim yasa key ya garkame ko ina,
Har bedroom dinsa ya kai Amana
Mamakin Amana yanda komai na gidan aka canja Sabo kamar ma ba gidan ba ya kara haduwa sosai.

To kije kiyi wanka mana mu kwanta ni na gaji bacci nakeji, kallonsa Amana tayi da mamaki yanzu fa 2pm tayi ma kawai sai mu kwanta ko abinci banyi mana ba,nayi order za a dinga kawowa kullum har na tsawon 1wk Baza kiyi girki ba hutawa kawai zamuyi,baccinmu zamu dinga yi kawai,
Baki bude Amana take kallonsa,Allah ni ba haka nasanka ba ka canja sosai sai kace Ayu,

Murmushi Alim ya saki me rikita tunanin mace daga bisani yace Amarya ce fa dole nayi doki dama ai bana gajiya dake kece dai kika fara koyar rowa.
Janta yayi har toilet tare da turata ciki kiyi wanka,dayan bed room din ya shige wanka shima yayi da Alwala,sannan yazo sukayi sallah Azahar, abinci ya jawo kaji da sauran kayan ci da sha,da kansa yake tura mata abincin sosai ba jira,har ta koshi ta mike tare da yin Brush ta fito ta koma dayan bedroom din ta kara shafa turaruka a jikinta tare dasa rigar baccinta tana gama Alim ya shigo ta baya ya zura hannu tare da hugging dinta,
A tare suka saki ajiyar zuciya,

Daukanta yayi cak har bedroom dinsa,kowanne ya kwanta a pillow sa sun kurawa juna ido ko wanne son dan uwansa na azalzalarsa,
Wani kallo tare da fari Amana ta sakarwa Alim,abin ba a magana wajen Alim tuni ya fara tafiya,Amana ce ta matso tare da komawa jikinsa ta lafe ta rungumeshi sosai,
Kiss ya manna mata a goshi,ta dago a hankali tare da aika masa da kallo ta manna masa kiss a lips tare da cewa na rama nima ai nafi ka,ni nawa a lips nama,murmushi Alim ya saki zai jawota ta koma kan pillow dinta,Alim a hankali kamar me rada yace warm night nace miki fa zamuyi,wanne warm night?warm afternoon dai cewar Amana ta furta tare da dawowa kan pillow sa ta kwanta Rabin jikinta a Nasa,Alim na kallon sama,
Amana shafa kirjinsa ta fara a hankali tare da masa magana cikin rada tana wani lumshe ido,shima Alim idonsa lumshe ya furta Honey zaki kasheni fa,
Botin din rigar Alim ta balle masa in a romantic way ta fara shafa kirjinsa tare da zura

harshenta a kunnensa,tana yi masa Zane da yatsa daya a kirji, Alim ya kusa suma ba shiri ya furta zan mutu Baby,

Murmushi Amana tayi tace to shike nan karka mutu ok,na daina ta furta tare da komawa pillow ta,

Cikin zafin nama a gigice a rude xuruf Alim ya koma saman Amana Bazan iya dauka ba nan ya hade hannaye su tare da fara kissing dinta ba ji ba gani tana mayar masa da martani, sun gama fita daga tunaninsu Alim ya dago suka kara kafe juna da kallon so, sannan ya furta warm afternoon fa Babyna yana a samanta sai gani nayi ya jawo blanket wuf ya rufesu ciki,

Minti daya Amana ta zuro hannu waje zata fito tare da bude bargon kara damkota yayi ya rufesu,kara budewa tayi fakat zata fito suna ta faman haki ya kara maidata mene haka malama ya kara jan blanket da mugun sauri ya rufe,

Minti daya Amana ta zuro hannu daga bargo tare da jefo rigar Alim,sai ga hannun Alim ma ta bargon ya jefo yar fingilar rigar Amana,

Pant Alim ya kara jefowa da karfin tsiya ai kuwa ya fada kan Mirror dake dakin, Amana ta jefo boxers din Alim ba a san me sukeyi ciki ba, bargo ne kadai ke filfila motsi suna ta sukur sukur a ciki kamar mayu.

Sun dade har wurin 5pm suna ta abu daya,Amana ce ta yi magana engine ka bari haka mana a huta sai dare kuma har fa anyi sallah bamuyi ba,Alim da kyar ya furta 5mnt pls,tun yaushe kake ta cewa 5mnt,sorry daga dai wannan shike nan cewar Alim.

Shuru Amana ta masa yace to ki tayani mana,ai ya zama dole ba sai ka fada ba,nan suka kara rufe kansu cikin blanket suka ci gaba har wurin magrib sannan suka hakura,

Wanka sukayi tare da tsarkake kansu sannan sukayi sallah la'asar da magrib,

Sai kallon juna sukeyi suna faman murmushi,

Amana ce ta kalli mijinta suna hada ido ya daga mata Babban yatsa na jinjina,

Amana ma ta daga masa tare da cewa kai za ayiwa haka ai,

Engine baka gajiya ba Hutu,Alim yace me lafiya kenan ke kanki ai sai ni din domin kinfi karfin rago,

Fuska ta rufe da tafin hannu Alim ya gwada muryarta aje ayi sallah a huta Baby baka gajiya, dariya tayi sosai yanda ya gwada maganarta, ashe duk karyane da kuma anci gaba sai kiyi luf ki Bada tallafinki kema,

Naji to yunwa nakeji cewar Amana cikin shagwaba kamar zatayi kuka, Waya ya dauka ya kira sai ga Abinci an kawo,suka zauna sukaci sosai sun koshi,Alim yace muyi baccinmu Amana tasan ba bacci yake nufi ba,tace dan girman Allah kayi hakuri sai gobe harfa ciwo naji kadan,

Kiji tsoron Allah ni na miki wanka fa Amma ban gani ba,to wai kai Allah ni sai na huta,

To ke dince ai ta daban ce naji kinfi ko yaushe ma kullum ke kara dandano kikeyi,

Zo ki min labarin me ya faru da bama tare,fada min wanda ya miki kallon banza ma a titi yaci ubansa nasa a daureshi,

Amana harda kara narkewa da shagwaba,a palo suka zauna tana kwance a jikinsa suna kallo tana bashi labari shima ya bata nasa cikin shaukin so,
Yana tabe tabensa a jikinta yace am so sorry my love ban kyauta ba ko? Amana ta daga kai tana shagwaba tace ae baka kyauta min ba kuma nasha wahala,nayi ta kuka kuma,amma ya wuce tnx da ka dawo gareni da wuri.

Alim yace hmm kin san halin dana shiga kuwa ai Allah ya Isa tsakaninmu da wanda ya kulla wannan sharrin,na kusa mutuwa fa na gode da kika dawo gidana tnx for loving me,
A kunne ya rada mata muyi sallah mu kara cin abinci muyi kwanciyarmu,dariya Amana tayi domin tasan kwanciyar tasa,haka sukayi kuwa dole ta hakura suka kwanta again ya ja bargo suka dinga abu daya har tsakar dare sannan sukayi wanka suka kwanta manne da juna ko kaya babu a jikinsu suna cikin blanket suna ta faman musayar kalaman so har bacci ya kwashesu me dadin gaske,
Asuba kuwa sallah sukayi Amana zata fara azkhar Alim yace muyi Babban azkhar kinji ga dadi ga lada, murmushi ta saki tare da cewa to muddafa manniru muje ya zanyi.
Haka suka karashe safiyar nan har rana ta fito sannan sukayi bacci, yunwace ta tashesu,

Mum kuwa tana jira kawai taji me Alim yake shirin yi aure ko me,shuru bata Jin duriyarsa,gashi Aabid din ma yana wajenta baya zuwa ko ganinsa,gaba daya Alim din ya canja mata,baya wani saurararta gaisuwa ke hadasu kawai a matsayinta na mahaifiyarsa,
Shiryawa Mum tayi zataje gidan Alim taga ko lafiya yake sannan suyi maganar aurensa.
Su Amana suna Palo a zaune saman kujera Alim ya fito da dukiyar fulanin Amana ya dage mata Riga yana ta faman Sha da wasa dasu,baram sukaji an banko kofa da sauri Amana ta fada kasa tare da gyara rigarta,Mum tun daga waje ta tambayi yan aiki Alim na gida ai kuwa suka ce yana ciki shi da Madam,tunda suka ce haka ta gane Amanace Madam,
Shine ta banko musu kofa cikin Jin haushi,
Tana tabbatarwa Amana ce farin ciki taji tace kin kawo kanki yarinya,

Alim ta kalla tace gobe kuzo gida Ku sameni ina nemanku ta juya tare da ficewa tana huci,ko gaisuwar Amana bata Amsa ba,
Gaba daya daga Alim har Amana jikinsu yayi sanyi,haka dai Amana ta shiga lallashinsa tana kwantar masa da hankali,
Da taga yaki daina damuwa tuni ta janyeshi bedroom ta mantar dashi komai da salonta nan suka baje Harka,

Washe gari Amana ta shirya tsaf tace pls kaje ka shirya muje kiran da Mum ke mana kar tayi fushi,Alim yace baza muje ba,Amana tace dole muje tashi kawai Mum guda fa haba,nan ta fara lallashinsa har ya yarda ya fara shiri,yana gamawa suka shiga mota Amana ke driving Alim yana gefenta ya Dora kafa daya kan daya tare da kwantowa a jikinta yana wasa da kirjinta.

Suna shiga abin mamaki Mum ta tarbesu da fara'a sosai sunyi mamaki nan ta fada kitchen tare da kawowa Amana juice Alim kuma tace kai naga kafi Shan malt ga naka,
Alim yace Mum abinda tasha zan Sha ni,Mum tana dariya tace zan mareka son kasha naka

tasha nata haka suka Sha lemo,Mum na hararar Amana a wayence,

Bayan sun gama Mum ta fara musu nasiha kamar gaske tana cewa su hade Kansu su so junansu,sosai tayi musu nasiha,dadi da murna wajen Alim da Amana ba a magana,Aabid ma da gudu ya sakale momynsa Amana.

Mum tace ga danki nan Ku tafi da abinku na huta nima,

Har yamma lis su Amana suna wajen Mum,har su Asiya da auta ana ta hira da matar Nura,

Kowa yaji dadin wannan lamari,Mum ce taja Amana dakinta tace yata ga dan dabarunmu na mata ki tsaya ki shanye abinki nasan halin dana bazai barki ki huta ba,

Mum tana mikawa Amana ta bar dakin,Haka kawai Amana taji abinda Mum ta bata Bai kwanta mata ba,kadan ta dan kurba ta shiga toilet ta zubar da rabi ta bar rabi a robar tare da ajiyewa a kan mudubi ta fito daga dakin,

Tana fita Aabid ya shiga ya zata lemo ne ya fara Sha,yaji zaki kuwa ya Shanyeshi tas ya ajiye robar ya bar dakin,

Mum tana shigowa taga robar ta zata Amanace ta shanye sai murna takeyi,

Wajen magrib Alim yace su tashi su tafi gida,kawai yaga Amana ta rike ciki tana hawaye,

Yana haka sai ga Aabid dinsa ya fito yana Jan ciki a kwance bakinsa yana ta fito da wani yawu yana kuka,

Da gudu sukayi kansa har su Asiya,

Mum tuni ta fara zub da hawaye tana kan Aabid dinta.

Alim ya rasa yanda zaiyi ga Amana ma na murkususu,kwasarsu yayi sai asibiti,

Mum sai kuka ta tabbata Aabid yasha abinda ta bawa Amana,

Abban Alim da yan gidan duk sun wuce asibiti,

Ana ceton rai,Amana ita har ta samu sauki ta tashi,Aabid ne dai rai a hannun Allah,an tabbatar da guba suka ci,Amana ta fadawa Alim abinda Mum ta bata,

Alim harda Kuka yana labartawa Abbansa abinda Mum tayi da wanda duk Bai sani ba,

Ran Abba ya baci sosai yace kasan da haka ka kasa yi min bayani tun tuni.

Mum kuwa ba abinda take so a duniya sama da Aabid,bata taba son kowa kamarsa ba,sai ihu take tana na zalunci kaina,jika na wayyo,Haka Abba ya sameta tanayi,

Yana zuwa ya kife ta da mari har uku sannan ya mika mata takardar saki daya,tare da cewa kafin nan da kwana daya ki barmin gidana, karamin hukunci na miki saboda albarkacin yayanki da daureki zanyi,kuma wlh jikana ya mutu har Ethiopia zan sa a kamoki a yanke miki hukunci,

Kije duniyace Allah ya isa tsakanina dake,

Alim ko tausayin uwarsu basu ji ba,Amana kuwa a ranta dadi taji da farin ciki a fili kuwa sai nuna jimami take,gashi Aabid dinta yana Shan wahala.

Mum tana kuka ta koma gida tana hada kayanta,Alim da sauri ya bita gida,ya bata kudi,ya siya mata ticket,ya kaita har airport yana bata hakuri,Mum tace ka yafemin dana,na cuceka da

yawa,Alim da hawaye yace ba komai Mum komai zai dai daita bakimin komai ba kaddarata ce haka,ki yafe mana muma,zanzo very soon kuma Abba zai dawo dake,haka Alim ya lallasheta ta hau jirgi a lokacin ta tafi kasarsu.

Su kuwa su Auta,Asiya,Nura haushin Mum sukeji kuma ko kallonta basuyi ba sunji dadi ma da Abba ya mata haka,

Amana kuwa tana kankame da Aabid tana hawayen tausayi.

Alim a gigice yake yayi nan yayi nan ya rasa inda zaisa kansa,ganin haka yasa Amana mikewa ta koma wajensa tare da rungumeshi tana afaman kwantar masa da hankali

Tama manta da su Asiya a wajen.

Ana haka doctor ya duba yaga Aabid baya numfashi ya auna tare da dagowa cikin damuwa ya maida bedsheet ya lullube Aabid gaba daya,cikin jimami yace sai hakuri Allah ya karbi rayuwarsa.

Babu wanda Bai kuka ba,Alim kamar mace wurin kuka,ana ta lallashinsa

AsmaBaffa

Tnx readers ayi hakuri haka labarin yazo,

Ina jiran sharhinku.

✳CIRANIN AMANA✳

185-190

Official

By
AsmaBaffa

Duk wacce take min comment wannan page dinta ne,na gode kwarai da sharhi,da masu kirana a waya jinjina gareku musamman Zulaihat.

Kafin kace me frnds din Alim duk sunzo, da dangi da dama,har mutanen Kano suna hanyar zuwa lagos kowa cikin bakin ciki da takaici da masu hawaye‹

Amana kuwa ba a magana Aabid dinta da suke zuwa schl tare Allah sarki sai kuka takeyi sosai Alim din ne ke lallashinta,

Haka aka hada gawa aka sallaceta tare da kai Aabid makwancinsa gidan gaskiya, Allah kasa mu cika da imani kayi mana kyakyawan karshe ka bamu lafiya da Nisan kwana me amfani.dangin su Amana gaba daya sunzo gaisuwa kwana daya sukayi har Amare su Badriyya da Angwaye su Huzaifa

Kwana uku da rasuwar Aabid mutane suka watse sai Nura,Alim,Auta,Asiya da Amana sai matar Nura da Abba,sune kadai a gidan har akayi bakwai.

Abba yace sai an kamo Mum an yanke mata hukunci daidai da abinda ta aikata,Alim ne yace Abba ka kyaleta ko dan darajarmu dan Allah haka Alim yayi ta bawa Abba baki sannan ya hakura.

Nura ma sun koma gidansu,Alim da Amana ma sunyi shiri zasu koma nasu gidan, Asiya dan Auta sai Abba sune kadai a gidan.

Suna komawa Amana ta gyara part dinsu bangaren da yan aiki basa shiga‹ ko ina yadau kamshi da kyalli,miyar jajjage tayi sharp sharp tasha kifi,sai farar shinkafa‹ salat ta hada da kuma zobo me dadin gaske,

Wanka tayi ta dau wankan sugar da mini skert tare da wata Riga ko cibi bata kai ba,gashinta ta gyara tana kamshi tayi kyau Sosai abin ba a cewa komai,

Bedroom ta nufa Alim ta hango ya dawo daga masallaci sallar isha,shima yayi wanka sanye da farar jallabiya fitted, duk ya dan rame saboda rashin Aabid,Amana ma tama fi Alim ramewa.

Hango shi tayi a gefen bed yayi tagumi tare da kurawa waje daya Ido da Alama tunani yakeyi,

Har Amana ta zauna a gefensa Bai sani ba,hannu ta Dora a kafadarsa tare da rungumoshi jikinta kwantar da kansa tayi a cinyarta tana wasa da gashinsa tare da lallashinsa,abincin ta kwaso tare da jerasu a gabansa,

Zata bashi yace na koshi,
Me kaci yau ko break fa kadan kaci,bari ma ka gani dole kaci bazan barka da yunwa ba,komai na duniya ai hakuri akeyi,haaaa bude bakin,budewa yayi ta dinga bashi har ya koshi itama taci‹
Bayan sunyi brush shirin bacci sukayi Amana tace me kake shirin yi wai?

Alim ne ya kalleta tare da cewa kinyi kyau,bashi na tambayeka ba ni,hannu ya miko mata ta kama ya jawota kan Bed ta fada jikinsa, cikin maganar rada yace muyi bacci na gaji,kwace jikinta tayi tare da furta ka daina wani langwayewa Malam ka saki jiki sosai ka tattaro duka basirarka yau yau ka dage Allah ya taimaka kamin ciki,yau ba bacci sai an samo Baby Insha'allah, dariya Alim yayi ba shiri,tare da cewa indai wannan ne ai ko kuka nakeyi karewar bakin ciki to sai na yi ina kuka ina yi,

Dadi Amana taji tasa Alim dinta nishadi gashi har yayi dariya Rabon da taga dariyarsa tunda Aabid ya rasu,
Kankameshi tayi tare da cewa to ka fara mana,dariya Alim yayi sosai ke yanzu haka akeyi sai kace wata Tasalla ko Kande matar kauye,

Murmushi Amana tayi ta furta kai kuma Lado ba,fuskarsa ta tallafe da hannu biyu tare da fara kissing dinsa sosai,Alim tuni ya kawo danger hugging dinta yayi ya shiga nuna tasa kwarewar,
Amana sai narkewa takeyi cike da shagwaba,Mijin nata kuwa ya gama tafiya domin tuni ya zarewa Amana rigarta,
Rakarkashewa sukeyi kawai Amana ta gama tafiya tayi nisa,little Aabid kawai take kira,Alim yana jinta kamar yayi dariya to shima ta kansa yakeyi dan bazai iya ba abinda yakeji yafi karfinsa,
Amana harda zabga Kukan sweet yau,Alim kuwa kwalla ce ta shararo ta sweet sabo da Amanarsa ba sanya itama ba a barinta a baya.
Yau sun Sha shagali a daren.

Da safe ma suka kara na Good morning,
Sun samu kwanciyar hankali waral dasu abinsu sai nishadi sukeyi,
9am Alim yayi baki wasu frnds nasa suka zo musu gaisuwa.

Fita sukayi Alim zai rakasu su ga garin lagos kasancewar a London suke rayuwa wannan ne zuwansu Nigeria na farko kuma yau da yamma zasu koma,
Sunsha yawo sannan Alim ya kaisu Airport suka tafi, sha'awar Amana ce ta bijirowa Alim bazai iya jira ba kawai Amananansa yake muradi,

Tun a hanya yana driving ya kira wayarta,ta kusa katsewa ta daga cike da shagwaba kamar zatayi kuka tare da kashe murya my Man,ai Alim kusan suma yayi yaji wani yarrrrrr....gaba daya ya rude,me martaba ta harba,murya a slow kamar wanda yasha kayan maye yace honey pls get ready ina hanya I need u Badly bazan iya jurewa ba,
Murmushi Amana tayi tace ok Allah kawo ka lafiya missed u,har ya kashe wayar ya kara kiranta ta daga yace na manta wlh,mefa? Amana ta tambaya

To say i love u,ina sonki my wife,murmushin Jin dadi ta saki tare da furta me too ina Sonka,bye Alim ya kashe.

Amana harga Allah yau bata mood din xxx amma kuma tunda Alim yace haka dole dan uban Mood din yazo cewar Amana tare da shigewa toilet ta kara feso wanka,
Ta Sha kamshi tasa gown da kyar ta rufe mazaunanta tayi kyau Sosai dama gata da manyan cinyoyi,
Alim a kofar gida ya bar motar ko gate Bai jira ya bude ba ya Parker motar kamar zai tashi sama ya shigo gida,ma'aikata sai mamaki sukeyi ko lafiya,Daya bedroom din ya fada a gurguje yayi wanka,tare da shafa turarukansa masu tsada da kamshi,Boxers yasa kawai ya fito yana duba matar tasa,

Bai ganta ba bedroom dinsa ya shiga ya hango a cikin blanket kanta waje tana masa murmushi,Alim yace lafiya?na ganki lullube a blanket,

Amana tace kaifa kace na Zama ready kuma na Zama kana tambaya ta see u ta furta tare da cuno baki,
Dariya Alim yakeyi sosai yace kedai akwai abin dariya shine kika wani kule blanket kanki a waje kamar wata rabbit ko bera,
Amana kuwa dama dan kawai ta sashi dariya tayi hakan,

Hannu ta miko wai ya taho,oya zo ayi sauri naji ka ko ka karo sweet,
Jawota yayi ya direta a kasa yana kallon shigarta wow kinyi kyau da tuni kin cuceni banga shigar da kikayi ba,
Muji nan ya fara shafa dukiyar fulaninta, ai Amana sai gashi ta fara layi tare da lumshe Ido kamar me bacci suna a tsaye,yake romancing dinta tana mayar da martani,Rada masa tayi Baby idan kace na tsaye zakayi bazan iya jurewa ba sai dai ka daureni da igiya, ai Alim Bai San sanda dariya ta kwace masa ba,

I love my Amana amma dole kiyi kokari kiyi domin duk style din duniya sai munyi,kullum ke kike bada style most of the time amma yau nawa zan kawo,Amana tace Bazan iya ba amma idan kaga na fadi ai ka fada musu,Alim yace ai to rikeki zanyi,hmm Baby kenan kai har wani karfi ne da kai,na tabbata idan ka fara to ko ni sai na iya zaneka bare kace idan an fara zaka iya tsayawa abinda karfi guduwa yakeyi,

Shuru Alim yayi tare da daukanta cik ya maidata bed nan suka fara baje koli,Amana yau kam tasha wahala hanun sa domin Har kuka tayi dan ba saurarawa kamar yau ne na farkonsa,
Ya bata wahala sosai amma itama taji sweet wanda yafi na baya ma cewar Amana.

Alim sai albarka yake sa mata kamar me sannan yace Abishirinki Amana tace kudi yan Dubu Dubu ba goro ba,murmushi Alim yayi,yace na biya mana aikin Hajji,suma su Ummanki duk na biya musu,next yr kuma su Hamza,Badriyya da Sakeena da mijinta duk zamu tafi na biya harda su.

Key din mota ya miko mata sabuwa dal me matukar tsada da kyau ya siyawa Amana,takaddu ya mika mata gashi wannan gidane na sai miki a cikin kano idan munje kano ciki zamu dinga Zama,

Amana ta rasa me zata ce ma addua ta fara rakarkatowa Alim baji ba gani kamar ta zare,

Alim yace to mene hakan kikeyi kayana nakine fa ki daina min godiya,

Amana tace kai da na iya rawa yau da har rawar Michael Jackson zanyi,

Me kake so na baka a duniya? Da murmushi Alim yace kin bani komai,kina min komai,bani da matsala,kawai kiyi ta sona,ki zauna Dani har a bada sannan kuma ki bani dadi ya karasa tare da kashe mata Ido daya.

An gama Dear  sai abinda kake so na Amana bada kanka a sare,Alim ya karasa mata da Naje wajen Abba nace ya fadi wlh ya furta wlh da muryar Yan daba yanda Amana takeyin magana da kafin yanzu,

Dariya tayi tare da furta Kana yawa fa.

Soyayya su Amana suke Sha kullum cikin kwanciyar hankali,har suka tafi Saudiya,kuzo kuga Badriyya na addua a jikin kaabah a fili takeyi uban kowa naji, Huzaifa yace to idan kinyi a hankali ma ai Allah zaiji sweety, dukansa Badriyya tayi kadan da wasa taci gaba da adduarta,Amana da Alim suna can gefe tayiwa kanta,tayiwa Babanta,Ummanta,uwa uba mijinta, yan uwa,da Sauran Alumma, Saida ta gama adduoi masu muhimmanci, a karshe ta dawo ta fara ta soyayyarta da mallake miji,tace Ya Allah mijina Alim kasa yayi ta sona,ubangiji Allah Allah yaaa Rab Alim ni kadai nawa,Allah ka mallaka minshi,haka Amana ta dinga adduar mallake Alim,Alim ya dinga ta sonta ita kadai,bata ma San a fili takeyi ba Alim na jinta,yana ta Jin dadi ga dariyar Adduar Badriyya ma da take cewa ya Allah dan nan dake cikina kasa ya gaji halin Ubansa na kwarai,Allah kayiwa dan Huzaifana Albarka yana kyautata min...Huzaifana mijina ka tsundumashi a Aljanna.

Sakeena kuwa ba ruwanta a hankali takeyin tata.,su Umma ma suna nasu bangaren abinsu.

Saida suka koma Hotel masaukinsu Alim yake ta tsokanar Amana da cewa aure zai kara Addua bata karbu ba,

Sun gama aikin Hajji lafiya sundawo banda Alim da Amana domin sun wuce London sati Uku sukayi sannan suka dawo gida,Amana tsaraba ba a magana,

Sun dawo da sati daya Alim yace ta shirya zatayi waec da Neco,murna sosai Amana harda tsalle,

Mum tana can a kasarsu ta rame tayi baki ta fige ta yage,danma Alim na kiranta kullum ya lallasheta,kuma yana tura mata kudi su Nura kuwa kawai a sati sau daya suke kiranta ma,Abba kuwa ko zancen Mum bayayi ba yaso yaji zancenta,

Amana tana zaune a kujera Alim ya shugo ya fada kujerar yana sauke gajiya juyawa yayi tare da kwantawa a cinyar Amana,Ta fara wasa da botin rigar sa tana masa sannu da zuwa,

Sai shagwaba yake mata,kamar karamin yaro tana ta lallabashi,wayar Amana ce tayi

kara,dubawa tayi taga Ya Kb dauka tayi suka gaisa suna wasa da dariya sannan yace wani tsoho tukuf yazo har gidafa yana nemanki,

Ya bamu labarin abinda ke tafe dashi kaf dangi munji komai harsu Badriyya da Sakeena Amma yanzu ya za ayi?gwara kiji abinda yazo dashi da kanki,Amana tace bari nama transfer kudi ka sakoshi a jirgi yazo zan sa a daukoshi daga airport,

Nan Amana take fadawa Alim yace ba matsala,haka kuwa akayi Alim ya tura kudi tsoho yazo lagos aka daukoshi har gidan Su Amana,sai kalle kalle yakeyi,

Abinci me aiki ta kai masa yaci ya koshi yayi Sallah,Sannan Amana tare da Alim suka fito wajen tsohon,suna ta masa kallon sani kamar sun sanshi.

Gaisawa sukayi da tsoho,Alim yace make tafe dakai? Kamar na taba ganinka,

Tsoho ya karkace yana goge hawaye tare da furta ba kama bace Dannan,yaro ba kama bace kun sanni idan zaku iya tuna Baba tsoho dake haskaku da fitila a lungun duhu,har na maka ihun kwarto aka biyoku,

Amana tace yes mun tuna mun ganeka amma lafiya Baba? Tsoho yace labarin me tsawo ne,sanda muke haduwa kece baki sanni ba amma ni na sanki nasan komai na rayuwarki,kuma nasan kuna da aure tun tuni,zuwa nayi na roki gafara Ku yafemin na yi muku babban laifi,zuciya da shedan suka sa na kasa hakuri,

Labari ya fara basu,watarana ke Amana tun kina budurwa kina kauye sannan kina fama da kuruciya kuma bakya barin ko ta kwana.

Ni na kasance tunda nake ban taba haihuwa ba a duniya har na tsufa,ina cikin bukatar haihuwa Allah yasa na auri wata kwatsam ta samu ciki ta haifamin Namiji,

Bani da kamar yaron nan na dauki son duniya na dora masa,ko zaginsa bana bari ayi,watarana ya tsokaneki kika biyoshi har gida kika lakada masa duka tare da farfasa masa jiki,readers idan baza Ku manta ba farkon novel din nan Amana yaro ya tsokaneta ta bishi har gaban uwarsa ta hada masa jini da majina,to wannan yaron Baba tsoho ke magana shine dansa.

Bana gida na dawo na tarar da yarona ance ke kika masa haka,raina ya baci nayi niyyar shiga malamai domin naga bayanki sai na fasa na shiga bibiyarki har Allah yasa naji labarin kin dawo garinku da zama ke da mijinki,

Ina sani nake muku magana har na gano gidan da kuke Zama dalilin ihun kwarto da nayi muku,

Muka biki har gida dan naga gidanku,hakan yasa na tafi Adamawa nayo hayar yaro na biyashi kudi yazo har gidan ya shige dakinki ya fito ya kulla miki sharri don naga na cusa miki bakin ciki sabo da naga duk duniya kin fi son mijinki da komai,

Yaron yana Adamawa yanzu ya shiryu sanadiyar wata yarinya da yake so,

Sai laifina na biyu wata baiwar Allah tazo garin neman gidan Babanki cewar Sulemanu yayiwa Yarta fyade ni na mata jagora ta ga gidanku,da dare ta dawo da matasa yan daba tasa sukayi wa Sulemanu duka suka karairayashi.

Nayi hakane sabo da son dana son kai da son zuciya,yanzu kuma nayi nadama naga banyi dai dai ba nazo Ku yafe min,domin yanzu dan nawa ya kangare yaro karami yanzu ya fada shaye shaye dalilin son dana ke nuna masa bana masa fada sai gata danake nuna masa,

Amana ce tayi ta maza tace sanda kace anyi maka haihuwa fa?har mijina ya baka kudin rago,tsohon yace yarinya mace aka haifar min,yanzu kuma duk wanda muka aikata muku ba a Dade ba sun rokeni idan na ganki na fada musu zasu zo neman gafara,dan Allah yarinya ki yafe min,Alim zuciya ta cika da takaici ji yake kamar ya masa mugun duka,

Sai dai ka karbi hukunci a koti domin baka ma da hujjar yi mana haka,ka zaluncemu kasa na zargi matata,da ace na saketa fa,kuma bayan yaron shi ya tsokaneta wannan hujja ce?kawai bakar zuciyarka dama can mugun halinka ne,kasa mun zargi mutane da yawa wanda Ashe basu suka aikata ba sai wanda kai bamu sanka ba,bamu damu da kai ba,mun manta dakai Ashe kai sharri kake kulla mana to baza mu yafe ba itama baza ta yafe ba kuma sai kasha dauri tsohon banza,bakaji dadin halinkaba cewar Alim....tsoho yaci gaba da magana.

AsmaBaffa

Godiya nake readers.
✳CIRANIN AMANA✳

190-195

Official

By
AsmaBaffa

Ku yafe min sharrin shedan ne,Amana nayi hakan ne a nufina dan na koyawa zuriarku hankali saboda abinda kukeyi a gari baku kyale kowa ba a garin nan mutanen gari,yan uwanku ma gudunku sukeyi domin da Sulemanu ya rasu da kyar suka zo gaisuwa saboda su Kansu baku kyalesu ba,sai gashi hukuncin Allah ya canja muku rayuwa,

Ku yafe min gafararku nazo nema domin idan ma a kotu an yanke min hukunci kwana nawa zan kara a duniya,

Nasan banyi dai dai ba,Alim cike da takaici yace pls ka kyalemu haka ni na zata mutumin kirki ne kai har nayi asarar kudina aka kawoka gidana,bana kaunar ganinka,kuma dole ka karbi hukunci dai dai da abinda ka aikata,Amana dai tana jinsu ta kasa magana sabo da mamaki daya lullubeta,Alim sai faman masifa yake saukewa tsoho,

Amana ce tayi magana ba komai Baba kanka ka cuta ka ganni dai baka rageni da komai ba domin mijina Bai sakeni ba Kuma Bai jira ya tsaya dogon bincike ba saboda ya yarda Dani muka ci gaba da zaman aurenmu,

Ka bani mamaki tsoho wlh da ace dane da nake Amanar Sulemanu Harka da a nan wajen saina bajeka,duk tsufanka saina barar da kai,a kan son yayanku Ku dinga mugun abu,wato na wani banza naka dukiya ko,Danka kuma ko yanzu ya min rashin kunya kaji da kyau saina ballashi ni matar Alim yar Sulaiman ba a ja Dani,murmushi Alim yayi yanda Amana take zabga kuri,

Ita kuma wacce ta yi sanadin Babana ina jiranta ka kawota,da yaron daka tura yamin sharri harda kwasheni da mari ina matar aure,ya gyara kumatunsa domin Idona idonsa sai mijina ya rama min Marin daya min.

Kaikuma sanadin tsufanka kaje halinka ya isheka amma ni na yafema har Abada,

Alim da sauri yace ke mene haka wa yace ki yafe,karka damu gashi munci riba tunda kaga na yafe kawai ka kyale maganar,ai na gaba yayi gaba na baya sai labari Allah yanason me yafiya kyaleshi kawai,

Alim yace to shike nan Baba an yafe ma ka kiyayi gaba,ba haka akeyi ba daga anyi ma abu ka rike mutum a zuciya har sai ka yi masa mummunan sharri.

Baba tsoho godiya ya dinga yi sannan ya danna waya tare da kiran Matar da ta ragar gaza Sulemanu Harka,da yaron da yaje gidan su Amana,adress ya basu na gidan Alim yace Suzo yana gidan ma.

Tashi Amana tayi tare da komawa sama cike da mamakin tsoho a fuska kamar mutumin kirki.

Washe gari da wuri sai ga matar ta shigo gidan Alim harda sanda tana dogarawa kayan jikinta duk sun yage,

Itama an bata abinci da ruwa taci ta koshi,da karfe biyu saiga Saurayin nan da yaje gidan su Amana,shima an masa saukar mutunci,har yau su Amana basu leko ba kuma gaba dayan bakin nasu suna bangaren masu aikin gidan nan aka basu masauki,

Shuru suna jiran su Amana shuru suna can suna soyewa sun manta da baki,har wurin 3pm sannan Suka fito makale da juna tare da bada Umarnin a kawo musu baki part dinsu,

Baki dai sai kalle kalle sukeyi sunga gidan da basu taba gani ba,Amana ta fara magana sannunku da zuwa,nan baki suka gaishesu kai a kasa,

Jin muryar ta yasa Saurayin nan ya dago tare da kallon wace wannan me muryar masoyiyarsa matar aure,

Ai kuwa karaf suka hada Ido da Amana ba wani bane face Deeni kwaro dan Adamawa wanda ya kai Amana asibiti,to wai ma ya Akayi Amana bata ganeshi ba time din da suna Adamawa,

Deeni Kwaro cewar Amana dama kaine ya Akayi ban ganeka ba? Mamaki da zufa ta ketowa Deeni,yana ina...Ina fara magana,lokacin kin shiga cikin tashin hankali ba tani kike ba ta mijinki kikeyi shi yasa ba ki Kula ba har nazo na kwada miki Marin daya gigita ki na fita da sauri,ni kaina wlh ban taba yin irin wannan aikin ba saida Baba tsoho ya rokeni sosai ina yin aiki kala kala a biyani kudi amma ban taba yin irin wannan ba,shi yasa ni kaina a tsorace nayi aikin,

Amana tace shi yasa nake ma kallon sani a Adamawa,Alim abin ya daina bashi mamaki magana yayi yace ni kam ina ganinsa na ganeshi,ko a ina na ganshi wlh sai na ganeshi amma ba komai rayuwa ce,Deeni har kasa yana bada hakuri,tare da furta na Dade da tuba kuma kin Sani a sanadiyarki na tuba wlh na daina komai sanda nake ganinki a garinmu,

Lokacin ban San ke matar wani bace kuma harga Allah ban gane kece ba sai yanzu,ki yafe min dan Allah Ku yafe min,

Amana murmushi tayi tare da furta ai ka cancanci na yafe maka,na yafe maka Deeni,Alim yace wai ke meke damunki ne yanzu ni gaskiya Amanata ta farko nake so bata yanzu ba,gwara Amana me Zafi da masifa ta,ke wannan Amanar ta yanzu ban gane miki ba,Dariya Amana sukayi gaba daya harda su tsoho

Matar ce tace gani nima dan Allah a yafe min,ni kun Sanni farin sani Saude ce,duniya ta dawo Dani haka,Amana tace na Dade da ganewa kece Saude,ko dan dukan da kikaci a hannuna na yafe miki,Alim ne ya kwalawa Amana Biro a kanta na gaji da wannan abin naki komai kice na yafe,

Amana tace idan bamu yafe ba mene ribar mu kawai ka kyalesu,Allah ma yana yafiya bare wasu mu,duniyar nawa take kowa yaje da halinsa,Halinka jarinka babu abinda dan Adam zai hanaka ko yi ma a rayuwa face da Sanin Allah,

Deeni kuwa shi ya taimaka min da tuni na mutu ya kaini asibiti ya biya kudin magani lokacin da bani da kowa bani da ko sisi lokacin da cikina ya zube,

Ka kusa aure kuwa?Amana ta tambayi Deeni,Alim ina ruwanki dashi kuma,Amana cikin rada suruntunta ya kaita tacewa Alim da fa sanda Ina Adamawa so na yakeyi sosai,sunansa Na me Kunu,bai San ni matar Aure bace,amma da na fada masa ya hakura,har address dinmu na bashi,niyya ta na bashi kanwata Salam tunda ta girma,

Kafin kace me Alim mood dinsa ya canja gaba daya ya bata rai sai muzurai yakeyi hannu yasa ya gyarawa Amana hijab dinta sosai sannan yace to Alhmdllh duk mun yafe muku,ke kuma Saude kin makara Baba da kika sa aka sassara ya rasu shariarku sai a lahira sai dai kiyi tuba Allah ya yafe miki nasa laifin, Allah kiyaye gaba,kuje driver ya kaiku wajen shiga mota Ku koma gida Allah kiyaye gaba,

Jansa gefe Amana tayi tace haba honey jirgi zaka biya musu,harara ya balla mata,pls kaji da kudin nan fa mene amfaninsu,to bari ni na biya musu a nawa kudin,Alim yace gwara da kikace ke ni dai bazan yi asarar kudina ba bare waccen munafukin yaron wlh karya kara zuwa gidana,kuma baza a bashi kanwarki ba salon a dinga zumunci dashi yana kallonki yana jin dadi,ko ya zauna da Salma ya dinga tunanin kamar kece.
Suyi sauri su bar min gida.

Amana kuwa Bedroom dinsu ta koma tare da jawo wardrobe wajen da Alim ke ajiyar kudi da yawa ta ebo tare da dubawa a hand bag, Alim yana Palo a kwance ta wuce da sauri ya jawota ina zakije ya kuma ganinki ya dinga sonki,yana sha'awar min ke, zuwa zanyi na sallamesu,kudina kika ebo? Yeah cewar Amana kudinmu dai,zauna to naje ni na sallamesu idan akan jirgine zan biya amma ki zauna baza ki kara lekawa Palo ba sai sun tafi,
Ai dai mayi Sallama ko da Deeni ne cewar Amana,Alim ne ya fita tare da banko kofa,yana zuwa yasa driver ya kaisu airport sannan yace tace ku gai da gida,Deeni kuwa yasan Alim ne ya hana ta fitowa sabo dashi,kawai sai yace ni dama Abuja zan wuce ba sai ka bani komai ba na gode ina da returning ticket dina,Alim yace Good tare da tabe baki,haka suka tattara driver ya kaisu suka ware,Deeni dama da kudinsa shi yana da sana'a.
Alim kuwa masu aiki ya kira yace su kara share masa Palo su goge shi tas su sa air freshener da yawa da turaren wuta,wai dan karma Amana taji kamshin kalar turaren Deeni kwaro domin Deeni kwaro dan gayune sosai kuma kyakyawane ba laifi,

Deeni kwaro kuwa Bai zarce ko ina ba sai kano har gidan su Amana,yaje cikin gidan ya gaishe da Umman Amana yana ta zura Ido ko zaiga kanwar Amana ya so ta ya aureta,yana zaune da Umma suna hira sai ga Salma ta shigo kuwa daga makaranta Salma yan Ss3,ai kuwa Deeni yaga Salma kyakyawa itama yar caras da ita,
Umma ya tambaya Umma wannan yarkice? Umma tace yar gidan Inna ce kishiyata, nan ya shiga ina..Ina...da kyar yace Umma zata bani ita,Umma kuwa taga Deeni ya shiryu sosai gashi dan garinsu tasan asalinsa tace me zai hana idan tana sonka,ka nemi soyayyarta.

Salma ce ta shigo dakin Umma tare da cewa Umma ina su Inna da sauran yara? Umma tace sun tafi gaishe da yayan Babanki Alhaji Shehu,zasu biya gidan sauran yan Uwa ma sabo da kulla Zumunci,
Shagwaba Salma ta fara wai Umma amma basu jirani ba nace zanje gidan Anty Maimuna fa,Maimuna itama yayar su Amanace me aure da yaranta.
Deeni a ransa yace naga waje irin wannan shagwaba haka me birgewa,
Salma gaishe da Deeni tayi sannan ta fita tana fushi,
Mikewa Deeni yayi tare da yiwa Umma Sallama zai tafi Adamawa,har kudi ya bawa Umma,

Umma ta kwalawa Salma kira,Salma na zuwa Umma tace kinga wannan Saurayin daya fita? Salma tace eh,to Sonki yakeyi kuma mutumin kirki ne,Antynki Amana ma ta sanshi sosai,maza kije Ku gaisa ki rakashi zai tafi gida a garinmu Adamawa yake.

Salma murmushi kawai tayi tare da zurma hijab ta fita wajen Deeni,jikin kofa ta samu Deeni yana jiranta,cike da kunya taje wajensa suka gaisa,Deeni da idonsa yake a tangare tuni ya tsara Salma saiga Salma kamar ta Dade da saninsa Suna ta hira,duk yaron da ya shigo in dai kanin Salma ne ko kanwa sai Deeni ya bashi Dari biyar sabuwa kar,
Haka suka gama Hira ya tafi tare da karbar Number Salma.

Gwaggo dasu Inna kuwa kaf yan uwan Sulemanu sai da suka je suka basu hakuri suka ce kuma za a ci gaba da zumunci,sosai sunji dadi,Alhaji Shehu yace zasu je har gidan su Amana da Badriyya da sauran yaran Sulemanu inda zasu ga mazauninsu a kara karfafa Zumunci.

Amana tana zaune Alim ya shirya zai fita office,Amana tace dan Allah Baby kaje Dani kaji gidan so boring idan baka nan,
Lallashinta ya fara tare da rungumeta yana goga fuskarsa a wuyanta tare da magana a hankali,ba dadewa zanyi ba,kinga anjima su Asiya zasu zo da Autan Mum,idan mun tafi kinga ba kowa gidan ko,kai ta girgiza shike nan to bari na jirasu,
Zagayowa yayi da ita gabansa tare da fara kissing dinta,ya naga kamar kina fushi,murmushi tayi ba fushi nayi ba kawai dai banjin dadi ko period dina ne zaizo I think,har yau bamu samo Aabid ba?na zata ma mun samu dana ga kina wani kiba da kyau,

To da alama bamu samu bafa dan Allah kayi sauri ka dawo a kara nemowa ko zamu dace kafin period yazo kasan yanzu mahaifa ta bude,na matsu a samu Aabid dina,dariya Alim yayi tare da cewa ai kece idan nace a kwana ana yi sai kice waye waye ai gashi nan anji samowa, shagwaba ta fara masa da badan ya daure ba bazai iya fita ba,
Yana fita ta zauna tare da kiran Badriyya suna ta Shan hira,bayan sun gama ta kira Sakeena ma,ta koma su Hamza da su Anty Maimuna,Sadiya da sauran yan Uwa.

Tana gamawa ta fada kitchen tare da shirya lafiyayyen girkinta,ta kara gyara gidan ko ina neat,Alim minti kadan zai kirata yaji wai ko period yazo sabo da sauri yakeyi kar yazo baiyi komai ba,
Wanka Amana ta fito tare da yin Sallar sa'asar ta shirya cikin Atamfa fara me zanen baki Riga da skert dai dai ita Dinkin zamani tayi matukar kyau Sosai duk wanda ya kalleta sai ya kara,tana fesa turare taji door bell,takawa tayi har kasa ta bude kofa Asiya ce da Autan Mum suka kwada Sallama tare da shigowa,
Amana da fara'a mutunci hade da karramawa ta tarbesu har palon Sama ta kaisu,suna ta hira ta cika musu gaba da lemuka da ruwa hade da dambun naman kaza,
Asiya tace na girmeki nesa ba kusa ba ni Antynki ce amma ya zanyi matar yaya dole nace miki Anty,dariya sukayi Amana tace ya Zama dole kuwa ko na fada masa ya zaneki.
Asiya tace rufa min asiri da masifar ya Alim akanki.
Yanzu dai ankon biki na kawo miki fa gashi kuma zan fada miki shirye shiryenmu sai kiji ko zaki kawo idea,
Auta yace hmm Anty Asiya zumudi sai mijin ma ya rainaki wlh danma ya Ahmad ne me hakuri,kin fiye zumudi,Amana tace jinji yaro da'allah rufe mana baki manya na magana.
Dariya sukayi duka,domin Autan Mum ya girmi Amana sosai.

Suna ta hira da tsare tsaren bikin Asiya sai ga Matar Ya Nura ta zo itama tare da mijinta Nura babban yaya,nan suka kacame da hira da nishadi,Amana da Asiya suka jera abincin da Amana ta dafa kala wajen uku,Asiya ta dauko wani mugun azababben foodflask guda hudu ta kawo,Amana da Sauri tace ke yan mata wannan na me aiki me gayya ne,na Oga kwata kwata ne,ko a Ido kin San na me girma Alim ne angon....kasa karasawa tayi saboda hada ido da sukayi da ya Nura,wayancewa tayi da murmushi tana sosa wuya,Asiya ta sheke da Dariya tare da matar Nura suna tsokanar Amana su Na Ogan zasu ci,

Amana ta kwashe flasks dinta ta mayar kitchen,ta bar musu nasu suma masu kyau amma ko kafar na Alim basu kama ba,

Alim ne ya shigo palon da Sallama yagansu suna ta ciye ciye ana ta labari,

Dan Zama yayi suka gaisa yana musu sannu da zuwa Amma idonsa yana ga Amana yana aika mata da kallo tare da harara wai bata je ta tarbeshi ba,

Kunya taji tare da dauke kai,ina zuwa Alim ya shige bedroom, Amana tana so taje wajensa tana dan Jin kunya wai zata yi musu wayo tace Asiya Amarya bari na dauko miki wani abu ko zai miki,zuruf ta shige dakin Alim,

Tana tafiya suka kama dariya wannan yarinyar da abin dariya take cewar matar Nura,Nura yace ina ruwanki yan sa Ido,

Alim daga shi sai towel iya kugu zai shiga wanka,yaji Amana ta rungumeshi ta baya tare da kwantar da kanta a bayansa,

Sai yanzu zaki wani zo,murmushi tayi yi hakuri kunya nakeji ta ya Nura,

To ya Nura tsaya ki gani shi a gabanki zaiyi abinda yaga dama da matarsa.

Muje kayi wankan kawai,suna shiga toilet yace sai ta shigo sunyi kuma ba iya wanka zaiyi ba ta gane nufinshi kin yarda tayi tace ni bana son kara wanka ga baki munyi kuma dadewa zamuyi fa,

Jeki to karki Dameni da Surutu kuma karki kara cemin kina son Aabid tafi, Amana magana tayi bata fito ba kamar kunkuni,Alim yace me kikace,Amana tace a'a cewa fa nayi Allah zai kawo ai,oh Allah ya taimakeki kuma idan banyi ba baza ki samu Aabid ba yarinya,

Dole ma kayi min na samu,toilet Alim ya shiga,Amana ta bishi ciki,to mene zaki kalle min tsaraici kuma? Dariya tayi ba kallonka zanyi ba kayi wankanka,a toilet din ta nemi waje gefen Bowl din wankan tayi zaman ta,Alim ya fara wankansa,tace haka akeyin wankan,shuru ya mata,can baka sabulunba fa,

Sabulun ya mika mata ungo karasa,hannu tasa zata karba ya jawota tana ihu ya tsundumata ciki tare da danna shower ruwa shaaa ya jikata gaba daya,

Ruwan na zubowa ya tubeta gaba daya  ya sake mata sabon wanka,sai kukan shagwaba takeyi masa,

Sai da ya gama murzata son ransa da kyar ya hakura towel daya ya daura musu tana cikin jikinsa kamar masu koyon tafiya suka fito ko mai bata shafa ba tasa doguwar Riga brown color ta dan gyara fuskarta sosai sannan ta zurma hijab har kasa wai kar su Asiya su gane anyi wani

abu gashi har ta sake wanka ta canja kaya.tana fitowa suna kallonta suka San anyi wani abu domin rigarta ana hangowa ba kayan dazu bane,

Auta a ransa yace kut Amma ya Alim jaraba ne daga dawowa shi yasa yake ta kallonta,muma dai mayi auren nan,Alim da 3qtr da T-shirt ya fito suka fara hira,Amana ta kawo masa abincinsa ta jera a gabansa ta cika gabansa tab,har yafi na bakin domin na Alim na musamman,abin mamaki hattana kalar spoon din Alim daban ne ba irin na kowa bane,

Alim ne ya kifta Ido Amana ta kau da kai,ya kara kashe mata Ido ta juya gefen Asiya,

Nufin Alim wai tazo ta bashi yaci abinci da kanta,ita kuma tayi kamar bata gani ba,

Su Nura suna kallon abinda Alim keyi,magrib na gabatowa suka ce zasu tafi har mota suka rakasu,Auta da Asiya motarsu daya,Nura da matarsa ma haka,

Suna tafiya a hanya Alim ya dagata sama tare da sabata a kafada har cikin Palo,

Amana ta fara waec a cikin jerin motocin Alim ake kaita tare da securities sai ta gama suna jiranta a dawo da ita gida,

Har ta gama waec suka fara Neco,

Tana gamawa ta shirya cikin tsadajjiyar motarta taje har kofar gidan Dan Uzuri,

Mutane da wanda suka Santa sun gaisa suna mamakin canjawarta domin basu gane Amana bace sam, saboda da kyau da haduwa da tayi ana kallonta an San Naira ta ratsata,

Tambaya tayi ko dan Uzuri na nan,suka ce ai Dan Uzuri ya Dade a prison da kyar aka sakeshi amma yanzu ya koma kauyensu da rayuwa,gida ta koma tana shiga Alim ta hango a Palo yana kallon News tana zuwa ta kwantar da kanta a cinyarsa tare da mikar da kafafunta a doguwar kujera yana mata sannu da gajiya har bacci ya dauketa.

Bikin Asiya yana ta gabatowa kuma Mum zata zo bikin Yarta sannan gidan Alim zata sauka,Alim ya kira Mum suna hira,Mum tace bawa matarka waya mu gaisa,Alim dai a tsorace ya mikawa Amana,Amana cike da ladabi kamar tana gabanta ta gaisheta,Mum cike da fara'a suka gaisa harda Jan Amana da hira.

Alhaji Shehu da sauran kannen Sulemanu ne suka yo waya zasuzo gidan Amana suga yarsu.

Murna wajen Amana ba a magana suma yanzu danginsu suna kulasu.Alim ta sanarwa shima yaji dadi ko ba komai dangin matarsa ne.

Korafi ya karbu Maman Minat,godiya da tunatarwa.

AsmaBaffa.
✳CIRANIN AMANA✳

195-200

Official

By
AsmaBaffa

Kwana biyu tsakani su Baba Shehu da Ahj Sani tare da kannen Sulemanu,sai su Anty Maimuna,Anty Sajida,Maryam da Sauran yayyen Su Amana mata,duk suka sauka a Lagos,kwanansu daya suka tafi tare da sha tara ta arzikin da me gidan na Amana ya musu,su Hamza kuwa da su Umman Amana sai bikin Asiya zasu tattaro suzo suma Asha biki dasu.

Alim ne ya dawo daga Office 5pm,Amana ta fito cikin hadewarta data saba me rikita Alim,rungume abinta tayi kam tare da masa sannu da zuwa tana sakin murmushin dake kara mata kyau,wani Apple Juice da ta hada da kanta ta dakko me zanyi a glass cup ta bawa Alim dinta yasha yana santi,

kashe murya tayi tare da kara kasa da ita can kasan makoshi tace muje ayi  wanka ko? shagwaba ya fara mata ni nayi wanka da kaina fa? Sai kace marar gata,ni dai ki min da kanki wani wanka na iya me kyau,

Dariya suka saki  gaba daya Amana tana dariya ta dan tureshi shagwaba kullum ko? Alim yaci gaba da shagwabarsa pls......mana ni ban iya wanka ba,yanda yake Abin Amana sai faman dariya take tace muje to,da sauri yace ok ko kefa,

Tsayawa yayi kamar jariri ta cire masa kaya,ta kaishi toilet ta fara masa wanka,aka zo wanke

wuya Alim ma bai son a taba masa wuya sai ya dinga dariya kamar yaro, Amana tasan halinsa tace daga wuyan na wanke, Yana dagawa tasa sabulu ai kuwa dama ta sani sai ya kyalkyale da dariya tare da makale wuyansa,

Halinka kenan kara dagawa yayi ya kyalkyale da dariya tun kafin ta taba wuyan yake makale abinsa,yana sorry to na tsaya,da kyar ya bari aka gama wankan.

Tazo ta fara shafa masa mai,Amana ta dan dakeshi a kafada cikin wasa,tsaya mana joo....aka zo sa kaya yace shi Baza a sa masa kaya yau ba sai gobe,to da me zaka zauna? Ki barni da towel dina nayi sallah fa saura magrib da Isha idan zanyi nasa kayan,
Kyaleshi tayi suka koma dining suna cin abinci,brush ta masa itama haka,

Chewgum ya zaro zai tauna a baki,Amana tace ina nawa?ka sanmin kaji ta fada kamar zata yi kuka,a kan Mirror na gani na dauko,to nawa ne fa tun yaushe nake ce ma ka siyo min ko sweet duk sun kare sai kace to ka manta,
Alim sai da ya gama taunewa da tsotse zakin ya dora chewgum din a harshensa tare da miko mata harshen ungo to karbi abinki,
Miko bakin tayi kuwa kamar tsintsaye ta karbo ta kama ci ta kara hade bakinsu ta maida masa chewgum dinsa, murmushi tayi tace yawwa yi min taunar yan gayu,Alim kuwa ya gyara ya fara taunawa da kyar yana yanga harda yin kwai kalar na yan gayu kamar wata mace,Amana kuwa tana dariya tace to ayi na yan kauye Alim ya koma cakal cakal yana tauna chewgum,Amana tace na karuwai fa? Ya koma kas kas kas yana taunawa,Amana tace wink me,ya juyo side to side din idonsa yana kashe daya tare da mintsinawa,
Yanda yake yi abin dariya Amana sai dariya takeyi.

Magrib nayi ya zura jallabiya sukayi Sallah,suna idarwa ya zare kayan ya daura towel dinsa,Amana tace ikon Allah muje to muci abinci,nan ma ya kama shagwaba sai da bashi da kanta,dama dazu kasa ci yayi da kansa,suna gamawa

Daukanta yayi har kan Bed ya kwanta a jikinta tare da rada mata wannan ne dalilin zama da towel kinga ba sai na sha wahalar cire kaya ba,

Kissing dinta ya fara hannunta ta dago a hankali tare da sakaloshi ta wuyan Alim suna ta kissing din juna,daga nan ya zare mata kaya ya fara wasa da sassan jikinta sun fita a tunaninsu,wayar Alim ta shiga kara tsayawa yayi da niyyar jawo wayar tasa, Amana ta jawoshi tare da makalkaleshi sannan ta furta wannan lokacinane fa,Alim kuwa yanda tayi maganar shi ya kara rikitashi ya fasa daukan waya,suka ci gaba da farantawa juna rai,
Waya dai tana ta kara basu san ma me takeyi ba sunyi nisa,

Bikin Asiya saura 2 days lokacin Mum tazo,da wuri Alim yasa driver ya daukota,gaskiya ko waye ya kalli Mum sai ya tausaya mata,ta kwanjale dama kuma ba wata kiba ce da ita ba,.
Ta fige sosai,Alim har kwalla ya goge da yaga Mum,Amana ma ta tausaya mata,ta tarbeta cikin mutunci,Mum kuwa anyi laushi kamar yarta haka ta dauki Amana,

Amana tana kusa da ita Mum tana basu hakuri ita da Alim,Amana tace mune zamu baki hakuri Mum munyi miki laifi ni da kanwata ki yafe mana,Mum tace haba a daina tuna baya ai laifina ne ba matsala,Alim dai bai san kan zancen ba, sai abinda Mum ke so Amana take mata,haka su Nura ma duk Kullum sai sunzo gaisheta,k ullum Mum asa albarka take da Kukan rashin Aabid ta sularta,ana haka har aka fara bikin Asiya,

Amana anci kwalliyar dinner party,Alim ya shigo yace ba wani dinner da zakije fa,Amana ta fara kuka taje wajen Mum dake shiri ta fada mata,Mum tace rabu dashi tare zamu tafi daga dinner ma kije can cikin yan mata Asha biki dake idan an gama kya dawo.

Alim yana wajen dinner sai yaga Amana da Mum sunzo,da sauri yaje wajensu yace wa yace kizo so kike Maza suyi ta kallonki jiba da Allah gyalen ma rikeshi kikayi,cike da shagwaba Amana tace kai kuma fa ai kallon matan kakeyi kuma Mum ce tace nazo,Mum tace ke muje ki rabu dashi,haka aka gama Dinner,Amana ta zirare tabi motar su Badriyya suka tafi cikin kawaye can gidan Abban Alim suna ta shagali da yan mata tare da yan Uwa,

Alim ya koma gida ba Amana ba labarinta har 2 na tsakar dare,dakin Mum ya shiga,Mum tana bacci yace Mum wai ina Honey,Mum tace tana jikin bishiya tana sakar zuma.

Babyfa nake nufi Mum tace tana bayan Uwarta,

Alim yace Mum Matata fa nake nufi kin kaita wajen dinner to tana ina,Mum tace ka kiyayeni kai kadai ne me mata wai ka hana yarinya sakewa a cikin kawaye,tana can wajen su Asiya,a ransa yace wai Mum ce zata nuna tafi son Amana a kaina,ikon Allah kenan,watarana me Sonka shine makiyinka,makiyinka ya koma me Sonka.

Alim takaici ya lullubeshi da haushin Amana,fita yayi kawai yawa mota key wurin 2:30 na dare,su Asiya Amarya suna bacci wayarta tayi kara,da kyar ta daga, fada ya fara ki turo min Matata ina waje kice wlh ta fito mu tafi,ta wani kashe waya,

Asiya tace haba yaya da daren nan kuma Mum ce tace ta zauna sai an gama biki,what zan Mareki wlh ki turo min ita yanzu cewar Alim kamar zai tashi sama,

Asiya tace jaraba ta mike ta Isa dakin da Amana suke kwance tare da Sakeena da Badriyya,

Duka ta bugawa Amana a baya tashi ki tafi mijinki yana kofar gida zai tashi gari akan zaki kwana,kin San Bai yarda ba kika zo? Tsakaninmu da gidan naku ai ba nisa gaskiya ya hanani bacci da masifa cewar Asiya Amarya.

Amana da bacci a idonta tace rabu dashi ni Bazan je ba,Sakeena tace Anty ki tashi kawai,Badriyya ma ta mike tace kin san dai mazan nan akwai son kai kar yayi fushi ki tafi, ni da Huzaifa ne da tuni na tafi,

To a tsohon daren nan fadin Amana ....wayar Asiyace ta kara daukan ruri Alim ne again,Amana tace ita kam sai gobe zata koma,

Minti 5 saiga Alim ya shigo har cikin gidan Asiya ya gani ta fito zata koma dakinta yace tana wanne room?tace tana wannan room din,ai kuwa fuu ya bubbuga kofar,Amana ta zata yan biki ne ta bude ya figota waje da karfi,Amana ta zille tana hakki tace sai gobe fa zan dawo,kizo nan

nace miki ko,Amana tace naki din,zagayowa yayi ta jikin kujera zai kamata,ta gudu jikin dayar kujerar,ya kara biyota,

Suka fara zagaye kujerun palon,ko wanne dake gidan nan yan biki kasa bacci sukayi suka tashi zaune Sabo da yanda ake ta guje guje da ture ture a palon wasu ma sun zata aljanune suka kara buya a room,

Alim ya kama Amana da kyar duk haki sukeyi,ya safa ta a kafada, kara bubbuga kofar room din da Amana ta fito yayi, Badriyya ta leko tana dariya,yace Sis miko min hand bag dinta da komai da tazo dasu,Ai kuwa Badrriya ta miko masa ya rike gyalen da Hand Bag suka bar gidan yasata a mota har gidansu yana masifa.

Suna zuwa ya kaita har Bedroom sannan yace nayi niyyar kyaleki kije Amma ni zaki raina ki tafi ba tare da Umarnina ba kan Mum tace kije,kin ma rainani ko? Shi yasa naje na dawo dake ta karfi naga kuma ta tsiya,ya karasa yana hucin masifa.

Amana taga ransa ya baci sosai tace to kayi hakuri shike nan ta juya ta kwanta shima haka can dai ya matsa jikinta tare da manneta tsam a jikinsa,Amana tana kwance ta kifa cikinta ta dago gwiwar hannunta tawa Alim elbow daya,da sauri ya matsa tare da rike wajen kirjinsa,harda Elbow ma akan kina Jin haushi na,Amana dai bata ce komai ba,taci gaba da kwanciyar ta,bai hakura ba ya kara daura hannunsa a saman bayanta,ba bata lokaci ta jawo hannun ta cikinta tare da ganya masa cizo,ba shiri ya dauke hannunsa,

Jira yayi aka dan dauki lokaci tunaninsa tayi bacci ya koma ya kara rugunmeta,kafarta ta buga masa a kansa kamar me magagin bacci,

Ba shiri Alim ya koma karshen bed ya kwanta yana murmushi a ransa yace masifaffiya akan na hanata kwana gidan biki,

Washe gari da safe Mum ta fara salati ganin Amana tana jera abinci a dining,amma bata ce komai ba har Amana ta duka ta gaisheta, Alim ya fito sanye cikin tsadajjiyar shadda kamar a saceshi sai kamshi yakeyi yana ta kallon Amana yanda take cika tana batsewa shi kuwa dariyar mugunta yake mata kasa kasa, tana kallonsa ta kara cika fam.

Mum kuwa abincinta ta Eba ta koma room dinta,Alim yana ganin ba Mum yace shirya na kaiki masifaffiya karki cinyeni akan biki,Amana cikin fushi tace bana so kuyi bukinku bazan je ba ka daina nuna mun ba yan Uwa na bane akan naje bikin gidanku duk duniya sai ta sani ka je ka daukoni cikin talatainin dare.

Alim yana kallonta har ta gama masifarta yace tooo Allah ya baki hakuri ni ba fada nake nema ba,shirya mu tafi,yatsina fuska Amana tayi Alim yace kinga kyan da kike min kuwa idan kina yatsina fuskar nan taki me kyau,

Fuska Amana ta hade tare da fashewa da kuka, wai tunda Alim yace tana kyau da yatsina fuska,shine ta koma kuka,Alim yace kaiiiii kinga kyan da kukan nan,ai ban San haka kike kyau da kuka ba kullum zaki dinga yi min?

Amana najin haka ta kama dariya,Alim yace kash kin cuceni mene zakiyi dariya ni nafi son

kukan kinfi kyau dan yi min,ai Amana sai ta dinga murmushi me kyau wai dan kar Alim yaji dadi yaganta tayi kyau.

Alim baiji dadi ba ganin Amanansa na fushi dashi sai yayi dana Sanin daukota jiya,suna gama break yace je ki shirya mu tafi Amana ta makale kafada,bata rai yayi ban son musu jeki shirya na kaiki,
Amana da sauri taje ta shirya ta fito suka tafi,suna zuwa zata fita Alim ya riketa ki tsaya muyi Sallama mana,shuru tayi tana kallonsa,kiss ya manna mata a goshi tare da tambaya anan zaki kwana? Amana tace eh,kiyi hakuri kinji nazo da dare na daukeki kinji? Make kafada Amana tayi wai ita kwana zatayi,kin San bana iya kwana ba ke,kunkuni Amana ta kama masa cike da shagwaba,ni bana gane wannen kunkunin naki wa ya sani ko zagina kikeyi,kallonsa Amana take baki bude cikin shagwaba tace ya zanyi na zageka,naji to dan Allah nazo na daukeki? Alim ya fada cikin shagwaba tare da yin kalar tausayi,
Amana tace a'a ni gaskiya kwana nake so,
Alim ya kara magana nine fa Babynki ni din? Amana ta make kafada,kwafa yayi tare da cewa to fita ki tafi sai da safe,Amana ta fice,Dear Alim ya kira ta har zata shige gidan ta juyo daga nesa yace nine fa? Amana ta kama sheshekar kuka,ajiyar zuciya ya sauke yace to jeki jeki daina kuka,nine?ta daga kai wai eh,yace to bazan dawo na daukeki ba sai gobe jeki...yana kallonta ta shige gidan.

Alim kuwa driver ya tura airport ya dauko su Umman Amana da kishiyoyinta dasu Hamza harda zaliha da Salma.

Direct gidan Abba aka wuce dasu nan su Amana suka dinga murna aka basu masauki,sunci sun Sha sun huta sannan aka kaisu wajen Abba suka gaisa cikin girmamawa,su Nura da sauran dangi duk sun gaisa an San juna,
Mum ma gidan ta taho suka hadu da sauran dangi ana ta shagali,sannan ta bawa dangin mijinta hakurin abinda tayi musu wai su yafe mata,

Washe gari su Umma gidan Amana suka dunguma suka Sha kallon aljannar duniya,kwana biyu Alim baiga Amana ba,har gidan yaje sau nawa bata nan wai sun fita shirya wajen dinner,anjima kuma ace sun wuce gyaran jiki da lalle,

Haka aka gama biki lafiya aka kai Amarya Asiya kano a jirgi,su Umman Amana da sauran dangi kaf Amare suka bi a jirgi suka koma kano,

Kowa ya shirya ya koma gidansa,Mum kuwa idan suka hadu da Abba ma harara yake Dalla mata,ba fuska bare ta sa rai zai maidata dakinta,har hakuri taje ta bashi amma Abba ya kara ci mata mutuncin da ba shiri ta hada nata ya nata tace zata tafi kasarsu,Alim yace ta zauna dasu Nura ko a bata gidanta daban ta zauna su kai mata yar aiki da kyar Mum ta yarda,

Ai kuwa gida karami flat me kyau Alim ya bata tare da me gadi da kuma yar aiki mace,Mum ta koma ciki suna zamansu lafiya,

Amana kuwa ranar da aka tafi kai Amarya ranar ta dawo gida da kanta,

Tunaninta Alim zaiyi fushi da ita amma sai taganshi sai murna yakeyi da dawowarta,
Rungumeshi tayi ta fara bashi hakuri me kikayi?ai ni naga dama na barki kema kin San da ace banyi niyyar ba ko yini daya bazan bari kiyi ba,
Na kyaleki sabo da ki samu nishadi da yan uwanki da iyayenmu shi yasa,ki daina bani hakuri ma,

Cike da murna ta fara kissing dinsa,bai direta ko ina ba sai saman Bed,
Tun daga yanda Alim ya fara murzata Amana ta raina kanta، tun daga yanda ya shigeta Amana ta fara bada hakuri ta gane mugunta ya shirya mata ba hakura yayi ba,
Saida tayi kuka sosai,ranar kusan kwana yayi,Amana cikin kuka tace da ka min irin wannan hukuncin ai gwara ka zaneni wlh,
Murmushi Alim yayi bana fada miki ba bana son musu,na barki kiyi kwana daya kwana nawa kikayi? Amana tace Uku,da naje kullum ina kike zuwa ba izinina kike bin yan mata kuna yawo,su Badriyya duk suna gida sabo da suna daraja aurensu,missed calls nawa na miki kinki dagawa dan kar nace ki dawo,atleast kin San kullum zan barki kije amma kin tafi kinma manta da aurenki,

Duk wannan Bai isheki ba da kukaje dinner kin zage har da rabon take away maza na kallonki duk abinda kikayi ina zuwa na ganki na tafi,bai kamata na kyaleki haka bama kin bata min rai da yawa,kara fisgota yayi tare da furta bari na kara goge miki rainin da kike min,Amana kuka ta fasa sosai tana bashi hakuri,
Wlh bazan kara ba na tuba,dan Allah mutuwa zanyi idan ka kara yi,
Ko tafiya da kyar zan iya,ke kika jawo ban so na miki horon nan ba Amma ba kya ji duk ranar dana ce kaza kika min musu saina miki wanda yafi wannan,
Da sauri Amana tace Bazan ma kara ba wlh na daina,dama tsautsayine.

Daukanta yayi tare da mata wanka ya gasata sosai sannan ya shiryata ya kawo mata abinci taci ya bata magani tasha ya kwanta tare da makalkaleta a jikinsa yana ta faman bata hakuri,

Washe gari da safe warkai Amana ta tashi ras da ita,Alim ta duba baya gidan,short note ya bar mata kan mirror,

Sweet heart dina na tashi kina bacci ban son tashinki, naje office ina da meeting,yanzu zan dawo,ki kular min da kanki, love u.

Murmushi ta tayi a hankali ta furta honey kenan jiya ya gama min muguntarsa amma na tsorata ni yanzu ma lallabashi zan dinga yi tunda idan ya fara mugunta Bai San ya bari ba.

Sati Uku da biki Alim ya samowa Amana private university me tsadar gaske take karanta microbiology,
Amana ta kara Zama classic girl tayi wata irin wayewa,murjewa hade da gogewa,

Yau watanta Uku tana zuwa schl bata da wata matsala burinta kawai ta ji ta dauke da ciki,ta haifo Aabid dinta amma har yau shuru kakeji.

Alim yanda yake gwadawa Amana so da kauna ga tattali,baya son bacin ranta,itama haka,Amman duk da haka idan tayi masa laifi sosai yake mata fada.
Itama Amana ba sanya idan ya mata tana hakuri sosai ta kyale watarana kuma yasha masifarta dole ya lallasheta,
Dama zaman tare watarana hakane dole a samu sabani amma an fi so farin cikin ya ninnika bakin cikin,sai da hakuri dole,

Mum kuwa sosai take nunawa Amana so,matar Nura ma haka,dan Auta ma tace ya nemi wacce yake so ya aura.
Amana ce a cikin toilet ta siyo pt na gwada fitsari ko tana da ciki,

Samu tayi ta dauki murfin robar ruwa ta tsula fitsari a ciki ta bare a bin tasa sai taga ya nuna bata da wani ciki ba komai,kuka ta fara yi tare da yin ball da murfin,ta jefa abin a dustbin,
Alim ne yaji kamar kukanta ya shiga toilet din ya hangota  tana ta kaiwa iska naushi,
Dariya ya farayi yasan me takewa kukan,Alim ya daukota yi hakuri hajiyata zaki samu ne Allah zaki roka,Amana tace ni sauri nakeyi,dariya Alim ya kara yi to muje aka kara gwadawa ko zai shiga,

Amana tace ka dage sosai iya karfinka,saura kayi wasa,suka kule bedroom ciki suka yini suna kashe arna,
Dama shi Alim burinsa kenan,har murna yakeyi Amana ta siyo abin auna fitsari taga ba ciki to dole ya kwashi gara.

Amana kuwa saboda taga har yau ba cikin sai kara gyara kanta takeyi da tsumin maganin mata masu inganci dan Alim ya dinga kasa hakura kullum ya dinga ta yi ko ayi sauri a samu cikin nan.

AsmaBaffa
✳CIRANIN AMANA✳

200-205

Official

By
AsmaBaffa

MASU YIN DOCUMENT WANNAN PAGE NAKU NE NA GODE SOSAI.PLS A DINGA KULA KAR A TSALLAKE KO WANNE PAGE KUMA KAR A HARGITSA PAGES,MISALI PAGE 10 A FARKO 5 A KARSHE,READERS BASA JIN DADI.NIMA IDAN NA GAMA ZAN KARANTA ABINA NAJI DADI,DOMIN A MA'AIKACIYAR GOMNATI AN CIRE PAGES DA YAWA,WANI KUMA ANYI SHI A HARGITSE BA DADIN KARATU.NA GODE SOSAI INA JINJINA.

Deeni kwaro soyayya tayi nisa shi da Salma,kowa yasan labarin,lokacin da Alim yaji masifa ya kamayi shegen yaro ya damesu ya hanasu sakewa,
Amana taje gida garinsu gidan da Alim ya bata kyauta  katon gaske ne a Rijiyar zaki,don haka tace ya kamata a raba gadon Baba kowa a bashi hakkinsa sai asan abin yi,
Haka kuwa malamai suka kirawo aka kara duba wasiyar Baba suka ce kowa ya yarda da wasiyar Baba?aka ce eh,sannan sukace wasiyya ta tabbata, gida kuma babu na kowa da gonakinsa aka siyar dasu aka bawa kowa gadonsa yanda Allah yace, gidan da suke ciki aka raba aka fitarwa kowa da nasa‹Nan Amana ta raba rigima tace ta siyawa Hamza gidan shine Babba shine Uba,Hamza yayi tsalle ya dire bazai zauna a kauye ba ta rike gidanta Abban su Huzaifa ya siya musu gida dukkansu manyan mazan  aure zasuyi kwanan nan,Amana tace to gida natane kuma na kowa ne kowa yayi zamansa idan yazo kauye tunda suna da dangi a kauye,

Sauran matan Sulemanu kuwa sunce su baza su kara aure yanzu ba sai sauran yara sun girma,Amana ta ce to duk su dawo birni Alim ya siya mata gida ta basu su zauna a gidanta iya dake Rijiyar zaki iya rayuwarsu, suma su bar kauye gaba daya kawai,
Wannan gidan kuma na kauye za a sa me gadi ya dinga Kula dashi duk wanda zaizo ganin yan Uwa na kauye sai ya zauna a gidan,

Kowa sai murna akeyi.. kayan sawa kawai Amana tace su Eba komai akwai a wancan gidan,su kb sai murna domin duk sun daina zuwa Cirani suna kasuwanci da karatu a kano,
Haladu kuwa  yace a daina ce masa Haladu, tuni yace wlh ya koma Mohd yanzu.
Amana bata koma ba sai da suka koma cikin kano aka gama komai,tayiwa yara transfer na schl,ta gama komai taga suna Zama komar ras,
Alim ne ya kirata tana dagawa ya kama fada wai har yau baki gama ba ki taho mana,Amana cike da shagwaba tace gobe zan dawo,Nutsuwa tayi tare da narke masa tace ranka ya Dade? Alim yace ina jinki sai wayo kike min kinki dawowa,zaki ce min wani ranka dade,
Murmushi Amana ta saki haba yanlabai me martaba,alfarma nake nema idan da Hali baza ka damu ba,Alim yace ina jinki kin San ma dole nayi,Dama mota nake so a siya min zan ajiye musu ta zirga zirga,
Shine kike kwane kwane,na baki dayan Atm din kije ki cira ki siya musu,nasan ke me hankalice kin San me ya kamata kawai kiyi ina ganin abinda kike abinda ya dace,    Da murna ta dinga ta godiya da kb sukaje suka siya aka ajiye musu dalleliyar mota katuwa kowa ya hau ta gida ce,dama Isa da Hamza su suna da motarsu.

Abinci ta cika musu gidan dashi komai da ya dace ta musu ta kashe musu kudi sosai.
Su Badriyya murna suke gasu ga yan uwansu a kusa,Su Maimuna da su Baba Shehu duk sunzo sunga gidan,,

Badriyya da Sakeena kuwa yan uwansu Mata dake aure a kauye suka basu kudi masu yawa su kafa jari suyi sana'a su dogara da Kansu suma tunda mazajensu ba masu Hali bane,

Washe gari da wuri Amana ta shirya, Kb da Mohd wato Haladu suka kaita airport,hannu ta mika musu suka tafa suna ta dariya sukace sai yar Cirani,wannan Ciranin Alkhairine gwara da Baba ya kaiki wlh,ashe ta hanyar za muyi arziki mu shiryu,

Mohd yace kai Man munyi fa iya shege,Amana tace musamman ni,Kb yace Hamza fa Kun mata,kai Hamza dan iskan duniya ne‹yanzu in kinga Yanda yake zuba love sai kinyi mamaki, dariya Amana tayi tace ah nima ina zuba tawa ba kara'i, Mohd yace hmm ke ai dama tun tuni ba kunya gareki ba, Haladu zan ma rashin mutunci fa cewar Amana,Haladu ya bata rai nace muku Mohd nake ni wlh rago ma zan siya nayiwa kaina hakikar suna,Dariya sukayi Amana ta musu Sallama tare da shiga jirgi sai lagos, ta koma gida lafiya

,Alim sai murna da nishadi yakeyi,yana shigowa ya dagata sama yana juyata tare da mata sannu da zuwa,
Lokacin ba wata wata suka fara cin Amarcinsu sosai.
Bayan sun nutsu suna hira tare da sakarwa juna kalaman so‹Alim yana wasa da dukiyar fulaninta masu gigitashi,
Yace yanzu Babyna wani gidan zan kara siya a kano kenan tunda naki kin bayar dashi idan munje bamu da masauki.

Amana tace sosai ma kasan wannan nawa ne sabo da ganganci ya zanyi na kashewa mijina zuciya ya dinga sauka a a gidana,mijin Hajiya ai kawai ka tsaya da kafafunka kaima ka siyi naka,dan bazai yarda zuciyarka ta mutu ba gida ma ace na matarka ne nan zamu sauka abun ba tsari,kuji Amana kamar ita ta siyawa kanta.

Dariya Alim yayi yace ba sai kin fada ba ai already na siya ma.
Volume din kida me dadin gaske ya karo musu a speakers dake katon palon nasu,Suna ji suna romancing juna.

Amana wasa wasa har ta kwashe 1year tana zuwa schl,ta gama level 1 tana level 2 yanzu second semester, tana kokari sosai,
Zama suke lafiya tare da tsantsan soyayya,

Su Nura sai rokon Abba sukeyi kullum yayi hakuri ya dawo da Mum amma yaki,sai da suka je har kano suka sanarwa yan uwansa suka sa baki tukun sannan yace zai dawo da ita nan gaba,
Abban Huzaifa da kansa ya dawo da Mum gidan Abban su Alim,

Mum da Abba sai kallon kallo,domin tsoronsa takeyi,haka takeyin duk abinda Zai faranta masa rai,yanzu kowa so take nuna masa,ba wulakanci,mutunta kowa takeyi,
Sai da Abba ya tabbatar ta shiryu sosai sannan ya fara Kula ta kadan kadan har suka koma suka cure gam gam.

Zo kuga biyayya wajen Mum,ga shiga dangin miji da son talaka,
Taja mutuncinta ta rike surukanta,
Tuni ta daina harkar kawaye masu mugun Hali,

Amana ta gaji da jiran samun ciki har ta hakura ko baza ta kara haihuwa ba ma,
Alim kuwa kwana 2 yaga Amana ta daina dauko pt ta auna fitsari,dauko mata yayi tana Palo tana rubutu yace Baby zo ki tsula mu auna Amana tayi muryar tausayi tace ai ni kuma na Zama sorry kishiya farilla gareni,tawa ta kare mutuwata tazo kuma domin rashin haihuwa nasan aure zaka kara ni kuma nasan mutuwa zanyi ko na fada daji,bazan iya hada wata da kai ba,gashi cikin ma babu,yanzu idan ka auro wata ta haihu ni bani da ko daya juya min baya zakayi,wata ce zata haifi Aabid sai ta fara kuka sosai.

Alim shi dariya ma ta bashi harda Kuka kuma dear,har kin karaya?har shekara nawa da aure?biyu da rabi kacal,
Kuma kin taba samun cikin nan bare ace ke juya ce,ki daina damun kanki in ma kishiyace ko kin haihu zan karata Alim ya furta da nufin tsokanar Amana,ai kuwa Bai shirya ba yaji Amana ta rufeshi da duka tana kuka wlh sai an saketa baza ta zauna ba,gaba daya ta haukace tana ta faman huci,
Alim riketa yayi yana dariya kasa kasa,mene haka kinga dole kishiya ta kwace miki miji kina wannan zuciyar taki,
Amana ta kara karfin kukanta har masu gadi da securities suna ji,sun dauka wani babban abune ya faru suka taho da gudu taimakon gaggawa suna ta danna door bell,Alim ne yace su koma ba komai madam ce rigimarta ta motsa,

Rike Amana yayi kam da siririyar muryarta tana kuka kamar ana yankata sai tirje tirje takeyi duk ta kwaye cinyoyinta a waje gashin kanta yayi buzu buzu,Alim yace kiyi shuru pls Amana tace wlh bazanyi ba sai ka sakeni ko kace ka fasa kishiya,ta kara tsagewa da kuka
Tana wayyo za aljanuna sun tashi,tayi muryar Aljanu,akan anga bama haihuwa,kace ni juyace bana haihuwa,Alim ne ya dan bige bakinta kadan ta masa shuru amma taki sai ihu da ta kara saki tace zai kashemu akan yana neman aure,yana ta marina akan Amarya zata haihu, murmushi Alim yayi yace Ashe da gaske Aljanune suka tashi? Amana tace baza mu saketa ba sai ka fasa kishiya,Alim yace to kuwa saina kara aure baku isa ba,Amana ta canja kalar kukan yara yan jirirai to shike nan zamu haukata maka mata,baza ka samu me maka girki ba,ba kwanciya tare,
Tun dare Bai maka ba kace baza ka taba yi mata kishiya ba har abada.ta kara shure shure tana fyar fyadiya kamar gaske,Dariya Alim yakeyi

yace ke uwar sharri,wasa nake miki fa,Amana tace wlh bazan yarda ba sai ka rantse ta ci gaba da kukanta,saida Alim yace wlh da gaske nake wasa nake miki ke baki San tsokana ba,me zanyi da matan ina da kamarki,

Goge hawaye Amana tayi tare da cewa ko kaifa dama nasan yaushe ma zaka mun haka ai kai dan Aljanna ne,Alim murmushi ya kara yi tare da cewa to ki kara rikeni da Amana sosai idan ba haka ba ta biyu tazo, Amana tace an gama ogana ranka ya Dade me martaba,
Takawarka lafiya zakin Amana daga ni ba Kari,little Aabid kuwa ko a buhun barkono sai na haifoshi, Dariya Alim ya fashe da ita tare da daukan Amana cak ya goyata a bayansa kana yace muje mu tafi garin barkonon ma gaba daya ki bani yaji me ginger da curry,Amana ta rada masa me maggi zaka ce,

Suna saman Bed Alim yana murza dukiyar fulaninta Amana ta lumshe ido,ido rufe taja yaji tare da cewa ko 'ya'ya Hudu ne ya dace a haifesu 1time saboda yanda ake Jin dadin nan,suna ta murzar juna Amana ta kara cewa yan uku ne ya kamata ko yan Hudu yanda kullum kake dura abu a ciki,
Allah sa dai receptors su ja su kaiwa egg din nan,na saka kwai nayi kwai har sun gaji,

Alim najin Amana sama sama tana ta surutanta wanda ba a hayyacinta take ba,
Yayi adduar Saduwa kenan Amana ma tayi tata,da kyar Jin yana yi,yana shigarta ta tace bismill...ah.....yan Hudu kuje Ku boye cikin mahaifa ni kuwa na santaloku,Alim ya rufe mata baki da nasa yana kissing,da karfi ta fisge bakin ta a slow kamar yar maye tace Abeg ka kyale min bakina nayi abinda naga dama kai hanaka ihunka nakeyi? To nima yau sai nayi abinda naga dama,
Alim yasan yanda Amana take burburwa a bed din,iya shegenta takeyi son ranta,kuma karawa Alim kaimi takeyi,kasa hakura yakeyi,domin suna hutawa su kara cin abubuwa sannan ya tafi wani round din haka yakeyi,yana so kuma ya dan dinga daga mata kafa,amma Amana sai ta jawo yayi ta karawa yanda zata dinga masa sexy abu,domin kalar ihun da take masa ma kansa na daban ne kara susucewa yakeyi,ko an gama sai ta kirkiro salon da dakansa zai kara manne mata.danma yayi sa'a she is so active a komai ba sanya,kuma zata dage iya yinta ta bashi abinda yake so,ta masa abinda yake so a lokacin da yake bukatar hakan,gata ta gama karantarsa,ta gama gane kan abinta,tasan duk abinda yafi so ta fannin komai na kwanciyar aure da sauran na zaman takewa,

Kamar wacce ta karanci fannin xxx yanda take bada style iri iri,tasan me zata masa,tasan kuma yanda zasu hadu su saita Kansu su dinga kawowa kusan lokaci daya.Alim kam gwarzon Oga ne,komai ya gama kwarewa shi yasa yake haukata Amanarsa da salonsa iri iri itama bata gajiya dashi,idan zai nemeta ko sau nawa ne saboda yanda yake jiyar da ita dadin duniya ba a magana karamar hauka takeyi.

Yau Saturday da yamma Alim yasa Amana ta shirya suka zaga gidan dangi da frnds dinsa masu aure,daga nan sukaje gaishe da Abba da Mum abin gwanin sha'awa.
A hanyar dawowarsu driver na jansu Alim ya kalli Amana dake kwance a kafadarsa yace mu

tsaya ayi take away? Yatsina fuska Amana tayi tace kullum sai ka shigo min da kayan kwadayi iri iri,komai kana siyowa kullum bafa ka shigowa ba tare da Leda a hannunka ba,a barshi duk ina da su sweet da komai,girki kawai na yi mana wani Abin marar nauyi,

Ko nama baza kici ba? Amana ta kada kai,beef meat? Kaza?dan shila? Kan rago? Cowtail? Fish? Icecream? Duk Amana ta kada kai bata so,

Ya kara rada mata a kunne sai me to ko cosmetics? Tace haba kaima kasan ba abinda babu,red eye liner fa?ko black? Dariya Amana tayi ta tuna sanda tacewa Alim ko jar jagira sai ya siya.

Yau suna dawowa gida Alim da kansa ya dafa musu indomie suka ci tayi dadi,sannan sukayi shirin bacci suka kwanta sai bacci,yau wacce rana ya bar Amana ta huta,

Can tsakar dare Amana ta farka da muguwar sha'awar Alim da ta rasa ta mene,Alim yana ta baccinsa hankalinsa kwance,Amana ta kare masa kallo harda kunna light,mikewa tayi ta shiga toilet, aka kara shiryawa tsab harda kara brush tare da watsa ruwa a jikinta,ta fito daure da towel,

Ta cire towel din ta jefar tare da fesa body spray,ta kara shafa wasu turaruka na musamman masu rikita me gida, haka ba komai a jikinta ta koma saman Bed,

Tare da shigewa blacket,Alim dan karamin boxers ne a jikinsa,Amana ta manne a jikin Alim tana ta faman juye juye,shidai Alim Bai San tanayi ba,tana so ta tasheshi sai tace kai karfa ya rainani,Can kuma tace to mene mijina ne,ni da dan kadan nake nemansa, shike nemana fa kullum Bai fi sau kadan na nemeshi ba,

Bari kawai wlh na tasheshi dole ya min nima tunda nayi duk yanda zanyi na masa wayo ya tashi yaki tashi ayi me gaba daya,

Nasan ma ina tashinsa zai kawo full light.

A hankali ta fara tashinsa ta hanyar sosa masa kunne da kyar ya bude Ido,bai jira komai ba ya jawo Amana gabansa ya kwantar da ita tare da kara kankameta yace sleep kinji yaci gaba da baccinsa,

Amana tace wlh sai ya tashi,kara mikewa tayi zaune,Alim ya kara damkota cikin bacci tare da rungumota ta baya,dukiyar fulaninta na cikin hannunsa,Amana kara rudewa tayi,ta fara tashinsa da baki, Baby...Dearna, ka tashi pls yunwa nakeji wai tayi masa wayo,da kyar ya kara bude idonsa ya daura idonsa akanta dama bata kashe light ba,

Kan Alim yayi wani Dum ya Mike zaune, kin fiye rigima Sha ruwa ki kwanta da safe sai kici,Amana komawa tayi jikinsa tare da kanannadeshi Alim baccinsa yaji ya gudu gaba daya kamar ya rungumi transformer haka yake Jin jikinsa dalilin abinda Amana ke masa a jikinsa,

A hankali tace I need u honey,Alim dama da kadan yake jira yace shine kika wani tsaya kina min nuku nuku.

Tuni Ya marzaye shima ya shiga toilet ya kara tsaftace ko ina,ya fito ya fesa Body spray, jawota jikinsa yayi yace yar Albarka yanzu zan miki service.

Shekarar su biyu da Aure cif,Badriyya ta haifi mace Sunanta little Amana ansha suna,watan

little Amana daya Sakeena ma ta santalo Namiji kato kyakyawa aka Sha suna tace a sa masa Alim ita kuma,

Hamza,Isa,kb,da Salma anyi bikinsu ansha shagali,inda aka kai Salma Adamawa gidan Deeni kwaro,
Ga Asiya ma da tsohon cikinta,Amana ta gama tabbatarwa maybe baza ta haihu ba ita, watanni biyu tsakani Amana tayi dan zazzabi kadan ta tashi, kullum sai cin Aya,ga yanda take sha'awar Alim,ta canja gaba daya,skin dinta kamar dafaffiyar kaza tsabar laushi,ta gaji ta daina pt test ta hakura,
Kullum sai kwadayi,Alim ma ya fuskanci wani abu da kyar ta yarda da Alim cewar ta kara test su gani,tana toilet tayi test aiko ta fito da gudun tsiya,tana oyoyo little Aabid,Aabid oyoyo,Alim ma murna kamar me,

Asibiti suka wuce aka kara test har ya kai wurin 4mths basu sani ba,nan aka gama musu komai daya dace suka dawo cike da murna,
Amana tace kar a fadawa kowa sai dai a ganta da katon cikinta, haka sukayi shuru ba wanda ya sani,ko kace kamar ciki ne dake Amana ko?, Amana baza tace eh ba,hmm kawai zata ce ko tace to wa ya sani abu a duhu ko shine ko ba shi bane.

Haka suka dinga rainon ciki har ya girma,kowa ya gani murna yakeyi musamman Mum da Abba,
Su Nura sai murna sukeyi ana tayasu murna,
Har cikin ya kai wata Tara,haihuwa ko yau ko gobe,da kyar take takawa,Alim ko fita baya yi yana manne da ita sai abinda takeso

Wata ranar talata Amana ta fara Jin ciwo kadan kadan ta fadawa Alim honey kamar fa nakuda nakeyifa wlh daurewa nakeyi kawai ciwon yayi yawa.

Da gudu Alim ya hada komai suka tafi asibiti,ya fadawa Mum tazo da Hajja me aikin Mum wata dattijuwa,
Amana ana dubata akace haihuwa ce,Abin mamaki tsabar juriyar Amana ko hawaye babu,yatsina fuska kawai takeyi idan ciwon ya motsa mata,
Alim ya kasa zaune ya kasa tsaye sai zirga zirga yakeyi baji ba gani.
Kamar shine me nakudar,
Amana kuwa daurewa kawai takeyi bata taba Jin ciwo irin wannan ba,amma bata ko ehem,ko Mum ta jinjina mata har dai yau bata haihu ba sai wahala da take Sha sosai ta fita a hayyacinta.

Alim ya rasa yanda zai saka kansa,Amanarsa kawai yake tunani da tausayi,gashi an hanashi shiga ciki.
Alim harda hawaye ganin doctor tace har yau bata haihu ba.

AsmaBaffa
✳CIRANIN AMANA✳

205-210

Official

By
AsmaBaffa

FINAL

Amana ta dan Dade kadan sannan Allah ya taimaketa ta santalo danta Namiji katon gaske,kyakyawa fari kwal kamar bature,readers yaron dake jikin poster din Ciranin Amana ba Aabid din farko bane wanda ya rasu,Aabid din Amana ne da ta haifa yanzu.
Alim murna kamar ya Haukace ganin Amananansa lafiya lau da ita,
Mum cewa tayi gidanta zasu koma da Amana baza ta koma gidan Alim ba sai tayi arba'in, Alim baiyi musu ba amma yace dashi za a koma gaba daya ai nan ma gidane ba matsala tunda gyara masa headquarter za ayi b a damuwa.

Dungumawa sukayi gaba daya gidan Mum, Alim yaki tafiya wai shine zai mata wankan,Mum ta koreshi,sai dare ya dawo tare da haurawa saman Bed yace honey ina ma yan uku kika haifo min,Amana ta Galla masa harara,tace dayan ma na gode akace uku zan haifo ai na shiga uku,ashe dana ke neman yan uku ganganci nakeyi wai wannan wahala haka,na zata mutuwa ce.murmushi Alim yayi yace na matsu kiyi arba'in na koma Ango,murmushi tayi tace me za a fasa mutuwa ko hisabi,ai Harka zamu koma sabuwa dal,

Tafa mata Alim yayi yace sai Amanata tawan ba sanya, juriyar nan taki tana birgeni,da watace gudun mijinta zata fara yi akan wuyar da ta Sha,ko kar ta samu ciki da wuri,sai kiga haihuwa daya ana fada tsakaninsu,

Fari Amana tayi da Ido tare da cewa ni da muka Dade bamu haihu ba,yaci ace kana da yara Uku yanzu kaga dole na bude mahaifa nayi ta haifowa idan nayi Uku sai na huta ko?
Alim yace good haka kuwa,Mum ce ta shigo tace tashi ka tafi dakinka Malam,

Haba Mum Alim ya fara shagwaba,Mum tace anan zan kwana,Alim ya bude baki kai Mum dan Allah ki tafi dakinki Abba yana gari fa,

Kunnensa Mum ta murde Amana tana dariya tace Mum kyaleshi dan Allah kin San halinsa da kafiya wlh idan ba haka ba aure zai fara nemowa kyaleshi ya kwanta,Alim yace gwara da kika samawa kanki lafiya dama wata ta manne min sai na nemota,Amana kamar zatayi kuka tace Mum kinji ko kyaleshi kawai,

Mum tace kinji kunya wlh kina tsoron kishiya ki zauna ya rainaki yana miki barazana da kishiya,

Sosa kai Amana tayi Mum baifa ce zaiyi ba nice dai nake tsoro kuma wlh idan yace zaiyi Allah saina ballata harda shi ma, murmushi Mum tayi tace ai nasan zaki iya aike kishiya ta shiga uku a hannunki,gwara karma mutum yayi domin korarta zakiyi da muguntarki kala kala,

Shagwaba Amana ta fara haba Mum ni Allah,Mum tace sai dai ki gayawa wani amma nice sheda,ni indai ina raye bazan bari ma ya miki kishiya ba,nasan ma bazai miki ba yanda yake Sonki,

Dadi Amana taji tace na gode Mum,koreshi ya tafi dakinsa,bige bakinta Alim yayi kadan ta kwalla kara,

Mum tace kwaji dashi can kunfi kusa,sai da safenku tare da kallon Alim tace ka kiyaye kaji na fada ma,ina ganin ba dai dai ba sai ka bar gidan nan ka koma gidanka,

Wannan yaro yana Shan kulawa wajen Amana,kullum yana hannunta ta hana kowa,da an karba zata dinga mika wuya tana lekensa,

Idan yarane ba manya ba Baza ta basu danta ba kar su jefar dashi ya fadi kasa wai,daga yayi uhum Amana dama kadan take jira zatace mikoshi na bashi ya sha ta karbe abinta,

Ko Alim masifa take masa wai yana shilla mata yaro zaiyi zazzabi,

Asiya dasu Badriyya kuwa da suka zo suna dauka kadan zata dan jira mintina kadan tace bani dana,har tsiya ake mata Amma Amana ko a jikinta,

Har ranar suna tayi dangi da abokan arziki ansha suna,yaro yaci sunan Aabid,Aabid ake ce masa,

An gama komai kowa ya koma gidansa,Mum kuwa da sauran dangi suna ta faman gyara Amana kamar sabuwar Amarya,

Alim dan albarka yayi dauriya da hakuri bai takurawa Amana ba sam,

Amma da kyar yake daurewa har sai da ya daina kwana gidan Mum saboda tashin hankali yake shiga yanda Yake kallon Amana tana kashe kala,gashi sai kara kyau da girma takeyi har akayi arba'in Aabid yayi wayo sosai gwanin sha'awa

Ranar kuwa da ta cika arba'in ranar Alim zuwansa gidan Mum yafi Goma yana jira yaga Amana ta Zama ready su tafi gida,Amma sai yaji Mum tace kano zasu tafi tare da Amana su zaga dangi,

Da bacin rai ya koma gida,Saida Amana suka gama zaga dangin lagos sannan suka wuce kano kwanansu 4 suka dawo lagos,washe gari Mum tace shirya maza na kaiki gidanki,wannan mijin naki kamar zai dakemu kina gani da kyar ya gaishe ni.

Amana ma tayi missing mijinta,har gida Mum ta kaita da yamma misalin 5pm,
Nan Alim ya fara fushi yana shagwaba,da kyar Amana ta lallashi abinta, yana dawowa daga Sallar magrib,yasa Amana ta kara bawa Aabid Nono ya koshi ya tattarashi ya kaishi wajen hajja,

Amana tace idan yayi kuka fa?,Alim ya ce can da matsalarsa yazo ya kankane komai ya barni cikin wahala,
Ranar Amana taga ta kanta a hannun Alim,ya gurjeta son ransa,

Sunji dadinsu sosai,Alim kara nutsewa yayi akan so da kaunar Amanarsa,
Kullum yana manne da ita ba sauki ba daga kafa,itama Amana hakan take irinsu daya.
Saida Alim yayi Hutu na 2wks sannan ya koma aiki,

Wata yarinya ce wacce sukayi university da Alim a london Teema take matukar son Alim,kullum sai tazo office dinsa kan ita sai ya aureta,Alim Amanarsa ta isheshi,bazai iya mata kishiya ba Sam,
Yanda yake mutuwar son matarsa me zai ci da wata,yayiwa Teema bayani amma taki yarda,shi kuma Bai son wulakanta dan Adam musamman yanda sukayi schl daya,yana ganin mutuncinta.

Yauma kamar kullum tana office dinsa,dabara ce ta fado masa yace Baza ki iya kishi da matata ba,Teema tace haba dai ai ni nafi karfin ko wacce kucaka, ka kirata mu hadu kaga yanda za ayi sai abinda nace dole ma ta hakura,
Murmushi Alim yayi,Teema da kuri tace kirata mana tazo na fada mata amma da sharadi idan ta yarda dole ka aureni,Alim yace kwarai kuwa.

Amana ya kira a waya tana jikin mirror tana sheka kwalliya ta daga,Alim yace kizo Office yanzu wata tana son ganinki wai zata aureni zata iya kishi dake shine nace kinfi karfinta ni mijin tace ne amma taki ji,wai sai ta ganki.

Kamar an watsa mata ruwan Zafi haka Amana ta mike, gyale ta figa a hannunta ko yafawa bata yi ba,Aabid dama yana wajen Hajja,motar da tafi ko wacce tsada da kyau a gidan ta shige tare da fisgarta sai office din Alim,Teema kuwa harda fitowa waje tana jiran Amana,
Alim sai dariyar mugunta yakeyi yasan yau Teema ko mari daya ne sai tasha a hannun Amana,

Motar Amana ce ta Parker tun daga parking kasan ba lafiya,tana fitowa Teema ta sume a tsaye ganin Amana,tunaninta Amana ba wata me kyau ko hadaddiya bace tunda tasan Mum kewa Alim aure,

Tun kafin Amana ta karaso daga yanda Amana take tafiyar gadara da takama gashi kana ganin idanunta kasan a bushe suke sun goge da duniya,
Duk wajen ya dauki kamshin Amana,shigarta kanta abin kallo ne wajen tsada da haduwa,
Alim ya fito waje yana ta faman murmushi da Ido ya nunawa Amana Teemace me son zama kishiyarta,Teema kuwa ta maza tayi,tare da hade rai wai itama shegiya ce,wajen Alim ta matsa tana masa wani kallo,
Hannu ta daga wai zata rike hannun Alim,dan Amana ta gani tasan suna soyayya.

Kafin ta ruko hannun Alim,Alim yayiwa Amana magana da Ido wai kullum haka take takura masa a Office,shi wlh ya gaji zai aureta,Amana da hannu ta yanka wuyanta wai sai ta yankashi,murmushi yayi,Teema kuwa taje tana hada hanunta dana Alim wai zata rike, Amana ta fincikota baya tare da kifa mata maruka har uku,
Tare da shake Teema ke karamar yar Iska kin sanni kuwa,Teema Ido ya firfito sai hawaye,sakinta Amana tayi tare da ja baya tana, bana Cece kuce da mutum na wuce nan,Dalla ja rubabben bakinki dake yar kauye zaki taba mijina da kazamin Hanunki kwartuwa ana zubar da aji ana bin maza,nafi karfin kishi dake,
Warning na miki kika kara zuwa Office din mijina sai nayi daga daga dake, Alim munafuki harda cewa sorry Teema kinga abinda nake fada miki gashi fuskarki ta kumbura kika ki yarda,ba laifina bane,

Teema share kwalla tayi tace amma Alim kayi asarar halinka wlh,sam bansan haka ka Zama lusari  sakarai ba,kai da kake dodon mata amma mace yarinya karama jibi yanda ta ke Baka Umarni,Alim yace uhm wlh kuwa ganemin hanya Teema aini a kanta na gama lalacewa,ta shanyeni na shanyeta idan ba ita rayuwata Baza ta yuwu ba,kinganta to bana jin yaren kowa sai na Honey ta,

Teema fuska kumbure tace Allah yaji kanka Alim,wlh ka haukace aikin banza kayi asara dai,kuma marin da tamin  Allah ya Isa wlh Bazan yafe ba,
Alim yace  taba mata miji da kikayi bata ce miki Allah ya Isa ba sai ke dan ta dan mareki,hukunci ta miki a duniya kafin Allah ya miki nasa,karki sake ki zagi mata ta wlh a nan zansa a tara miki gajiya uban waye ya kawoki Office din mijinta,
Amana tace a bar mana Office yanzu ehe, Baby muje gida an tashi a Office yau Baza ka zauna ba sai gobe kuma,
Alim yace an gama ranki ya dade,ya kwaso wayoyinsa ya rufe Office yabi Amana,yace Securities su kai motocinsa gida Madam tace a tashi a Office haka,
Amana harda jin dadi Alim yabi maganarta,abinda idan yaga dama idan ta yi ba dai dai ba sai ta gane kurenta ba wani mijin tace.

Teema kuwa motarta ta shiga tace Amma na maru wlh,wannan jarabace da ace na kulata Dukan tsiya zata min,ga shegen iya mari,hannunta laushin tsiya Amma idan ta dakeka sai kaji ajikinka,
Kamar namijine ya mareni,yaje ya zauna da jarabar matarsa,mijin tace shege,dan iska,tsinanne ta dakeni Amma ko a jikinsa koma ya mata fada.wannan Alim ai shine dan iskan

marar mutunci suje can su karaci jarabarsu ko kallonsa wlh Bazan kara ba tunda bashi da mutunci haka Teema ta dinga zage zage har ta koma gida.
A ranar ta nemo tsohon saurayinta me sonta da take masa wulakanci suka shirya zai turo ya kwashi tsohuwa Teema..domin Teema Sa'ar Aleem ce 33years itama.

Amana a mota sai faman dariya sukeyi da Alim yanda Teema tayi,Amana tace sai ni wlh har aja Dani ko wacce shegiya ce, tana driving Alim ya mika mata hannu ta rike tare da hadewa da sitiyari tana tukinta,

Tana Driving Alim na tabe tabensa a jikinta,yana dora hannunsa a kirjinta Amana tayi slow da mota ta kara fincikar motar,yana kara tabawa Amana ta gangare kasa tace zo ka karbi driving bazan iya ba ai sai kasa muyi hatsari ai,
Dariya Alim yayi tare da cewa na gaji ban iyawa,na daaina tabaki muje pls,
Driving taci gaba har gida,

Wannan shekarar Amana da Alim sukaje aikin Hajji again suka koma umrah tare da Aabid dinsu,Amana na zuwa schl tana karatunta sosai yanzu tana final year,

Salma ta gidan Deeni kwaro tana dauke da ciki haka matan su Hamza ma,
Shekarar Aabid biyu a duniya Amana ta samu ciki za ayiwa Aabid kani ko kanwa,
Murna sukeyi sosai,tana gama degree dinta da wata biyu ta santalo Danta Namiji shima,
Ranar suna aka sa masa sunan Baban  Amana Sulaiman suna ce masa Irfan,

Aabid an girma an zama dan saurayi,
Amana tana jin dadinta suna zamansu lafiya ita da Alim da yaranta,
Sai abinda sukeso, har ansa Aabid a schl, Amana ba abinda bata Yiwa Alim don ta faranta masa,sai abinda yakeso,kullum Amana cikin gyaran jiki da kwalliya a haka take kara susuta Alim,ya gama matowa a kanta,akan Amana sai dai a mutu,

Ga tsananin biyayyar da Amana ke masa,uwa uba ga iya kwanciyar aure,ta gama da Alim gaba daya, baya ganin kowa a gabansa sai Amana.
Kullum cikin soyewa suke basa iya zama ba tare da juna ba,
Bayan bikin Ameer dan Autan Mum da Amaryarsa Minat.
Alim yace Amana taje tayi masters,haka ya kara biya mata private schl ta fara masters,
Tana gama masters ta kara samun cikin na Uku,
Wata tara ta haifo yarta mace zukekiyar gaske me kama da Alim,Daga nan Alim yace ta huta haka da haihuwa sai nan gaba an dan dade.

Yaran su dagwas dagwas dasu gwanin sha'awa su uku, Aabid kullum baya fara'a cikin muzurai yake da kaninsa Irfan ya masa Abu ko Mufeeda kanwarsa zai samu ya zanesu,baya daukan raini kamar Babban mutum haka yake,
Yanzu ya daki mutum ba ruwansa,mugune Aabid na karshe,baya wasa da Yara,ko cikin Yara ya shiga yan uwansa sai dai kaji Kukan Yara ya bubbugesu ba ruwansa,kannensa ma tsoronsa

sukeyi,
Mugun tsoron Amana sukeyi yaran nata don sun San idan sukayi laifi ba ruwanta zata hukuntasu,shi yasa suka taso masu hankali nutsatsu ko ina suka je zaka gansu cif a nutse,kallo Idan Amana ta musu sun San me take nufin.
Alim ne ke shagwaba su ma baya son ana taba su.

Alim ne kwance a bedroom dinsa Amana na gefensa,Mufeeda ta kwankwasa kofa Dad...Dad....ta kwalawa Alim kira, Alim ya mike tare da bude kofa,Ify Mufeeda? Ni a wajenka zan kwana Ya Aabid dukana yakeyi,wai muyi bacci,
Amana ce tazo wajensu tace Baza ki kwana ba Mufee ki koma Bed dinki,me ya kaiki wajensu ke dana ce ki je dakin Hajja ki kwana,

Kuka Mufeeda ta fara ni...ni bana son wajen Ajja.
Alim ya kalli Amana tare da yin magana kasa kasa yace yarinyar zata hanani sakewa yau,kin kuma san Bazan iya jure rashinki ba,
Amanace ta riko Mufee tana lallashinta ta maidata dakin Su Irfan ta dorata a Bed dinta,Aabid sai fushi yakeyi su baza su kwana da mace daki daya ba,
Momy pls mu baza ta kwana a room dinmu ba.
Amana tace zan taka wuyanka Aabid ka rufe min baki,kunyi karatu kuwa yau kaida Irfan?yes Momy cewar Irfan,gobe zan duba na gani ai Amana ta furta.

Shuru Aabid yayi Irfan yace sorry Mum zan kula da ita,
Hararar Aabid Amana tayi tare da cewa idan naji kukan yarinyar nan Aabid saina karyaka.
Shuru sukayi Amana ta dinka masifa ta kashe musu light tare da rufawa kowa blanket ta rufe musu kofar ta koma wajen mijinta, suka fara baje Harkar da suka saba ta sunna..wajen Sunna basa sanya.

ALHAMDULILLAH

Ina matukar farin ciki da godiya ga Allah daya bani ikon kammala wannan littafin CIRANIN AMANA.
Godiya da jinjina gareku readers,masu sharhi,godiya etc,masu yin Document,masu kirana a waya

Bazan manta daku ba mutanena na:
AsmaBaffa fans club

taskar fiddausi so dangi

Hause of Hausa Novel

Zauren Queen mermu

Samarin Bana fans

Maraicin so fans

Da sauran groups da wanda nake ciki da wanda bana ciki na gode sosai Allah ya bar kauna.

Next coming novel dina nan gaba Insha'allah

DUK INDA TA FADI.

Poster din novel din zaku ga guy din frnd dina ne sosai da sosai,yanda muke dashi yasa na sashi a poster University daya mukayi class dinmu daya.labarin ba nasa bane kar readers kuce labarin sane😂 sai na huta sosai zan fara New novel.

Ku karba readers👊👊👊👊👊👊 1 blow irin na Amana nayi wa ko wacce.😂😂😍😍😍😍 Am gonna miss u all 😭😭😭😭 Bye.

👍👍👍👍👍👍

AsmaBaffa